(MUR YAR SHAHIDAI)

# Zukata MASU KUNA

Mata Takwas
Na
Majamiar Karkashin Kasa
Da
Labarunsu Na Bangaskiya
Mai Tsada
A Cikin Tsanani

Hausa
460-0335
Rcvd 3-15-11
HOF

**(MURYAR SHAHIDAI)**

*Zukata Masu Kuna*

# Hearts of Fire

## Hausa Edition

Copyright 2015 Voice Media

info@VM1.global
Web home: www.VM1.global

All rights reserved. No part of the publication may be reproduced, distributed or transmitted in any form or by any means, including photocopying, recording, or other electronic, or mechanical methods, without the prior written permission of the publisher, except in the case of brief quotations embodied in critical reviews and certain other noncommercial uses permitted by copyright law. For permission requests, email the publisher, addressed “Attention: Permission Coordinator,” at the address above.

This publication **may not be sold, and is for free distribution** only.

Gabatarwa Daga Gracia Burnham v

Godiya vii

Gabatarwa: Zukata masu kuna cike da karfinhali da ba da kai 1

Adel: Har a tsakiyar Tsoratarwa ma...Akwai sa rai 5

Purnima: Diya da aka sa a kaso, amma ruhunta yantacce ne 42

Aida: Murya domin marasa iya fada aji 71

Sabina: Shaida ce ta kaunar Kristi 103

Tara: Rayuwa a cikin gudun hijira 151

Ling: A cikin makarantar azabtuwa 181

Gladys: Hanyar rayuwa ta gafartawa 220

Mai: Dawowa cikin kasar Vietnam... domin yin wa'azin Bishara 246

Takaitattun bayanai. 281

*An sadaukar da Wannan Littafi*

*Ga*

**Sabina Wurmbrand**

*Wata Murya Domin Shahidai.*

## *Gabatarwa*

An Karrama ni ainun da aka ce ni na gabatar da Littafi irin wannan. Bazanyi kuskuren fara yin tunanin gama kaina da irin wadannan tsayayyu kuma fitattun mata na bangaskiya ba.

A yayin da nake karanta labarin su na ban mamaki da karfin hali wanda duk mai karatu zai san daga Allah yake. Na kan shiga matsayinsu a zuciyata a yayin da nake karatun domin na fahimci irin abinda suka ji.

A shekarar 2001 a watan Mayu zuwa watan Yuni na 2002 a lokacin da mijina Martin dani kuma muka yi zaman kamammu ana garkuwa damu a karkashin yan ta'adda ta kungiyar Abu Sayyaf a dajin kasar Philippines. Ni kaina na zama wadda ta fitar da rai, na gwammaci mutuwa. Nazama mara mahalli ga kuma yinwa kamar zata kasheni….. amma nawa kam, ina sane da cewar da zarar lokacin saki na ya zo, zan farfado zuwa ga rayuwa ta da na saba na yanayi mai yanci. Yanzu gani a zaune a Amirka a cikin gida maikyau ga abinci a yalwace ga kuma kungiyoyin ba da taimako a yayin da wadannan mata sukecin gaba da jimre wahala a zaman jarumawan sojoji na Yesu.

Saboda haka a yayin da nake wanka da ruwa mai dumi, na kan yi addu'a. A lokancinda nake yin ado na shirin fita zuwa yin jawabi, na kanyi addu'a. a lokancin da nake kaiwa ina kawowa wajen sayayya domin yara na, na kan yi addu'a. A lokancin da nake tuki, idan na wuce kofofin majami'u a cikin gari da lamba mai rubutu a kofa, na kanyi addu'a. Na kanyi addu'a domin dukan wadanda basu mallaki irin abin da nake da shi ba. Ga wadanda suke cikin shan wahala domin ban gaskiyar su ga Yesu. Ga su wadanda suke jin ba su da amince wa da gaskiya, ina addu'a domin su, haka kuma nake

kowa, amma duk da haka sun dage sun kuma cigaba da addu'a domin kaina a cikin jeji. "Ubangiji ka barsu su iya jin Kusancinka. Ka taimakesu, suci gaba da zama kafąffu a cikin bangaskiyar ka da
Yake al'amarin sai kara tsanantawa yakeyi. Ka basu damar tsinkayar alheranka domin susani cewa su ba kadai suke ba. Kuma a karshe na sani zaka kasance."

Babbar fata ita ce, kowane dayanmu da ya karanta wannan littafi zamu yi shirin sabunta ba da kanmu wajen bada dama Allah yayi anfani damu a yadda yaga tafi dacewa idan ma har yana nufin zuwa inda zamu iya shan duka, ko ma kisa domin kawai zama mabiyin Kristi, Bari mu sami karfafawa daga wadannan mata talikai.

Allah baya bamu jarrabawa da tafi karfin mu. Da wannan jarrabawa zai bude mana hanyar tserewa (Zai ba da kome da muke so) ta haka kuwa zamu iya mu jure, ina bada gaskiya cewa Allah ya na yin dukan abu daidai. Amma mutum baya yi. Mutum ya gurbata wannan kyakkyawar duniya. Idan har akwai wani abu kyakkyawa a wannan rayuwa, daga Allah yake. Yana da shiri kuma shi Makadaicine Mai Iko duka. Muna jira cikin hakuri domin nasa lokaci a yayinda zai maida komai ya zama sabo.

Bari Allah, ya bamu alherinsa domin muyi rayuwa domin sa har zuwa wannan lokaci, kamar yadda wadannan mata suka yi. Shi mai daraja ne.

-Gracia Burnham
-Kungiyar-Mishan ta Sababbin Kabilu.
-Marubuciyar Littafin: A Gaban Makiyana.

# Godiya

A lokacin da muka fara zartadda wannan aiki a madadin Kungiyar Muryar Shahidai mun sani cewa aikin zai bukaci mahimmata da dan dama. Na farko muna da bukatar samun matan Krista wadannda zasu yarda muyi amfani da shaidarsu. Idan ko babu labaru daga garesu to kuwa babu Littafi kenan, a garesu kuwa muke mika matukar godiyar mu.

Kowane babi na wannan Littafi (banda na Sabina Wurmbarand suna da bukatar mafassara. A cikin fiye da rabin wadannan labaru, sai da aka shirya wurare na musamman a boye kuma aka dauki tsaurar ran matakai, da ba domin taimako da goyon baya daga ma'aikatan Muryar Shahidai (VOM) ba da wannan aiki bai yi nasara ba. Sabili da batun kasada a yanzu haka ba zamu iya ambatar sunayen wadannan ma'aikata ba. Amma muna mika godiyar mu ga dukan wadanda suka ba da taimako a cikin dukan kasashen da muka yi tafiye tafiye. Muna kuma mika godiyarmu ta musamman zuwa ga director na VOM.

TOM White wanda ya shugabanci yin azancin sarrafawa kuma yana daya daga cikin wadanda suka sa hannu wajen tattara labarun Aida da Mai. Shugabancin Tom da irin hangen sa na zama murya ga Maja mi'u masu shan tsanani a yau yana cingaba da taimako mara misaltuwa ta wurin kawo dabaru masu kan gado. Todd Nettleton shi ya taimaka da rubuce rubuce da shirya littafin (Kuma yana tare da ma'aikatan Muryar hahidai (VOM) tare da Sue Ann Jones. Dukanku kun ba da gagarumin taimako. Mun Gode.

Yawancin lokaci ba abu ne mai sauki ba a ga bayan irin wannan aiki da ya shafi tsanantawa da kuma wadansu

mawuyatan al'amura game da bangaskiyar mu. Amma Greg Daniel da abokan aiki a (W. Publishing Group) sun sake tabbatar da ba da kansu ga kawo wadannan labaru na tsayayyu kuma masu karfin zuciya gaba gaba. Godiya muke domin kokarinku na kawo wannan Littafi mai suna "ZUKATA MASU KUNA" ga tabbata.

Kuma godiya ta musamman zuwa ga yayan mu, Jordan da Elena, wadanda cikin da'a suka hakura da ganin ya da Baba na tsawon lokaci da muke fama da tafiye tafiye zuwa kasashen waje. Muna addu'a wadannan labaru zasu zama wani bangare na tushen bangaskiyar ka.

-Steve Da Ginny Cleary

# Zukata Masu Kuna Cike Da Karfin Hali Da Ba Da Kai

An sace, an daka, an daure a kurkuku. A kasashen duniya da yawa a yau wadannan kalmomi sun zama kamar ma sun hada dangantaka da zama Krista. Kuma ga Kristoci mata a wadannan yankuna, akwai kalubale: Akwai Kyama a cikin zamantakewa na mutane ta duban wasu da halin wariya a dalilin cewa su ba su isa a basu shugabanci ba su dai kawai abin a mulka ne talikai sai dai maza su shugabancesu.

Zukata Masu Kuna, Littafi ne na labarin wasu mata guda takwas wadanda, baicin dukan alamura, sun nuna karfin zuciya na fiye da misali, ga kuma ba da kai ga kaunar Yesu Kristi da majami'ar sa. A cikin matsi mafi tsanani, suka zama shugabannni wadanda suka nuna karfin zuciya da tsayayya wajen kin janye wa daga bukatu da dama da ke kalubalantarsu. Akasi ma dai sai ta wurin shan wahala suka sami 'yancin su na zama daidai da ta maza a wannan matsayin, a wasu wurare ma wahalar da suka sha tafi muni.

A lokacin da muka fara yin shawarar fito da littafi ta shaidu game da matan Krista da suka sha tsanani a dalilin ban gaskiyar su, mun fuskanci kalubale da dama.

Na farkon farko, mun so shaidar su ta zama na tsarar zamanin yau. Wannan yana bukatar muyi tafiya zuwa kasashen da matan suke da zama kuma a yawancin lokaci na fuskantar tsanani harwa zuwa yanzu.

Kuma munso mu nuna misali na mata wadanda ba wai sun fuskanci wahala kadai ba, amma wadanda suka nuna suna da kwazo na shugabanci. A karshe, gaba da labaran ciwo da azaba, muna so mu nuna misalan abubuwan koyi game da tsayayyar bege da yadda wadannan mata, har ma cikin mawuyacin hali suka sami hanyar nuna kaunar Kristi ta haskaka.

Muhimmin abu ne a lura cewa matan da aka ambata a wannan Littafi kalilan ne daga cikin mata masu yawa kewaye da duniya wadanda suke fuskantar irin wadannan al'amura.

Mun zabi mata wadanda zasu iya wakiltar kasashe dabam dabam inda ake azabtadda Kristoci, kuma mun zabi wadanda zamu iya samun saduwa da su daya bayan daya. Wadanda muka sami yin hira dasu, yawancin su, sukan gaya mana cewa, a zatonsu akwai wadanda suka fisu, wadanda suke da labaru mafi tausayi fiye da nasu. Babu wacce take sha'awar nuna kanta a zaman wata jarumar Kristanci.

Labarun nan sun kunshi abubuwan ban mamaki dabam dabam a yayin da wasu matan sun yi fursuna a kurkuku na tsawon shekaru, wasu ba suyi kurkuku ba sam sam amma sun sha jimirin wahalu masu tsanani. Shekarunsu na haifuwa ya sha bam bam kwarai kuma sun fito daga al'adu dabam dabam da tarbiyyu dabam dabam, daga Kristoci zuwa Muslmi, Hindu ko Marasa yarda da Allah (atheism). Abu mafi ban mamaki ma shine anniya da ba da kai da yake iza kowace mace a cikin su fiye da yadda dan-adam ke zato da kuma gazawa da aka sani na dan-adam, duk niyyarsu da dagewar su yazo iri guda suna kamanta juna.

Addu'ar mu ita ce, ka sami karuwar zuzzurfan ba da kai da tsayayyar alkibla na iya sarrafa wahalun rayuwa. Idan dai mamaki kawai kayi na irin wadannan shaidu to ba muci nasara ba. Idan har ka sami daya daga cikin labarun nan ya kamanci wani bangare na irin rayuwarka, kuma idan ka sami karin karfafa wa daga wadannan misalai na karfin zuciya mara misaltuwa to munci nasara, haka kuma su wadannan matan da suka yarda suka shaida labarunsu gareka.

A farkon wannan shiri mun so mu dukufa ga ibada a karshen kowane babi. Amma bayan mun tattara labaran, sai muka lura bai zama lallaiba. Domin a shinfide a cikin shaidarsu akwaibangaskiya ta gaske. Mun gaskanta wadannan kyawawan labaru zasu kunna tartsatsi a cikin rayuwar ka, yayin da kake nazarin wannan Littafi "**ZUKATA MASU KUNA**"

**MURYAR SHAHIDAI**

# Adel: Har A Tsakiyar Tsoratarwa Akwai Sa Rai

Indonesia:

*5:00 na Yamma, Litinin 10 Ga watan Janairu 2000*

Akarkashin inuwar itatuwan kwakwa da iska ke motsasu daga ge te zuwa gefe, Adel ta tara yaran a guri guda adadinsu kusan hamsin. Tana daga murya a yayin da ta fara raira waka, Mu yan yakin Yesu ne." sau ta lura da tsoro da ke idanun yaran a yayin da suka shiga raira wakar tare da ita.

"Bana so na mutu!" daya daga cikin yaran ya fada. Bai cika shekaru goma da haifuwa ba.

"Ba mutuwa zamu yi ba. Taho ka tafa hannu tare damu." Adel ta jingina zuwa gefensa tayi masa magana a cikin kunnensa domin waka da ake yi bazai bari yaji sosai ba.

Tsorataccen yaron yadai shiga yin waka kamar dai baya so. Suka sake raira wata waka, suna tafi da hannayen su da ke rawar tsoro.

Adel tana kokarin kawar da yara daga kuka da ihu da akeyi a can gangare da ke da nisan mil daya daga inda suke tawurin sa su wakar da kuma tafawa.

Ta sani lalle ne ta hana yaran yin kuka. Musamman masu dan girman. Idan har daya cikin su ya barke da kuka za a sami damuwa.

Adel tayi sha'awar jarumtakarsu. Har wadansu iyaye wadanda ke tattare rukuni rukuni a kewaye da yaran suna nuna alamar karfafuwa domin ganin yaransu masu zuciya.

A yayin da suke cikin yin wakoki, Adel ta zuba ido akan taron yaran sai ta hango yayanta guda biyu. Christina wacce take da shekaru tara da haifuwa, da kuma Christiano mai shekaru bakwai. Adel mai karfin zuciya ce, sai kuma ta kara tabbatar wa kanta cewar zata iya zama mai karfin hali domin yayanta-da dukan yaran, amincin ta ya ta'allaka ne kacokan ga Kristi. Tana damuwa game da su, musamman Christiano don bashi da garin jiki kuma yayi ma shekarun sa kankanta. Shiru a tsanake Adel ta yi wa Allah addu'a domin samun kariya kuma tayi godiya domin ta sami damar daukar Littafin ta Mai Tsarki kafin su gudu subar gidajen su inda aka kai musu hari. Sai ta bude zuwa wani shafi da takan yi amfani da wata aya a ciki, sai ta karanta da murya, "Zan iya yin dukan kome ta wurin Krist wanda yake karfafa ni." Sa'annan sai Adel ta juya karshen Littafinta inda aka rubuta wasu wakoki, sai taci gaba da bi da yaran ga raira wata wakar.

Suna cikin waka kuma sai wasu yaran suka fara cewa suna jin yinwa da kishirwa,. Tun da tsakar rana suke kan wannan tudu kuma gashi yanzu alamun faduwar rana ta nuno kanta tangaran domin haskenta ya fara zama launin durwa  durwa can bisa gajimarai. Faduwar rana abin sha'awa ne kuma abin kallo, a wannan tsibiri mai suna Dodi ta kasar Indonesia. Amma asubacin yau tana nuna tabbatacciyar alama cewa bakinciki zai tasamma wannan kauye.

Jim kadan kuwa ihun da Methu ya yi tayi kara da yawa har tasha kan muryoyin yara masu waka. Ki gudu/Adel, ki gudal" Adel ta yi maza maza ta tafi gefen tudu tayi kokarin ta duba ko zata hangi wani abu a cikin ranar da ta rigaya ta kusan gama faduwa. Dakyar ta ke iya hangen masu hawowa kan tudun. Methu ya sake magana da karfi yace, Adel! Yi sauri! Lalle ne ku gudu zuwa cikin kurmin daji."

Maimakon yin haka sai Adel ta sandare don tsananin razana, domin karar harbe harben bindigogi da ake yi kuma suna ji a can kan tudu, ga kuma hayaki na tashi sama cikin gajimarai da ke shiga duhu dalilin faduwar rana. Sun cuna wa kauyen wuta. Kowane gida a kauyen zai kone, tana sane kuwa cewar har da nata gidan.

Ta shiga cikin tunani mai zurfi kuma mai tada hankali game da me zata zaba nayi. Zuwa zata yi ta taimaki Methu wajen

kokarin sa na haye wadannan tuddan duwatsu, ko kuwa garzayawa zatayi wajen ya'yan ta? Abubuwan na faruwa kamar da kyaftawar idanu. Haka ma tunanin rayuwar mutum yakan zo ya wuce a cikin dakiku kalilan, a cikin karamin lokaci fa Adel tayi tunanin rayuwarta da ya wuce da kuma rayuwarta nan gaba duka tunanin nan biyu suka yi kicibis a lamirin ta.

Yayana kaunatattu guda biyu... da mijin da nake kauna ainun.... ga shi rayuwar mu tare tayi kyau.

Sai ta juya wurin ya'yan, sai ta sake duban Methu, duba na karshe. Kuma nan take, sai ta tuna da wani dan shekaru goma sha bakwai wanda yake zaune akan karagar mahaifiyarta ba tare da an gayyace shi zuwa gidanmu ba gashi da taurin kai ga rashin tsoro.

## "A YANZU KAM ALLAH NE KADAI ZAI RABA KU"

Watan Yuli 1989:

"Iya, ya yi kama da biri!" Adel tayi tsaki, tana leke ta kofar dakin dafa abinci daura da falo inda matashin saurayi ke jira. Abin bai burge uwarta ba. Tana ganin cewa Adel ba ta kai shekarun yin aure ba, amma ya kamata ta nuna da'a tayi wadan saurayin godiya domin irin kokarinsa da dagewar sana sha'awar diyar ta da aure. Yakan ziyarci gidan kusan lokaci guda a kullum it kuwa ji take shin ana lallabata ne ko kuwa fusatata akullum. Methu yayi zamansa daram akan karagar ya sake bambayar sa da ya saba yi. Alhali kuwa Adel ta sha bashi amsa sau da yawa, amma bamu sani ba ko Methu yaki ya gamsu da amsarta ne ko kuwa yaki ya saurareta ne da gangan.

"Bana so nayi aure. Ni karama ce. Idan ma har naso yin aure, ba zan so na aure ka ba;" Adel ta nanata. Ita ma shekarunta goma sha bakwai ne, ga kuma kyaunta ya kawo kai. Amma bata da sha'awar kulla dangantaka ta saurayi da budurwa koda shike tana da zarafin yin haka.

Methu bai yi wata jayayya ba, kuma bai fusata da feleken ta ba. Shidai ya zauna da hakuri ya sake yiwa Adel bayani cewa ita zata zama matarsa. "Wannan ko shiri ne na Allah. Idan ma kina tunanin cewa nayi kama da biri."

Adel tayi dariya ba tare da buda baki ba a yayin da taga uwarta tana murmushi.

Ba tare da saurarawa ba Methu ya sake yin tambayar sa, "To, zaki aureni? "

A sani babu wata makama wajen ba da amsar wannan tambaya, sabo da haka sai Adel ta zauna kawai, tana tunanin yaushema zai tashi ya tafi ya basu wuri. A karshe Methu ya tube rigar da ke wuyansa, ya nade ta da kyau sai ya ajiye mata akan cinyarta. "Gashi" Injishi, " Tunda ba zaki amsa mani ba, rigata za ta jira bayan na tafi."

Adel kuwa me zata ji da irin wannan abu da saurayin nan mai nuna aniya ta gaske yayi idan ba lallaba ta yakeyi ba. Watakila ma dai ai ba shi da aibu....

Bayan wata uku kuwa Adel da Methu suka yi aure.

Auren gargajiya akayi bisa ga al'adun su. Bukin ya faru ne wata rana a cikin watan Oktoba da tsakar rana akayi har dare. An ba da abinci har sau biyu ga dukan mut anen kauyen da suka halarci bukin. Dukan wannan tunani ya zo ma Adel cikin karamin lokaci tana fama da waswasi da doki da damuwar cewa ita fa bata kai shekarun yin aure ba alhali ma shin yin aure yanzu ba babban kuskure bane? Ita ce ta farko a cikin yaya bakwai da zata fara yin aure, ta kaka ma za ta fahimci wannan sabon matsayi nata a zaman matar aure? Fadakarwa daga pasto kadai ne ya kwantar da hankalin ta bayan bukin ya watse, "Adel," in ji shi "Allah shi kadai ne zai iya raba ku da Methu daga yanzu"

Adel ta sami juna biyu bayan wata guda da auren, kuma ko da shike cikin ya dau cikakken lokaci, ta haifi kwantacce bayan doguwar nakuda mai tsanani. Adel da Methu sun jijjiga ainun da wannan rashi.

Amma bayan wata hudu sai ta sake samun juna biyu, a wannan karo ta haifi bakwaini wanda ba' a zaton zai rayu. Abokai da suka ziyarce su, sunyi ta sanyaya wa Adel rai suna karfafa ta cewa a lokacin da jaririn zai rasu tayi karfin zuciya "Jariri na ba zai mutu ba!" Adel ta amsa da taurin kai. Zuciyar ta a rinjaye take game da haka shi ya sa bata yarda da ra'ayin kowa ba kona iyalin ta ko na makwabta. Ba za ta sake yin rashin wani da kuma ba.

Adel ta kwantar da diyarta akan matashi kuma tayiwa yar diyar ta magana, tare da yin addu'a ga Allah a lokaci guda. "Me yasa kika fito duniya Christina 'ta rada. "Baki cika lokacin ki ba a cikina, amma kuma gaki. Kuma ko da shike kinyi kankanta, da ni da Methu muna kaunarki kwarai, kuma na

sani Allah zai kiyaye ki ya tsareki kuma.

Iyalin ta da mutanen kauyen suka yi mamaki, domin Christina ta farfado tayi girma kamar kowa, lafiyayyar diya kuma ta sami kani shekaru biyu da rabi gaba aka sa masa suna Christiano.

Farincikin Adel da Methu kuwa yana da yawa.

Ba da jimawa kwarai ba bayan an haifi Christian suka kaura. zuwa cikin gidansu na kansu. Gidan na da dakunan kwana guda uku, galibin gidan anyi ne da itatuwan gwangwala. Gida ne mai sauki, amma dai nasu ne. watakila bayan yayan sun yi girma ne za su iya samun gidan da yafi wannan girma. Wannan abu ne da za su sa rai ga yi gaba. A yanzu kam, suna da farincikin fita daga gidan iyayen Methu. Kusan dukan iyalin da suke kauyen Adel Krista ne su, kuma tana taimakawa da darusan majami'a na yara cikin marmari.

Akwai fiye da yara hamsin wadanda kusan yawancin su sa'annin Christina da Christiano ne, kuma Adel takanji marmarin karanta musu labarum Littafi Mai Tsarki masu dadi wadanda kakanta ya kan karanta mata tana karama. Abin ya dace da yake gashi yanzu tana yin abinda kakanta ya yi mata-shaida bishara-idan ma dai ga yaran makwabtane.

## JIHADI NA TAFE

Adel da mutanen kauyenta suka cigaba da rayuwar su cikin saukin damuwa, har sai lokacin da wasu Musulmi daga kauyen da ke makwabtaka dasu suka kai musu ziyara ta "aikin hukuma!"

Ko da shike ba ta farga ba a wannan lokacin, tashin hankalin ya fara ne tun daga karfe uku na ranar tara ga watan Satumba 1999, ranar da, idan aka tuna baya, Adel ba za ta taba iya mantawa ba. Taji ana hayaniya sai tayi maza ta fito waje nan da nan, kuma ta hangi tutarsu. A jikin tutar kuwa kalamu guda biyu kawai aka rubuta da manyan harufai. " Linti DAmai," Ma'ana " Kauna da Salama", Kewaye da wannan tutar kuwa akwai mutane talatin, maza, mata da yara daga wani kauye mai suna Dahma.

Wani mutum wankan-tarwada mai matsakaicin shekaru ya yi shela yace, "Mutanen Dodi," mu makwabtanku ne, kuma ya

kamata mu yi wa kanmu alkawarin zaman lafiya." Ko da shike ba ya amfani da na'urar amsa kuwwa katuwar muryarsa na fita a sarari. Yana tsaye gashi nan dogo kuma siriri a jingine da dandamalin katako na dakin taro. Bai kamata a sami tashin hankali a tsakanin Musulmi da Krista a kauyuka da ke makwabtaka ba, inji shi. Kamata ya yi duka a zauna lafiya.

Adel da sauran jama'a da suke kewaye da dandamalin suna saurare domin babu wani tashin hankali ko alamarsa da ya ba faruwa tsakanin makwabtan kauyukan nan, amma duk da haka sai suka amince da wannan batu da aka kawo, wadanda ma suka wuni a kauyen.

Daga baya a wannan yammacin, bayan Methu ya dawo daga aikin tono ma'adinai, sai Adel ta bayyana masa abin da ya faru "Amma batun jita-jitane"? Methu ya tambaya.

An jima ana jin jita-jita cewa tara ga watan tara 1999 zata zama bakar rana ga Krista mazauna tsibirin Dodi. Amma Methu da Adel suka yi watsi da jita-jitar a zaman jita-jita ce kawai. Gashi yanzu kam sun amince da wannan ziyara tasu kuma suna ganin babu sauran wata fargaba. Alhali ma dai dukan yaransu sunyi ta wasa da yaran mu tare.

Anyi kusan watanni hudu ba tare da wani abu ya faru ba ko kuma wata shakka, mutanen tsibirin Dodi kuwa suka yi watsi da jita-jitar har sai bayan Kirsimeti. A lokacin da wani saurayi dan kasuwa ya dawo kauyen a yayinda aka hana shi fita daga tsibirin domin wata tafiya da ya shirya yi. Mutanen kauyen suka tambaye shi ko me ya sa ya juyo da sauri haka? 'Sun hana ni barin garin, " in ji Yulpius.' Wanene? Kuma domin menene?" Wani mutum ya tambaya, sauran jama'a kuwa suka shiga cikin damuwa.

Yulpius ya ci gaba, " Wasu gungun Musulmi ne suka hana ni, ni kuwa bansan dalili ba. Da farko gaya mani suka yi wai bai kamata nayi tafiyar a wannan lokacin ba wai akwai hatsari. Ni kuwa naki na gaya masu cewa lallai ne na bar tsibirin domin sayo kayan sayarwa da ke karanci, amma basu ma nuna alamar kulawa ba.

Sai suka fara bata rai sosai cewar wai ni Krista ne. Na gane wadansu daga cikinsu na cikin tawagar musulmin da suka zo sukayi mana shelar zaman lafiya na waiwai din nan. Da yake bana son wani tashin hankali, sai na juya na dawo gida."

Da Adel da Methu da sauransu kuwa suka fara zullumi game da labarin Yulpius, suna tuna abubuwan da suka faru a baya game da tara ga watan tara, amma basu ga wani tabbacin akwai hatsari ba, don haka me zasu iya yi? Sa'an nan fa a ranar goma ga watan Jan airu abin da suke tsoro ya shigo ma tsibirin su.

TAMFAR GUGUWA GAMAGARI

Adel tana hutawa tare da Christiano da ke ba bu lafiya da rana tsaka a yayinda hayaniya da ta fara tashi yasa suka farka, Adel ta fito ta kofa a guje sai ta hangi tarin hayaki na tashi can nesa da su. Gidajen Krista na cin wuta. Daga nan fa sai hayaniya da dimauta. Lallaine su arce daga gidajensu.

Musulmi dubu uku masu dauke da mugayen makamai na tafe mawuyacin abu ne a sa rai ga dakatar da wannan hari.

Adel ta koma cikin gida a guje tana yi wa Christina da Anto tsawa. Amma ba bu wanda ya amsa. Adel kuwa sai tayi ta faduwar gaba zuciyar ta na bugawa dig-dig-dig a yayin da take neman inda yaranta suke, tana shiga tana fita tana kiran sunayen su da karfi. Can sai wani ya gaya mata cewar sunga yaran sun rigaya sun fice sun nufi kan duwatsu na bayan kauyen. Adel ta koma ciki a guje ta kwashi wasu yan abubuwa cikin gaggawa da ta sake nufar kofa garin fita sai ta hangi Littafin ta Mai Tsarki akan tebur sai ta koma ta dauka sa'annan tayi waje a guje domin arcewa.

## "IYA, MUTUWA ZAMU YI?"

Karfe shida na Yamma Litinin Goma ga Janairu 2000. Methu da sauran mazaje na kauyen suka kafa daga suka hana Musulmin shiga kauyen har na tsawon awa hudu, amma ina

Tunda suna dauke da adduna, touchila da bindigogi. A halin yanzu kuwa kauyen ya kama da wuta ko ina, da kuma karar maharan na "Allahu Akbar! Allahu Akbar" ya cika ko ina. Methu da sauran mazaje suka arce cikin jin tsoro suka haura tudun gini mai santsi da sa rai cewa yan jihadi za su gamsu da barnata gidajensu da dukiyoyin su kawai. Amma maimako hasalarsu ta aikata mugunta ta rigaya ta shiga zuciyar kowannen su, ba da jimawa ba kuwa sai gasu suma suna hauro tudun, suna harbe harbe da bindigoginsu da ido rufe akan taron Kristocin.

Methu da Adel suka yi maza suka tara yaransu wuri guda a yayinda kowa ya fara gudu yana nufar inda yasa gaba, domin kokarin kaucewa harbin bindiga, sai suka tsoma kansu cikin zurfin ciyayi sukaci gaba da rarrafe a ciki da sauri sauri zuwa cikin kurmin jeji. Amma wannan mawuyacin tafiya yaji musu a hannayensu da gwiwoyinsu a yayin da ruwan sama mai karfin gaske ya fara fadowa yana maida kasar ta zama cike da tabo.

Bayan da suka yi rarrafe na tsawon awa biyu a cikin wannan bakin kurmi sai suka iso wata rumfa a bakin wata gonar kwakwa wacce ba a amfani da ita. An kafa wannan rumfa da take da gefe uku kuma da rufi, manoma ne suka yi amfani da rumfar domin kare kansu daga rana a lokacin girbi. Da fatar cewa a daren yau za a yi amfani a wannan wuri a zaman mafaka domin wannan gajiyayyun iyali. Sun gaji tibis da ba zasu iya kara yin gaba ba.

Nan da nan kuwa barci ya kwashe Christina da Christiano, Adel ta kwantar da su akan wata tabarma da aka saka da gwangwala wacce suka taras a cikin rumfar. Kamar dai sauran iyalin suma yaran suna jike caba caba da tabo. ko da shike wannan tsohuwar rumfa tana bada rufi amma jinkar na cike da ramuka inda ruwan sama ke diga yana kara jika yaran.

Anan fa Adel ta kasa gajin hakuri. Kamar yadda ruwan sama ke diga a cikin rumfar akai akai, sai hawaye suka fara

zuba daga idanunta a yayin da ta fara kuka.

A lokacinda ta sami dan kwanciyar hankali sai ita da Methu suka hadu a takure suka yi addu'a, sa'annan suka zauna shiru tare da iyayen su cikin dukan wannan dare mai tsoratarwa. Da jijjifi kuwa. Christina da dan'uwanta suka farka. Sannu a hankali kuwa suka zo ga fahimtar wannan mugun dare mai ban tsoro wanda suke zaton cewa ya wuce, ashe kuwa da gaske ne suka zauna suka zuba wa manyan nasu idanu, tare da sa rai zasu ji kalamu masu karfafawa. Amma shiru kake ji domin tsananin tsoro gashi kuma babu wanda ya san ta cewa.

A karshe sai Christiano yace, " Iya, ina jin yinwa" sai idanun Adel suka fara tara hawaye, tana kokarin kada hawayen su zubo, amma ina, a lokacin da ta dauko yaronta domin ta rungumeshi tuni ta barke da kuka.

"Adel ki daina irin wannan kuka haka", Methu ya roke ta. " Zan fita na nemo abinci, " Yana kokarin karfafa matarsa, amma shi kansa yasan cewa abin ya kai ga wata makura. Hankalin Adel a tashe yake domin ganin wannan matsayi da ya'yanta kaunatattu suka shiga.

Methu ya shirya zai koma kauyensu da aka rigaya aka ragargaza domin nemo abinci, Amma Adel ta roke shi da kada yayi haka, amma kuma ta san cewa dole ne ayi wani abu, domin babu yadda zasu yi su cigaba da zama haka a cikin wannan rumfa babu abinci ko ruwan sha.

Amma fa da Methu ya tafi, sai ta ga karmar lokacin baya tafiya. Da tsoro da damuwa suka sha kan Adel sai ta jagoranci iyalin ta suka koma cikin dokar kurmi. Sannu a hankali kuwa sai suka gamu da wasu mutanen kauyensu wadanda suka boye a gefen wata gonar masara.

Adel ta jagoranci Christina da Anto tare da iyaye mata ta cikin jerin masara a gonar, suka kakkarye goyon masara da suka yi kwari. A kalla dai sun sami abinci.

Bayan wani lokaci sai Methu ya dawo dauke da

gwangwaye guda goma sha biyu na cocacola. Wannan shine kawai abinda ya samowa yara. Amma a yayinda yara suka yi shirin bude gwangwayen Coca Cola, sai akaji harbi kuma babu wanda ya gane ko daga ina harbin yake fitowa, sai dukansu suka yi kwanto a kasa, ba tare da sanin ina yakamata su nufa domin arcewa ba. A karshe dai Christina ta kalli Adel ta tambaya, "Iya, mutuwa zamu yi?

I, zamu mutu, Adel tana yin wannan tunani a cikin zuciyar ta, amma ta sani lallaine tayi karfin zuciya domin ya'yan ta. Sai ta jawo su duka biyu kusa da ita tace musu kome zai daidaita.

Adel ta sani cewa kalmomin bakinta na kwantar masu da hankali ba zai dauki gurbin hakikanin gaskiyar matsayin wannan bala'i mai tsoratarwaba. Ta san me ya kamata ta yi, Kuma zai zama tattaunawa mafi wuya da za ta taba yi da ya'yanta, amma Adel ba ta da zabi. Dole ne ta gaya musu.... "Christina da Anto, ku dube ni kuma ku saurare ni a hankali. Idan mutanen nan masu jihadi suka kama mu, zasu tambaye ku ko kuna so ku zama Musulmi. Idan kuka ce a'a mai yiwuwa ne su kasheku. Sai Adel ta zuba ido tana kalion kwayar idanunsu. Ta sani cewa amsa madaidaiciya guda daya ce kawai. Amma ta kaka kananan yara irin wadannan zasu iya samun karfin zuciya?

Duka yaran biyu suka ba da amsa mai sauki, "muna so mu bi Yesu" Ba tare da bata lokaci ba sai Adel ta bude Littafi Mai Tsarki da ta taho dashi zuwa wata aya da take tunaninta tun lokacin da suka arce daga gida. Kakanta yasha karanta mata wannan aya tun tana karama shi yasa ma har ta haddace wannan ayar: Zabura 23, sai ta umurci yaran su maimaita karatun da take yi musu sai kuwa ta fara:

Ubangiji makiyayi na ne, bazan rasa komi ba. Yana sanya ni in kwanta a cikin makiyaya mai danya. Yana bisheni a gefen ruwaye na hutawa.

Yana wartsakadda raina:... Hakika ko tafiya nike yi ta tsakiyar kwari na inuwar mutuwa ba zanji tsoron kowace

masifa ba, gama kana tare da ni.... Taci gaba da yin haka har saida yaran suka haddace. Dukansu kuwa suka yi karfin zuciya amma fa Adel tana nan tana ta tunanin ko suna fahimta da irin tsananin matsayin da suke ciki.

Tunanin haka kuwa yasa idanun ta suka yi kwalla amma sai tayi maza maza ta share da bayan hannunta, sai ta tambayi "Christina ba kya jin tsoron cewa zasu kashe ki idan kika ce ke Krista ce?"

Sai Christina ta kawo fuskarta kusa da na uwarta, ta dubi cikin idanunta, sai ta amsa a hankali, "Iya, idan kin yarda kada ki 'damu, bana jin tsoron mutuwa."

Bayan da karar harbe harben bindigogi ya lafa, su da suke cikin gonakin masara suka watse. Da Adel da Methu da iyalansu suka koma cikin duhun jejin kurmi, inda sukayi ta tafiya har na kwana biyu. Sukan yi ta tafiya a cikin duhun dare suyi barci na karamin lokaci kafin su sake tashi da jijjifi. A wasu lokuta Methu ya sadu da mutanen kauyensu kuma yaji labarin an kashe wasu Krista. Domin tsananin kaunar iyalinsa kuwa sai ya kara nutsawa cikin kurmi.

Kowa ya gaji, kuma a karshe Methu da Adel suka farga cewa bai kamata a kara matsa wa yaran da irin wannan tsananin tafiya na ba dare ba rana ba. Ko da shike suna dauke dadan tarin madarar kwakwa, amma yinwa tana ji musu, Adel kuwa a duk lokacin da daya daga cikin yaranta ya nemi abinci sai ta fashe da kuka. Harma sun gamu da mahaifin Methu da kuma dan'uwansa.

Sun isa wani wuri da Methu yake kyautata zaton cewa ana iya hutawa ba tare da wani hadari ba, sai ko ya tara busassun ganyayen kwakwa domin ya dora yara akai. Anan kuwa, sai shi da dan'uwansa suka yi shawarar zuwa can domin suga ko zasu samo wani abin da zasu iya ci.

A cikin karancin shekaru irin na Anto, shi bai gane da dalilin da yasa babu abinci domin su a cikin yan kwanakin nan ba, ya ko fito fili yace a bashi shinkafa da kifi. "Yanzu babanka zai

dawo, kuma watakila ya kawo maka kifi. Sa'an nan zamu ci, inji Adel, tana kokarin ta karfafashi. Amma ita ta sani ba lallai bane Methu ya samo wani abinci domin ṣu, sai ta rungumi Anto, tana waka tana tangada shi.

## JININ YESU SHINE MAFI IKO DUKA

Kasa da minti goma bayan fitar Methu, sai Adel taji karar muryar Methu, da farko sai tayi tunanin cewa hauka yake da irin wannan karagi haka, sanin cewa mai yiwuwa yan jihadi suna kusa. Amma sai ta gane cewa an rigaya an yi wa Methu zobe, shi ya sa ya ke yin magana da karfi domin suji suyi maza maza su tsere, taji irin kalmomin da suka tayar mata da hankali can baya, "Gudu Adel Gudu!

Kafin Methu ya kuma sake kira da karfi, sai Adel taji karar bindiga mai sairafa kanta. Nan da nan kuwa ta tashi tsaye, amma da yake hannayen Anto na rike da wuyar uwarsa, sai tayi kamar zata fadi . Can kuma ta hangi Christina ta ruga a guje ta nufi inda taji muryar Methu. Adel ta kira da karfi domin ta tsaya, amma ina an makara. Wadansu mutane saye da fararen dogayen riguna sun rigaya sun kewaye su.

Anto yana kwance a wurinda Adel ta ajiye shi. A lokacin da yayi kokarin tashi, daya dga cikin mutanen nan ya buge shi a gadon baya da fadin addar sa, Adel ta yi ihu ta jefa kanta akan danta domin ta kare shi daga wani karin bugu. Taga yadda yaro ya razana don tsananin tsoro har ya kai shi ga suma, amma kokarin ta na taimakawa Anto bai yi tasiri ba domin daya daga cikin Musulmin ya kama gashin kanta yaja har ya rabata da kasa.

Aka danne wuyan Adel da wata adda mai caba-caba da jini a yayin da mutanen suke kokarin janta zuwa gindin wasu tagwayen itatuwan gwangwala. Ta san manufarsu a yayin da suka fara yaga mata tufafi. A lokacin ma tana rungume da Littafin ta Mai Tsarki amma sai Littafin ya fadi a kasa kamar dai tufafinta. Adel ta rufe idanunta, cikin zuciya kuwa tana

addu'a domin iyalinta, kuma tana rokon Allah ya ceceta kadasuyi mata fyade.

Ana haka kuma sai Adel ta ji muryar uwarta tana kara da na uwar mijinta da kuma danta Anto, kuma ta sani cewa mugayen mutanen nan da suka kore su daga gidajensu suke yiwa mutanenta kisan gilla. Abin yayi mata yawa. Don wannan tsanani kuwa suma tayi ta kasa tsayuwa ta durkusa kan gwiwoyin ta a yayinda ta ga wadanda suka tasamma iyalin ta sun juyo kuma sun nufo kanta. Jini na diga daga kaifin adduna. Jinin Anto. "Ya Ubangiji!" in ji Adel. Ba tare da sanin abin da zatayi ba, daya daga cikin mutanen ya dauki rawaninsa mai jike da gumi ya nada akan Adel. A jiki kuwa an rubuta, "Allahu Akbar." Da dan karfin da ya rage mata kuwa 'Adel ta yi magana da karfi, "Jinin Yesu shine mafi-iko duka"

"Ita Krista ce! Alade kawai! Kazamar Alade! Bari mu yi mata fyade kawai mu manta da ita, "in ji wata murya. A yanzu kuwa musulmi masu yawa sun kewaye Adel, suna ta shawarwarin abin da zasu yi da ita.

Suna magana ne da harshen su, ba tare da sanin cewa Adel tana fahimtar su ba.

Garin yin kokarin boye irin razanar da take ciki, sai Adel ta yi addu'a a zuci, tana cewa Ubangiji, idan ka yarda ka taimake su domin su farga da abin da sukeyi: Mugunta ce santsa ... idan ka yarda ka sa su, su gane. Ba zasu iya sanin abin da sukeyi ba. Ba abu ne mai yiwuwa ga manaluki ba. A yayinda taci gaba da yin addu'a, a cikin hayaniyar da ake yi a gabanta wata murye mai magana kasa kasa ta rada, "Adel ke ce?" Tana daga kai sai taga wani mutum da suka kama daga kauyen su. Sunan sa Hans. Shi Hans an tuhe shi zindir kuma jikin sa na zubar da jini ainun. Sai zuciyar ta ya kara shiga damuwa domin a yadda ta ganshi ta san da wuya ya rayu zuwa gobe, sai ta tambaye shi ko ya ga Methu da Christina amma ya girgiza kai yace a'a.

Daya daga cikin mutanen ya tara tufafin Adel ya bangaje mata a hannayen ta amma ba a bata izinin sawa ba.

Ta dubi kasa ta kalli Littafin ta Mai Tsarki, wanda aka yayyage mata Kaca kaca.

Aka sa kamammun nan guda biyu a gaba zuwa wata turbar hawan dutse mai mugun hawa da gangara ana yi masu kaimi da kaifin adda a jikunan su inda yafi zafi. A yayinda turbar take kara zama siriri Adel ta dubo kasa daga kan tudu da suke, sai ta lura da irin tsawon tudun da suke, kuma sai tayi tunanin cewa tsalle daga nan a fado abune da bazai yi wuya ba. Ta sani cewa mai yiwuwa a kashe ta idan tayi tsalle, amma haka din ma ai yayi. Ka taimakeni, Ubangiji! Idan ka yarda, ka tamakeni, ta ci gaba da roko. Da yake ta daddage wa jarabar tunanin yin tsalle, a karshe sai suka isa kan dutsen, inda fiye da mayakan jihadi guda dubu suke tattare. Masu shekaru dabam dabam, wadansu ma basu kai ashirin ba, amma dukansu suna saye da tufafi iri guda, doguwar farar riga da kuma nadin rawani aka.

Da bakin bindiga kuwa wani soja ya tilasta wa Adel da Hans su tsaya a bayan juna. sojan nan kuwa mai matsakaicin shekaru ne kuma mai fadaddar kafada, ya ajiye bindigara a gefe a hankali kuma ya zaro adda. Adel ta dudduba kewaye, amma sai ta lura cewa da ita da Hans ne kawai Krista a cikin dinbin mutane masu saye da fararen dogayen riguna. Sai ta rufe idanunta, don tabbatar da cewar kai harma tana sa ran cewa nan ba da jimawa ba za a yita ta kare.

A cikin yan dakiku kuwa, sai taji jini mai dumi na zuba daga fuskarta da jikinta. " Jinin Yesu shine mafi iko duka! Tana fadi akai , akai da karfi. Hans ma yana yin haka. Tana kuma jin muryar wasu a fusace suna ihu suna fada daga nesa. Bata yarda ta kuskura ta bude idanunta ba, a zatonta idan taci gaba da rufewa zuwa wani dogon lokaci, za ta bude su ne taga kanta a can daya gefen, a samaniya. Amma bayan ta jima na lokaci mai tsawo, ba bu yadda zata yi illa ta bude idanunta. A gabanta kuwa sai ga gangan jikin Hans da aka yi kaca kaca da shi.

## KALMOMI MASU SAUKI GUDA BAKWAI

Jikin Adel na jike da jini amma ba ta iya fadar ko jininta ne ko na Hans ba. Tana cikin tsananin jin zafin duka, da musulmin nan maza suka yi mata, amma babu alamar wani budadden rauni a jikinta. Yanzu kam muryarta ta dishe amma sai da tayi kokarin maimaita kalmomin Jinin Yesu shine mafi iko!" Ta wata hanyar ta sani cewa Allah yana kare ta. Da ta mutu fiye da sau akara a yanzu. Anyi fiye da awa biyu daga lokacin da suka tube mata tufafi suka fara dukanta. A yanzu ta rigaya ta sani cewa Anto, uwarta, uwar Methu da Hans sun rigaya sun mutu, kuma tana jin kamar sauran ma haka. Amma har yanzu ita tana da rai ba zai yiwu haka ba kuwa sai da dalili. A cikin tsakiyar wannan balai ta wata hanyar Adel taji a jikinta cewa tana tsinkayar wani bege na ban mamaki. Jerin gungun mayakan Jihadi suka tara kayan yakinsu suka shaida wa Adel cewa lokacin tashi yayi, ita ce zata zama jagorarsu, inji su. Suka tura ta gaba kan layi, ta jagorance su gangarowa daga kan dutsen ta turba mai kwane kwane ainun ta daya gefen dutsen. Adel ba ta ma da tunanin ina zasu tafi, ita dai tafiya kawai takeyi cike da tunanin irin mummunar kisa da aka yi wa Hans tana kokarin fitarda dukan wannan daga tunaninta. Watau gutuntula shi da suka yi bai gamsardasu ba, saida mutanen nan suka sa masa wuta ya kone kurmus.

A lokacin da suka sauko karkashin dutsen, basu kara nuna bukatar Adel ta ci gaba da jagoranci ba. Mutanen suka tunkuda ta ta fuskanci hanyar kauyen Dahma, kauyen su, suna ta jan gashin kanta mai tsawo, suna cin zarafinta suna ta marin tsiraran jikinta da fadin addarsu. A kowane hari da suke kawo mata kwa Adel tana ta kira da murya, "Jinin Yesu ya fi komi iko!" A wasu lokuta daya daga cikin mutanen yakanyi gudu ta bayan Adel yana barazana da addarsa ta bayan Adel, sai ta fadi a kasa kamar yar tsana tana rike da kanta a tafin hannayenta, sai taji kamar ana soka mata allurai guda dubu a cikin kanta, amma idan ta bude hannayenta ta duba sai tayi mamaki babu jini.

## YAKAR KIYAYYAR DA KE DAGA CIKIN CIKI

Bayan da Adel ta ura cewar Allah yana kare ta ta hanyoyin ban mamaki sai karfin halinta ya karu. Amma me ya sa? Ba ta iya gane dalilin da yasa har yanzu tana da sauran numfashi bayan an kashe dayawa ta mummunar kisa. Har masu kamata ma a daburce fuskokin su suke, kuma tana mamakin ko suma kansu suna tambaya ta kaka wannan mata mara kariya take jimre wa irin wannan kai harin. Abin da yafi basu haushi ma shine taci gaba da kira gamdda Jinin Yesu.

A karshe sai daya daga ciki ya tsayar da ita, iya tara ganyen taba ya sa wuta, sai ya cusawa mata cikin bakinta. Idanun Adel suka hasala da taga ana kawo tabar a gabanta. Ta yi kokarin taki amma, ina ba zata iya hana wannan kakkarfan mutumin nan yin haka ba. Yanzu kam yana jin cewar ya rufe bakin wannan "kafirar,"sai ya juya yayi murmushi yana gamsuwa da ketar da yayi. Amma ta fitar da hannunsa daga bakin Adel ked a waja, sai ta tofar da korannan ganyen taban nan kuma tayi magana da karfin zuciya, " Jinin Yesu yafi komi iko" Wadannan kalmomi masu sauki guda bakwai sun zama abu na zahiri a yayinda matsayin Adel na azabtuwa yana cin gaba.

Rana ta fadi, amma farin wata ya haskaka musu turba a yayin da suke kusantar kauyen Dahma. Adel tana iya hangen fitilu daga cikin gidaje da inuwar yara suna guje gujen su. Sai ta tuna da nata kauyen inda yara ta sukan yi nasu wasan kamar dai yadda wadannan suke yi.

Tawaga ta tsaya, sai aka ce wa Adel tasa tufafinta. Samari guda biyu wadanda basu fi shekaru ashirin da haifuwa ba ne aka bari domin gadin Adel da ribalbal a hannayensu, sauran kuwa suka shiga kauyen. Adel ta tambayi samarin nan ko sun san abin da ya faru da diyar ta. "I mun kashe ta," inji daya daga cikinsu. Jikin ta kuwa ya bata cewa karya suke yi, amma tana ganin kiyayya muraran a cikin idanunsu. Ita ma kuwa tana jin kiyayya na taso mata a can cikin cikinta, sai kuwa tayi addu'a ga Allah ya dauke mata.

Da jimawa kadan bayan haka kuwa sai aka shigarda Adel a cikin kauyen, inda aka kuma shiga tozarta ta ana azabtar da ita. Mayakan nan mugaye ne, amma tana cike da karfin hali. Idan har lokacin mutuwar ta ne yayi ko ma da a hannun sojojin jihadi ne to a shirye take. Harwayau Adel ta lura da cewar ita kadai ce kamammiya da ake gani. Bata ma iya tunanin kintata yawan wadanda aka kashe. A wannan lokacin fa ba ta san wanne yafi muni ba a mutu ko kuwa a shiga hannun irin wadannan mugayen mahaukatan mutane. Duk da irin azabtarwar, ta ci gaba da shela da karfi, "Jinin Yesu ya fi komi iko" a duk lokacin da wani soja ya gana mata azaba a jikinta da yasha azabtuwa.

An sake tube Adel zindir a shalkwatar ba da umarni na yan jihadi. Wasu mata guda uku suka kai ta bayan daki inda aka yi mata wanka da ruwan sanyi a cikin bahon karfe mai tsatsa. "Idan kun yarda bari nayi wanka da kaina," Adel ta roka. Amma suka ki, bayan da Adel ta sake rokon su, sai suka yi mata duka da wasu itatuwa da aka sifanta kamar cokula: bayan wanka da ruwan sanyin sai aka bata wata tsohuwar taguwa da wando mai huji. Ainihin tufafinta tufafine na "Kazamar alade", matan suka shaida mata, saboda haka za a kona su.

## "A INA KRISTOCIN SUKA BUYA?"

Mutane guda goma sha daya aka nada domin su yi wa Adel tambayoyi, wadansu talatin ko arba'in kuma suna kewaye da su. Ta gane wasu daga cikin shugabannin sune suka zo kauyensu da tuta ranar tara ga Satumba suna shela, "Salama zuwa ga tsibirin Dodi." Mutumin da yake shugabantar masu yin tambayoyin shine wanda yayi magana akan dandamali a ranan nan. Sai fa Adel ta fara jin kiyayyar mutanen nan na taso mata domin ganin cewa mutanen da suka zo domin neman yin sulhu da zaman lafiya su suka dawo suka kai masu hari a kauyensu. Kuma suka kashe mata abokan ta da iyalinta, har da danta masoyi Anto.

Yanzu, a yayin da suka sa ta ta zauna akan wani kujerar katako a tsakiyar dakin, tana mamakin ko menene ma'anar salama ta zaman lafiya irin tasu.

"A ina sauran Kristocin suka buya?" wannan dogo kuma siririn mutum ya tambaya.

"Ba zan gaya maka ba. Ko da kashe ni zaka yi, ba zan amsa ba." Adel tasan inda yawancinsu ke iya buya kuma tasan me zai faru da su idan ta fada.

Haba: Ai ba zamu yi musu komai ba. So muke kawai musan inda suke. Baki so ki tafi gida? 'Adel ta yi zamanta shiru, ta ki amsa tambayoyin su. Aka ci gaba da tambayoyin har tsawon minti talatin, aka kuwa kara marinta a kumatu. Aka sa mata kwaryar abinci a gabanta, amma sai taki ci sai mutane biyu suka tilasta bude bakinta karfi da yaji suka cusa mata abinci. Adel ta tofar, ko da shike kwana uku kenan ba ta ci abinci ba.

Labarin kin cin abici na Adel da kuma kin amsa tambayoyinsu ya bazu nan da nan a kauyen Dahma, mutane da yawa kuwa suka taru a shalkwatar ba da umarni, suna cewa, "Ku bamu ita! Zamu gutuntula ta kuma mu sakata a karkashin kasa!"

Da jin muryoyin nan masu hasala, Adel ta cika da kiyayyar su kuma tsoro ma ya far mata. A karshe dai wani dattijo mai suna Sabar ya shigo cikin dakin. Alamunsa basu nuna cewa shi mai hasala kamar sauran ba. Ya durkusa kusa da inda Adel take zaune, ya tambaye ta ko za ta iya fadar inda sauran Krista suke a boye.

"A'a, ba zan iya ba, " ta amsa a yayin da tsoro ya rufe ta kuma hawaye suka fara zubo mata. Sabar ya tashi kuma ya gayawa mai bada umarn. "Zai fi dacewa idan za a bar wannan diya ta taho tare dani. Idan ta kara jimawa anan za su kasheta." Wani taro na maza suka cigaba da tsoratar da Adel wai zasu kasheta yayinda ake raka ta zuwa gidan Sabar. Suka yi alkawarin zasu dinga tsayawa a waje har zuwa lokacinda zasu yi sa'ar kai mata hari. Amma Sabar ya gaya

mata, babu abin da zai sameki anan, kina iya kwanciya a daya dakin nawa".

Shigarta cikin dakin nan mai karancin shinfidu ke da wuya sai Adel ta rufe kofar sa'annan ta zauna akan gadowata sakakkiyar tabarma nanfa ta fara zubarda hawaye tana tunanin masoyin dantaAnto.

## "KINA TUNANIN ZAI IYA CETONKI DAGA WANNAN?"

Washe gari wadansu sojoji saye da kayan sarki suka shigo kauyen, nan da nan kuwa aka kaisu gidan Sabar domin su ga Adel. Tambayarda suka yi mata bai sha bambam da na sauran ba. "A ina sauran Kristocin suka buya?" Har wayau Adel taki ta bada amsa, sai aka barta ta koma dakinta, amma tana iya jin maganarsu daga cikin daki. Sojojin nan masu daddagewa suna da manufa guda daya su samo sauran Kritoci - kuma sun yanke shawarar zasu tafi tare da Adel a zaman jagorarsu." Abin ya tsoratar da Adel. Sai ta kudurtar a ranta cewa gara ita ta fara mutuwa.

Da rana kuwa matan kauyen guda uku suka kawo wa Adel abinci, amma har yanzu taki ci. A yayinda matan suka fara yin magana a tsakaninsu, sai Adel ta gani cewa ai ta san su can baya, sun fito daga cikin suka kauyensu kuma a lokacin haifuwarsu Krista ne su. Amma sai suka auri musulmi suka sauya addininsu. Daya daga cikin matan, Umi, ta fara sukan ra'ayin Adel a tsegunce. "Ai laifinki ne ya sa danki da uwarki suka mutu. "Kin ki ki tuba ki shiga addinin Islama, amma yanzu gashi kina' jin shi a jika. Kina so ki bada gaskiya ga Yesu, amma a zatonki kina jin zai iya cetar da ke daga dukan wannan?"

"Yi shiru, Umi! Ki daina magana irin wannan," daya daga cikin matan ta umurce ta. " Me kike zato (Kina zaton Mohammed zai cecemu?") Adel ta lura da laushin fuska da ke tattare da wannan mata, kuma kafin su tafi su barta Adel ta rungumi wannan mata ta fara kuka sai ta rada mata a kume

cewa wata kila watarana zan iya sake juyowa ga Kristi."

Adel ba ta iya rabewa ba ko bayani ne take yi, ko kuma tambaya akan ko yana yiwuwa ta iya dawowa. Sai ta dubi fuskarta mara fara'a ta fada a hankali, "Idan da gaske kina so ki dawo ga Ubangiji shi zai kirkiro hanyar yin haka din."

Dare na karatowa kuwa sai sojojin suka dawo. An yanke shawara cewa ayi wa dukan Kristocin tsibirin kofar-rago, kuma Adel kawai tafi dacewa ayi amfani da ita domin taimaka kakkama su. Da zarar an kamasu sai a tara su a kone su duka babu wanda za a bari da rai. Adel ta sani cewa ba abinda zata iya yi ta hana wannan mugun shiri nasu, sai ta kulle kanta a daki ta shiga addu'ar neman karfafawa, idan suka dauke ta na zaman jagora kuma taki to ta sani mutuwa zatayi tabbas.

Wasu maza anan waje a gidan Sabar suka fara shewa, sai Adel tayi rarrafe zuwa jikin bangon gidan ta leka ta tsagun bango domin taga ko menene dalilin hayaniyar.

Mayakan sun kamo wasu iyalin Krista. An kashe mijin, da matar da yayanta uku kuwa suna kan hanyarsu ta zuwa Dahma. Taji su suna cewa sunan matar Rose. Sai gaban Adel ya fadi a yayinda ta ke komawa kan tabarmarta. Tasan iyalin sarai. Daya daga cikin yaran sa'an Anto ne kuma sukanyi wasa a gidansu tare kusan kullum. Can kusan tsakar dare Sabar ya dawo gida, fuskarsa na daure. Adel kaka zamuyi: sojojin sun nace akan zaki tafi tare da su".

Adel ta yi mamaki da yace mu. Kusan ma shi Sabar yana nuna damuwa akan wahalar da take sha. Tausaya mata dayake yi ya dora ta akan dan karamin tsibiri na kwanciyar rai cikin tsakiyar makiya. Amma Adel ta sani bata da wani zabi. "Gaya musu suna iya harbe ni nan take. Bazan tafi tare da su ba. "Me ya sa kike jin tsoron su?" Sabar ya tambaya. 'Domin na san shirinsu. Na ji lokacin da suke magana, ni kuwa bazan sa hannu domin taimakon a kashe kowa ba," ta amsa . Sabar ya bar dakin. Adel kuma ta ki cin abinci har yanzu kuma ga rashin barci.

Alfijir na ketowa kuwa sai aka sami labarin cewa an kashe wani iyalin Krista kuma.... An kama karin mata da yara kuma an sami wata karamar yarinya. Adel kuwa taci gaba da tunanin ko za ta sami labarin Christina, da abin zai fi kyau. Wannan tunani ne, amma taki jinin abinda mamaguntan sojojin nan zasu iya yiwa kaunatacciyar diyarta baiwar Allah.

## CHRISTINA:

Wajajen karfe hudu na asuba. Adel tana mika kukanta ga Allah, "Me yasa ba zaka bari na mutu ba?" Hawaye share share, suna zuba a yayin da take cingaba da, tambaya, "Me yasa?"

Barazanar kashe ta da wasu keyi kuma bai tsaya ba, saura kadan wani cikinsu yaci nasarar sukarta ta wurin zura addarsa zuwa cikin daki. Biyu daga cikin matan auren nan da suka ziyarci Adel baya suma sun dawo. Suna rokonta taci abinci.Amma taki. Taci gaba da zama a dakinta, tana kokarin samun yin barci cikin wannan asubanci, amma yawancin lokaci tana takure ne da bango tana kuka.taci gaba da yin addu'a domin Methu da surukanta-amma mafi yawa takanyi addu'a domin Christina.

## DAGANAN FA SAI LABARI YA ISO.

"Adel! Adel!" Sabar na kiranta a yayinda ya shigo dakin a guje. Akwai wadansu maza a waje, "Sunce sun kama diyarki, Christina."

Wannan kasadace.... babbar kasada, amma dole Adel ta sani. Zai yiwu kuwa ace Christina tana raye? Ko kuwa wani rudi ne na keta domin yin wayon fit ar da ita daga gidan Sabar? Akwai hanya daya kawai da zan iya tabbatar da haka.

Suka yi tafiya a cikin karamin jirgin ruwa zuwa kauyen (Wanda Adel ta roka Sabar ya taho tare da su kuma ya yarda)

Abokan Anto. Ita yar shekaru bakwai ce kawai. Adel ta rungumi wannan yarinya sosai. Tayi kuka tana kwaye wa yarinyar gashin kanta daga fuskarta. Sananniyar fuska ce ta iyali da suke abokai.

Adel ta zauna kusa da Maksi a wannan tafiya zuwa Salubi. Ganin Maksi yana sa Adel ta tuna da Anto ainun. Amma wannan dan tsanaki ya katse a lokacin da ta hangi sojoji suna jiran isowarsu a daya gabar kogin. Suka fizge Adel daga cikin jirgin ruwan, tunanin irin muguntarsu kuwa ya sake dawowa. A yayin da Maksi ta ga irin farmaki da aka kaiwa Adel abin ya razanata ainun. Sai tayi ihu da karfita fara borin-jiki tamfar mai farfadiya. Da taji karar yar karamar kawarta sai Adel ta sake yin shelarta, "Jinin Yesu ya fi komi iko!" Yanzu fa sai ta fara shakkar cewa batun zuwa Salubi yana da nasaba da batun Christina. Begen nan da take dashi kuwa sai ya fara shudewa da sauri sauri a yayin da aka ci gaba da yi mata duka. Sabar yafara rokon su da su daina. Yayi kokari ya kubutar da Adel daga hannunsu, ya kaita cikin wani gida a gaban gaci, inda ake rike da sauran kamammu. Anan ne ya gaya mata cewa zai koma, babu sauran wani abu da zan iya yi maki. Idan na kara yin katsalanda nima zasu kashe ni. Kiyi hakuri."

Akwai wasu mata a cikin gidan wadanda jikinsu ke rawa lokacin da suka ji hayaniyar mutane a waje na cin gaba. Adel kuwa ta rufe fuskarta da hannayenta tana kuka a lokacin da taji takawar sawaye sun nufo ta. Da ta daga fuska kuwa sai taganta. Christina ce!

Christina ta jefa kanta a cikin uwar tayi kuka, Iya, Iya!" Suka rungumi juna tam-tam, Christina kuwa ta fara yin kokarin bude bakinta, tana cewa Iya, kiyi hakuri, Iya, kiyi hakuri. Sun kashe ita kaka. Kuma naga gawarsa, Iya naga Anto.... Shi ma sun kashe shi. Wayyo, Iya!"

"Na sani Christina .... Na san cewa an kashe su." Tunanin yayi yawa Adel kuwa sai ta fara kuka baji ba gani. Christina ta rasa abin da zata ce, sabo da haka sai tayi ta yiwa uwarta sumba akai akai.

## BIDAR WATA AMSA WADDA BA ZATA ZO BA

A cikin daren rana ta shida da kamata an tara Adel tare da wasu kamammu guda sittin aka gaya musu cewa dole ne su zama musulmi washegari da safe.

Bazan taba zama Musulmi ba, Adel ta maida murtani, Wannan ya yi kyau, ba lallaine ki zama ba, Amma kuwa idan baki zama ba, idan har daya daga aikin ku bata zama ba, zamu kashe ku duka," mai ba da umarnin yace." Jinin su kuwa zai koma kanku.

Krista fa suka taru a wannan daren domin suyi shawara. Wannan shine lokaci na farko da aka barsu su wanzu haka tun ranar da aka kai musu hari. Suka yi ta rungumar juna suna ta zubar da hawaye. Suna shawara guda na abinda ya kamata ayi: shin zasu yarda su musulunta ko kuma su shiga cikin mukamin zama shahidan Krista?" Muna iya maimata kalmominsu; muna iya fadar irin addu'oin su. Allah yasan zukatan mu; Ba zai shar'antamu ba," wani mutum ya bada shawara. Ta kaka zamuyi haka? Bayan mun dage zuwa wannan matsayi. Watau duka ya zama a wofi kenan?" "Yaya batun yayi ammu? Ashirye muke muga an kashe su a gabanmu? Shin ko Allah yana son dukanmu mu mutu anan kauyen musulmi?"

Wannan jayayya taci gaba zuwa wani tsawon lokaci a yayinda Adel take tashawarwari game da wannan mugun matsayi da suke ciki. Idan domin kanta ne; tana iya kin ta musultunta ta sani bangaskiyarta zai kaita har ga karshen wannan al'amari. Amma zai dace ne anniyar da zata daukar wa kanta ya kaddara rayuwar wasu, har da Christina. Wannan kaka-ni-kayi na cin Adel a zuci kamar annoba a yayinda tayi kira ga Allah domin samun amsa. Babu amsar da ta zo.

Washegari-kuwa sai aka tara dukan Kristocin a filin gidan. 'Kun yanke shawarar ku? Zaku Musuluntako zaku mutu?" Wani mayakin jihadi ya tambaya.

Babu wanda ya yi kuru domin fara ba da amsa har kananan yara ma babu wanda ya yi magana, cikin matsayi na tsoro da razana da kuma gwagwarmaya da akeyi na can cikin lamiri domin iya cin gaba da zama cikin bangaskiyarsu. Mai ba da umarni ya fara damuwa da irin wannan kafiyar tasu na yin shiru sai ya ba da umarni ga sojojin da ke karkashin sa a cikin harshen su. Sai sojojin suka dawo dauke da cokula guda goma sha biyu kuma abin mamaki shine sai suka fara dama tabo kamar wata al'ada suna cusawa Kristocin a baki suci. Wannan mai ba da umarni ya mari Adel a kumatu a lokacin da ta to far da tabon." Cinye shi? Cinye shi yanzu" yana yi mata tsawa.

Adel ta ki aka kawo mesar ruwa ana fesa wa kamammun daya bayan daya wai ana yi musu" Wankar shiga Islama" kuma musulmin dake wurin suka shiga yin karatun hadda ta ayoyi daga Kur'ani. Bayan da suka kare, sai sukayi rawa kamar wadanda suke buge da barasa sai suka yi ta auna bindigoginsu suna harbin iska wai sun yi nasara na juya Krista zuwa Islama. Kristocin suna tsaye shiru tare suna kallo cikin rudewa yadda sojojin suka ci gaba da wannan bukin nasu na banza.

Amma zukatansu sun kadu a yayin da suka ga sojoji dauke da gwangwayen fetur sun nufo wannan taron. wani hafsa mai kyakkyawan ado kuma mai ruwan kwarjini ya taho a gaban sauran. Adel ta gane shi cewa shi shugaba ne daga Tsibirin Java. Ba tare da nuna ko alama ba, a tsanake ya ba da umarni ga hafsoshin su tara Kristocin a cikin daya daga gidajen a jika gidan da fetur.

Aka tura su a cikin wani bukka, razanannun Kristocin suka fara ihu a yayin da suke tattara yara guri guda suka kewaye su. Basa tsoron su mutu domin Kristi. Kowane dayan su iya tabbatar da haka a akai a cikin wannan lokaci na kawo musu hari.Amma tunanin a kone mutum da ransa da kuma ganin a cuna wa ya'yansu wuta abu ne mai wuyar jimiri gabadaya tare suka durkusa, su na kuka ga Allah ya cece su daga irin wannan mummunar mutuwa.

A yayin da suke addu'a, sai jayayya ta barke a tsakanin sojojin a can waje. Suna muhawarar ko su kona Kristocin. Daya daga cikinsu yace ai anyi musu wanka zuwa Islama kuma zasu yi wa wannan jihadi amfani. Nan da nan aka yarda. Idan kamammun nan sun yarda su shigo aikin jihadi, wannan zai tabbatar da ba da kansu ga Allah kuma zai sa a bar su da rai.

## LADAR YIN TAWAYE

Da jin jayayyar da ake yi a waje, Adel da sauran suka shiga wani matsayi na firgita. Ba amsar da suke nema kenan ba. Amma dole a yanke wata shawara. Idan manyan suka yarda su fita tare da sojojin zuwa yin jihadi na gaba, za a bar kowa. Idan ko ba haka ba za a jika bukkar da fetur, kuma a kona kristocin. Razanannun Kristocin nan suka narke akan gwiwoyin su, suna kallon juna domin samun karfafawa kuma suna mamakin ko wanene zai yi kuru ya fara yin magana. Mai bada umarni kuwa ya shigo cikin bukkar yayi shelar wannan labari mai dadi. Idan har shekarunka sun kai na rike adda, kazo ka hadu damu muyi jihadi. Abin da ban sha'awa!

Fushin da ke tattare a cikin Adel kuwa ya taso ainun a yayinda take sauraren irin wannan ba'a mai sa tashin zuciya da ake yi wa kamammu. Amma da irin wani karfin hali yazo mata, sai ta tashi tsaye. Sai mai bada umarni yayi murmushi, yana zaton ya sami mai bada kai ta farko.

A maimakon haka sai ta fuskanci' sauran mutanenta. "Kada ko wanne acikin ku ya tafi tare dasu. Idan zasu kashemu, to gara su kashemu ana; akalla muna tare da juna".

Mai ba da umarnin nan ya fusata da irin wannan kangara nata, saiya cabke ta a hannu yace "Me kika ce"

Adel ta maimaita, "Ba zamu shiga cikin jihadi ba. Yanzu dai idan yarda ki fita" sai ya matse hannun Adel da karfi, yana kallon cikin idanunta idanun sa na bayanin irin fushin da yake dauke da shi a fili. Amma Adel ta gaskanta Allah zai tsirar dasu. Kuma ta sani sarai cewa wannan kangara da tayi a sarari zai zo da sakamakonsa.

A yayin da kwamandan nan ya juya ya bar dakin, sauransu sukayi ta sha'awar irin tsayayya da tayi, suna mamakin ko watakila ta rigaya ta zama sanadin kaddararsu.

Abin mamakin shine, sai sojojin ma suka fice, aka kuma fito da su daga cikin bukkar.

Makonni biyu kenan suka wuce, kuma Adel dai ana cikin yi mata barazana akai akai. Musulmin sun sani cewa sauran mutanen suna samun tasiri ne daga Adel, saboda haka suke tunanin kashe ta. Ta fara cin abinci da yake Christina tana matsa mata akan tayi haka din.

Shugabannin sojoji suna ta kaiwa suna kawowa zuwa kauyen a kusan kullum domin shawarar abinda za ayi da kamammun. Sunyi shakkar ko wankan Islama da aka yiwa Kristocin nan na gaskene, kuma sukayi maganar cewa da ma sun kone su domin cingaba da sukeyi na kazamtarwa. A wani kokarinsu na karshe wai na tabbatar da shigarsu ga Islama, sai sukayi shawarar cewa ayi wa dukan matan kaciya.

Wasu daga cikin matan suka damu kwarai suka fara yin kuka. Jayayyar da sukayi ya tabbatar da shakkar da kwamandan kauyen yake yi, nan kuma sai yayi naci da a kashe su. Amma sauran har yanzu sun amince cewa kristocin zasu yi amfani idan aka barsu da rai. Saboda haka aka sami yarda a tsakanin musulmin cewa a yanzu kam za a barsu da rai.

Amma fa sun kwashe dukan yara mata da basu balaga ba, har da Christina aka yi musu kaciya ta danyen-hanya. Zafin yana da tsanani Christina kuwa tayi ta kuka. Adel ta tafasa da fushi, amma dai sai tayi kokari tasha kan fushinta. Al'amarinda take ciki mawuyaci ne fiye da yadda ake zato, amma kallon al'amarin da diyarta ta shiga yafi muni a gareta Adel fata kafa kiyayya da dukan musulmi amma ban da Sabar. Ta sani cewa kiyayya itace cutar-daji ta ruhi kuma gafartawa kuwa shine kadai makari. Amma fa kamar gafartawa tana can nesa, abin da bazai yiwu ba. Abin da kawai zata iya yi shine addu'a.

Wasu makonni shida suka sake zuwa ba tare da wata barazanar kisa ba, amma Adel tana zamne cikin damuwa mai zurfi. Tana ganin irin kallon da musulmin suke yi mata, kuma wasu ma sunyi kokarin suyi mata fyade. Tana ganin alamar kwadayin su na jaraba na karuwa a yayinda kwanaki ma na karuwa, kuma tana tunanin har zuwa yaushe zata iya cin gaba da tare su. Kai har kwamandan kauyen yasha tunkarar ta, ta hanyoyin da basu dace ba. Tana duba hanyar kasancewa tare da Methu, tana tunanin ma ko yana da rai?

## METHU

Babu zato, babu tsammani wata safiya wata karamar tawaga ta ma'aikatan gwamnati suka zo Salubi a cikin karamin jirgin ruwa. Tawagar tana aiwatar da bincike ne game da labarin wasu kamammun kristoci a kauyen, tuhumar da sojojin musulmi suka yi musu. Amma fa Nahor mutumin da yake da jirgin ruwan Krista ne, kuma ya taba jin labarin cewa akwai wata mata mai suna Adel da ake rike da ita a wurin. Bayan da ya sauke fasinjojinsa, nan da nan sai ya shiga nemanta.. "kece Adel?" Nahor ya tambaya a hankali bayan wani ya nuna masa ita. "Wanene kai?" Adel ta tambaya tana shakkarsa. "Furtawarta haka ke da wuya sai Nahor ya rungume ta ya fara zubar da hawaye. Naji dukan labarinki da matsayi da kike ciki", inji shi.

"Menene? Ta kaka kayi ka sanni?"

"Methu ne ke gaya mani."

Adel fa ta kasa yarda da abin da kunnuwanta ke gaya mata. Methu yana da rai! Na farko kenan fiye da sati shida, sai farinciki yazo mata tayi murmushi. "Methu yana da rai" "ta tambaya domin ta tabbatar ko taji daidai". Kwarai kuwa, yana nan araye. Ko zakiso rubuta masa yar wasika?" Nahor ya tambaye ta.

Nan da nan tunanin rubuta wa Methu ya shiga ran Adel. Tasha tunanin yaya za ayi a sadu can baya! Amma ta sani

akwai al'amura da yawa na damuwa. "kwarai ina kaunar rubutawa Methu, Amma akwai abinda ya kamata na fara yi. Yi sauri! bani alkalami da takarda".

Adel ta zauna ta dukufa ga rubuta sunayen dukan kamammu, tana cikin rubutawa sai taga kwamanda ya shigo. "maza, tafi da wannan, Nahor. kuma idan ka yarda k ayi sannu sannu!" Adel ta rungumi Nahor rungumar ban kwana, sai ta bace daga wurin, tana bacin rai da yake bata iya ta rubuta wasika zuwa Methu ba. Inama da ta sami damar gaya masa dukan abubuwan da suka faru....tana kaunarsa kuma tana jin rashin sa kusa gareta.....ga kuma rashin lokaci ya hana, kuma sai ya zama wajibi ta aika da sunayen wadanda ke tsare. Ko shakka babu, suma iyalansu na cikin damuwa. Yanzu fatanta shine ya zamana babu wanda ya ganta tana magana da Nahor.

"Me kike rubutawa?" Kwamanda yazo cewa ba ma magana kadai Adel tayi da mai jirgin ruwan ba amma har ta bashi wata guntuwar takarda "me kika rubuta?" kalmomin sa suna fitowa da irin murya ta mai fushi ainun yana rike da wuka kasa da wuyan Adel.

Da tsayayyar murya kuwa, Adel ta gaya masa, "Abin da nayi kawai shine na rubuta sunayen mutanen da kake rike da su a zaman fursuna anan."

"Me kika yi?" kwamanda yana tafasa. Adel fa anan sai tayi tunanin mutumin nan zai soka mata wukar da ke hannunsa a wuya, amma na farko kenan da tsoro ya kau mata. Ta gama aikata abin da ta gasganta ya kamata tayi shi, kuma ta sani cewa Methu yana da rai. Yau kyakkyawar rana ce, ranar da ko mugun kwamandan nan ba zai iya bata mata ita ba. Yanzu na tabbatar wa tawagar gwamnati cewa babu wanda aka tsare anan dakin yarjejeniya. Yanzu kuma gashi kin basu sunayen fursunoni! Ke alade kawai! Zaki biya da jibi"

Kwamanda kuwa sai da ya cika wannan buri nasa. Aka yi wa Adel dukan kawo-wuka da rana a rannan da kuma wasu ranaku da suka biyo baya.

Kasa da watanni biyu daga wannan ranar aka sake zuwa binciken kauyen Salubi. An rabarda jimilar sunayen da Adel ta aika ofisoshin gwamnati da kuma Iyalansu harda Methu. Labari ya iso ga Adel cewa, Methu na tafe tare da tawagar gwamnati domin ya dauke ta tare da Christina".

Adel tana murna. da ita da diyarta sun haye munanan halaye da ba a iya misalinsu, gashi kuma yanzu zasu tafi gida?" Amma Christina tana tambaya cikin shakku. "Zamu sami damar tafiya da Baba. "kakakenan idan basu yarda mu tafiba?" Adel ta lura da irin damuwar da ke cikin muruar Christina kuma ta sani cewa tambayo yin da tayi suna da tushe. Sai ta rungumi diyarta mai karfin zuciya tana tunanin ko wace irin dabara zasu yi su hana a sake su. Washe gari kuwa sai ta gano.

## "BA ZAN IYA TAFIYA TARE DA KAI BA"

Aka sa Adel da Christina suka tsaya a gaban taron kamammu da aka tara. Kwamanda ya shaida wa kristocin nan, yace, "Nan ba da jimawa ba zamu dauki Christina da Adel zuwa Dahma domin ta sadu da mijinta Krista". Labarin zuwan Methu ya rigaya ya bazu a ko ina da sa rai da gaske a tsakanin kamammu. Sun san Adel. Idan aka yarda ta tafi, ba zata huta ba sam sam har sai taga kowa anan ya fita. Adel zata zama turbar su ta samun yanci.

Daganan sai kwamanda yaci gaba da irin barazanan nan tasa da suka saba gani: Za a tambayi Adel da Christina ko zasu so suci gaba da zama da ku anan ko kuma su barku su tafi tare da Methu. Idan kuwa daya daga cikinsu ta yarda ta tafi tare da Methu to zamu kashe sauranku duka." A yayinda yake fita kuwa, sai ya sunkuya a gaban wata yar yarinya da ba ta fi shekaru biyar ba, ya fito da wuka daga kubenta, ya danna a makogwaron yar yarinya da ke ta rawar jiki don tsoro kuma yace da yake mamugunci ne, "har ke".

Kristocin suka tsaya tsit suna zuba wa Adel idanu. Ta kaka zata yanke irin wannan shawara? Suna mamaki. Kuma suma suna tunanin idan da sune ke a matsayinta wace irin shawara zasu yanke.

Adel ta sani cewa babu wanda zai ba ta laifi ko Christina idan suka zabi su tafi tare da Methu. Amma kafin tace komai, kwamandan yace, "Mu tafi".

Yanzu? Adel ba ta da labarin cewa Methu ya rigaya ya iso kuma yana jiransu.

Dukan abubawa suna ta faruwa da sauri sauri. Tana bukatar lokaci domin tayi addua, kuma tayi shawara ko kwamandan zai kashe su duka da gaske ne ko kuwa barazana ce kawai. Ta kaka kuwa zata juya wa Methu baya?

Amma kuma ta kaka zata zabi shawarar da zai iya kawo mutuwar sauran kamammu?

Kafin ta farga, sai gashi ana raka ta zuwa dakin da Methu yake zaune tare da hafsoshin sojoji. Suna shiga kenan sai kwamanda ya rada mata a kunne, yace "ki tuna idan wata cikinku ta yarda ta bishi, zan kashe sauran duka ba su kadai ba, Methu ma kashe shi zanyi, na rantse, zan kashe shi shima. Mugayen kalmomin nan nasa suka kashe mata jiki, ya fitar da duk wata shakka da nake yi wai ko barazana yakeyi. Adel tana iya ganin ukubar da ke cikin idanun Methu. Wanda yana marmarin ya koma gida tare da matarsa da diyarsa! Watanni uku a gareshi, yayi tsawo, amma yanzu kama kwai bege. Kuma a dage yake kuma Adel ta sani cewa ya rigaya ya kudurta a ransa bazai koma ba sai tare da su. Dukan abinyi shine addu'a domin samun karfi.

Wani hafsa ya gabatar da kansa wai shi Mallam Said, kuma ba tare da bata lokaci ba ya tambaya, Adel, kina so ki tafi tare da Methu, ko zaki "cigaba da zama a Salubi?" Adel tasan cewa za a yi mata wannan tambaya, kalma na bin kalma. An rigaya an umurce ta ga yadda zata ba da amsar. Ta yi kokari ta yi magana, amma lebunan ta sukayi motsi ba tare da muryar ta ta fito ba. Mallam Said ya maimaita tambayar da daga murya. "Adel, kina so ki tafi tare da Methu ko zaki ci gaba da zama a Salubi?"

Adel ta kalli Methu, wanda yanzu ya fara yin mamakin abin yana daukar dogon lokaci kafin ta amsa.

"Methu...." Hawaye na zuba a fuskarta a yayin da ta rasa sanin me zata ce. "Bazan iya tafiya tare da kai ba".

Methu fa a shirye yake yayi tsalle daga kan kujerar sa, ya gudu wajen Adel ya tambaye ta dalili, amma sai ya dakatar dashi, ya hana shi yayi magana. Nandanan kuwa Said yayi wat Christina wannan tambayar. Adel kuwa tana ta kuka a yayin da ta ke kallon diyarta, da yake ba ta da tabbacin irin amsar da zata bayar bata sami damar tattaunawa da diyarta ba game da wannan, shi yasa Adel take tsoron cewa yanzu kam zasu kashe dukan kamammun harda Methu kenan, idan har daya daga cikinsu ta yarda ta tafi tare da Methu. Amma ta kaka ma diyarta yar shekaru tara zata iya rabuwa da uwarta tabi ubanta?

"Baba, ba zan iya in tafi tare da kai 'ba. Kayi hakuri....." Christina tayi ta kuka, tana faman kokarin baiwa ubanta hakuri da kuma bayanin matsayinsu.

Mallam Said ya katse magana ta hanyar rashin da'a, "Gashi. mun gama. Ba zamu kara sauraron wata magana game da wannan ba. An gane?"

Aka baiwa Adel da Christina minti biyar kacal tare da Methu karkashin kulawa da umarnin cewa su gaisa amma ban da yi wa juna rada. Adel ta kyale wannan dokar taci gaba da magana a hankali tana adduar kada suji ta. "Methu ya zama dole ne na amsa haka din. Suna barazanar kashe sauran idan muka bi ka. Idan ka yarda kada kayi bacin rai dani. Idan dai ina raye to bazan taba fitar-da-raiba. Na sani wata rana, zamu sake wanzuwa."

Methu ya dubi kyakkyawar matarsa, yana ganin azabar da ke idanunta kuma yana sha'awar karfin halinta. Babu sauran abin fadi. Said ya fara magana, "Na rigaya na yanke shawarar abin da zanyi da ke. Kin jawo mani damuwa masu yawa, kuma ke tabbas mai rikici ce. Na yanke shawarar cewa daya daga cikin mutane na zai aure ki. Watakila zai iya yin iko da ke."

Adel bata iya gaskanta wannan ba. "Bazan iya auren kowa ba! Na rigaya nayi aure da Methu!"

"Na gaya maki. Methu ba namiji bane. Alade ne shi, kuma ban amince da wannan auren ba. Idan kika ki auren mutumin da na zabo maki, zansa dukansu suyi amfani da ke." Kwamanda kuwa ya nu na cewa ba zai saurari wata jayayya ba kuma. Adel kuwa ta gane da haka ta wurin duban fushkarsa da ke turnike. Babu wata hanyar kaucewa. Adel ta tafi wajen sauran mata kamammu ta roke su su taimake ta, ta sani da wuya su iya yin wani abu amma akalla zasu iya goyon bayanta na yin kiyayya da sa auren dole. Amma basu tabuka kome ba suka yi gum, suna tsoron nasu rayuwar. A karshe daya ta ce mata, "Idan ba ki auri daya daga cikinsu ba suna iya yi mana fyade kuma su kashe mu duka".

Hankalin Adel ya tashi. Tayi iya kokarinta ta tsaya ga taimakawa matannan amma gashi yanzu tana ji kamar an ci amanar ta. Sai ta fara kuka, "Ta kaka zaku maisheni tamfar wata hajja a sayar da ni kawai domin ku ceci kanku?"

Sauran matan kuwa suka bata hakuri suna rike da juna suna kuka. Sun sani wannan ba zai zama na karshe da za a aurar da wata acikinsu ba.

A lokacin da aka tilasta mata ta tare a gidan Almin mijinta tare da Christina, Adel ta dauka al'amarin ba zaifi haka muni ba. Amma al'amarin ya fa kara yin muni. Bayan yan watanni sai Adel ta dauki ciki.

## SABUWAR RAYUWA

A watan Oktoba matsayin sosuwar rai na Adel yayi kasa ainun. Ji take matuka cike da hajijiya. Wadannan dabbobi sun kashe mata da da uwa kuma sun sha yi mata duka fiye da sau a kirga. Yanzu ma ta fara gaskanta cewa sun dauke matasa rai da takeyi na sake saduwa da Methu. Wannan kiyayya da ta fara a wannan bakar rana da aka kamata yana habaka da sauri fiye da sabuwar rayuwa da ke cikinta. Tayi ta kuka a yayinda take neman mafita amma jariri da ke cikinta fa, ga Adel kam, tuni ne kawai na abin da suka dauke daga gareta.

"Ba zan kara barin su dauke kome daga gareni kuma ba," ta yanke shawara.

Sai ta jira zuwa lokacin da taga ita kadai ce. Sai ta dauki wuka a cikin kicin. Yana da wuya a gaskanta cewa abubuwa sun tabarbare haka, Adel tana tambaya ko me yasa ta rayu zuwa yanzu domin kawai ta zo ta shiga irin wannan fid-da-tsammani. Ta sani Allah ne ya ceceta, amma ba ta da sauran sha'awar rayuwa. A hankali kuwa ta sa wukar a ruwan cikinta, ta rufe idanunta tayi addu'a ga Allah ya gafarta mata.

"Iya ki tsaya!" Christina tayi ihu a yayin da ta taho a guj'e ta cabki wukar daga hannun uwarta. Adel kuwa sai ta fashe da kuka ta fada kan dabe. Christina ma tana kuka kusa da uwar. "Iya, me kike yi? Bai kamata kiyi wa kanki irin wannan ba. kuma wannan jaririn bai yi laifin kome ba.

Adel tayi kuka na dogon lokaci duk lokacin da kalmomin Christina suka zo mata a rai. Ta roki Allah ya gafarta mata a yayin da tayi ikirari game da kiyayyar da take dashi ga masu tsare su.

Sai ta fara fahimtar yadda ya rage kadan fushinta ya kashe rai da baiyi laifin kome ba, kamar dai yadda mayakan jihadi suka yi mata. Ko da shike ba ta kaunar ta gafartawa wadanda suka azabatar da ita nan da nan, ta sani dole ne ta yi na'am ta bari alherin Allah ya yi aiki. Kiyayar da take dashi shi ya hana kaunar Allah na ikon warkaswa wanda yanzu ta fara ji. Sai Adel ta fara shafa cikin ta tana magsana da junabiyun a zuci. Da sa rai cewa ya'mace zata haifa, sai tasa mata suna Sarah.

Sarah, ki gafarta mani. Ki gafarta zunubin uwarki. Bakiyi laifin kome ba. Ke ce abu maikyau da ke fitowa daga irin wannan mummunan matsayi, ina kaunar ki".

Duhu na yayewa a lokacin da taci gaba da yin addu'a kuma tana magana da Sarah. Adel ta dauki wannan diya da zata haifa a zaman magabaciya, don wanda ya kashe mata da. Amma yanzu ta gane jaririyar ta ce kuma daya daga cikin halittun Allah. Dayantaka ya tabbata a yayinda ta rungumi yayanta duka biyu.

Washe gari Adel ta dauki takarda, sanin cewa ya kamata ta rubutawa Methu. Lalle ne ta gaya masa dukan abubuwa da suke faruwa, kuma ta roke shi gafara. Ko da bazai kara daukarta a zaman matarsa kuma ba, ta gane, kuma ba zata bashi wani laifi ba. Tana kaunarsa kuma tana duba hanyar sake saduwarsu. A yayin da take rubutu sai hawayenta ya; zuba akan tawadar, ya kuma bata rubutun, ta na tunanin koma zai iya karanta wasikat.

A lokcin da ta gama shafi shida, ga Adel anann yana daya daga cikin abubuwa masu muhimmanci na wasikar nuna kauna da ta taba rubutawa. Sai ta nade wasikar a hankali ta boye, tana addu'ar samun damar aikawa Methu.

Ranar 24 ga watan Disamba, aka tilastawa dukkan kamammun su yi aiki a gonar kwakwa. Aiki ne mai wuya, musamman ga Adel, wadda take dauke da juna biyu mai tsawon watanni shida. Amma kuma kamammun sun lura da cewa ranace ta jajibirin kirsimeti, kuma kowa na tunanin dadin hutu da akan samu can baya. A wannan daren lokacin da Adel ta fara gungunin amon wakar da ake kira SILENT NIGHT saura kuwa suka dauka. Jim kadan kuwa aka fara waka a yayin da masu tsaro suke saurarensu cike da rashin yarda. Ko wannensu a sane yake da hatsarin yin wakokin kirsimeti game da Yesu. Mai yiyuwa ayi musu duka, amma da alamar babu wanda ya damu. Idan ma za'ayi musu horo to agaresu kam jin dadi da more yin wakar ta biyasu.

Da dare ma suka yi waka suka tuna da iyalansu. Jikinsu na tsare a fursuna, amma ruhun su na da yanci a yayin da suka ci gaba da wakokinsu. Washegari sukayi kuka, kukan bakinciki da na farinciki, suna makoki game da rashin yancinsu amma cike da begen farinciki zuwa gaba. Ba zasu taba mancewa da Kirsimetin da suka yi tare ba a cikin gonaki.

A ranar 18 ga watan Maris aka haifi Sarah.

Yanzu da yake jaririya ta iso, Christina ta ga lokaci yayi da zata gaya wa awarta, "Lallai ne kiyi kokarin tserewa, da ke da Sarah kawai. Lallaine ki tafi. Idan kuwa baki tafi ba to dukanmu zamu mutu anan".

"Ba zan iya barinki ba, Christina, bazan taba iya barinki ba", Adel ta tabbatarwa diyar ta.

"Iya, ki saurare ni. Dole ne kibar nan", tsayayyar yar shekara goman nan ta dage da roko. "Almin ba zai taba bari mu fita tare ba. Amma idan dake da Sarah kuka fita, zai zaci lallai zaku dawo. Lallai ne ki isa wajen baba. Shine zai zo ya dauke ni. Wannan ita ce kawai hanyar tserewar mu."

Adel ta san cewa diyarta ta fadi daidai, amma ba ta san yadda za ta sarrafa wannan shawara ba. Bata ma sani ba ko Methu zai karbe ta. Yanzu kuma ga Sarah. Adel da ba ta da karfin halin shirin tserewa da irin wadannan tambayoyi da ba a sami amsoshinsu ba.

Ananan kuwa sai amsar ta zo a watan Afrilu. Adel tayi ta daukar wasikar da tayi wa Methu fiye da tsawon wata shida, da fatar zata sami na aikawa. Watarana wasu yara sun ziyarci kauyen da rana tsaka, sai dama ta samu. Adel tasan daya daga cikin su, a hankali kuwa sai ta tafi inda suke wasa. Sai tayi maza ta baiwa yarinya da ta sani, ta kuma gaya mata ta tabbatar wasikar ta shiga hannun mijinta Methu. Yarinya ta karbi wasika.

Adel ta taka zuwa gida, tana addu'a wasikar zata isa ga Methu.... tana addu'a ya gafarta mata .... tana addu'ar fata cewa har yanzu yana kaunarta. Kuma a kullum Adel tana leke leke a cikin kauyen tana dokin ganin ko wannan yarinya zata dawo kauyen domin yin ziyara. Bayan yan kwanaki kuwa batun jira yakare.

"Ko kin ga Methu? kin bashi wasikata?" tana tambayar yarinyar da ta baiwa' wasika, "I, na baiwa Methu. kuma a lokacin da na bashi, shima ya bani wannan in kawo."

Adel ta yi mamaki a yayin da yarinya ta ba ta wasika. Methu yayi mata takarda kafin ma ya karbi nata. Daga ganin ambulo na wasikar ta gane cewa ya dade yana dauke da wannan wasikcar, kamar dai yadda nata ma ya dade.

Tayi shawarar karanta wasikar nan take amma sai ta janye shawarar.

Kaka kenan idan Methu ya ki ta? Kaka kenan idan ya rigaya ya sake yin wani aure? Tunanin Adel fa yayi zurfi a yayin da ta yi sauri ta koma gida, ta yaga ambulo. Sai gabanta ya fadi a yayin da idanunta suka fada kan kalmomin.

Adel, ko kin haifi ya'ya goma daga maza goma zaki ci ga ba da zama matata. Baki iya tunawa da abinda pastor ya gaya maki? Allah kadai ne zai iya rabamu daga ranan nan. Ina kaunar ki. Methu. Adel ta sami amsarta zata shirya hanyar tserewa.

## TSEREWA DA TSERARWA

Bayan wata biyu ranar 18 ga watan Yuni, Almin ya baiwa Adel izinin ziyartar wasu yan'uwa a wani tsibirl da ke makwabtaka da su. Bayan da ta rike Sarah sosai, Adel ta jawo Christina a yayin da take hawan karamin jirgin ruwan fito. Amma Almin ya jawo Christina baya. "Zata zauna anan".

Adel ta roki Almin ya bar Christina ta taho, amma yaki. "Bazan tafi ba idan Almin ya ki. Ya sani matarsa zata gudu idan Christina ta tafi tare da ita. Amma sai ta rungumi uwarta tayi mata rada a kunne, "Iya, kiyi mini alkawari cewa dake da Sarah zaku tafi wajen Baba ina rokonki. "Ni bani da damuwa". Adel ta rike Christina, tana mamaki wai ta kaka ma zata taba barin Christina ita kadai. Amma rokon da Christina keyi, yadda diyarta take da jarumtaka haka. Adel tayi mata sumba tace sai mun sadu. Ta sani wannan gani ne na karshe har sai dogon lokaci, ko ma watakila har abada.

Adel ta tsaya a jikin shingen jirgin, tana kallon Christina na nisanta daga gareta a yayin da jirgi ya fara tafiya. Ta rungumni Sarah ta fara kuka a yayin da take tambayar kanta ko wannan shawara da ta yanke haka ya dace. Ba ta da wata niyyar ziyartar wasu dangi. Za tayi maza ta tafi wajen Methu kafin Almin ya gane cewa tserewa ta yi. Sa'annan fa za a san yadda za a yi a dawo da Christina.

Sai da aka yi kwana bakwai kafin Adel ta isa inda Methu yake kuma Adel tana kaucewa saduwa da Methu har zuwa

wannan lokaci, tsoron cewa Almin zai san abin da take shiryawa. Ta zauna akan gado shiru rike da Sarah a bayan daki na masaukin baki tana jira cike da doki. Shin Methu zai bukace ni kuwa? Taci gaba da tambayar kanta, kuma yaya batun Sarah?

Ko da shike gashi Adel ta sami yanci, amma ji take kamar haryanzu a takure take. Mugun abin ma, ji take kamar ta zama maci amana. Ta sake yin aure kuma gashi ta baro diyarta a baya. Ta kaka ma Methu zai taba iya gafarta mata? Tayi ta bimbini tana tambayar kanta akan irin wannan shawara da ta dauka har barci ya dfauke ta.

Sai kwatsam Adel ta farka domin karar shigowar Methu a gidan ya tashe ta. Sai kuwa ta rungumi Sarah wacce take barci, kuma ta tashi tsaye. Da yake ta gamsar da kanta cewa tayi mummunan kuskure sai ta ba da kanta ga tunanin gudu daga gidan. Ba ta ma yi tunanin inda zata je ba, zata dai gudu kawai. Ba zata iya fuskantar Methu ba.

Amma kafin takai kofa. Methu ya shigo. Ba tare da ba ta lokaci ba sam sam ya shiga daki ya yi ta kuka na farinciki, yana rungume da matarsa. Sa'annan ya dubi kasa wajen jaririya da Adel ke rike da ita, sai yayi murmushi. To wannan ita ce sabuwar diyar tamu. "in jishi. Adel tana zubar da hawayeamma hawayen farinciki ne a yanzu kam tana nuna kaunar wannan ranar sake saduwa da aka dade ana dako. Adel tana son manne wa Methu har abada, domin ta more wa kusantakar su wanda ya zamar mata abin-jingina na kwarai a kewaye da ita. Amma ta sani lallai ne Methu ya tafi. Ta sani ba zata sami kwanciyar rai ba har sai ta jira a cikin tsima kwana daya bayan daya, amma bata ji kome daga Methu ko Christina ba. Kaka kenan idan har sun rigaya sun kashe Christina? Kaka kenan idan Methu ya rigaya ya muitu? Dukan wannan laifi na ne? tana ta kokarin kawar da wadannan tambayoyi daga zuciyarat ta wurin kai kukan ta ga Allah domin karin tabbaci.

Adel ta sami kwanciyar hankali a cikin ayoyin manganar Allah wanda ta rasa a lokacin da take a tsare na tsawon

watanni goma sha takwas.

Ta tuna yadda yan jihadi suka sassara mata Littafi Mai Tsarki a cikin jeji. Adel ta bude Filibbiyawa 4:13 kuma kamar dai yadda ta saba, sai ta karanta duka da murya mai karfi: ina iya yin dukan abubuwa ta wurin Kristi wanda yake karfafa ni." Ta tuna da ranar karshe da ta karanta wadannan kalmomi. A lokacin da suke kan dutse na bayan kauyen su a ranar farko ta kai musu hari. Abin kamar shekaru aru-aru ne suka wuce tun lokacin, kuma ta leka lahira ta dawo. Ta sani al'amuran fa basu kare ba tukuna, kuma ba zata iya daina yin tunani game da Kristina ba, tana ta juyayin cewa ashe kuwa bata ci amanar diyarta ba.

Sati biyu kenan da tafiyar Methu kafin Adel ta sami labarin cewa yana tare da Christina kuma zata je ta same su nan take. A karshe zasu sake haduwa a zaman iyali guda.

Hawaye na farinciki suka zubo mata a yayin da take wa Allah godiya cewa Methu ya ci narsaar cetar da Christina. Amma yanzu, tana tunani wane irin mataki Almin zai dauka na komawa da su can?

## JAWABI

A lokacin da muka yi hira da Adel, da ita da Methu suna karatu a wata makarantar koyon ilmin tauhidi wanda ba a ambaci sunansa ba, suna nazarin koyon zama masu bishara. Ko dashike anyi watanni da dama tun ranar tserewar ta, da Adel da iyalinta a kullum gudu suke daga wuri zuwa wuri domin su bace wa Almin, wanda, yake ta farautarsu ta wurin taimakon musulmi masu yawa da yasa su yin wannan. An kuskure kama Adel har sau biyu.

Akwai al'amura masu fa'ida guda biyu da Adel ta ke fuskanta bayan fitowarta. Na farko shine wani abu da a farko take tunanin ba zata taba iya yi ba a zamanta na Krista ta sani dole ne ta gafarta wa sojojin jihadi.

Sarrafa mafi wuya ta fara ne da daukar juna-biyu da tayi, a lokacin da Christina ta tunasheta cewa diyar da ke girma a cikin ckin ta ba ta yi laifin komai ba. Wannan jaririya Sarah bata da laifi. Adel ta sani tana iya fadar kalmomin "Na gafarta" amma fa akwai bukatar su fito daga zuciya, in da gafartawa ta gaske ke fitowa. A cikin watannin farko na tserewarta, Adel ta kan dauki lokaci domin yin addu'a, takanyi addu'a domin ceton wadanda suka ji mata ciwo da kuma iyalin ta. Ta bada gaskiya wannan addu'a shine mabudi zuwa ga iya gafarta musu a ckin zuciya.

Al'amari na biyu ma yana cike da kalubale. Lallai ne Adel ta gafartawa kanta. Domin auren dole da Almin, galibi takan maida kanta cewa ita maci amana ce. Alhali ma wasu Krista sun tabbatar da wannan hali nata na baiwa-kanta-laifi, kuma irin wannan tunani ya zamam mata tamfar wata annoba a lamirin ta, yin haka kuwa ya jawo mata damuwa sosai, musamman a lokacin tserewarta. A wasu lokuta tana gaskanta cewa Methu da sauran abokai Krista zasu juya mata baya domin wannan auren dolen. Wasu lokuta irin wannan hargitsi na birnin rai ya fi wuyar sarrafuwa idan aka kwatanta da a zabar da jiki da ya jure.

Lokacin da Adel ta fito daga fursuna, akwai wani iyali masu aikin mishan wadanda ke abokai ne ga Methu kuma wadanda suka yi aiki tukuru a kasar da ma kasashen waje domin taimakon irin halin da ta shiga. Su suka karbe ta kuma suka yi tattaunawar kwantar da hankali na karfafa al'kiblar ta.

A lokacin da Adel ta fuskanci mijinta, Ubangiji ya hamzartarda lamirinsa, kuma kalmomin farko da suka fito daga bakinsa sune, "Adel, ke ba maci amana bace." Dajin haka, sai Adel ta fashe da kuka, kuma daga wannan ranar ne ta fara gafartawa kanta.

Adel da Methu sunci gaba da yin aiki wajen samun shika na wadanda aka tsare su tare. A kullum tana jin nauyi a ranta cewa har yanzu akwai wasu da aka ambaci' sunayensu a wadannan shafuka da har yanzu suke tsare.

Tana neman addu'oin mu.

# *Purnima:*

## Diya Da Aka Sa A Cikin Kaso, Amma Ruhunta Yantacce Ne.

*Bhutan:*
*Daya Ga Watan Maris, 1993*

Dare na karatowa ga kuma sanyin hunturu a lokacin da yan sanda suka sake zagayowa domin yi wa wani taron masu bi kofar rago a kwashe su a kaisu ofishin kantoman yankin. Purnima yar shekaru gomasha uku kuwa ta kadu tana rawar sanyi domin an tilasta mata tare da wasu cewa su tsaya a tsaye a cikin filin gidan a yayin da ake tayi musu tambayoyi. Hafsoshin sukayita damunsu da tambayoyi iri guda a kullum. “Menene yasa kuke so ku zama Krista?” “Daga ina ake aiko maku da taimako?” Wannan kasa ce ta bhudanci, kuna ka da mutuncin mu, ta wurin yin na'am da bakon addini daga waje. Me ya sa kuke so ku juya fushin jama'ar ku gaba da ku?”

Daya bayan daya aka yiwa masu bin nan guda 35 tambayoyi cikin tsawon dare mai sanyin gaske. Hafsoshin guda ashirin ne, yawancin su kuwa kattaine masu bada tsoro. Purnima kuwa ta tukura a yayin da wani hafsa ya yi wa wani dan'uwa Krista mari a kusa da ita. Wasu da ke cikin kungiyar sun yi kuka, wasu kuwa suka yi kokarin yin bishara. Yar yarinya Purnima kuwa ta tsaya a gaban kattan nan yar mitsila da ita tana addu'ar samun karfin halin fuskantar wadannan tambayoyi.

"Wanene ya baki izini kiyi bukin kirsimeti a cikin kauyen Purtah? Nan fa kasar Bhutan ne. ba ku da izinin yin bukin kirsimeti a kasar ki dawo addinin Bhudanci, ko kuma ki bar Bhutan." A yanzu fa wannan hafsa yana fuskantar Purnima ne a sarari, kuma taji wannan zabi da ya bata ya shige ta sosai. Kuma kuna bauta wa wani addini dabam. Me wannan zai zama?"

Ko kadan Purnima ba tayi shakkar cewa shi wannan hafsa da gaske yake ba. Agaresu wannan batu ne na mutunic cewar ko su sami kristocin nan su dawo garesu ko kuma su yi shaidarsu a fili cewa masu cin amana ne kuma a tilasta musu subar kasar. An rigaya an kore ta daga gidansu da ma kauyensu. Ba ta ma san ina zata nufa ba, amma kuma tasan abin da yakamata tayi.

"Ba zanyi musun Kristi ba! Kuma bana so na bar kasa ta, kuma bazan bar Kristi ba. Shine kadai ke iya cetona-ko kai." Purnima fa sai taji jikinta yana rawa a yayin da take yiwa wannan hafsa mai jan fuska magana cikin kangara, amma a zuci kuwa tsayayya ce, a wannan lokacin kuwa sai ta gane cewa nata ya same ta. Da ita da sauran kuwa aka basu kwanaki biyar kacal da su kwashe nasu ya nasu. Aka gaya musu su tafi kasar Nepal.

Kwana biyar. Purnima tana da sauran kasa da kwana bakwai ta rabu da irin rayuwa kadai da ta sani. Wannan labarin barazanar da hafsa ya yi ya bazu a cikin kauyen, yarta da mijin yarta kuwa sun rigaya sun tashi, da yake suna tsoron a taba rayuwarsu. Yanzu da yake an ngaya an maida kristoci masu cin amana ne, wasu daga cikin kauyawan masu fada aji suka yi amfani da wannan dama domin kai musu hari.

Kafin Purnima ta tafi, akwai abu guda daya da ya wajaba ta yi. Tana da bukatar ganin uwarta. Fiye da shekara guda kenan tun lokacinda iyayen ta suka kore ta daga gida. Yanzu kuma gashi ta sami kanta tana lalaba dawowa da tabbacin cewa sun rigaya sun sami labarin lallaine zata bar kasar, tayi addu'ar fatar iyayenta zasu yarda su ga yar yarinyarsu gani

na karshe. A karkashin duhun dare kuwa Purnima ta koma gidansu inda ta girma, gidan da aka tilasta mata ta bari tun tana yar shekaru goma sha biyu kacal.

## WARKASWA TA AL'AJIBI

Purnima ta girma ne a wani kauyen Bhudda da yake cikin gabashin Bhutan mai tuddai kuma cike da ni'imar ciyayi da itatuwa. Mahaifin ta shine bokan kauyen kuma shine yakan shugabanci al'adunsu na yin tsafi da kuma yankan dabbobi domin korar mugu ko mugunta da ke barazanar yiwa jama'arsu barna. Awannan iyali akwai mutane takwas amma bisa ga matsayin rayuwa na wannan kauyen ba za a ce dasu masu arziki neba amma kuma ba matalauta ba, amma suna da babban gida kuma akwai kusanci da juna. Sival, wanda yake auren yayar Purnima Maya ma tana zaune tare da su. Ita Prunima watakila da tayi girmanta na rayuwa kamar kowa a kauyen da ita Maya mai laulayi bata sami warkaswa na ban al'ajabi ba.

Purnima tasha zubawa ubanta idanu har na tsawon shekaru uku yana ta tsafi da kaji akai akai akan wata matsafarsa da yashrya, ana kada ganga da suka dana suna kiran rohanai wai su zo su warkar da diyarsa. Daga baya sai Purnima taje ta zauna a bakin gadon yayarta tana jira yayarta ta sami sauki, amma ina Maya bata samun sauki. Takanji dama dama a wasu ranaku wasu kuma ba haka ba, amma zafin ciwo mara saurarawa na ciki da kuma tsananin ciwon kai shi ke sawa akullum tana kan gado wataran ma na tsawon kwanaki. Ganin yadda yayar ta take foma, Purnima ta tambayi uwarta, "Me yasa rohanan suke hauka haka? Me yasa hadayun nan na tsafi basa aiki?" Amma ba a taba bata amsar wannan ba.

Yanzu kuwa, bayan shekaru masu yawa na rashin lafiya, Maya ta mike. Babu sauran ciwo.... babu sauran karar ciwon kai. Iyayen Purnima suna farinciki diyarsu ta sami sauki, amma fa basa yin farinciki da wannan sabuwar magana ta Maya cewa Yesu ne ya warkar da ita.

"Ta kaka zaki fadi irin wannan? Ta kaka zaki kawo irin wannan rashin mutunci a cikin gidan mu masu addinin Bhudanci, kuma bazan kara sauraron batun wani bakon allah daga wata kasa ba. Kin gane? Ban da wata magana kuma!" Ya fusata ainun. Fiye da haka yana tsoron abinda mutenen kauyen zasu zata idan suka sami labari. Alhali ma dai, shi kansa yana tsoron abin da zai faru da rayuwarsa.

Amma Maya da Sival basu yarda suyi musun wannan sabuwar bangaskiya tasu ba. a lokacinda daya daga cikin abokanan Sival ya sami labarin rashin lafiyar Maya, sai yayi ikirarin cewa shi fa Krista ne a boye, kuma ya baiwa Sival Littafi Mai Tsarki, kuma ya gayawa Sival cewa shi yana bada gaskiya Yesu zai iya warkarda Maya. Kuma ya warkar da ita. Bayan haka kuwa sai bangaskiyarsu ta habaka dasauri a yayinda suke cin gaba da karanta sabon Littafinsu Mai Tsarki tare.

"Idan har kun nace da kuci gaba da zama Krista, ba zai yiwu kuci gaba da zama anan ba". Mahaifin Purnima ya shaida wa Maya da Sival a wannan dare na karshe. "Mutanen kauyen ba zasu taba yarda ba. Muma korar mu za ayi, kuma wannan sabon addini naku zai kawo zubar da mutunci da balai ga dukan iyali."

Purnima ba ta ji dadin korar da aka yiwa yayarta da mijinta ba daga gidan nasu. Amma ko da shike ita yar shekaru goma ne kewai ta gane sarai cewa abin da ubanta yake fadi gaskiyoya ya ne ta sani mutanen kauyen ba zasu taba yard da wani sabon addini ba amma duk da haka ita kam ba zata iya jure wa ba illa ko da asirce ne dole ta yi al'ajibin warkewar Maya da kuma fasalin fuskarta da ya kara haske a lokacin da Maya take tattara nata ya nata domin fita daga gidan da shi kawai ta sani duk rayuwarta, karin gishiri kan gyambo ma dai Maya tana da juna-biyu na tsawon wata shida.

Bayan da suka tafi, sai gidan ya zama kamar anyi mutuwa. Uwar Purnima ta yi bakinciki, ubanta kuwa cike yake da gigita game da wannan abinda ya faru da iyalinsa.

Purnima taso tayi wa uwarta magana game da Maya, amma ba a ma yarda kowa ya ambaci sunanta ba. Kuma ba a yarda kowa ya ziyarce ta ba acan inda suke hijira, wani dan karamin bukkar gwangwala a kusa da wani kauye da ke makwabtaka da su.

Amma a lokacin da Purnima ta sami labari cewa Maya ta haifi da namiji, bata iya kara yin hakuri kuma ba. Tayi mamaki cewa yar'uwarta ta haifi yaro lafiyayye, kuma har yanzu ta kasa kawar da halin tambayoyi karfafa da suke yamutsa mata tunani: Wane irin Allah ne zai warkar da wani ba tare da ya nemi lada ba? Menene Sival da Maya suka samu a wannan addini da ya basu karfin kalin dagewa gaba da iyalinsu kai harma da jama'arsu-har zuwa ga matsayin korarsu daga gidansu?

Wadannan tambayoyi sunsa Purnima ta saci jiki zuwa wajen yar'uwarta domin yin ziyara mai hadari ta farko. Ta yanka ta gonaki tana bin cikin itatuwa domin kada a ganta, nan da nan kuwa ta kawo ga yar ta da suka rabu makonni da dama. Ayayinda Maya ta bude kofar dan bukkar ta mai ban tausayi taga Purnima na rawan jiki a kofar, fuskarta na jin ko tayi laifine ya sauya sai hawaye ke zuba tana rungumar kanwarta.

Purnima kuwa sai ta fara satar jiki tana ziyartar Maya. Ba ta jimawa, wani lokaci ma minti goma sha biyar kawai take yi. Amma a kowace ziyarar, Maya takan karantawa Purnime labari daga Littafi Mai Tsarki, kuma takan saurara a natse, tana rike dukan abin da taji. Labarin Musa shi yafi bata sha'awa. Ba kadai ta wurin irin iko da Allah ya aikata ta wurin yin amfani da shi ba, amma tawurin batun da Allah ya gaya masa ya bar gidansa zuwa maser kuma ya zama baki mai shelar maganar Allah, ko da shike yana dai na. Idan da zata zama Krista, to tafiso ta zama kamar Musa.

Shekara na biye kume Maya ta sake haifuwar ya', sunanta Esther yawan ziyarar Purnima kuwa sai karuwa yake yi. Ga ita Purnima kuwa satar jiki zuwa gun Maya da ya'yanta-ya zama wani kuru da take marmarin yi tabi ta turba zuwa

kauyen. A tunaninta idan ma aka kamata, ba za ta sami wata matsala kwarai ba, da yake ita karamar yarinya ce.

Amma fa ita uwar Purnima ba ta yiwa al'amarin kallon haka. "Purnima, dukanmu biyu munsan abin da kike yi", ta shaida mata haka watarana. "Na fa rigaya na rasa diyata guda, bana so na rasa wata kuma. Kin gane?" Purnima ta kada kai akan cewa ta gane, a yayinda uwar taci gaba da bayani cewa addinin Krista addinin kasashen waje ne kuma addinine na talakawa futuk. Bai dace da kauyen mu ko kamar mu ba. Sival da abokinsa ne suka yaudari Maya," in ji uwarta.

## JAYAYYA BARO-BARO ZUWA GA ALLAH

Amma Purnima tana jin dadin lokaci da suke kashewa tare da yar ta, saboda haka sai wannan ziyare ta boye ta ci gaba. A ranar Kirsimeti, sai Maya da Sival suka baiwa Purnima dama tazo wajen dan taron da suka fara tun watanni 18 da suka shige. Ziyarce ziyarcc masu yawa zuwa wurin yar' uwanta ya shuka iri na bangaskiya a zuciyar Purnima, kuma ta saurari wa'azin da aka yi game da haifuwar Kristi-yadda aka haifeshi ta wurin budurwa domin ya kawo ceto-sai taji ita kanta jayayya ce ga tayi kira ga Allah a cikin zuciyar ta.

Tayi kwanaki tana rike da shawarar ta da ta yanke na karbar Kristi ba tare da ta gaya wa kowa ba, sai da ta sake satar-jiki ta tafi wajen Maya ta shaida mata cewar tana bukatar ayi mata baptisma. Maya ta yi farinciki da wannan shawarar da kanwarta ta yanke, amma a cikin ranta kuwa ta damu game da yadda Purnima zata iya isar da wannan labari ga iyayensu. Bayan sati uku, a ranar wani lahadi da safe aka yi wa Purnima baptisma. Ta fito daga cikin ruwa cike da tabbatar bangaskiyar ta. "Maya, yanzu kam nasan abinda ya kamata na yi. Dole ne na gaya wa iya da baba labarin, bazan iya kara boyewa ba. Ina so kowa ya sani cewa yanzu kam rayuwa ta ta Kristi ce-kuma ban damu da abin da zasu fada ko yi ba!"

"Amma kuwa Purnima, kin yi kankanta; ke yar shekaru gomashabiyu ce kawai, kuma kin san abin da zasu yi. Kin tabbata a shirye kike domin haka? Ni ina da Sival tare dani, shi yasa barin gida yafi mani sauki. Watakila ya kamata ki dan saurara gaya musu labarin kuma kici gaba da yin addu'a."

Purnima fa bata yi hakuri ba. "Bazan iya yin haka ba, Maya. Yanzu na fahimci dukan abubuwan da nake ji, dukan abubuwan da kika gaya mani daga cikin Littafi Mai Tsarki: Ban taba jin yadda nake ji yanzu ba can baya, kuma na sani wannan zahiri ne, kamar yadda kika fada. Ta kaka zan iya boye haka can cikina ba tare da gayawa iya da baba ba? Bayan haka ma, ai ina da ke..."

Jikin Maya fa yayi sanyi da jin wadannan kalmomi, sai ta rungumi kanwarta. Lallai kuwa ina nan dominki a kullum. Ko kinaso mu tafi tare?" "A'a" inji Purnima. Zuwanki kusa da kauyen yana da hatsari. Kada ki damu. Babu abin da zai same ni."

Maya ta zuba ido tana juyayi a yayinda kanwarta ta ruga a guje ta nufi hanyar gida. Tana mamakin irin wannan rashin tsoro na kanwarta kuma.

Ko da shike tana tsoron abinda iyayen zasu yi, tana yin alfahari ainun game da Purnima domin karfin zuciyarta. Watakila Ubangiji yana da wani shiri na musamman dominta, tayi murmushi.

A cikin halin yarinta ta yar shekaru goma sha biyu, Purnima ta shigo gida kenan sai kawai ta yi barin-baki, "Iya, na zama Krista. "Uwarta ta tsaya cak da jin haka.

"Na tabbata wasa kike yi", ta fadi tare da faduwar gaba. "shekarunki basu kai na ki zama Krista ba, kuma bayan haka, na gaya maki cewa nifa bazen yarda na sake rasa wata diya ta ba."

Amma fa Purnima ta kara tabbatarda wannan shawara da ta yanke. "Iya ni bana so na tashi na tafi kamar yadda Maya tayi ina so in zauna anan. Amma na rigaya na yanke shawara na zama Krista, kuma ba bu abin da zai sauya mani ra'ayi."

An tilasta mata ta tashi a wannan daren. A yayin da ta kama hanyarta da ta saba bi zuwa gidan Maya da yan komatsanta, sai taji uwarta tana kuka. Ta sani uwarta tana kaunar su duka biyu, amma iyayen na tsoron abin da mutanen kauyen zasu yi musu.

A can baya, Purnima takanji tsoro, amma a yayin da take tafiya a cikin duhu, ta yanke shawara ba zata kara jin tsoro ba.

Tayi zaman ta tare da Maya da Sival tun daganan, takan jin dadin zamanta da su, rayuwa a gurin a matse yake, saidai suna ta gwagwarmayar su ta yau da kullum na rayuwa. Sa'annan fa aka fara kame kamen kristoci a ranar Kirsimeti ta 1992, dai dai shekara guda kenan da Purnima ta tuba ga Kristi.

Yan sandan kauyen sun fara nuna damuwa game da yadda yawan kristoci na karuwa a wannan yankin, saboda haka sun dau wata aniya akan masu bi. Kristoci sun yi jimirin kira da ake yi musu kuma a tuhume su har sau goma a cikin yan makonni kalilan, kuma a kowane karo sukanyi kokarin rinjayar su ko kuma su tursasa masu suyi musun Kristi su dawo ga tashansu na Bhudanci. An sha marin su ko ma dukansu; an rike wasu ma har kwanaki bakwai ko fiye a wani babban wuri da ake tsare mutane, inda ake yi musu duka sosai. Mata kuwa da aka tsare ana wulakanta su ana dora musu laifin karuwanci.

Domin haka kuwa wasu mambobi daga kungiyarta suka yarda suka yi musun Kristi, amma ina Purnima kuwa sai kara kafiya take yi.

Yanzu ga Purnima, yarta Maya da mijin Maya, Sival, da abokansu na makwabtan kauyuka wadanda sukan yi sujada tare lokaci na sabon umarni daga hukuma zuwa garesu mai sauki ne amma da tabin zuciya; "ku bar Bhutan".

## "KAKA AKAYI KIKE DA IRIN WANNAN KARFIN HALI?"

Garin ratsawa ta gonaki, Purnima ta hangi hasken fitilu da ke haskakawa ta tagogin gidansu inda ta tashi.

Tana ta juyayin me zata gaya wa uwarta, tana tunanin wai shin ko uwarta zata barta ta shiga gidan. Ba suyi magana koma ganin juna ba tun daren da aka kore ta. Yanzu, da yake an tilasta mata ta bar Bhutan, tana jin ko zai yiwu ta sake ganin nwarta kuwa.

A yayinda ta kusanci kofar gidan, sai tayi shawarar ta shiga kawai". Iya iya nice." "Purnima!" uwarta ta rungume ta" idan kin yarda ki gaya mani cewa kin dawo gida da zama. Gaya mani cewa ke ba krista kuma ba. Purnima tayi shiru na gajeren lokaci. Ta tuna da cewa uwarta tana cikin bakinciki, hawaye sun fara zuba, bata so ta kara wa uwarta karin bakinciki, amma kuma dole ne ta sanar da ita, "iya, zan bar Bhutan, yan sanda basu yarda in zauna anan ba. Kiyi hakuri."

Uwar ta dubi karamar diyarta tana kishin irin wannan karfin zuciya nata. Amma gashi ita karamar yarinya ce bata san kome ba. "Purnima, baki ma kai shekaru gomasha hudu ba. Yaya kike da irin wannan karfin zuciya? Ta kaka zaki bar kasarki gaba daya?"

"Ba kin kasar nayi ba, iya," tana sharbe." Kasata ce ta kini." Ta san irin kaunar da uwarta takeyi mata, kuma ta sani uwar bata taba sha'awar tilasta mata barin gidan ba. Amma kowa cike yake da tsoro. Tsoron Krista, tsoron Kirsimeti, tsoron Kristi.

"Purnima tana mamakin ko menene yake basu tsoro? "Gashi: Karbiwannan," baban Purnima ya bata wani dan karamin kunshin kudi. Amma fa kiyi lura kwarai. Ya dubi fuskar diyarsa da ke zubar da hawaye, ya rungume ta kuma yayi maza ya bar dakin. Purnima ta dan kara tsayawa da uwar na karin yan mintuna, tana kokarin haddace dukan fannonin fuskar ta, muryarta, yadda idanunta sukan haskaka duk lokacin da tayi murmushi. Uwarta kyakkyawa ce, kuma bata san yaushe, ko kuma, idan zasu taba sake saduwa. Suka sake sumba sai Purnima tayi waje fita ta karshe.washe gari sai ta hadu da wasu Kirista da sukanyi sujada tare, wadanda aka tilasta musu su bar Bhutan. Gwamnati ta basu mota ta daukesu daga kauyen na Purtah zuwa iyakarsu da India. Daga can kuma suyi ta kansu.

"Wa zai zama shugabanmu" suna yiwa juna wasa, domin kokarin hutar da zukatansu. Babu daya cikinsu da ya taba fita daga yankinsu. Kuma babu daya cikinsu da yake da wata masaniya game da inda suka nufa.

Bayan da motar safa ta wuce iyaka kadan sai ta tsaya sai yan hijirar nan guda tara suka sauka. Suna kallon motar tana zubar da hayaki ta salansa a yayin da ta juya tayi tafiyarta. Ganinsu na karshe kenan na Bhutan, yanzu kuma gashi ta tafi. Gaya musu akayi wai kawai suyi ta takawa da kafa su ratsa duwatsun India zuwa cikin karar Nepal.

## MAFARKAI MASU TSORATARWA

Kristocin nan sukayi tafiyar kwanaki uku da kafafunsu ba tare da wata damuwa ba amma fa sai kara gajiya suke domin hawa da sauka kan duwatsu. Da suka isa karkashin wani jibgegen itace a gefen hanya wanda babu irinsa kusa, John wanda ya zama kamar shine jagoransu, ya bada shawara su kafa sansaninsu a nan karkashin itacen domin hutawa na kwana daya ko fiye da haka domin su dawo da karfinsu. Babu bukatar wani sauri, amma kuwa tabbatar halin shiga kaka nikayi ya fara bullo kai, Purnima kuma tana kara jin tsorata, ba ta son saura su sani, amma a kullum ta kanyi kuka idan taje kwanciya, kuma tun da tabar kauyensu tana yin mafarkai akan uwarta wannan yaren ma ba zaisha bam bam ba:

Ki tsayar dasu!" Amma babu amfani, uwar ta ta zauna shiru akan kujerarta kamar babu abin dake faruwa.

Takwas ga watan Maris, ranar haifuwar Purnima. Purnima ta matsa wajen uwarta, suna duban sama cikin hasken farin wata da dare. Sukan yi sha'awar kallon taurari tare, suna nuna wasu siffofi. Da yake ita ce karamar, Purnima takan sami damar kashe lokaci tare da uwar, kuma takan fi jin dadi duk lokacin da suke tare su biyu. To mai bukin ranar haifuwa, me zakiyi da yake yanzu kinyi girma? Inji uwarta tana yi mata wasa.

"Nayi girma?" Me kike nufi da nayi girma? Ni yar shekaru goma sha hudu kawai, "in ji Purnima, tana kyalkyacewa. Galibi takan sami kanta tsakanin jin yarinta da kuma tunanin cewa akwai hakin daukar nauyin zama babba nan gaba, amma a daren yau kam ita dai diyar iya ce kawai.

Farincikin Purnima bai yi tsawo ba, an yanke shi da wuri a lokacin da ta hangi hafsoshi guda hudu sun fito daga cikin gonaki sun nufo su. Sai ta fara jin tsoro, bayan da ta lura cewa mutanen sun nufo tane, abin mamakin shine da alamar uwar ta bata ma farga da abinda ke gudana ba.

Kafin Purnima ta tsere, hafsohin nan hudu sun rigaya sun kewaye ta, daya daga cikinsu ya cabki hannunta, ya danne da dogayen yatsunsa har saida taji zafi kamar jini ba zai iya wucewa ta jijiyoyin ba "Sake ni! Kana ji mani ciwo!" tana rook, hankali kuwa aka janye Purnima daga gidan su, duka kuwa kamar bacewa suka yi zuwa can nesa. "Iya! Iya!" muryar Purnima na fuskantar hanyar gidan" idan kin yarda ki taimake ni!

Purnima ta farka da matsananciyar karkarwa, taja dogon numfashi a yayin da hankalin ta ke dawowa ga zahirin alamari. Tanajim dandanon gishiri daga hawayen da ya bushe mata a wajajen bakin ta. Tana ta juyayin wai shin ko zata taba yin sabo da kadaici haka.

Akwai duhu ainun sai dan hasken wata ake hange yana dan haskaka rassan itatuwa a bisa kanta. Da jikin ta ya fara rawar sany, sai ta yafa rigarta sosai kewaye da kafadun ta. Kuma ta kunsa rigar sanyin ta domin tayi matashin kai. Purnima ta dubi cikin duhun daren nan, sai take ta mamakin shiru tsit na duhun dare abin tsoro ne.

Wai shin lallai yau ranar haifuwa ta ce? tana tunani. Purnima tayi kokari ta gane kwanan wata nawa ne, amma ina, al'amura da suka gudana a cikin yan makonnin nan, sun faru ne da wuri wuri daya bayan daya har yasa ta bata wajen lissafin kwanakin wata. A yanzu ma dai ba wannan take ji ba.

. abinda tafi ji yanzu shine yadda zata haye wadannan kwanakin, makonnin kai har shekaru masu zuwa. Ita dai dukan abinda ta sani shine tana marmarin gida ainun. A yayinda ta sake kwanciya sai ta tuna da fuskar uwar da kuma yadda uwar ke rike ta da kauna.

## A KUKKUJE, JINA-JINA....KUMA BABU KUDI

"Tashi! Tashi ku kawo kudinku, sa'annan zamu barku ku rayu!"

Karar muryoyi masu magana da karfi suka tada Purnima daga barei ta farka firgigi da taji dukar kafa da takalmi kankura a hakarkarin ta.

"Na ce tashi!"

Zafin ya ratsa jikinta a yayin da wannan mutumin da ba ta sani ba ya sake kai mata shuri da kafa. Ba ta iya sanin mutane nawa ne suka kawo musu hari ba ammma barayin suna da yawa wannan kungiyar nata da basu da yawa basuyi wata ja'in'ja da barayin ba.

Jin karar kukan abokan tafiyarta ya shaida mata cewa suma ana cikin kai musu hari. Purnima tayi kokari ta kare kanta a yayin da suke shuri suna duka. Tsoro ya kamata ainun amma sai ta tuna da wata aya a Littafi Mai Tsarki, tana zaton daga cikin Bishara ta Matta ne "kada kaji tsoron wadanda ke kashe jiki kawai", tana ta maimaitawa kanta tare da adduar cewa ba fatanta ne wannan ya zama kaddaraba, sai kuwa ta tuna da kunshin kudi da ubanta ya bata. A yayin da barayin suka jujjuye kayansu ko ina domin kwashe musu abin da suke da shi. Purnima tayi kokarin dauke kudin da ta boye a cikin kayanta kafin barayin su gane kudin. Hannunta ya kai kan abin da take nema kenan sai taji an sake shurar ta da kafa ta baya yayi mata zafi sosai, sai tayi kuka ga Allah a yayin da take kare kanta ta wajen kokarin mirginawa daga wannan shure shuren da ake yi mata da takalma kankura akai akai.

Bayan da barayin nan suka yiwa yan hijirannan kaca kaca, kuma suka kwace musu duk mallakarsu, sai barayin suka jera hudu daga cikinsu a layi har da Purnima. Babu daya daga cikinsu da ya isa yace uffan a yayin da suke tsaye a gaban barayin su guda goma sha biyu, ko wanne da fuskarsa a rufe.

Purnima ta dubi sauran da ke tsaye da ita, ko wanne a narke cikin tsoro. Ta sani ba wani abune mai wuyaba a wajen barayin nan su harbe mutum su kashe nan take. "Kada ku kuskura ku gayawa yan sanda" daya daga cikin mutanen ya gargade su a yayin da yake razana da karamar bindiga a gaban su, "idan kuwa kuka yi zamu dawo mu kashe ku" da yatsarsa a kan kunamar bindigar, kuma sai ya fara nuna bindiga a fuskar ko wane mutum domin ya shigar da kalmomin da yayi. Purnima ta rufe idanunta tana zaton ko zata ji tashin bindiga. A lokacin da ta bude ido barayin sun riga sun tafi.

Mutanen suka duba irin barnan da aka yi musu. Kodashike sunyi godiya ga Allah da ya tsare rayukansu, dukkansu a kukkuje suke kuma sunyi jina jina, kuma da kansu suka farga cewa basu da komai da ya rage musu. Barayin sun kwashe komai, har da tufafinsu. Basu taba zaton tafiyarsu zuwa Nepal zai shiga irin wannan hali ba.

Washe gari John yayi kokarin ya tsai da wata babbar mota ta aikin gona wadda ke daukar kaya na katako. Dajin cewa motar ta nufi Nepal ne sai ya roki direba a yayin da sauran sukayi maza suka fito. Ko zaka yarda ka daukemu? Bazamu iya tsayawa anan ba akwai hatsari"

Kuna da kudi? Dattijon direban ya tambaya a yayin da yake fitowa daga motar, ya lissafa abin da zai iya samu ya sa a aljihu.

John yayi masa bayanin yadda aka yi musu fashi acikin daren nan da aka wayi gari, a yanzu ma dai sun rasa dukkan mallakarsu. "ka taimaka" ya ci gaba da bayani wasu daga cikin mutanen tafiya da kafa ma da kyar suke yi domin tsananin duka da suka sha. Amma bayan yaga irin raunukan da suka samu, direban motannan yaki ya dauke su. Har yanzu shi manufarsa ta cin riba ce.

Da John da sauran suka fara juyawa domin wannan dama da ta leko ta koma, sai kuwa Purnima tayi magana. "ina da wasu kudi". Sauran suka dubetacike da mamaki suna al'ajabin cewa yaya za'ayi ace tana dauke da wasu kudi, bayan irin jidalin da suka shiga. Mafasannan sun birkita komai da komai a cikin bincikensu. "Bari dai kawai na boyesu cike da kula". Inji Purnima, tana ta murmushi a yayin da ta mika kudin ga direba. Mafi kankanta a cikin yan gudun hijira guda tara ta zama jarumarsu a yayin da kowa ya rungumeta suna zuba kayansu a bayan motar. Wannan kuwa ba shine na karshe da karamar Purnima da azancinta zasu yi amfani ba.

Fitowar rana ya shakatar da wannan kiristoci ya kuma taimaka wajen korar sanyin kwana a waje a cikin sanyi mai shiga kashi, kuma a kan kasa mai danshi. Kuma a lokacin da yawancinsu suka mori wannan dama domin suyi dan gyangyadi Purnima kuwa sai ta sake tunawa da uwarta, kuma a lokaci na farko da ta fara tambayar kanta cewa shin shawarar da ta yanke ita ce dai dai kuwa? Watakila da tayi bangaskiyarta a boye kamar yadda Maya ta taba shawartarta. Sai ta bude Littafinta Mai Tsarki da Dibal ya bata bayan anyimata baptisma, kuma ta fara godewa Allah domin barayin basu ga amfanin Littatfin ba.

Tana bude shafuna sai Purnima ta sami ayoyin da takanji dadinsu. Ta sha karantasu sau bila adadin kuma ta sa maki domin ta ganesu da sauri cikin sauki. Tun lokacin ziyararsu ta farko zuwa Maya tana kuma jin dadin labarin karfin hali, jarunta da kasada na cikin Littafi Mai Tsarki. Tayi tunani game da Maryamu da Yusufu da suka tsere zuwa Masar, kuma game da Dauda da yake gayawa Sarki Saul, kuma ta tuna da labarin Musa wanda shine tafi sha'awar labarinsa a cikin Littafi Mai Tsarki, ta sani cewa tana tare da wata kyakkayawar tawaga.

## SAKE HADEWAR YAN GUDUN HIJIRA

Rana na faduwa kenan sai direba ya tsaya a wani garin India da ake kira Ason, kuma ya gayawa fasinjojinsa cewa

yana bukatar karin mai kuma zai debi wasu kaya. Zasu yi yan awanni kafin su ci gaba da tafiya, in ji shi. Samun zarafin mike kafafunsu, sai Purnima da sauran suka fara takawa a cikin gari, garin haka kuwa sai suka hadu da wani pasto na garin.

Asalin paston daga Bhutan yake, kuma yayi mamakin labarinsu da kuma yardarsu subar kome a baya domin subi Kristi. Purnima ce ma tafi bashi mamaki, sai yaja John a gefe guda ya tambaye shi ko shekarunta nawa ne.

Ban tabbatarba ko goma sha uku ne, ko kuma goma sha hudu, in ji John, "akwai iyalinta a cikin wannan tafiya? Pastor ya nemi ya sani.

"A'a iyalin yan uwanta sun nufi Nepal, amma sun rigamu tashi, bamu san a ina sukeba a yanzu".

Pasto fa ya tausayawa Purnima. Sai ya tambayi John idan zai iya kiran Purnima tazo ta zauna tare da iyalinshi. John yayi na'am cewa wannan shawara mai kyau ce. Dama shima ya damu game da ita, ya kuma karfafa paston da ya mika wannan shawara ga Purnima da kanta.

Purnima tayi na'am da ta zauna tare da pasto da matarsa. Abu ne mai shakatarwa a sake zama cikin wani iyali. Amma fa ba iyalinta bane, kuma taci gaba da yin addua domin ta sake saduwa da Maya. Ba ta yaye hakan za iya faruwaba, ita dai addu'a take hakan ya faru.

Bayan wata uku pasto ya gayyaci Purnima ta tafi tare dashi wani taron krista a wani gari. Ta ko amsa da farinciki, ba tare da sanin cewa mijin yarta Sival ma zaije ba. Tayi farincikin sake ganin Sival nan take ta yanke shawarar bin Sival a yayin da zai koma Nepal, shawarar da pasto da matarsa suka yi bakin ciki akai "kin tabbata kina so ki tafi" Purnima? Pasto ya tambaye ta, shin kin san yaye wahalar zama a Nepal yake? Za'a tilasta miki zama a sansanin yan gudun hijira".

Purnima ta saurari maganganunsa masu kissa, kuma tasan gaskiya ya gaya mata. Pasto da matarsa sun rike ta kamar diyarsu, kuma akwai ciwo ace zata barsu.

Amma ta yanke shawara. I na tabbata, ta amsa, ina so in zauna tare da nawa iyalin. Na gode da dukan abin da kuka yi mani, amma na ba da gaskiya wannan shine nufin Allah domina".

Purnima da Sival sun isa sansanin yan gudun hijira da yake a arewacin iyaka tawe Nepal da dare cikin hadari, saboda haka bata sami ganin yaya tsarin sabon gidanta yake ba nan take. Abin da kawai take so a lokacin shine ta sake ganin Maya. Yan'uwan nan suka rungumi juna da kururuwar farinciki. Daga baya Purnima ta bingire da barci akan tabarmar gwangwala.

"Purnima, tashi!" Esther tana guje gujenta kewaye da Purnima, tana tafa hannayenta tana dariya a cikin dan bukkansu da ke cike da mutane. Lokacin da Purnima ta bude idanu abinda ta fara lura dashi shine itatuwan gwangwala da aka kafa kuma aka yi rufi da leda akan bukka. Da ta tashi zaune, sai taji surutai kamar akwai mutane guda dari a kofar bukkan.

Nan da nan kuwa yanayin matsi na sansanin da tsananin talauci na dubbunan iyali da suke zaune wurin ya zama tabbatccen al'amari ga Purnima. Dada karin kallon sansanin shine dade karin fid da zuciya a gareta.

Maya kuwa murna take domin sake saduwa da kanwarta, sai tayi ta kokarin karfafa wa Purnima zuciya. "Saurara, Purnima", tana gayawa kanwarta. "Na sani wannan wurin yana doyi, amma hannun Allah yana tare damu a kullum, ko da a ina muke. Lallai ne ya samar mana da aikin yi anan. Kiyi tunanin dukan mutanen da suke nan, wadanda basu taba jin labarin Kristi ba. Kuma kinsan yadda hankalin mutane yakan jawu zuwa gareki. Sukanyi sauraro a lokacinda kika gaya musu maganar Allah watakila domin basu saba ganin irin wannan mai wa'azi da ta ke karama kuma kyakkyawa ba".

Purnima ta nuna jin kunya kuma tayi murmushi, "mai yiwuwa haka din ne," in ji ta. Amma har zuwa yaushe kike jin zamuci gaba da zama anan? Kina jin shirin Allah kenan cewa ba zamu kara sake komawa gida ba?"

Maya bata da amsa, amma sai ta ja Purnima kusa da ita ta rungumeta. Tana so ta nuna karfin hali domin kanwarta, amma gaskiyar itace ita ma takanyi wannan tunani.

Da tafiya tayi tafiya sannu a hankali sai Purnima ta fahimci dokokin zama a cikin sansanin. Yi kokari ki karbi takardar "Lizinin fita" duk lokacin da ake son fita waje cikin kauyuka. Kada ki gaya wa hukuma cewa zaki fita yin wa'azi da raba kasidu. Kada ku dinga yin taron Krista mai tara mutane da yawa a cikin sansanin, kuyi haka rukuni rukuni da kuma gidajen addu'a. Kuyi amfani da wannan dama ta koyar da harshensu da ake yi a aji da dai sauransu. Wannan sansnin yan gudun hijira na da nashi al'adar rayuwa ta musamman da Purnima bata taba yin zato ba.

## TSANANIN SON ISAR DA BISHARA

Abu mafi gamsarwa da rayuwa a cikin sansanin ga Purnima shine fadadar da majami'a take cin gaba da yi a cikin dubbunan yan gudun hijira. Tana jin dadin samun kwanciyar hankali a tsakanin iyalin Kristi da kuma abokantaka da ta kulla sannu a hankali. Sau da yawa da ita da abokanta sukan sulale su fita rukuni rukuni, ba tare da an gane ba domin ziyartar wasu Krista da ke sansanoni da kauyuka masu makwabtaka da su, sukanyi amfani da wannan dama domin kara koyon harshen su a yayin da suke yin bishara. Purnima takan fi jin dadi da irin wadannan kaiwa da kawowa na karfin hali da jarunta inda kuma ta fara ganin irin baiwa da Allah yayi mata na iya raira wakoki da kuma tsananin tausaya wa batattu. Da yake ta dulmiya acikin tsananin son isar da bishara, har ma ta kusa mancewa da wuyar rayuwar talauci na cikin sansani.

Purnima da abokanta suka cigaba da isar da bishara ga wadannan sansanoni har zuwa shekara na biyu inda aka kama su. Kungiyar ta harama ne da asubanci na wata lahadi da safe a watan Agusta domin yin wata tafiya ta awa biyu zuwa wurin Hona.

Hona ya sami labarin wannan kungiya ta Krista a sansanin yan gudun hijira, kuma ya gayyaci rukunoninsu suzo suyi sujada a gidansa kuma suyi bishara a kasuwar kauyen. Purnima da sauran kuwa sukayi na'am.

Shiru, a hankali kuwa suka sulale biyu biyu uku uku har suka kai su gomasha daya daga sansanin yan gudun hijira, suka hadu tare kamar mil guda daga masulala .

Dauke da Litattafai Masu Tsarki, yan kasidu da kuma molon turawa. Kristocin suna dokin yin bishara a wani sabon kauye ga mutanen da watakila basu taba jin bishara ba. Amma sun sani cewa dole suyi hamzari su dawo sansani da faduwar rana.

Sun isa gidan Hona da rana tsaka, bayan yin sujada na wani lokaci, sai suka kama hanya zuwa kasuwa. Sun shirya su fara raira wakoki kenan sai yan sanda suka tunkari Purnima da sauran. "Kuzo taredamu", suka umurta.

Cike da firgita wannan rukuni basu da zabi illa su bi hafsoshin nan, can kuwa sai suka sami kansu a zaune a gaban wani kaftin mai idanu kuru-kuru.

"Daga ina kuke" ya tambaya, wanene ya baku izni ku fita daga sansani? Wnene ya baku izni ku yada addinin ku a Nepal?"

## BAKU DA WATA DAMA ANAN

Haka suka wuni suna jira a cikin matsara mai duhu a yayin da kaftin din ke tuhumar su daya bayan daya, mazan da farko matan daga baya. Purnima ta fara gajiya, kuma tana tunanin cewa wannan ai wani rashin fahimta ce kawai, sai tayi shawarar ta kalubalaci hafsan. "Ai bamu yi wani laifi ba. Me ya sa kake rike mu anan? Ka barmu mu tafi lallaine mu koma sansani kafin faduwar rana.""Babu!" kaftin ya tsawatar zamu ajiye ku tare damu a daren yau, a gobe kuwa akwai gayyata daga kwamanda na yankin."

Ganin yadda wannan kaftin yake nuna farincikin kama su da kuma tsaresu yasa Purnima ta takura. Da ita da sauran mata guda uku. an kulle su ne a cikin wani karamin daki, kazamin daki inda suke a takure tare suna kira ga Allah a cikin dukan daren, suna neman kariya daga gareshi. Suna sane cewa yin bishara a Nepal yana iya zama da hatsari, amma dayawa da basu taba jin bishara ba suna karba da doki, don haka ladar yin haka yaci ayi kasadar.

Washegari da safe yan sanda suka tara kristocin nan guda gomasha daya wuri guda. "Idan kuna da kudi, kuna iya sayen wani abinci na rana." Daya daga cikin hafsoshin yashaida masu. "yanzu kam zamuyi wata doguwar tafiya a kar."

Purnima ta dubi abokan tafiyar ta, amma bata damu sosai ba. Ta amince za a daidaita batun a yau a can ofishin kwamandan yankin.

Suka wuni suna tafiya a cikin jeji, Krista guda goma shadaya da yan sanda guda tara dauke da bindigogin su. Ina jin ana yi mana ganin mu wadansu mugaye ne, Purnima tana wannan shawarar cikin birnin ranta kuma tana zuba idanu akan bindigogin. Jikin ta ya yi tsami domin tafiya akan hanya mara kyau.

Da yake da ita da sauran basu da kudi, basu da abinci kuma ba su da ruwa sai kawai lokacin da suke haye wani rafi.

Duhu ya riga ya yi a lokacinda suka isa ofishin kwamandan yankin. Purnima ta gaji ainun ga sanyi ga yinwa, amma duk da haka tana cike da karfafawa cewa Allah ya na tare da su, kuma tana da karfin zuciya cewa ba da jimawa ba zasu koma gida. Amma waman sa rai ya sha kashi tun daga fara tuhumar su da akayi. Hafsoshi guda biyar ne suka zauna a bayan tebur cikin dakin yin tambayoyi mara haske sosai suka yi ta yiwa kristocin tambayoyi da tsawa da nuna fusata: Wanene ya baku izini ku yi bishara a kasuwar Ihapa? Wanene yake taimaka maku? Daga ina kuka sami kayan aiki? Ku kazaman yan gudun hijira ne! Baku da wata dama anan."

Dukan wanda yayi kokarin ya bada amsa ga wannan tambaya mai tsawa sai a mare shi a shure shi kuma, amma fa idan basu amsa ba ma dukansu ake ana shurin su. Anyi tambayoyi da duka na tsawon lokaci, har sai da wani hafsa ya shiga yace, "ya isa. Babu sauran duka a daren yau. A basu abinci, sai gobe zamu ci gaba.

Matsayin wannan dakin kurkukun har yafi na farko. Purnima ta kwana da kumallo na matsarmama da ya taso mata har makogwaronta yayinda doyin cikin matsaran ya bugo ta a hanci. Daben simintin yana da sanyi, kuma babu ko bokiti ma da zasu iya yin amfani dashi domin yin bahaya.

Da safe kuwa Purnima da sauran matan suka jira a cikin matsarar su da faduwar gaba.

Hafsoshin suka fara fito da fursuna daya bayan daya suna musu tambayoyi. Kwamandan yankin ya shaida wa Purnima cewa, suna da shaida cewa da ita da mutanen ta sun rushe haikali na Bhudanci kuma suka la'anci allolinsu.

"A'a, ba gskiya bane!" Purnima tayi farat don mamaki. Hafsan nan ya mare ta sosai a fuska.

Ke karamar makaryaciya mai tsiwa!" yana tsawa. Ki gaya mana gaskiya kawai, domin ki sami horo mai sauki. Idan kikaci gaba da yin karya, zaki tafi kurkukun tarayya na dogon lokaci." Purnima ta fara gigita, amma ta dage. Kari bisa kari ana marinta ana shurarta, bayan wani lokaci kuwa sai Purnima ta shiga wani matsayi na zurfin tunani a yayinda muguntaar mutumin nan ya sha kanta. Banda barnar da barayi sukayi musu a wannan daren farko a India, bata taba sanin cewa mutane zasu iya zama mugaye irin haka ba. Amma fa kwanaki 28 nan gaba ya zama lokaci ne a gareta na ilimantarwa game da shan tsanani. Ga yarinya yar shekaru gomasha biyar kam darasi ne mafi tsanani.

Kwanaki na tuhuma sukayi ta ja a yayin da hafsoshin nan suka ci gaba da anniyar su ta karya karfin zuciyar Purnima da abokan ta. A kullum abu guda akeyi, sai dai kawai su basa iya sanin wa za'a fara kira tsakanin su domin tambayoyi da azabtarwa.

Tambayar da amsar batayi daidai ba, mari, wata tambayar, wata amsa mai rashin daidai, wani marin. Haka akayi tayi.

A cikin dakin sarkar su kuwa, Purnima da sauran mata sukan yi waka a hankali, kuma suyi ta yin addu'a har zuwa tsakar dare, suna kokarin karfafa juna da kalamu kyawawa". Kawai ku dage zamu ga karshen wannan, kuma zamu tafi gida, "suna rada a cikin duhu.

Gida, Purnima tana gatse a cikin tunaninta, yanzu kam akwai dangantaka na kalmomin.

## YIN HASKE DA SALAMAR ALLAH

A lokacin da Purnima ta ke cikin sansani ta kan tuna da iyayenta a kullum, kuma takan ji rashi kwarai na rabuwa da gida na can Bhutan. Amma yanzu tana jin rashin yar'uwarta da wannan kazamin karamin bukka ne cikin sansanin yan gudun hijira mai cika da batsewa kuma tana ta tunanin kananan yayan yartako sumekeyi a yanzu haka tana kuma damuwar cewa ko yaya Maya take jure wa rashin dawowarta. Ko ta sami labarin inda Purnima take?"

Wayyo, Maya, kiyi hakuri da irin wannan damuwa da na jawo maki. Nasa yanzu hankalinki a tashe yake, Purnima tana tunani.

Alhali ma dai, wasu Krista na cikin sansanin, tare da paston su, sunji jita jitar kama wannan rukunin kristocin. Harma sunyi tafiya zuwa inda ake tsare dasu inda Purnima da sauran ke tsare, inda hafsoshin suka basu kashi aka kuma kore su. Kuma an sanar da su goma sha daya kamammun game da haka, kuma wannan cinzali da akayi wa abokansu yayi musu zafi ainun. A rana ta ashirin da biyar na tsareta, daya daga cikin masu gadin yayiwo sammako domin Purnima, kwamandan yankin yana jiranta a cikin dakin nan na tuhuma, ashirye domin ya huce muguntarsa akanta. Kamar dai kullum ya fara yi mata tambayoyi: "*Wanene ya gaya maki cewa kiyi wa'azi*"? kinyi kankanta. Watakila ba laifinki bane. Tabbas wani ne ya rude ki zuwa wannan addini tare da alkawarin zai baki' kudi.

Wanene yake aiko maki da taimako? Idan kika gaya mana ko wanene shi, za a daina dukanki. Watakilama a barki ki koma sansani.

Ga Purnima kuwa mintoci masu zuwa suka zama kamar ba zasu kare ba. Ga gajiya ga rashin kuzari daga rashin abinci-akan basu shinkafa sau biyu a rana-ga jikima dumu dumu don rashin samun yin wanka amma duk da haka tana jin salamar Allah yana haskaka a cikinta a lokacin irin wannan tuhuma. Samun sakewa da take yi a gaban Kristi yana taimaka mata da gaske a yayin da takanyi addu'a domin Allah ya gafarta wa masu azabtar da ita ya kuma ba ta karfi domin dukan abinda ke tafe agaba. Purnima ta kara yin karin karfin hali a yayinda take jiran mari. Tasani cewa ba zai so amsar da zata bayar ba. "Ban karbi Kristi a dalilin kudi ba ko kuma wani taimako ko wani abu! Na karbi Kristi domin yayata tayi shekaru uku tana rashin lafiya, sai kuwa ta karbi Kristi ta kuma sami warkar wa da farinciki da salama. Babu wani dalili dabam.

Cike da jin takaici kuwa, kwamanda ya matso kurkusa da fuskarta. Jin warin numfashinsa da ganin fusatarsa ya tsoratar da ita amma tayi kokarin dagewa. "Karya kike yi!" yayi tsawa a fuskarta "Na sani kina boye mani wani abu. Ba gaskiya kike fadi ba. Yanzu kam dole ne ki tafi fursuna na dogon lokaci. Ashirye kike domin wannan? Kafin ma Purnima ta amsa yakai mata mugun mari, har ya ture kujerarta. Ku maida ta cikin dakinta, ya umurta.

Abokan dakin Purnima suka bude baki da suka ga yadda take ga kujajjen fuskarta ya fara kumburi da mari. "Kada ku damu" Purnima tana yi musu karya cewa ai zafin bai kai yadda suke ganin fuskarta ba, tana zubar da hawaye. Matan dai sun san ba haka abin yake ba tunda su ma sun sha duka da wulakanci a hannun mugayen nan. Suka yi ta kokarin,kwantar wada Purnima hankali na iya kokarinsu. Suna juyayi game da rashin yarda da abinda suke fadi da yan sandan sukeyi.

Yan sandan basu taba yarda cewa Purnima da sauran basa samun wani taimako na kudi daga kasashen waje ba. Sun hakkake cẹwa daga waje ne kawai za'a kawo Litattafai Masu Tsarki da kuma kasidu, domin addinin Krista addinin kasashen waje na yaduwa a cikin kasar ba tare da tilastawa ko alkawarin wata lada ba.

Yan kwanaki na biye anyi sune shiru a yayin da Purnima da sauran suke ta juyayin ko me zai faru dasu nan gaba. Yin addu'a da raira wakoki ya taimaka ga kwantar da hankulan su da kuma kashe lokaci. Amma Purnima tanajin damuwa game da shiru da masu tsare su sukayi suka kyale su. Mesukeyi? Me yasa ba zasu barmu mu tafi ba? Tana juyayi.

## "NI FA MAI ALBARKA CE"

A karshe kuwa ranar talata da safiyar 20 ga watan Satumba aka sake tara tawagar a ofishin kwamandan yankin. Purnima tasan cewa akwai wani abu tafe domin, har zuwa wannan ranar an ware matan fursunonin daga mazan. Shiru kake ji a yayin da aka sa su su shiga layi, kwatsam aka kuma sa musu ankwa aka iza su gaba sukayi maci zuwa dandalin kauyen inda mashar'anta mai rufin kwano yake. Purnima taji dadin fitowa sarari ta ṣha iska da rana, ko da na dan lokacine, da yasa har ta ma manta da al'amarin da ke gabansu.

Dakin na cike lokacin da aka kaisu har gaba aka zaunad da su kusa da lauyan su. A daya gefen dakin kuwa, lauyan gwamnati ne akan su gomasha daya. Amma da aka karanta musu cajin karya-wanda a ciki akwai rusar da haikalin Bhudanci da kashe shanu masu tsarki-sai Purnima ta fara jin dama dama. Watakila yau zata zama ranar da zasu samu a sake su. Tabbas alkali zai ga cewar basu da laifi. Lauyan su ya kare su sosai, amma lauyan gwamnati yana bin wani umarni ne da aka bashi, kuma yin misali da kristocin nan shine manufarsa a yayinda rana ta ja har zuwa dare. Saida aka kusan kai karfe goma na dare kafin alkali ya yanke nasa shawarar kuma aka zartar da hukumci ga gajiyayyun mutanen nan.

Purnima ta tashi a tsaye a lokacin da aka kira sunanta tare da na sauran. Ta girgiza ainun da taji alkali ya furta da kakkausan harshe cewa za a kaisu kurkukun tarayya na daurin shekaru uku.

Shekaru uku. Kalmomin nan fa suka ratsa tunanin Purnima. Purnima tayi wa Allah alkawarin zata zama mai aminci, ko da ina ne ya aike ta tun fitar ta daga gidansu.... daga kasar Bhutan...... zuwa sansanin yan gudun hijira. Amma kurkuku? Tarufe idanunta, kuma ta nemi karfafawa daga labarun Littafi Mai Tsarki da ta haddace. Sai tayi tunani kamar Yesu na zaune bisa kan dutse, yana cewa masu albarka ne su wadanda ake kuntatawa..... masu abarka nesu.... Da ta gane gaskiyar batun sai 'ta tsaya. Ni mai albarka ce...."

Yana da wuya ayi tunani cewa hukumcin dauri a kurkuku albarkane; lamirin Purnima da kuma ruhunta sunyi na'am da tabbacin haka kafinma zuciyarta ta karba. Amma acikin kwanaki masu zuwa, wadannan fursunoni da yake suna maimaita wadannan kalmomi tare. Yanzu kuwa sai aka sa masu ankwa su biyu biyu aka fitar dasu daga dakin shari'a domin yin mawuyaciyar doguwar tafiya ta ratsa jeji.

An gina gidan kurkukun bisa kan wani dutse a wuri mai nisa. A lokacin da Purnima ta sake yin tunani da yadda shari'ar ta gudana, sai ta kara amincewa da cewar akwai shirin Allah game da abubuwan da ke faruwa dasu. An kaga musu laifi, kuma gashi zasu tafi kurkuku a dalilin Kristi. Wannan masaniya yana kwantar da hankalin Purnima, kuma yasa tana murnar samun damar wannan kira zuwa ga shan wahala domin Kristi. Duban abokanta guda goma da suke takawa tare suna ratsa jeji kuma ya fahimtar da ita cewa tana tare da amintattu.

## "BARKANKU DA ZUWA JAHANNAMA"

Sun isa kofar kurkukun da karfe uku na asuba. Ta hasken farin wata kuwa Purnima ta sami ganin yadda katangar kurkukun yake da tsawo kewaye da gidan da babbar kofar shiga da wani irin kara garin budewa.

Wannan wuri yana da wani yanayi mai tasalima ainun kuma alamarsa ma kamar ya taba zama babbar sansanin mafaka tą yaki, amma yanzu ya rigaya ya lalace don rashin gyara. A yayin da suka ratsa filin cikin gida zuwa wajen gidajen, Purnima ta saci duba baya don taga rufe babbar kofar nan a bayansu. Karar haduwar kofofin nan kuwa saida aka jishi a cikin kurkukun, sabon gidanta.

Aka baiwa Purnima da sauran mata wasu fale falen tabarmi da aka saka da tattaka aka kuma shigar da su cikin daki. Wurin da duhu baki kirin amma a hankali idanunsu suka fara ganin alamun siffofin mutane a kwance a kan dabe.

Sai wata irin murya mai tsoratarwa daga kasa tace," Barka da zuwa jahannama."

Purnima tana dokin sanin su wanene ne abokan dakinta. Laifin me suka yi? Masu aika aika ne? Zasu so ta? Wadannan tambayoyi da bata san amsoshinsu ba tukuna ya fara damunta, sa'anda ta sami wani dan fili a gefen bango sai ta kwanta a kanannade. Agajiye take tilis amma tsoro ya hana barci ya kwashe ta.

Cikin yan awowi kuwa sai taga dan hasken rana ya shigo ta kananan tagogin sama can kan bango, wanda ya baiwa Purnima da abokanta damar ganin inda suke sosai. Dakin bashi da girma amma kuma ba a matsu ba. Akwai wasu fursuna guda biyar a dakin su, kuma ko wace mace ta ware kewayenta, tattare da yan komatsanta kewaye da ita akan dabe. Dakin wanka, idan harza a iya kiran sa haka din, anyi wani dan tudun siminti ne kusa kusa da bango. Akwai tasar wanka mai tsatsa amma babu sabulu, babu ruwan zafi, ba bu kofa. Wani rami da ke ajikin simintin ya shiga cikin wani rami da ake wanka wanda Purnima take zato na ba-hayane kuma ta wurin irin warin da takeji, ba a taba wankewa ba wari da yake fitowa daga ramin ya cika dakin. Bangon kurkukun na cike da kazamta a ko ina ga kuma tsohon penti da ke dayewa domin rashin gyara na dogon lokaci. Daben yana da sanyi, ga danshi ga kazamta.

Wani dan karamin kofa, daidai tsawo zuwa fuska, yana baiwa fursuna damar hangen filin cikin gidan ta gefen sashi mafi girma inda maza suke. Can gaba da filin akwai hanyar takawa da kafa daga inda ganduroba suke zuba ido, ko da shike Purnima ba ta ga wasu gandurobobi ba tukuna Tulasa ita ce shugabar sakai na dakinsu,

"Me ya kawo ku nan?" ta tambaya gatsetse, tana kallon Purnima. "Kinyi kankanta a kulle ki, ba ki zaton haka?"

"Ban sani ba ko nayi kankanta". Purnima ta amsa, "amma muna nan ne domin mu Krista ne".

"Krista?" kamar ma Tulasa zata tofar da kalma, "me yasa zasu kulle ku domin ku Krista ne? "Ai wawanci ba karya dokar kasa ba ne". sauran suka taya ta yin dariya. Sai ta gabatar da kanta, amma babu dadadan kalamu a muryarta. Cewa sukayi na kashe surukata, tayi gurnani. Saboda haka zan dade anan, kuma zanso idan zaki iya kame wa kanki!" Purnima kuwa me zatayi, illa ta zuba wa wannan mata idanu, ko da shike taji zafin kalamun Tulasa marasa dadi. Amma ta wata hanya Purnima na hangen mutunci da kula sunyi tarayya a bayan wannan fuska ta waje, kuma daga wannan lokacin, tayi ta addu'a ga Allah da ya bata damar samun haka din.

Tulasa ta koma gefen ta na dakin, tana ta ambatar kalmomi na sabo akai akai. Purnima ta lura cewar tana da isassun barguna da wasu kaya, alamar cewa Tulasa dadaddiya ce anan, kuma yan'uwa ko abokai sun sha kawo mata kaya daga waje. Sababbin zuwa kuwa basu zuwa da kaya illa wadanda suke saye da su. A wannan safiyar farko, sun tattaru tare sunyi addu'a, da daukar shawarar zasu farayin haka a kowace juma'a. An baiwa sababbin zuwa wasu kayan girki, kuma a kullum ana raba musu abinci sau biyu, galibi shinkafa da dankali.

Wani lokaci ma akan basu wasu yan kudi domin sayen abin da suke so.

Ba da jimawa ba kuwa kristocin nan suka gane cewa iya sabawa da zaman fursunan ta wasu hanyoyin yana kama da iya sabawa da zaman sansanin yan gudun hijira:

Ka koyi sanin dokokin, ka kauce wa dukan wata rigima, kuma yi lura da abin da ke tafe ta baya.

Bambamci kawai da ake gani baro baro a tsakani shine rashin yanci da kuma kin shiga tsakani na gandurobobi duk lokacin da wata fada ta tashi a tsakanin fursuna da fursuna.

Amma, Purnima tayi tunani, a kalla ba zasu fuskanci tambayoyi da doke doke na kullum kullum ba anan, kuma zasu mori lokutan su na hutawa da kuma sujada, duk da damunsu da kuma ba'a da abokan dakinsu ke yi musu da munanan kalmomi. Abu mafi tsoratarwa ga Purnima shine jarabar gandurobobin, wanda ta fara ganin alamun tun saukarsu.

Watannin farko suka ja, Purnima kuwa bata samun isasshen barci. Tazo ta gane dalilin da sauran basu matsa wurin kwanciyar su kusa da bango: Akwai sanyi kwarai. Gashi tana samun laulayi da gabatowar hunturu, kuma bata da kayan rufa ballantana bargo. Sannu a hankali kuwa fatar da take da shi zuwa gaba ya fara zama fitar da rai. Yin lura da abubuwan da ke faruwa, Purnima ta fara shiga damuwa game da ganin tarkon Shaidan zai kamata da irin wannan rauni na ban gaskiya da suka sha mata kai. Sai kuma ta sake tunani, wai ashe ba tayi babban kuskure ba. Mafarkan ta na tunawa da gidansu, na uwarta, sun sake dawowa, yasa ma faduwar rana ya zama abin damuwa. Tayi shirin bada kai.

Watarana Purnima taji kuka da ihu na zuwa daga sashen maza da rana tsaka biye kuma tana jin muryoyin masu fusata ne cewa “Kamashi! Ba sabon abu ne ba fada ta barke a sashen maza, amma a lokacin da taji wata murya tayi tsawa tace karasa shi kawai. Mataccen Krista ba zai iya yin bishara ko waka ba!” Purnima ta sani cewa wannan barazana na gaske ne. Tulasa ta gaya mata cewa an kashe wani a sashen maza kenan suma suka iso.

Sanin cewa daya daga cikin Krista yan uwanta ne wanda yake fuskantar kisa a hannun abokan dakinsa, Purnima tayi ta kiran ganduroba, amma babu wanda yazo. Ta fada kan tabarmarta tana sharbe tayi addu'a. A wannan lokacin ne ta gane zaman fursuna na yan uwansu maza yafi nasu zafi da ake tattara kamar dari biyu a daki guda, yawancinsu kuma mugayen masu laifi ne fiye da nata. Ta lura da irin tausayi da takeji a yayinda daya daga cikin mutanenta na shan duka a waje, watakila ma kasheshi akeyi.

"Ya Allah," tana addu'a ina roko kada ka bari su kasheshi, ina roko kada ka bari ya mutu."

Sa'anan tayi kuka a wannan karon kuwa ba domin kanta kadai ba, amma domin dukansu.

Wani dan'uwa mai suna Ashok shine aka kaiwa wannan hari a sashen maza; ya rayu, amma dakyar. Godiya ga samun saukin sa, sai fa ta dage ga kawar da hankalin ta daga nata al'amura Purnima da sauran mata na dakinsu. Ta sani cewa ya kamata ta zama da kwazo idan tana so ta rayu a cikin shekaru uku din nan. Amakonni da suka wuce ba jikinta kawai ta barci ba amma har lamirin ta da ruhunta sun shiga kurkuku tare da ita, dole ne kuwa wannan matsayi ya sauya. "Nuna mani abinda zan iya yi, Ubangiji" ko da ta halin kaka." Ina da yanci na na bauta maka" koda ta halin kaka" Yanzu ne ma abin ya fado mata cewa Kirsimeti ya kusa....

## KYAUTAR KIRSIMETI

Mutumin da kawai an sanshi da suna "Kawu" ya zama sananniyar fuska a kurkukun tarayya. Ya dade a ciki kuma yakanyi yawonsa ko ina a cikin kurkukun a sake, sababbin zuwa galibi sukanyi tsammanin ko shima ma'akaci ne na cikin kurkuku, amma ba haka bane.

A kowane mako yakanyi nashi zagaye na dakuna yana tambayar fursuna ko zasu so bada sautu zuwa kasuwa.

"Ina kwana, Purnima," yana mata kira me za'a samo maki yau, ko kuma so kike ki adana dukan kudadenki har sai an sallameki? Menene ma dalilin adana wa? Menene ma amfanin su in ba kashewa ba?" Yana fadar wadannan maganganu kenan, sai wata shawara ta fado mata. Hakane! Abinda zanyi kenan. Kawu ka jira!

Tayi sauri ta kunsa dukan kudadenta da ta tara a hannun Kawu ta cikin yar kofar dakinsu, ta rada masa abinda zaiyi mata da kudin. Tana kallonsa a lokacin da ya juya ya tafi, tana addu'ar ya iya sayo mata abinda ta gaya masa daidai. Kawu ya dauka ko tayi batan hankali ne da ya saurari irin sautun nata,

Da ya dawo a ranan nan, ya isar da sautun ga hannun Purnima da ke ta duba hanyar dawowar sa. "Duka na ciki." Kawu ya tabbatar mata. "Amma, har yanzu ji nake kamar hankalinki ya gushe. Zaman kurkuku na iya jawo haka."

Purnima tayi murmushi na godiya ta mika hannu ta dan kofar tasha hannu dashi. Sai ta fara yin shirye shiryenta sauran suna kallo. Can fa suka kosa, suka fito fili suka tambayeta wai shin menene takeyi, amma Purnima bata ce kome ba sai taci gaba da aikinta. Ta wuni tanayi, amma ta dage da ganin cewa tayi shi daidai.

A karshe, bayan ta gama, sai ta gusa gun sauran kuma tayi shelarta: Tunda nazo nan Allah ya nufe ni da na adana kudin fursuna da ake bani. Ban san daliliba sai yau da safe ne nasan abin da ya kamata nayi. Na roki Kawu ya sayo mani kaji masu kyau da ganyaye da zai iya samu. Yanzu kuwa, na dafa su duka-domin ku." Sukayi shiru kowa na duban kowa don mamaki. Tulasa ta dube ta da shakka, tana neman wata "hujja" tana mamaki me yasa Purnima wadda ita bata taba yiwa kalamu masu dadi ba zatayi irin wannan abu. "wai me kike magana akaine? Wannan wayon na menene?" tana tambaya cikin gatse.

"Kawai so nake muci tare, Tulasa. Saboda haka kumuci!"

A wannan daren fa mata suka mori abinci mafi kyau da suka taba tunawa. Har gandurobobi ma suna wucewa suna leke. Labari ya bazu a cikin kurkukun: Purnima ta shirya buki!

A wannan daren Tulasa ta bar gurinta ta matso wajen Purnima. "Me yasa kika yi mana wannan?" ta tambaya, tana nuna mutunci da amincewa ta farko ga Purnima.

Bamuyi maki kome ba mai kyau illa ba'a ga ke da şauran tunda kuka zonan. Kuma wannan kudin ki ne, duka gaba daya. Kina iya amfani dashi domin kanki, amma kika kashe su duka akanmu?" Tulasa dai bata gane da irin wannan kirkin ba. A tunaninta cikin biyu ko wawiya ce ko kuma mai wayo ce kwarai, kuma tana kokarin ta gane wannene a ciki.

"Tulasa" Purnima ta fara, da murmushi a fuskanta, "Ko kin taba jin labarin Kirsimeti?

Ta wannan hanya ne abutar da ba a zata za ta yiwu bat ta fara tsakanin mai laifin dauri na kisa da karamar mai bishara. Purnima ta bata labarin yadda tayi ta zama Krista a lokacin wani bukin kirsimeti shekaru uku baya Purnima tasha yiwa Tulasa maganar Kristi cikin watannin da suka wuce, kuma abin mamaki su biyu sun zama abokai ainun. Ta wata yar hanya ma ganin Tulasa yakanyiwa Purnima tuni na uwarta saboda haka yarinyar takanji kusantar wannan mata mai shekaru fiye da haka, ko da shike bata san abinda gobe zai kawo ba. Purnima tayi shawarar fuskanta da karfin zuciya. Ta gane inda raunin ta yake, amma ba ta yarda ta gaza ba. Zata fuskanci kalubale kuma ta barwa Allah sauran, kamar dai yadda Musa yayi.

## JAWABI

An sallami Purnima tare da sauran kristocin nan bayan watanni gomasha hudu da kwanaki shida. Batun tsare su ya isa sansanin hijira kuma har ya watsu zuwa ko ina a duniya. Wani taro na shugabannin Krista na kasa da kasa suka fara aika takardun kara zuwa gwamnatin Nepal domin a sake su. Mun sani kuna rike da Krista guda gomasha daya a kurkukun tarayya," akan nuna daya daga cikinsu ma karamar yarinyace!"

Daga baya aka shaidawa Purnima da sauran cewa sallamarsu cikin lokaci ya zama da albarka fiye da yadda suka zata.

Hukumar kurkukun sunyi shirin rufesu har na shekaru bakwai (gyaran dole da akayi na daurin wanda ya sa wani ya tuba ya zama Krista).

Nan da nan bayan shikarsu, hukumar kurkuku suka yi mamaki, domin sun nemi izni su gana da abokan dakinsu. Bayan zaman kaso na watanni uku, kristocin sunfara samun taimako daga iyalansu. Yanzu kuwa sun baiwa abokan dakinsi mallakarsu da suka tara harma da karin kudin da Purnima ta sake tarawa da shirin yin wani bukin zuwa gaba. Kuma sun tunawa sauran an azabtar da sune domin ban gaskiyar su ga Yesu Kristi. Kuma an karfafa su da tsaye isu tsaya sosai ga ban gaskiyar su." Goma shadayan nan sunyi alkawarin tunawa dasu, da kuma dukan fursuna, a cikin addu'insu.

Muhimmin abu ma shine, daya daga cikin mutanen da suka yi wa Ashok duka ya fito gaba yace," wata fitila mai haske ta shigo mana a cikin kurkuku. Amma yanzu gashi zata tafi."

Kafin su kama hanya sai Purnima ta rungumi Tulasa, wacce ta zama Krista (An saki Tulasa lokacin da aka juya hukumcinta. A yanzu haka shugabace wajen hidima a cikin majami'a.)

Daga lokaci na farko da Maya ta karanta mata labarin Littafi Mai Tsarki, Purnima na sha'awar aikin da Musa yayi. An kore shi daga kasarsa, kuma ko dashiƙe bai iya magana sosai ba. Allah yayi amfani dashi ta gagarumin hanya. Haka ma, Purnima wadda takanji kamar ta gaza, domin karancin shekarunta, ta zama kamar wata shahararriya a kewayen Nepal. Akan gayyace ta lokaci lokaci domin shaida a majami'u na kewaye da sansanin yan gudun hijira inda take da zama har yanzu tare da Maya, Sival da yayan yarta guda biyu.

Addu'arta shine na watarana ta koma Bhutan, kasarta, taga uwarta kuma ta yada bishara.

# Aida:
## Murya Domin Marasa Iya Fada Aji

*Russia:*

*Yuni 1968*

Bata da bukatar lauya, Aida Mikhailovna Skripnikova bata da bukatar mai tsaya mata, musamman ma wanda gwamnatin Soviet zata nada. Tafi so tayi maganartada kanta ta gabatarda batun ta a gaban alkali. A zaune a gefen mai kare laifi a cikin mashar'antar Soviet ta duba sama ta hangi hoton fuskar Lenin uban wannan irin shiri da ke rike da ita a yanzu haka.

Mai tuhumar laifi baiso haka ba, ba yaso mai laifi ta kare kanta da kanta; watau wai wannan yana nufin an ba ta yanci ainun, ya kuma nuna cewa wannan mai kare kanta ta kwanta a asibitin mahaukata, takaka zata iya tsayawa ta gudanar da kare kai daga yiwa kasa laifi?

A karshe alkali ya goyi bayan Aida, lauya mai kare ta kuwa ya fice daga kotu, aka bar Aida ta gudanar da kare kanta. Wannan ba shine zaman Aida acikin kotu na farko ba kuma ba shine caji na farko da aka taba yi mata akan batun ban gaskiyar ta na Kristi ba. Idan alkali ya same ta da laifi ya aika ta zuwa sansanin kwadago, ba zai zama zuwanta wurin na farko ba kuma. "Ina, ai tayi jimiri da irin wadannan a baya.

Abinda yake dabam ayau shi ne ba zata karbi wani mai kareta na wofi ba wai shi mai kariya ne daga gwamnati. Wannan shine lokaci na farko da kanta, dalla dalla tana bayanin batun ta a madadin mutanenta na bangaskiya a cikin kasarta.

Laifofin da ake tuhumar ta dasu suna da yawa, kuma alkalin yana karanta kowane daya filla filla da murya tamfar ma kamar an tabbatar da laifin. An tuhumi Aida da zama a garin Leningrad ba tare da izni na sosai ba (an janye izinin ta) Ana kuma tuhumarta da zama yar kungiyar rukunin majami'a da basu da ragista da kuma laifin raba kasidu na Krista.

## JAFA'I GABA DA GASKIYA

A cikin dukan cajin da aka yi, kalma guda daya tak ta hada wadannan batutuwa ita ce: jafa'i, masu tuhuma sun nuna cewa Aida, ta diba kuma ta rabar da "labarunta" wadanda babu gaskiya a ciki" tana shaida yadda ake kama Krista, ana kaisu kotu kuma a dauresu a cikin kurkuku a kasar Soviet. Mafi tsanani ma a idanun gwamnati shine cajin da akayi mata na cewar ta baiwa baki na kasashen waje labari, tana bari labarun da suke kaskanta kasar Soviet yana isa kasashen waje.

Kamar dai yadda mai tuhuman nan yake fuskantar wannan kalma guda daya, haka ma kariyar Aida. Nata zai dangana akan gaskiya. Idan labarin da ta aika gaskiya ne, inji ta to kuwa ba zai zama jafa'i ba. Kuma tayi shirin ta nunawa kotu cewa labarin cike yake da gaskiya.

A yayin da suke karanta mata caji, shine Aida ta gane da cewa yan sanda suna bincikenta sosai da sosai. Suna sane da batun Miss Jursmar, wannan kyakkyawar mata da tazo daga Sweden, wacce ta shiga kasar domin ta karbi takardu daga hannun Aida. Suna sane da ranar da kuma wurinda suka hadu ta mika takardun. Sun kwace dan littafin bayanai na Miss Jursmar, wanda yake kunshe da bayanai na saduwa daAida.

Harma alkalin ya jera kowane batu da kuma takardu da Aida ta mika wa Miss Jursmar yana amfani da wata murya ta ba'a da raini.

"Jursmar ṭayi kokarin fitar da takardun da ta karba zuwa kasashen waje, alkali ya nuna, amma a lokacin da kwastam suke caji sai suka gano takardun nan da aka ambata kuma nan da nan aka kwace su." Sai ya dubo daga mazauninsa na tuhuma don ya harari ita mai kare kanta, da alamar wani murmushi na cin nasara a fuskarsa.

Suna sane da David, wani Krista aboki daga waje, da kuma wata mujallar Krista guda ana kiranta, (Herald of Salvation). Aida ta aika masa. Sun sani cewa ta tafi wani wuri kuma domin ta sadu da yar'uwarta wacce ta baiwa wasu mujallu da ake rabawa Krista daga baya a majami'un karkashin kasa. Yansanda sun nuna alamar sanin dukan wadanda ta sadu da su da kuma dukan wata guntuwar takarda da ta bayar.

Aida tayi shiru tana mamakin kome ya rage da suka kama, wanda sakamakonsa zai hana asan adadin kristoci da suke a tsare.

Kari bisa kari a yayin da yake karantawa sai wata kalma tayi subul daga bakinsa. Bisa ga tuhumar, Aida ta rabar da takardun karya da gangan domin yiwa kasar Soviet da kuma dokar gurguzu jafa'i"

## RASHIN TSORO MAI TSANAKI

Aida ta zauna shiru kuma ita kadai a gefen masu kare laifi, ga rashin dadin zama akan kujerar da take, ta zaci zata ji dimauta ko cika da damuwa, maimakon haka sai tana jin rashin tsoro da kuma tsanaki, da kuma jin kamar Kristi yana nan tare da ita a cikin dakin. Yesu ya gaya wa mabiyansa da kada su damu game da abinda zasu fada a lokacin da suka fuskanci sarakuna da alkalai, don haka bata damu ba da yan

sanda suka tambaye ta, alkali yace, cikin cigaba da karatunsa, bata amsa laifinta ba, ko da shike ta yarda cewar ta aika takardu da raba kasidun Krista, an sami irin takardun da ta aika a cikin gidanta, inji yan sanda, afili suna kokarin tabbatar mata da laifi. Ta gayawa yan sanda cewa ai' takardun da ta aika babu jafa'i a ciki amma yayi bayanin gaskiyar matsayin majami'a anan kasarmu."

A karshe dai alkali ya gama karatun tuhumar. Ya zuba wa Aida idanu yace, "Mai kare kai ko an fahimci caji da akayi maki?" Sai ta dube shi da rashin jin tsoro tana kallon idanunsa, "I" "Kin karbi laifinki?" "A" a, muryarta a natse kuma, alkali ya dubi takardar sa sai yace za'a fara shara'ar, nan take kuwa yace Aida zata zama shaida ta farko.

## IYALI DA BAKINCIKI YAYI MUSU TARNAKI

A lokacinda ta fara bin Yesu Kristi tana yar shekaru ashirin da daya, Aida bata zaci cewa hanyar da zai bi da ita zai kai har ga shiga kotu ba. An haife ta a cikin iyalin Krista wanda yasa tasan ko wanene Yesu. Amma iyalin ta suka shiga cikin bakinciki mai tsanani a lokacinda aka tsare mahaifinta a shekarar 1942 domin yaki ya shiga aikin soja. Anyi masa alkawarin za a bashi takardar dauke masa yin aikin soja, amma wannan takardar izni bata samu ba. Maimakon haka aka kashe shi, ya bar Aida tana yar shekaru biyu kacal da ba zata ma iya tunawa da shi ba.

Ya bar uwar ita kadai domin gudanar da rayuwar wannan iyali a wata karamar al'umma a Siberia, kuma tayi haka ta wurin yin aiki tukuru da addu'oi. Takan karantawa yaranta daga Littafi Mai Tsarki akai akai. Kuma duk da kasadar kamu da kuma azabtarwa da ke akwai, ta kan kai yaran zuwa taron Krista da sukeyi a boye a gidajen juna. Wani lokaci kuwa ta kan tsaya a waje idan ana taron domin duba alamar ko yan sanda ko soja na zuwa. Aida ta tuna sarai lahadin da yan sanda suka mamayi wani taro a gidansu. A lokacinda sukatafi, sun dauki kawunta da kuma wasu Krista guda biyu maza da aka sa wa ankwa aka tuhumesu da yin laifi.

Abin bakinciki shine cewa uwar Aida ta rasu lokacin da Aida take yar shekaru goma sha daya. Daya daga cikin abinda Aida bata iya mantawa game da uwarta shine yadda takan damu cewa ko zai yiwu ya'yanta su girma kuma suyi watsi da ban gaskiyar ta. Wannan ba juya baya na ganganci bane, ko rashin nuna sha'awa. Aida tana hannun wata yayarta, kuma ta wurin sake wurin zama akai akai suka daina zuwa taron majami'a. A makaranta kuwa akan koya musu cewa babu Allah, kuma sannu a hankali kuma har kiran sunan Allah ma ya bace daga cikin gidansu.

## SABUNTAR BAN GASKIYA

Aida ta kaura zuwa Leningrad (yanzu St. Petersburg), tana yar shekaru goma sha tara. Wanta Victor, ya girmeta da shekaru biyar, yagama aikinsa na sojan ruwa kuma yana zaune acan, Aida kuwa ta kaura can don ta zauna kusa da shi. Watarana sai batun tattauna zancen addini ya taso a cikin tadinsu da suke yi. Aida tace, "Ni ban sani ba ko akwai wani abu wai shi Allah ko kuma babu." Irin tsanani da ya nuna wajen ba ta amsa ya baiwa Aida mamaki," Ni ban ma taba yin shakka ba! Na sani akwai wani abu da ake kira Allah."

"Aida tayi fatar ina ma da zata ji yadda dan'uwanta yake ji ba tare da shakka ba. Amma tana bukatar kafa hujja.

Ba da jimawa kwarai ba bayan wannan hira da wanta, Aida tabi ta wani kantin dadaddun litattafai, kuma ta tuna jin wani ya ambaci cewa wani lokaci kantin na sayar da Litattafai Masu Tsarki. Kusam ma kamar babu gaira babu dalili ta kusa kai ta shiga ta nemi ta sayi guda. Akawun ya gaya mata cewa Littafi Mai Tsarki na wuyan samuwa kuma kantin basu da shi. Aida ta juya zata tafi sai wani da ya shiga kantin yin sayayya ya biyo ta zuwa waje kuma yayi mata tallar Linjila akan kudin ruble guda gomasha biyar.

Kusan ma duk kudin da take dashi kenan, amma ta baiwa mutumin domin sayen wannan tsohon littafi. Wannan

sayayya da Aida tayi ya burge wanta, musamman ma domin yazo a daidai lokacin da yake bukatar sa ainun. An gano ciwon daji a cikin jikinsa, kuma likitocinsa sun gaya masa cewar wannan ciwon na iya kisa. Victor ya gaya wa Aida ta tafi dakin addu'a a shaidawa abokai abinda yake ciki.

Aida kuwa tayi kamar yadda ya umurce ta, abokan kuwa sukan je akai akai domin su ziyarce shi dominsu karakarfafashi. Ta lura da yadda zuciyar sa tana kara karfafawa a yayin da cuta take ragargaza jikinsa zuwa ga mutuwa. Tayi mamaki da ganin ban gaskiyar sa a cikin Kristi yana kara karfi akai akai a yayinda jikinsa ke rasa karfi akai akai. Tana begen samun ban gaskiya da kafa hujja irin yadda wanta yake dashi ya fuskanci mutuwa ba tare da damuwa ko tsoro ba amma tare da tabbacin gidan sa na har abada.

Watanni hudu bayan gano wannan ciwo, Victor ya rasu. A tsaye a gefen gadon sa, a lokacin da rayuwarsa ta duniya ke karewa, Aida taji a jikinta cewa sha'awar wanta shine ta sani cewa ba cewa yake yana "bankwana" ba amma, cewa yake "sai mun sadu".

Aida tana son wannan karfin zuciya, wannan tabbaci, rayuwar Victor-da kuma mutuwarsa, ya kara amsa mata tambayoyin ta. Ta tattauna sauran tare da abokan Victor daga gidan addu'a. a karshe shawarar da ta yanke ya fito fili. Zata bi Kristi a cikin bangaskiya.

Wannan shawara ce da ta zama mai tsada ga wannan budurwa, ammafa wanda ba zata taba yin da-na-sani akai ba.

## MUSAYAR RUBUTACCEN ADABI DA KALMA

"Ko zaki iya yin bayani game da caji da ake yi maki?" inji alkali. "I, zan iya," Aida ta amsa, sanin cewa alkalin da kansa ne zai fara yin tambayoyin. A wannan shara'ar shine maiyin kara, shine alkali mai bin shara'ar kuma shine hukumar

yanke shara'ar. "Na yarda da gaskiyar raba adabi kamar yadda akayi bayani a cikin tuhuma da kuma wanda na baiwa kalmar yadda aka fada."

Ta yarda da bayanin. Wannan shara'a zatayi sauri fiye da yadda nake zato. Da ma ta rike lauyanta, mai yiwuwa mai tuhuman nan yana yin tunani kamar haka.

Da alkali ya nace, sai Aida tayi lissafin kowanne daga cikin mutanen da ta basu takardu kamar dai yadda aka jera a cikin takardan tuhuma. Sai ta nuna damuwa game da tuhumar inda suke kiran wata yar takarda wai adabi ne, alhali kuwa takardar ba ta fi shafuka biyu ko uku ba, amma ta yarda cewa ta bada wannan takardar ga baki daga kasashen waje.

"Kome da kome da ke cikin tuhumar daidaine?" alkali ya tambaya bayan da ta gama. "I" ta amsa. "Dukanin batun raba adabi basa dauke da sharudan karya na jafa'i da gangan ga kasar Soviet da kuma karya dokokin gurguzu; watau ma'ana wannan bai zama laifi ba a karkashin sashe na 190/1 na dokoki kuma rabarda adabi kansa ba laifi bane. Saboda haka, ni ban karya doka ba."

Maimakon ya fuskanci furucinta kai tsaye, sai alkali ya tambaye ta batun matar nan yar Sweden, Miss Jursmar wacce Aida ta baiwa takardu, har da takardun shara'ar wasu kristoci guda biyu da akayi a kotun Soviet. Aida taki ta fadi inda suka sadu da Miss Jursmar, tana cewa ai wannan batune na tsakaninmu da ita kawai."

Sauraren yadda Aida ke gabatarda batutuwan shara'ar nan, sai mai tuhuma ya fara nuna farinciki, yana mamakin ko wannan budurwar Krista zata iya kara kariya fiye da abinda ya zaci zata iya.

Da kullatar zuci kuwa, Aida ta bada bayanin cewa da ita da Miss Jursmar suna da abokin jiyayya a Sweden, kuma shi abokin ne ya shirya saduwarsu. Miss Jursmar ta kawo littafin linjila guda hamsin sababbi, wadanda Aida ta shirya ta baiwa mambobin majami'a na karkashin kasa-amma yan sanda

suka kwace su. A maimakon haka kuwa, Aida ta baiwa Miss Jursmar takardu, hade da wasiku da kuma bayanin shara'ar, domin ta tafi dasu ta kaiwa wadanda take yiwa aiki, watau su Slavic Mission, Daga can za'ayi dabi a wallafa a rabar a cikin duniya.

"Me yasa ta baiwa Jursmar takardun Herold of Salvation da kuma Fraternal Leaflet, har hade de takardun shara'a da akayi a Moscow da Ryazan da kuma wasikun Khoren da Makhovitsky?" alkali ya tambaya da zafi zafi.

"Da ta karanta su ta sami sanin irin rayuwar mu na majami'a anan," Herald of Salvation ita ce mujallar da nafi so, Fraternal Leaflet kuwa takanyi sharhi ne game da irin rayuwar mu na majami'a, kawo mu a gaban shara'a ya zama daya daga cikin fama na rayuwar majami'a wanda yakai ga cewar idan har kanaso ka sami labarin majami'a a Russia, dole ne kuma kasan labarin kai Krista a gaban sharia."

Tabbas ga wanda ya zabi yabi Kristi sau-da-kafa, shiga dakin shari'a ya zama sashen sa na rayuwa a kasar Soviet. Kame kame, duka da dauri sun zama rabo na bin Kristi anan, kuma ita mujallar majami'ar karkashin kasa sunyi na'am kuma sun wallafa wannan batu na gaskiya.

Alkali bai iya gaskanta cewa Aida zata amince da wata mata da bata jima da saduwa da ita ba ta bata sirri irin wadannan.

"Ga masu bi, abuta takan yadu a cikin sauki," Aida tayi kokarin bayani, "Ina iya tafiya wani gari dabam daban taba zuwa ba, in sadu da masu bi da ban taba sani ba, kuma bayan dan lokaci kadan tare dasu sai mu zama abokai na kusa. Masu bi wani babban iyali ne, kuma muna da sha'awar kome da kome da ya shafi juna."

Sai mai tuhuma ya fara tsoma tambayoyinsa da na alkali, yana tambayar Aida game da dukan adireshi da ke cikin dan littafinta na hannu. Yana so ya sani ko ta rubuta musu dukansu. "Wasu daga cikinsu," Aida ta amsa.

Sa'anan kuma dadan nuna bacin rai ta kara, "Ban taba rubuta wa abokai na kasashen waje wasiku ba."

Wadansu masu bi da suka zo sauraron wannan shari'a suka ji dadin haka suna boye murmushin su a yayin da mai tuhuma ya daga kai ya dubi Aida da jin kalamunta. Sai ya fara ambatar kowane suna da ke cikin dan littafinta na hannu.

## KARFIN ZUCIYA NA MUSAMMAN DOMIN BISHARA

Aida bata fara zama wakiliya tana aiki a bakin dagar majami'un Soviet ba. A lokacin da ta karbi Kristi, ita wata kyakkyawar budurwa ce yar shekaru ashirin da daya, cike da doki game da sabon Abokinta kuma tana marmarin gayawa kowa da ta gani game dashi.

Yanke shawararta ya faru ne a lokacin wani farkawa a majami'ar Baptist a cikin kasar Soviet. "Zuwa wani lokaci dai, ban gaskiya na raguwa," take fadi daga baya, "kuma kwatsam sai ga farkawa. Abin da na gani akwai mamaki, naga matattu-wadanda suka mutu a cikin ruhu suna sake tashi, masu nuni kuma suna nuna kuzari mai karfin zuciya kwarai. Nazo ga sanin darajar kaskanci da hakuri, da darajar gwagwarmayar majami'a. Wannan lokaci zuwa gaba bai iya zama haka kawai ba, sai tare da sa kai.

Sababbin abokanta daga gidan addu'a na Victor sun karfafata game da yin bishara. Takan gansu suna dab'in kati da ayoyin bishara a jiki da sakonni da ke iza masu karantawa cewa "Su tuba su bada gaskiya ga kyakkyawar bishara."

Sukan saka katunan acikin akwatunan gidan waya, wanda ya taba kawo damuwa a Leningrad, har yakai ga bugawa a shafin farko na jaridar yankin.

Daga ranakun farko na tafiyar ta ta Krista, Aida tana da karfin zuciya na musamman da kuma himma na shaida ban gaskiyar ta ga wasu.Watanni kalilan kawai bayan karbar Kristi, Aida ta kirkiri wata hanya ta musamman na marabtar

ranar farko ta shekarar 1962. Ta sayi katunan aika gaisuwa wanda yake dauke da penti na shahararren mai zane da ake kira Claud Lorrain na fitowar rana bisa wata babbar matsayar jiragen ruwa. Tayi aiki tukuru kwana da kwanaki dukan lokaci da ta samu, tana rubuta sakonni masu sauki a jikin kowanne da hannunta:

## MURNAR SABUWAR SHEKARA TA 1962!

### Fata Ce Ta Sabuwar Shekara

*Rayuwar mu na wucewa da sauri*

*Daya bayan daya, ba tare da saninmu ba*

*Bakin ciki da bacin rai su bace*

*Rayuwa ita take batar dasu*

*Wannan duniya mai wucewa ce*

*Kome da ke cikinta zai zo ga karshe*

*Rayuwa na da muhimmanci, Kada kazama mara tunanin gobe*

*Wannan duniya mai wucewace*

*Kome da ke cikinta zai zo ga karshe*

*Rayuwa na da muhimmanci, kada ka zama mara tunanin gobe*

*Wace amsa zaka baiwa mahaliccinka?*

*Meke jiranka abokina, gaba da kabari?*

*Ka amsa tambayannan tunda sauran haske*

*Watakila gobe, a gaban Allah,*

*Zaka tsaya domin bada amsa na kome*

*Yi tunani mai zurfi game da wannan.*

*Domin ba zaka dawwama anan duniya ba watakila ma daga gobe shikenan rabuwarka da duniya har'abada!*

*Ka Nemi Allah Tun Yana Samuwa!*

Wannan rubutacciyar waka da aka rubuta a jikin katin aika gaishe gaishe ya kare da yin kira mai sauki, kamar wanda taga abokanta sukayi: "Ku tuba ku gaskanta Bishara mai kyau."

Bayan ta cike dukan katunan, Aida ta kwashe ta nufi yanayi mai kankara ta fita waje. A babban dandalin da ke gaban babban gidan nan na ma'adanar kayayyakin Tarihi na Addini da na rashin yarda da Allah (Atheism) wannan yarinya mai bakin gashi ta fara mika wa mutane katunan, tayi aikinta maza maza, tana ta rabawa mutane gaisuwar sabuwar shekara.

Ta kusa gama rabawa kenan sai taji wani hannu mai karfi ya cabke ta, "Menene wannan? Wani fusataccen mutum ya tambaya yana motsi da katin a fuskarta.

"Katin sabuwar shekara ne, "ta amsa, tana kokarin janye hannunta da ya koma, sai ta zama yar karama da yake tana kusa da wannan katon, kuma sai ta damu domin rikon yana kara zafi. Ya dudduba sa'annan ya fara kiran dan sanda da yake tsaye a gefe. "Bamu da bukatar wannan anan," Yana gaya mata a cikin fushi. Bai sake ta ba saida dan sanda yazo ya kamata a daya hannun kuma ya fara kaita cikin motarsa.

## FARA DANDANA AL'AMURA MASU ZUWA

Wannan shine ziyarar dole ta Aida zuwa ofishin yan sanda. Aka tsare ta tsawon awowi kafin a sake ta, amma sai da suka bude fayil akanta, suka kuma rubuta dukan bayanai game da wannan katin gaisuwa nayin bishara a ciki. Aida ta zauna a tsanake tana amsa tamboyin sa, gata shiru da mamakin irin karfin zuciya da take dashi. Allah yana tare da ita, tana sane; bata da bukatar jin tsoron hukuma. Tana juyayin ma shin ko wani ya taba gaya wa wannan hafsan game da kaunar Kristi domin sa.

Yan sanda suka kai rahoton abinda ya faru ga wadanda suka dauke ta aiki da kuma gida da take da zama.

Farkon karawarta da dokokin shara'a ya faru a watan Afrilu, lokacin da wata hukuma, comrades court" watau (Kotun Abokai) tayi zaman sauraron shaida ta kawo kararta. Aida ta zauna akan benci a gaban mutane uku da ake kira "Comrades" wanda zasu zartas da hukumci. "Masu kawo kara", watau mutane mazauna unguwar kuwa aka shigo dasu domin suyi kararta. Wani tsoho kuwa yana rawar jiki da bacin rai yayi kururuwa, "Bana kaunar na shaki iska iri guda tare da ita. "Bana kuma kaunar tafiya cikin duniya tare da ita."

Sauran shaidu suka ce Victor ya mutu ne domin Baptist basu bari ya nemi magani ba (abin mamaki na fadar haka, Aida tana cewa a ranta, tunda Victor ya rasu ne a cikin asibiti). Maganganun masu kararta ya kara bata mamaki ta wani fanni kuma. Wai shin cajin da aka yi mata ba batune ne rabar da katin Krista neba? me ya shafi wannan da batun wanta? Aida tayi kokarin tayi magana domin ta kare kanta, kai har gwamruwar Victor tayi kokari tayi magana, amma taron cikin kotu suka tsawata masu. Akarshen wannan shara'ar, masu kallo na cewa a tura batun Aida zuwa kotu mafi hurumi inda za a iya bada hoto mafi tsanani. "Akai kotun jama'a! akai kotun jama'a!" suna fadi gaba dayansu.

Aida tana mamakin yadda yan katuna na gaisuwa ya haddasa irin wannan kiyayya a cikin mutanen nan. Su abokai uku dinne suka janye takardar iznin zama a Leningred na Aida kuma aka tilasta korarta daga aikinta. Bayan da shaidu suka yi magana, taron masu kallo basu gamsu cewa hukumci yayi tsanani ba. Suka tashi tsaye suna buga sawayensu akan dabe suna yi wa wannan yar Yarinyar nan da take tsaye a gabansu kururuwa, suna nema a tsananta horon. Domin kare lafiyarta saida masu tsaro suka raka ta ta fita ta kofar baya.

Wannan hukumci da kotu ta yanke, ba a aiwatar dashi ba har zuwa wasu watanni, domin baiwa yan sanda damar zuba ido da karin shaidu gaba da wannan budurwar Krista-ba wai shaidar karya dokar kasa ba, amma shaidar ayyukanta na kristanci.

Aida taci gaba da zama a Leningrad, tana famar neman aiki duk inda ya samu. Rayuwarta ya shiga mawuyacin hali, amma wadannan wahalun duk dandanon abubuwanda ke tafe ne.

## KIN KI KI LASAFTA KANKI DA DOKOKIN MU

Yanzu kuwa, acikin shara'ar ta da ke gudana, da alkali da mai tuhuma suka cigaba da yin tambayoyi ga Aida game da kowane suna na mutanen waje da suka gani, da kowane irin batu da ya wakana.

Na biye kuma, suka shiga batun dab'in takardun Krista da Aida ta rabar. Alkali ya dauki daya daga cikin mujallun da daya daga cikin kayan shaida da aka tara a hankali kuwa ya fara bude shafuka yana neman wuraren da yasa maki. Da ya sami wurinda yake zaton sunfi shigarda ita ga tabbatar yin laifi, sai ya fara karantawa da daga murya, yi layi. A karshen ko wace jimlar magana, sai ya harari Aida, yana kalubalantar ta da tayi bayani ko kuma ta hakikantarda batun,

"Ni bansan batun tsananta wa wasu dariku na masu bi ba, "Aida ta amsa a gajiye Kristan Evengelical da kuma na majami'ar Baptist ne na sani kawai." (Muna rubutu ne game da azabtarwa)

Mai tuhuma ya nuna cewa duk mutumin kasashen waje da ya karanta wannan zai yi tsammanin dukan kristoci na cikin kasar Soviet suna fuskantar tsanani. Sai ya fara daga inda alkali ya tsaya, yana karanta mujallar yana ta tuhumar Aida bisa duk kalmomin da yake kin yarda da su. Sai ya nuna wani sharhi a cikin daya daga mujallun cewa yayan Krista suna fuskantar tsanani a cikin makarantun Soviet. A fadar sa ai makarantun suna kokarin gyara barna da wasu iyaye masu himmar karya suka gurbata tunanin yara da wasu al'adu na banza. "Doka ta hana tilastawa kananan yara wani addini," inji shi yana daga kai yaga ko alkali na biye da abinda yake fadi.

"Amma doka bata haramta tilastarda (Atheism) watau addinin musun cewa akwai Allah." Aida ta may masa.

"Atheism ba addini bane. A bar yaro ya yi girma, sa'annan shi da kansa zai yanke shawarar manufarsa game da wani batu na gaskanta wani abu, ba a tilasta a gayawa yara?" Aida ta tambaya, tana sa idanunta ga duban mai tuhuma da kuma alkali." Doka ta haramta wannan, cewar akwai Allah, amma doka ta yarda ace babu Allah?" babu wanda yace kala, sai alkali ya sauya darasin, sanin cewa bashi da amsar wannan. Sai yace "kada ita mai kare kai ta ratse daga batun gabansu."

Mai tuhuma yaci gaba, yana karanta karin maganganu daga cikin wata mujalla. "Kinsan cewa dole ne ayi rajista na kungiyoyin addini?" ya tambaye ta. "Na sani," kuma Aida tasan cewa ta wurin yin rajista majami'a tasa kanta a karkashin gwamnatin kwaminisanci kenan-gwamnatin da ke musun kasancewar Allahn da majami'a take bautawa.

"Kungiyarku ba suyi rajista ba; saboda haka an hanaku yin taro, amma ba domin akwai tsanantawa ga masu bi a kasarmu ba," in ji shi, tamfar wani malami mara hakuri mai koyar da yan ajin ABCD.

"Kungiyarmu ta nemi tayi rajista," Aida ta amsa a tsanake, "Mun aika da takardar nema, amma aka ki."

"An ki domin baku yarda kubi dokokin kasar ba." "Wadanne dokokin ne bamu bi ba?" ta tambaya. "Kuna neman ku bude Sunday School, kuma kuna so ku shirya ayyukan addini domin kananan yara." "Bazan iya tuna cewa kungiyarmu ta nemi bude Sunday School ba, "Aida tafurta. "Kuma bisa ga doka, iyaye na iya koyarda ya'yansu yadda suke so." "Babu ba zasu iya ba! "Mai tuhuma yafadi. "Doka ta haramta shigarda kananan yara acikin kungiyoyin addinai. Amma kuka ki kubi dokokin kasarmu."

"Bisa ga tsarin kundin kasar nan, muna da yancin bin addini da mukeso. Wannan yana nufin ayi ikirarin laifi zuwa ga ban gaskiya," Aida ta amsa. Ma'anar itace abin yiwuwa ne a shaidawa kowa game da Allah-watau, wani yayi da'awar ban gaskiyar sa ba tare da tsangwama ba. Ba hakane ba?"

Anan Aida tana gabatar da kututun batun shara'ar ta. Tsarin kundin Soviet yace mutane suna da yanci su bada gaskiya kamar yadda suka zaba, kuma su bi ka'idar ban gaskiya tasu. Duk da haka shugabannin Soviet suna tsoron irin ban gaskiya ta Krista, sunfi son dukan amincewa da dogaro na mutanensu ya zama kamar babu mai iya yi musu sai ita Communist Party.

Sharewa da kawar da batun addini, a garesu, zai kai mutane ga amincewa da ita party din ainun.

"Har yanzu ma, alkali ba shi da amsa ga tambayar Aida. Saboda haka yanzuma ya sake sauya darasi, yana cewa, idan batutuwan da ke ciki gaskiya ne, me yasa Aida ta bayar dasu a boye?

"Bisa ga tsarin kundin kasarnan, muna da yancin bin addini da mukeso. Wannan yana nufi ayi ikirarin laifi zuwa ga ban gaskiya," Aida ta amsa. Ma'anar itace abin yiwuwa ne a shaidawa kowa game da Allah-watau, wani yayi da'awar ban gaskiyar sa ba tareda tsangwama ba. Ba haka neb a?"

"Domin su da suka nuna tsanani basa so, duk lokacin da labarin tsanani da suke nunawa ya fito fili aka sani," inji Aida, tana magana tamfar wata lauya, sai kace ba itace mai aiki a masaka ba. "Na sani cewa acikin takardu da na baiwa Miss Jursmar babu wadansu labarin ne karya da gangan. Acikin Herald of Salvation da kuma a cikin Fraternal Leaflets, inda akayi bayani irin halinda masu bu suka ciki, anyi bayanin haka kamar yadda gaskiyar take. Na yarda daku cewa abin babu sha'awa, amma fa wannan itace gaskiyar a zahiri, kuma dole ayi maganar. A lokacin da nake mikawa Miss Jursmar takardun. Na sani cewa yin haka zai iya sa a kulla ni. Na gane da haka. Amma wannan bazai sauye gaskiyar abin da takardun suka fadaba."

"Domin su da suka nuna tsanani basa so, duk lokacin da labarin tsanani da suke nunawa ya fito fili aka sani," inji Aida, tana magana tamfar wata lauya, sai kace ba itace mai aiki a masaka ba.

"Na sani cewa acikin takardu da na baiwa Miss Jursmar babu wadansu labaru na karya da gangan. Acikin Herald of Salvation da kuma a cikin Fraternal Leaflets, inda akayi bayanin irin halinda masu bu suke ciki, anyi bayanin haka kamar yadda gaskiyar take. Na yarda daku cewa abin babu sha'awa, amma fa wannan ita ce gaskiyar a zahiri, kuma dole ayi maganar. A lokacin da nake mikawa Miss Jursmar takardun, na sani cewa yin haka zai iya sa a kulle ni, na gane da haka. Amma wannan bazai sauya gaskiyar ɐbin da takardun suka fada ba."

Mai tuhuma ya dubi abinda ya rubuta sai ya zauna. A karshe dai yiwa Aida tambayoyi yazo. Na farko dai makwabtan tane, da Anatoli da Alla Lavrentiva. Da alkali da maituhuma suka tambayesu: Ko ta taba yi muku magana game da ban gaskiyar ta? "Ko ta taba baku takardu?" "Ko tana da akwatin talbijin ko radiyo?" "Ko tana kashe kudi fiye da abinda take samu? "Yaya take adonta?" "Me take dafawa?"

Tsakanin Anatoli da Alla babu wacce zata ce Aida mai laifice.

"Aida tana shiri da kowa," inji Anatoli. "Batun kirkin ta kansa ake ambata."

Aka kuma kira wani makwabaci aka cika shi da tambayoyi game da tufafin Aida, halinta da aikinta.

A karshe aka kira yar'uwa mai bi, Marja Akimovna Shurlova zuwa kan kuje rar shaidu. Ta san Aida na tsawon shekaru biyar, sun sha yin sujada tare, kuma lokacin da Aida ta fito daga kurkuku na tsawon shekara guda, Marja ta bata wuri ta zauna.

Yanzu kuwa Marja amsa cewar ta taba taimakon Aida.

"Kince an sallami Aida daga aiki domin ita maibice." Alkali ya tambaya." Me yasa ke ba a kore ki daga naki aiki ba? tabbas kina aiki.""Nawa lokacin ne baizo ba tukuna, "Marja ta amsa.

Marja taci gaba da fada cewa bakin waje sun taba zuwa dakinsu da Aida, amma ba ta san ko ta basu ko kuma karbi wani abu ba.

A lokacin da Aida ta tashi tambayar kawarta, ta tambayi Marja game da tsanani da ake nunawa Krista. Murja tayi lissafin Krista da aka yiwa tambayoyi ko kuma yan sanda su ka yi cajin gidajensu da kuma wadanda aka tsare.

"Na sani cewa anci tarar masu bi, "Marja ta shaida. "Anci tarar sukovitsyn...." "Me yasa aka ci tararsa? "Mai tuhuma ya katse tambayoyin da Aida takeyi. "Domin ya yi addu'a" "Ya shugabanci yin addu'ar a gidan Lukas. Ana taro a gurin."

"Yawwa!" inji mai tuhuma, kusan ma ihu yake yi don nasara. Anyi taro a wurin da babu izni. Kuna da gidan addu'a, kuje can kuyi!"

Daga baya kuma, mai tuhuma ya sake shigowa a lokacin da Marja tayi shaida cewa ita ma anci tarar ta domin shiga taron Krista. "A ina akayi taron?" ya tambaya, "A cikin jeji."

"An haramta yin taro a wurare na hukuma shi yasa akaci tarar ku." Ya kadawa alkali kai da dan murmushi na gamsuwa a fuskarsa.

"Ai babu kowa a cikin jejin, mu kadai ne muka yi taron mu muka watse, amma sai aka kama wasu akan hanyar tafiya gidajenmu." Marja ta fadi wasu karin inda yansanda suke yiwa Krista kwarzaba akai akai suna tsare su, daganan sai aka sallameta.

Shaida ta karshe ita ce Yekaterina Andreyevna Bolko, kawar Aida kuma mai bi ce. Ta shaida cewa Aida kawarta ce, ta kuma shaida cewa ita mai kirki ce kuma mai tausayi."

Yekaterina ta fadi yadda yan sanda suka tafi gidanta, suna neman Aida. Hafsoshin nan sun nuna a fili cewa Aida yar leken asirin kasa ce, kuma suka matsawa Yekaterina da sauran makwabta su gaya musu ko sunga Aida a cikin ginin nan.

Yekaterina fa ta nuna afili cewa ita shaida ce da taki jinin masu tuhuma. Wani lokaci ma amsarta yakan zama kalma guda daya tak. Wani lokaci kuma ta zauna shiru bayan anyi mata tambaya.

"Me kika sani game da ziyarar mata daga Sweden zuwa Skripnikova?" mai tuhuma ya tambaya.

"Bansan kome akai ba, washe gari ne na sami labari.

Ya sanda sun zo wurin Aida a gida a lokacin sami wasu takardu a hannun wata bakuwa kuma Aida ce ta bayar."

Mai tuhuma ya tambaye ta game da zurfin karatunta, wanda ya tsaya a ajinta na goma. "Me yasa baki cigaba da karatun ba?"

"Naso na tafi makarantar koyon aikin magani," Yekaterina ta amsa," amma a shaidar takardata sai suka rubuta wai ni Krista ce kuma member ce ta darikar Baptist rukunin masu jayayya (Schismetic) saboda da haka ba za'a bari na shiga makarantar koyan aikin magani ba. Da na shiga ma kora ta zasuyi."

"Kuma ba ki ma kokarta ba? "tana jin muryar yin ba'a a cikin makogwaron lauyan.

"Na sani daga misalin wasu cewa ba zasu bari ba."

Alokacin da dama ta samu ga Aida tayi tambayoyi, sai ta dubi kawarta, tafara da tambayoyin yau da kullum, sannan ta fuskanci batun yadda mulkin Soviet ake kwntatawa Krista, Aida tayi tambaya game da wasu masu bi da yan sanda suka ci tararsu, Yekaterina kuwa ta lisafta su, ta bada bayani game da wasu.

"Me yasa kuke zuwa yin addu'a cikin jeji?" Alkali ya shigo maganar" Kuna da gidan addu'a a Tudun Poklonnaya. Me yasa baku tafi can ba? kungiyarku ba ta da rajista. Kunyi taro a wurin da baku da izni, kuma kuna kawo damuwa a bainar jama'a. Shi yasa aka ci tararku."

"Mun nemi ayi mana rajista, taronmu a cikin jeji bai dami kowa ba a cikin Lavriki.

Mai tuhuma ya tambaye ta, ko ta amince ita yar kasa ce mai biyayya, wadda tayi kudurin kebe dukan dokokin kasar?

"Ina kebe dokokin kasa," Yekaterina ta nace.

"Kuna taro a jeji, kuma a gidan Lukas, kuma kungiyarku bata da rajista," mai tuhuma yana nuna zafin rai, "Watau bakya kebe dokokin kasa." Da karfin zuciya kuwa tayi misali da Lenin, wanda yace dokoki gaba da ban gaskiya abin "Kunya ne."

Ba tare da son yayi musu da wasu kalmomi daga daya daga cikin wadanda suka kirkiro kwaminisanci ba sai ya sallameta.

## MUNZALIN KARAYA

Aide tayi kokari tayi sujadar ta ta ban gaskiyar Krista ba tare da ketare dokokin Soviet ba. Iokacin farkon watannin zamanta Krista, takan tafi gidan addu'a da akayi rajista akai akai. Tana farin ciki da jin dadin yin sujada tare da yan'uwa masu bi-amma ba tareda sanin siyasar da ke cikin majami'u masu rajista ba tukuna.

A yayin da taci gaba da yin sujada da kuma yin hidimomi, sai batun kayyadewa ya fara zafafa mata. Tana hidimar binciken Littafi Mai Tsaki tare da matasa ta kungiyar su, amma aka gargade ta da cewar ta bari domin shugabannin majami'a mai rajista sun fi kula da dokokin kwaminisanci fiye da batun ceton rayuka.

Aida ta tuna da majami'ar gida da take zuwa tare da uwarta. Tana tuna da yadda takanji kasancewar Allah acan, da kuma yadda akan marabci kowa matasa da yara kuma a koyar dasu. Kebe yara daga jin bishara bai yi daidai ba ga Aida, kuma wannan bai saje da koyarwar Littafi Mai Tsarki ba.

Munzalin karaya yazo a lokacin da Aida ta fara aiki a madadin kristoci da ke cikin kurkuku domin ban gaskiyar su. Da farko, nufin ta shine ta saurari labarunsu ta kuma raya wata mahada tayin addu'a da kuma agaji domin su. Su shugabannin majam'iu masu rajista suna da jerin sunayen wadanda suke cikin kurkuku, amma wannan jerin sunayen wai sirri nena kasar, amma ba bayani ne da ya kamata Krista su sani ba.

Ga Aida kuwa ai wannan ne ma abinda ya kamata saura su sani. Ta kaka kristoci a cikin kasar Soviet kuma kewaye da duniya zasu iya addu'oi da bada taimako ga daurarun nan yan'uwa maza da mata a cikin Kristi idan har basu da labarin wahalun da suke sha?

Aida tayi aiki domin samun fitar da magana a waje, kokarin da ya kawo ta gaba da gaba da shugabannin majami'u masu rajista.

Watau batun shine, ta wurin yin amfani da magana kalilan, hukuma takan yi aiki a cikin majami'a daga ciki, ta wurin yin amfani da shugabannin." daga baya Aida tace "sunaso su gabatarda kafa takunkumi da zai taushe rayuwa ta ruhaniya ta majami'a. Kuma, a zahiri sunci nasarar yin haka ainun a shekarun 1960."

Wannan matsayi na shugabanni a mike yana cin karo da kokarin Aida na aika labarin daurarrun masu bi zuwa waje koki, cigaba da zama a cikin majami'a mai rajista kuma kiyi aikin kare kanki, ko kuma, ki hada kai da majami'ar karkashin kasa domin kiyi aikin kare yan'uwa maza da mata dake cikin kurkuku. Jawo ta da majam'ia mai rajista keyi na zahiri ne. Ai dama a wannan rukunin dan'uwanta yake kafin rasuwar sa, kuma tana da abokai da yawa a ciki.

Amma Aida taki ta bi shugabanni wadanda gashi afili sunfi nuna damuwa da izinin gwamnati maimakon yan'uwansu Krista da ke cikin kurkuku. Sai ta bada dukan karfinta da kokarinta ga majami'ar karkashin kasa, da sanin cewa zata ji ajikinta domin wannan shawara data yanke.

A ranar hudu ga watan Yuni, 1962 sai aka buga wani labari a Smena, wata jarida bakin gangar gwamnatin Soviet. Kan maganar labarin shine "Kada ka zama gawa a cikin rayayyu" na neman karyata akasarin masu bi na majami'un karkashin kasa musamman. Manufar gwamnati ita ce babu Allah, kuma wannan labarin yayi wa wadadasuka yi shawarar bin wani abin da suke zato mai kyau ne tare dayin ba'a da gori.

A lokacin da Aida ta ga wannan labari, sai ta fara shirya maida murtani, na kariyar ban gaskiyar ta da na wadan da ke masu bi. Sai ta aika amsar ta zuwa Smena, amma kuwa suka ki su buga.

Da anan batun zai tsaya, amma sai Aida ta nuna wa masu bi jaridar Smena din da kuma amsar da ta aika, sukayi sha'awa suka nemi a basu sukai gida, ba da jimawa ba kuwa aka buga da yawa, kuma aka rabar daga mai bi zuwa mai bi, ako'ina cikin kasar Soviet. Mambobin majami'ar karkashin kasa sukayi mamakin karanta irin wannan tsokana akan ban gaskiyar su, kuma suka karfafu ga karanta amsa mai ma'ana da daya daga cikinsu ta bayar.

Sai ga Aida a shafin farko na Zamizdat, wani sabon yayi na dab'in takardu da kasidu.

Hukumomin gwamnati ba zasu iya duba kowace madaba'a ko na'urar buga takardu, ko daukar hoto na ko ina a cikin kasar Soviet ba.

Ta wurin rubuce rubucen ta Aida Skripnikova ta zama sanan niya ga dubunan masu bi da bata ta ba saduwa da sub a. kuma sanin ya shahara ta wani fanni da kuma tsakanin yan sandan sirri.

## KUTUTUN ASALI

An shirya wasu da zasu bada shaida a shara'ar Aida, amma basu zo ba. Amma duk da haka alkali yace a cigaba.

Aida tana jin takaici, tana cewa kotu ta kasbe lokaci mai yawa tana shiga batun gidanta, tufafinta, har da irin dafuwar da take yi maimakon duban tushen dalilin wannan shara'a.

"Ina rokon kotu tafi maida hankalinta akan kututun asali na wannan shara'a," tayi roko. "Misali, ina da bukatar yin bayani game da dalilin da yasa ba a yiwa kungiyarmu rajista ba. Na farko, gaya mani, wace doka muka karya, da zai hana ayi mana rajista?"

"Ke mai kare kanki, ce" alkali ya amsa, "Kotu ce mai yi maki tambaya, ba kece zaki tambayi kotu ba."

Da ganin yadda alkali ya bata rai, abin so ya samu kenan ga mai tuhuma sai ya fado ciki, ni ban ma gane abinda take tambaya ba." Aida taja dogon numfashi, ta natsu." Ina tambayar kotu da ta fi maida hankali ga tambayoyin da sukafi wajaba da wannan tuhuma, kuma bai kamata maganganun da ba su shafi batun ba su sha kan ainihin asalin shara'ar da kotu take dubawa. Rokona ne farko kenan. Na biyu shine domin rokon ka, da kotu domin sanin rana takamaimai da aka kwace takardar izni na na zaman Leningrad."

Alkali ya tambaye ta ko menene muhimmancin sanin wannan rana. Aida tayi bayani cewa shara'ar ta nuna cewa yan sanda na tara bayanai game da ita da jimawa kafin takardar izinin zame nata yakare. "Idan ana yi mani shara'a game da takardar izini na, amma ba domin ayyuka ne na Krista ba, to me yasa ake bincikata kafin izinina yakare?" ta tambaya.

"Ina iya gaya maka dalilin da yasa ake tuhuma ta," ta cigaba. Sau biyu ina magana da baki daga waje a gun addu'armu, ina tambayar su bani Littafi Mai Tsarki. Wadannan tambayoyi guda biyu suka shiga kunnen hukuma."

"Batun takardar izini bashi da halaka da wanan shara'a, "inji alkali. "Ana tuhumar ki da laifin raba labarun karya domin yiwa dokokin gurguzu na kasar Soviet jafa'da gangan."

"Amma ai tambayoyi game da aiki da takardar izinin zama su akayi ta baiwa hankali a cikin wannan shara'a," Aida ta amsa.

Kotu tayi sha'awar yin wadannan tambayoyi, ba domin za'ayi cajin ki akai bane, amma domin dole ne kotu ta auna kwarjinin shugabancinki.

Mai yiwuwa sabon abu ne a gareki kotu ta tambayi yaya halinki yake, Lallai ne kotu tasan wace irin mutum kike. A wajen yanke shara'a kotu takanyi la'akkari da irin kwarjinin mai kare kai."

Aida tace, idan dai da gaske kotu tana son sanin halinta, to ashe abu mafi muhimmanci shine kotu tasan tushen gaskiyar batun labarinta.

Rokon ta na karshe ga alkali shine akira shaida daya na karshe, Miss Jursmar, yar Sweden wacce ta baiwa takardu. "Littafin hannu na wannan mata anyi amfani dashi domin yin shaida gaba dani." Aida tayi bayani, amma idan zamu fahimci abinda ta rubuta sosai sai a gayyace ta tayi bayani.

Alkali ya nuna alamar saurarorn wannan tambaya tata, yana neman ra'ayin mai tuhuma, sai ya zartar: Bayan neman shawarwari kotu ta zartar cewa rokon mai kara bai karbu ba."

An kara yin wasu yan tambayoyi kafin kotu ta rufe a wannan ranar. Abinda kawai ya rage shine muhawarar karshe. Ga mai tuhuma kam zai sami damar kare tsarin gudanarwa ta gwamnatin Soviet, zai yi bayanin cewa a halin gaskiya Krista suna da yanci na ban gaskiyarsu, idan suna yarda da bin dokokin kasar.

Ga Aida kuwa, wannan zai zama damarta ta karshe, zarafi na karshe na tayi magana domin kare kanta da kanta, kuma a madadin yan'uwa maza da mata na majami'a. Tana jin nauyin wannan batu da ke gabanta, da sanin akwai kasadar sake kulle ta, amma tana karfafa ta wurin kwantar wa da zuciya da Uba na sama yake yi mata.

## KOKARTA "SAKE-ILMANTARWA"

Ga Aida kulle mutum ba zancen banza bane. Ta dandana can baya. Bayanda kotun Comrades suka janye takardar izinin ta a shekarar 1963, ta dauki lokaci tana ziyartar yar'uwarta a Ukraine, inda tsayayya da karfin zuciya na masu bi acan ya burge Aida. Ta dawo Leningrad da sabuntar karfin hali. Yan sanda suna zuba mata ido, amma Aida ta shiga birnin. Shiga babu takardar izni yana iya sa a kamata, amma duk da haka taci gaba da aikinta na Krista.

Aida da abokanta suka cigaba da taruwa a jeji a bayan gari domin su kubuce kamu kuma anan cikin jeji a shekarar 1965 aka yi mata kamu na farko, tana yar shekaru ashirin da biyar.

"Yan sanda sun iso kuma suka fara bin mu a guje," wani ya bada shaida daga baya. "Sun tura mu sun kama mu a gashi. Suka kwashi mutane, da yawa; akaci tarar wasu, wasu kuma aka daure sati biyu biyu."

Aida tana daya daga cikin kamammu, sai yan sanda suka shirya ayi shara'a Acikin takarda, cajin bai shafi addini ba koda shike an kamata ajeji ba cikin birni ba, amma aka tuhumeta da rashin takardar izini na zama a cikin birnin Leningrad.

A wannan shara'ar, a cikin wani karamin dakin taro a cikin ginin Rayon Court. Ba a ma baiwa Aida damar yin magana ba. Wannan shara'ar ga ta ga irinta ne kawai, suna kokarin nuna adalci inda babu shi sai suka karanta hukumcin da aka zartas, hukumcin shekara guda a kurkuku.

Wannan hukumcin bai tsoratarda ita ba. Ta kanyi sujada akai, akai tare da yan kurkuku masu bi, kuma dayawa ma ashirye suke su shiga kurkuku idan har zuwa can ne Kristi ya jagorance su. Yanzu kuwa nata lokaci ne.

Manufar zuwa kurkuku ga tunanin shugabannin Soviet shine wai domin sake-ilmantar da fursuna. "Wadannan talikai an batarda su." Haka ma'aikatan hukumar ke fadi,

"yanzu kuma dole a nuna musu kuma su rinjayu da gaskiya da kuma ikon tsarin gudanarwa ta Soviet: Uwa ma bada mama, kasa mai daukaka."

Biye da darusan sake ilmantarwa mai cin rai. An tilasta wa Aida ta kwana a cikin mugun sanyi, akan daben siminti. Basu taba samun isasshen abinci ba, kuma wanda ke akwai watarana baya ma dacewa da a baiwa dabba. A lokacin tsare ta har an tilasta mata shiga asibitin mahaukata. Bayan bincike na kwanaki kuma aka dawo da ita a kurkuku. Watanni da tayi a mugun gurin nan ya kara kunci ainun ga wannan yarinya mara tsoron yin magana mai tsattsaurin ra'ayi.

Aida fa bata dauki sake ilmantarwar Soviet ba, maimakon gurgunta amincin ta wannan al'amuri kara karfafa ta yayi. Maimakon hana ta shaida bishara, ta bar kukuku da kara jin marmarin shaida gaskiya ta Yesu.

Yanzu kam tasani sarai ko menene sakamakon yin haka, amma bata taba ja da baya ba.

## "GWAMNATI BATA SA BAKI"

Yanzu lokaci yayi na mahawarar karshe game da shara'ar Aida ta biyu. Gabatarwa ta farko ta mai tuhuma ne, kuma ya zabi da ya fara da ambatar wasu daga cikin tarihin majami'a a kasar Russia.

"Bayan da akayi babban juyin juya hali na Mulkin Gurguzu ta Oktoba anan kasar mu, sai aka ware batun majami'a daga kotun gwamnati, kuma dukan masu bada gaskiya ga addinai dabam dabam suka sami dama ta yancin ban gaskiyar su." yana fada ji-ji-dakai. Amma daganan sai mai tuhuma ya shiga baiwa Kristocin Evangelical da Baptist da majalisar majami'u laifi wai suna karfafa masu bi da su kangare wa dokokin kasa.

"Su kungiyoyin da ke goyon bayan majalisar majami'u basu da rajista," mai tuhuma yayi caji. Tararrukan su marasa

izni suna faruwa ne a cikin gidaje wurare na jama'a. An yiwa wasu masu bi hukumci karya dokar da hana shigowa da bakon addini. Majalisar majami'u takan gabatar da wannan cewa ana nunawa addininsu tsanani. Majalisa majami'u tasha faman gwagwarmaya da hukuma har na tsawon shekaru bakwai."

Daga tarihin majami'a da sauransu game da masu bi, sai mai tuhuma ya fuskanci ainihin batun shara'ar Aida. "Skripnikova tana da mahada ko ina acikin kasar, amma muhimmin aikin ta shine na shirya sadawa da kasashen waje. Lallai ne anan muce ta kuwa nuna iya yin haka sosai," yana gatse.

Daganan kuma sai muryarsa ta zama da dama dama. "Rayuwar Aida ya fara ne da rashin sa'a, domin kuwa an haifeta ne a cikin iyalin Baptsit anyi rashin sa'a ne, da muka bari ta kubuce mana, amma munyi wa Aida magana ainun kuma muka bayyana mata batun halin tana kiyayyar jama'a a fili."

A yayin da yake karasa kalmominsa, sai muryar sa ta fara fitowa yana kara yin magana da karfi, na farko ya ambaci takardun da aka samu a gidan Aida. Daya daga cikin sharhi na takardar ya ambaci wani wai shi Kryuchokov cewa a wajen shara, arsa a Moscow, "Su yan'uwa dake cikin kurkuku da sansanai ba suna shan wahala ne domin sun karya dokokin Soviet ba; suna wahala ne domin sun dage da yin ban gaskiyasu ga Ubangiji!!

Mai tuhuma ya kada kai don bakinciki." Dukan wadannan maganganu ne na yin karya da gangan domin yiwa gwamnatin Soviet jafa'i, kuma babu wanda aka azabtar domin ban gaskiyarsa. Gwamnati bata sa baki a sha'anin kungiyoyin addinai idan basu ketare dokokin hana shigo da addinan kasashen waje ba. Saboda haka laifin Skripnikova mai kare kanta na raba takardu akai akai dauke da labarun karya da ke yiwa gwamnatin Soviet da dokokin jama'a jafa'i ya tabbata. Wadannan batutuwa suna kunshe a sashe na

190/1 na tsarin karya dokokin kasa. Saboda haka ina roko cewa kotu tayi wa mai kare kai horo, Aida Skripnikova na daurin shekaru biyu da rabi a cikin kurkuku."

Da wannan, sai ya zauna, yana wani shan-kanshi na gamsuwa a fuskarsa.

## "GA KRISTA HANYA GUDA DAYA CE KAWAI KE AKWAI"

Alkali ya juya wurin Aida, ya nuna mata cewar yanzu lokacinta ne na gabatarda kariyar ta.

"Ina da niyyar nayi magana game da gundarin cajin da ake tuhuma ta dashi," ta fara, muryar ta sarai kuma ga tsanaki. "Amma wasu tambayoyi ma sun shigo ciki, saboda haka suma zan ji dasu, ko da shike, kamar yadda aka fadi, basu da halaka da wannan shara'a."

Ta fara da nuna kin yarda da wasu kananan batutuwa da mai tuhuma ya kawo, kamar wasikar da ta rubutawa Pravda a 1958 zuwa aiki da tayi a dakin bincike na wata ma'aikatar gine gine daga baya. Sa'annan ta fara fuskantar bututuwa mafi muhimmanci.

"A lokacin da nace an kore ni daga aiki na domin ban gaskiya ta, an gaya mani cewa, "wannan magana ce ta yin karyar ganganci," Amma ga abinda ya faru; Bayan shikata daga kurkuku na sami aiki a wata madaba'a. Bayan mako guda da fara aiki, ina wajen taron addu'a lokacin dayan sanda suka zo suka dauki sunayen mu. Na sani zasu kai rahoton a wajen aikina, "Inji Aida.

Kowa da kowa na cikin madaba'ar sunyi mamaki da jin cewa ni mai bi ce, sai suka fara gayamani, tun daga farko, idan ban canja ra'ayi naba, za a koreni. Basu boye gaskiyar wannan batu daga gareni ba. Sun gaya mani a fili: Madaba'ar ma'aikatace ta siyasa. Ba kowa ne zaiyi aiki a ciki ba! Sun fadi haka ko da shike wannan madaba'ar tana karkashin gudanarwa ta hukumar jiragen kasa ne, kuma babu wani abin sirri da ake bugawa a gun sai takardun cikawa na jiragen kasa, izinin shiga jirgi da takardar tsari na tafiye tafiyen jirage.

Bansan me ke wurin ba da baza a iya amince ni dashi ba," ta cigaba.

"Abubuwa suka yi ta tafiya a haka har mako uku. Sa'annan aka kirani zuwa ofishin manaja akace mani an koreni daga aiki. Lalle kam ai ba zasu fito fili suce sun koreni domin addinina ba, domin babu wata doka irin haka da ta yarda a kori mutane domin addininsu. Saboda haka suka koreni da hujjar cewa ana rage yawan ma'aikata. Lokacin da na tafi hawan bene na layin kantuna nace musu an sallameni daga aiki domin rage ma'aikata, ma'aikata sunyi mamaki domin daya daga cikin injunan dab'i ya dade a tsaye domin karancin ma'aikata.

"Manaja ya gaya mani, 'Ba zamu iya daukan ki ba domin iznin zamanki bai hada da cikin birnin ba-sai kace da farko basu ga cewa ina da takardar a haka ba, kuma kamar ma shi manajan bai duba takardu naba can baya."

Aida ta gayawa kotu cewa, da yake yan sanda sun fara yi mata tambayoyi, ta sani cewa ba za'a jima dayawa ba kafin su sake kamata. "Watanni shida kacal suka wuce tunda aka sake ni, kuma inaso inyi abubuwa masu amfani kafin na sake komawa cikin kurkuku. Ina da aikin dazan kammala."

Ta ja dogon numfashi. Bada kariya ga wannan shara'a abu ne mai gajiyarwa; yana bukatar zura ido na hankali, na sosuwar rai da na ruhaniya wanda yake mai wuya ne a jure na dogon lokaci. Sai ta roki alkali hutun lokaci na minti goma, alkali ya yarda.

Lokacin da aka dawo, Aida ta yi batun ta musamman ma game da rabarda kowane irin takarda da kanta ba laifi bane, kuma idan tuhuma bata sami bayanin karya na ganganci a cikin mujallar Herald of Salvation da Fraternal Leaflet ba, ba zai yiwu a sami hujja na shar'anta niba. "Saboda haka wajibi ne nayi magana game da abinda suka kunsa aciki."

Sai tayi magana akan wani haramtaccen taro na krista da shugabannin Krista da'aka yi a cikin mujallar da ta bayar.

Dokar 1929 ta ce masubi suna da damar su shirya taro," Aida tace amma maimakon a bada izni, hukuma suka fara tsanantawa wadanda suka nemi iznin yin taron.

Na biye, wanda ya gabatarda bincike ga mai tuhuma ya tsamo kalmomi guda goma sha bakwai da ke iya jawo hargitsi a cikin mujallar. Bisa ga mai binciken, wadannan kalmomi suna dauke da labarum karya na ganganci kuma na yiwa kasar Soviet da dokokin mulkin gurguzu jafa'i"

Yanzu kuwa sai Aida ta juya ta fuskanci alkali. "A lokacin da take bada shaida, Miss Boiko ta fara fadar abinda Lenin yace; zan karasa abinda ta fara fadi: A cikin Russia da Turkiyya kadai ake samun dokoki masu bada kunya da suke aiki har yanzu wajen gaba da wasu addinai. Wadannan dokoki sukan hana fitowa fili ayi addini ko kuma su hana yadawa. Wadannan dokoki mafiya rashin adalci ne, abin kunya ne kuma ga danniya. Yanzu kuwa inaso in jawo hankalin kotu game da wannan kalma farfaganda. Lenin da kansa ya kira hana farfaganda na ban gaskiya rashin adalci kuma abin kunya."

Ta sake jan dogon numfashi, kuma ta cigaba. Yanzu zan gaya maku yadda aka kama ni. A ranar Afrilu II na tafi taron addu'a. sai na lura cewa ana bi na amma ban bashi muhimmanci ba.

Amma washe gari, sai gayan sanda gidana kuma suka kamani. Kuma an binciki gidajen wasu masu bi. Game da shara'ar ta kadai anyi binciken gida sau goma sha daya: sau uku a Leningrad, sau hudu a Perm, sau uku a Kirovograd, kuma sai daya a gidan yar'uwarta a Magnitogorsk. Ana iya fahimtar binciken da aka yi a gidana da gidan yar'uwata. To amma menene dalilin cajin gidajen masu bi? An cajesu ne kawai domin an karanta a direshinsu acikin littafi hannu nawa. kuma adukan wurare nan basu sami kome ba da ya shafi wannan shara'a.

Na biye kuwa Aida ta shiga batun "abinda yasa ake yimana tsanani domin ban gaskiyar mu, amma ana gaya mana cewa

wannan labarin karya ne na ganganci, ana muku shari'a ne don ketare dokokin Soviet. Ni mamba ce ta kungiyar da bata da rajista, wacce ta nemi ayi mata rajista, dukan kungiyoyin mu sun aika da takardun nema, har ma hade da tsarin dokokinmu-kuma a yayinda muka yi haka, ba a gaya mana, "Kada kuyi kaza da kaza; doka ta hana: Maimako, sai ace mana. Ku sa hannu a takarda kuyi alkawarin ba zaku ketare doka ba, wannan ba shine ka'ida mafi daidaita na yin rajista ba.

Aida ta lura da cewar alkali ya fara nuna damuwa, saboda haka sai tayi sauri domin ta karasa bada kariyarta. "Masu bi ba zasu iya yin alkawarin kebe dokar da ta hana su suyi magana akan Allah ba, kuma su hana iyaye kawo ya'yansu zuwa ga ban gaskiya. Da dukan yarda da kebe dokokin hukuma, babu iyaye Krista da zasu taba yarda da dokar da ta umurcesu su girmadda ya'yansu su zama masu musu cewa babu Allah (Atheists). Sun gwammace su sha kowace irin azaba da kakeso sun gwammace tsayawa a gaban alkali maimakon yin alkawarin yarda da irin wannan doka.

"Kristi yace muyi bishara ga kowane mahaluki," Aida ta cigaba," kuma masu bi ba zasuyi na'am da wata doka da take haramta musu yin magana game da Allah da kuma game da ceto ba. Babu wani tilon mai bi da zai yi haka. Ko da shi ba mai aikin mishan bane ko kuma mai bishara, ko da shi wani ne da bazai saurari irin wannan doka ba domin ko bai iya wa'azi ba, zai iya samun wata dama watarana ya gaya wa wani maganar ceto. Saboda haka masu bi ba zasuyi alkawarin bin irin wannan doka ba sam. Kome yawan darajar da suke baiwa hukuma, wannan doka kam karya ta zasuyi.

Zan sake maimaitawa: Masu bi ba zasu yarda da dokar da ke tilasta musu suyi musun bishara ba. Shi yasa idan akayi mana shara'a domin karya wannan doka, mukan gamsu da cewar ana hukumtamu domin ban gaskiyar mu.

Nasani cewa Herald of Salvation da Fraternal Leaflet basu dauke da wasu labarum karya na ganganci.

Amma a lokaci guda, nasan abinda ake nufi idan aka aika su kasashen waje. Na sani akwai hadari, shi yasa nake aikawa da kaina."

Aida ta dan tsaya ta, tattara karfinta domin shigarda kalamunta na karshe, kalamu da take fatar bari dasu wadanda zasu yanke mata shara'a. "A wani lokaci mutane sun lura cewa babu adalci a hanawa mutane yada addininsu, yanzu kuma basu gane wannan ba. Yanzu cewa suke ka yarda da kanka kayi addu'a, amma kada ke kuskura kayi wani batu game da Allah ga kowa. Danne akidar wasu da karfin dole bata zama cin nasarar akida. A kullum ana kiran irin wannan baubauci.

Alkali ya katse mata magana, ya gaji cewar wai wannan mai laifi tana yin wa'azi acikin kotu. "Ba maganar majami'a ya kamata kiyi ba; kiyi magana a kanki kawai," inji shi yana nuna ta da yatsa.

Aida fa bata daddara ba," Ga Krista kam hanya daya tak ne akwai," ta fada, babu abin da Krista zaiyi illa ya ki yarda. Da zarar kasan gaskiya, to fa ma'anar ita ce bin wannan gaskiya, in ma ta kama a sha wahala domin haka. Ba zan iya zama dabam ba, bazan iya aikata wani abu dabam ba. Ina kaunar yanci, kuma ina kaunar zama tare da iyalina da kuma abokaina. Amma bazanso nayi abinda ke cin karo da lamirina ba. Menene amfanin yanci'a gareni idan har bazan iya kiran Allah Ubana ba? Sanin cewa tunani na da ruhaniya ta suna cike da yanci yana karfafa zuciyata da kuzarina kuma. Shikenan abinda nakeso na gaya maka."

Aida ta zauna gama ta gabatarda batunta kuma zuciyarta ta kwanta.

Bai ma kula da abinda ta fada ba kuma ma bai rinjayu da kalamu masu ma'ana da tayi ba, alkali ya daure Aida shekaru uku a kurkukun Soviet, hukumcin da ya zarce wanda mai tuhuma ya shawarta da wata shida. Aida tabar kotu a tsakanin wasu dogayen masu tsaro guda biyu.

Amma kulle ta bai iya hana aikinta ba. Kamar yadda ya kamata kuwa, saida aka dauki labarin shara'ar Aida yadda ya dace a hankali cikin mawuyacin hali akayi ta rubutawa a jikin kyallaye daya daya har guda ashirin da akayi ta yankawa daga jikin zannuwan gado da yaduna makamanta, sa'anan akayi fasa-kwaurin fitarwa daga kasar Soviet. Masu bi ko ina a duniya suka karanta labarin "Aida ta Leningrad" suka yi ta yin addu'a domin wannan yar'uwa mai cike da ban gaskiya.

Aida ta fito daga sansanin gwale gwale na fursuna a watan Afrilu goma sha biyu, 1971. Bayan fitowar ta, ma'aikatan suka gaya mata wai bata koyi komai ba daga horon da ta sha. A halin gaskiya ta koya dayawa, amma ba abinda masu kamata na Soviet suka so ba. Ta cancanci digirin digirgir na ban gaskiya ga Allah, kuma taci ribar fahimta na kwarai na farin ciki mai zurfi da gamsuwa wanda yakan zo daga yi masa bauta. Ta zama cikakkiyar mamba a cikin yan'uwantaka da Bulus Manzo yake kira "Zumunci nashan wahalarsa".

A yau, Aida Skripnikova tana zaune a St. Peterburg. Ban gaskiyar ta ya rayu gaba da mulkin wannan gwamnatin da tayi kokarin rushe ta. Yau, doka ta yarda Krista kamar ita su taru domin yin sujada da kuma yin wa'azi. Kwanaki majami'arta sun taru domin yin bukin shekara ta arba'in da kafa ta da kuma tuna taimakon Allah ga mambobinta. Akayi nuni na musamman domin girmama wadanda aka shahidantar domin ban gaskiyarsu.

# *Sabina:*

## Wata Shaida Ta Kaunar Kristi

*Romania:*

*1945*

Mutanen Russia sun kori yan Nazi daga cikin Romania, a yanzu kuwa suna daukan matakai na kawo kome na al'amuran gwamnatin Romania a karkashin ikon su. Kokarin su na farko shine su tara dukan malaman addinai zuwa taro; Russia suka sa wa wannan taro na addinai suna" Taron MajalisarAddinai."

Manufarsu ita ce na samun goyon baya daga shugabannin addinai. Amma ga Sabina kam wannan ba wani abu neba illa wayo na samun shankan mutane domin su sami yin iko su maida shugabannin addinan na Romania su zama kayan aiki kawai na gwamnati.

Sabina macece mai karamin jiki, Richard mijinta ya fita da tsawon kafa daya da rabi, amma tana da gagarumin kauna domin Kristi. A zaune a gefen Richard a wajen taron kuma tana jin wani pasto yana bada kansa a fili ga kwaminisawa da suka mamayi kasarsu ta gado. Sabina ta dunguri hannun mijinta, ba zaka tashi ka wanke wannan kuniyar daga fuskar Kristi ba, Richard? Tana rokonsa. "Lallai ne kace wani abu, suna tofa wa sunan Kristi miyau!"

Richard ya dubi taron da ke cike a cikin ginin majalisa. Abin babu dama. "Cikakken yancin gudanar da addini!" shine taken da kwaminisawan suke shela. Suna yakin neman zaman tare tsakanin Allah da maigirma shugaban majalisa, Joseph Stalin. "A yaudari duniya ba abu ne mai wuya ba". Richard ya yi magana a hankali.

Richard da Sabina suna cikin taron nan na wajen mutum dubu hudu, da bishop, bishop da pastoci, firis, firis, da rabbi rabbi, da mulawa duka an cika wurin zaman yankallo da kasan ginin gaba daya. Musulmi da Yahudawa, Protestant da masu ra'ayin rikau watau (Orthodox) an sami wakilincin dukan addinai.

Har ma sai da akayi sujada aciki kafin afara taro. Shugabannin Kwaminis suka zagaya sukayi gaisuwa da manyan shugabannin har suka sha hannu da babban Bishop, Sa'annan aka fara. Petru Groza da aka sani cewa dan amshi ne kawai na Moscow, ya yi bayani cewa sabuwar gwamnatin Romania tana cike da goyon bayan ban gaskiya ta addinai, kowane irin addini, kuma zasu cigaba da biyan limamai, kamar yadda ake yi a da. Alhali na dai, za'a kara musu kudi! Akayi tafi da jin haka.

Bayan da Groza yayi magana, firistoci da pastoci suka amsa. Daya bayan daya suka nuna farin cikin su game da amincewarsu da batun addini.

Gwamnati zata iya yin dogaro da majami'a idan har majami'a zata iya yin dogaro da gwamnati. Wani bishop ya furta cewa siyasu kala-kala sun sha neman hada kai da majami'a a cikin tsawon tarihin ta. Yanzu kuma launin ja zai shigo, sai ya nuna farin cikin sa. Kowa na murna. Kuma aka watsa nuna farin cikinsu ta sautin rediyo ga dukan duniya nan take daga dakin taro.

"Yayi" inji Richard, "Zan tafi gaba nayi magana. Amma idan nayi, to ba bu sauran maganar cewa kina da miji."

Sabina tasan gaskiya yake fada kuma su sauran

shugabannin ạddinai da ke Magana a cikin tsoro ne na me zai faru da iyalinsu da mukaman su da albashinsu. Amma kuma tasani cewa ya kamata wani ya yi karfin zuciya ya fallasa kwaminisawa maimakon cika iska da kalmar baka da karairayi. Ta daga kai ta dubi Richard a idanu, sai ta amsa, "Bani da bukatar matsoraci a zaman mijina."

Richard ya kada kai shiru. Ya cika kati na samun damar yin magana ya aika can gaba kwaminisawa suka yi farinciki. Pastor Richard Wurmbrand, Limamin Krista daga Lutheran, sananne a ko ina cikin kasar, kuma wakilin majalisar majami'a ta Duniya, yanaso yayi wa taro magana. Yanzu kam suna samun cigaba!

## LOKACI NA NUNA KARFIN ZUCIYA

## DA FADAR GASKIYA KUMA

Da Richard ya kama hanya zuwa gaba domin yayi magana sai wuri yayi tsit. Sabina a lokacin kuwa ta shiga yiwa mijinta addu'a.

"Godiya gareku domin wannan dama ta haduwa tare kuma ayi magana acikin yanci,"

Richard ya fara, "A yayinda ya'yan Allah suka taru mala'iku ma sukan taru domin jin hikimar Allah. Saboda haka hakin kowane mai bi ne kada yayi wa mutumin duniya yabo ko kuma, shugabanni mu yabi Allah mahalicci da Kristi mai ceto, wanda ya mutu akan giciye domin mu." Gaba daya cikin dakin taro ya fara sau yawa zuciyar Sabina kuwa cike yake da farinciki. A karshe, sại ga manufarsu ta furo faganda ta kwaminisanci ya zama ta Kristi.

"An dakatarda damar da aka baka ta yin magana!" Burducca, limanin addinin al'adu ya zabura ya tashi tsaye.

Richard, yaci gaba da karfafa abokan aikinsa shugabanni da su kafa yardarsu da biyayyarsu ga Allah, ba ga mutum ba.

Taro kuwa suka fara yin tafi. Sun sani Richard yana da gaskiya, amma shi kadai ne mai karfin zuciyar fadan abinda ya kamata a fadi.

"Katse abin maganar!" Burducca yayiwa yaransa tsawa. "Ku kawar da mutumin nan daga kan dakali. Yanzu!" muryar Richard tayi shiru, saifa taron gaba daya suka fara cewa," Pastorul! Pastorul!" sai fa taronya hargitse, albarkacin haka kuwa ga Richard sai ya sulale ta baya ya fice kafin ma wani ya tareshi.

Sabina kuwa ta zauna shiru tana kallon abinda ke faruwa. Tana alfahari da karfin zuciyarsa na tashi tsaye domin Kristi. Amma wannan alfahari yana kuma kunshe da juyayi a yayin da ta fara yin tunanin sakamako da zai biyo baya na mijinta da yayi magana gaba da su Russia.

A kullum Sabina da Richard suna da zuciyar tallafawa mutanen Russia. Sukan yi maganar aika ma'akatan mishan na Romania zuwa Russia domin yin wa'azin bishara. "yazu inji Richard da Sabina Allah ya kawo mutanen Russian a garemu.

A lokacinda mutanen Russia suka fara sauka a Romania da kakar 1944, da Richard da Sabina yar shekaru talatin da daya, sun fita domin su karbe su da furanni da kasidun bishara a zaman. Yahudawan Romania dakansu biyu sun sha wahalar da ba a iya misaltawa a hannun yan Nazi. An kashe dukan iyalin Sabina a cikin sansanin gwale-gwale, kuma an taba kama Richard har sau uku. A lokacinda Sabina da Richard suka fara zama Krista, sun bada kansu suyi aiki a tsakanin batattu, ko da wane irin zunubi suke yi. A shekarar 1944 wannan ba da kai yakai su ga isa ga yan Nazi masu tserewa da kuma yan kwaminis masu sababbin shigowa.

A zamanin mamayar yan Nazi, Sabina da Richard sun boye Yahudawa da yawa masu kokarin tserewa a gidansu. Sa'annan kuma a lokacin da yan Nazi suka zo tsarewa, suma an boye su. Daya daga cikin sojojin Nazi da suka taimakawa, ya tambayi Sabina me yasa Bayahudiya zata boye abokin

gabarta dan Nazi? Sabina ta gaya masa a saukake cewa ita ba ta da abokin gaba kuma Allah yana kaunar dukan masu zunubi. Yayi mata godiya tare dayimata alkawarin cewa indai har Nazi suka sake kwace mulki suka dawo to zai sa ta acikin kurkuku.

## SAYEN LOKACI

A lokacin rani na 1944, Sabina da Richard sun mori yin sujada cikin yanci na wucin gadi. An tafi da tsoho mai mulkin kama karya na Romania, Ion Antonescu zuwa Moscow sa'anan aka dawo dashi aka harbe. Shugabannin majami'u masu ra'ayin rikau wadanda suka yi amfani da zalunci akan Yahudawa da Protestants a yanzu kuwa mulkin danniyan nan tasu ta innanaha ta kau.

Yawancin Romaniyawa suna zaton cewa a karshe gashi sun sami gwamnati mai dimokradiyya, amma ga Sabina kam ba haka take ba.

Bayan wannan babban taron Al'adu babu wani hari na hukuma gaba da Richard, amma jim kadan sai yan kanzagin kwaminis suka fara zuwa akai akai domin fasa taron sujada a majami'u da yake shugabanta. Daga mako zuwa mako wasu matasa marasa kamun kai sukan turo kansu a bayan majami'a su dinga yin feduwa, suna ba'a kuma suna tura magana ana cikin sujada.

Daganan fa sai suka fara samun gargadi na farko. Sabina tana aiki a majami'a tare da Richard wata rana sai wani farin kaya yazo yayi magana da mijinta.

"Ya gabatar da kansa cewa shine Inspector Riosanu" "Kaine Wurmbrand? In hakane to kaine mutumin da naki jininsa a rayuwa ta." Da Richard da Sabina suna kallonsa da mamaki." Amma domin a nuna maka babu wani jin haushi," yaci gaba, "Nazo ne don na dan sanar dakai.

Akwai babban fayil cike da rahoto game da kai a

Shalkwatar yan sandan sirri. Na gani. Wani yana bada rahoto akanka kwanakin nan. Kasha yin Magana da yan Russia da yawa, ko ba haka ba?"

Sai ya tafa kakkausun tafin hannayensa masu kama da samfefa tare yace. "Amma sai nayi tunani ko zamu iya yin yarjejeniya." Idan za'a iya bashi cin hanci, yace zai iya lalata takardun yabatar dasu.

Sai Sabina ta shiga maganar, sai suka yarda akan wani farashi. Ya cusa kudin a cikin aljifun sa, Riosanu yace, kasami sauki. Maikai musu rahoton shine"

"A'a," Sabina ta shigo da sauri. "Ba maso musani." Sai Inspector ya dubi wannan mata mai karamin jiki da doki. Amma Sabina ta girgiza kanta. Ta sani basu da bukatar sanin ko wanene ke bada rahoto akansu. Idan har suka san kowanene neshi, mai yiwuwa su nuna masa kiyayya-zunubin yin haka kuwa zai zauna a kansu.

Haka kuma, Richard da Sabina sun sani cewa wannan kudi da suka biya ba zaisayo masu zaman lafiyarsu ba. Wannan a hannun Allah yake. Amma watakila sun saya wa kansu wani dan lokaci da kuma wata daman samun kafa majami'ar karkashin kasa

Wajajen karshen 1947 ne aka fara kama Krista akai akai, kuma Sabina ta rasa abokai dayawa da aka kai fursuna. Watarana da tsakar rana a lokacin hunturu Sabina tana gida, tana rashin lafiya tari da sanyi sun dameta sai taji ankwankwasa kofa. Da ta bude kuwa sai tayi mamakin ganin Vera Yakovlena, wata likita yar Russia da ta sani amma ba sosai ba tana jira. Likitannan batazo ne domin ta duba lafiyarta ba, amma domin ta isarda sako mai tsamari. Fuskarta da ban tausayi a lokacinda take gayawa Sabina labarinta.

Vera tazo ne daga wani gari a kasar Ukraine inda mutane dayawa dake shugabannin Krista da kuma sauran masubi, harda ita aka kaisu sansanin gwale gwale na Siberia wadanda kali an daga cikin su ne suka iya dawowa da na.

"Munyi aikin sharar daji, maza da mata tare," inji Vera, "Dama iri guda aka bamu: Ko mu mutu da yinwa ko mu daskare a sanyi mu mutu."

Wannan likita ta mika hannu tari ke Sabina da hannunta mai cike da tabo yana karkarwa. "A kullum mutane suna ta mutuwa, suna suma su fadi akan kankarar hunturu don tsananin gajiya," inji ta.

Watarana aka kama Vera tana magana da wani fursuna game da Kristi.

Horon wannan shine aka sa ta ta tsaya akan kankara na tsawon lokaci bayan ta cire takalma. Da yake wannan horon bai bari ta kammala aikin ta na wannan ranar ba masu tsaro suka yi mata duka.

Yawancin fursunonin wannan sansani mutuwa suke yi domin rashin imani da kuma mummunan yanayi, amma Vera ta rayu. Yanzu tazo wurin Sabina, ba don komai ba, amma domin ta fadi irin amincewar Allah zuwa gareta, har ma a cikin sansani gwale gwalen. A cikin tsakiyar bakincikin ta da bukatunta, Allah ya nuna ikonsa.

Kan Sabina nayi mata ciwo. Maimakon yin tunani akan al'ajibin, bata tunanin kome kuma sai na cewar mai yiwuwa ita ma a gaba ta shiga cikin irin wannan hali na shan wahala. Menene ma'anar wannan abubuwa? Tana juyayi.

Da Vera ta tashi tsaye zata tafi, sai Sabina ta roke ta da ta tsaye ta kwana ko kuma a kala ta jira dawowar Richard gida domin ya saurare ta kuma ya san abinda ke faruwa da yan'uwa maza da mata. Amma Vera ta rigaya takai bakin kofa. A gajarce ta tsaya tace, "Yan sandan sirri sun tafi da mijina. Yana kurkuku shekaru goma sha biyu kenan yanzu. Ina juyayin ko zamu sake saduwa anan duniya." Sai kuwa ta fice.

"Shekaru goma sha biyu! "Sabina ta maimaita kalmomin da makyarkyata. Ta kaka wani zai iya jure wannan dogon lokaci?

Dage azabatarda Krista da kwaminis keyi sai kuruwa yake yi, shawarar tserewa abin yi ne. "Ba a makara ba, Sabina," Richard ya fara. "Har yanzu muna iya tashi, dayawa suna sayen hanyar fita."

Sabina ba ta amsa ba, tasani cewa Richard baifi ta son su fice ba. Amma hadarin yananan. Kuma dole su tuna da batun Mihai, dansu masoyi mai shekaru takwas dan su tilo. Richard yaci gaba "Lokacin da Nazi suka kamani an sake ni bayan yan makonn kawai. Kuma kema suna iya kamaki Sabina. In aka yi haka faru da miha?"

Richard ya tabo inda Sabina take da laushi. Ta sani cewa idan aka kama su duka biyu a lokaci guda, Mihai zai rasa inda zai sa kansa. Mai yiwuwa ya karata akan titi titi, yana rokon abinci. Wannan abune da zaiyi wa uwa wuyar fahimta. Har yanzu dai, Sabina ba ta amsa ba.

A karshe sai Richard ya tuna mata abinda wani aboki ya gaya musu: "Ku tsirar da ranku," inji shi, yana maimaita kalmomin da mala'ika ya yiwa Lot" kada ka juya ka duba baya."

Daganan Sabina ta amsa.: "Tsirar da wane rai?" ta tambaya.

Sai ta shiga dakinsu ta dauko Littafi Mai Tsarkin ta domin ta karanta maganar Yesu da murya a sama: "Dukan wanda zai ceci ransa rasa shi yakeyi: amma dukan wanda zai rasa ransa sabili da sunana samunsa yake yi."

Tana rufe kodadden littafinta sai ta tambayi Richard, "Idan ka tashi ka tafi yanzu, shin zake iya sake yin wa'azi gameda wannan aya a gaba?"

A yanzu kam batun tashi ya tsaye anan, kuma cikin yan watanni gaba za'a sake dubawa.

## DAINA KASANCEWA

Ranan lahadi da safe, 29 ga watan Fabrairu, 1948, Richard ya bar gida zuwa majami'a, ya juya a yayinda yake fita ta kofa, yace Sabina, zan ganki acan."

Amma lokacin da Sabina ta isa majami'a sai ta tararda pasto Solheim acikin karamin ofis, yana cikin bacin rai. Richard bai iso ba inji shi, "Amma kuma yana tunani da yawa a ransa. Kila ya tuna da wasu batu na hamzari ne kafin lokacin sujada."

"Amma kuma yayi mani alkawarin zai ganni anan a cikin rabin awa," Sabina ta fadi, da alamar jin tsoro a cikin muryarta.

"Watakila ko ya sadu da wani aboki da ke bukatar wani taimako." Inji Solheim "ai zai iso."

Pastor Solheim ya shugabanci sujadar a yayinda Sabina take ta buga tarho zuwa abokai amma ta gane Richard baya tare da kowannensu. Tsoron ta ya kara zurfafa.

A wannan akwai lahadi hidimar daurin aure da Richard zai gudanar a majami'a.

"Yanzu, kada ki damu," Pastor Solheim ya na karfafa Sabina. "Kinsan mutumin naki. Kin tuna lokacin nan da muka je taron sansani da rani, sai ya tafi sayen jarida da safe kuma sai ya bugo tarho cewa bazai dawo ya karya kumallo tare damu ba?"

Sabina tayi murmushi da wannan tunanin. Richard ya tuna da wani al'amari na gaggawa kenan ya tafi Bucharest. Haka ne. kila haka din ya sake yi," inji ta tana kokarin rinjayar kanta.

Cin abincin rana na lahadi a gidan iyalin Wurmbrand ya kan zama da fara'a, kuma a cike da mutane. Ba a samun abinci da yawa kwarai, amma Krista sukan taru a can suyi hira kuma su raira wakoki. Ga wadanda suka sami zuwa kuwa yakan zama musu abu mafi armashi na cikin mako.

Yanzu kuma gashi suna zaune a cikin gidan, shiru suna jiran Richard. Amma baizo ba. Saida Pastor Solheim ya gudanar da hidimar wannan daurin aure. Sabina ta buga tarho zuwa dukan asibitoci kuma har ta zagaya dakunan marasa lafiya na gaggawa, da tunanin ko ya sami hadarin mota ne, bata iya samunsa ba. A karshe tayi wa kanta shirin abinda yakamata tayi: ta tafi ma'aikatar Al'amuran cikin Gida. Tabbas an tsare Richard.

Daga nan ne fa nema na awanni da makonni da shekaru na bin sawu daga ofis zuwa ofis....na bude duk wani kofa da ke iya buduwa ya fara.

Sai tunanin Vera yazo wa Sabina, wacce aka rabata da mijinta na tsawon shekaru ashirin. Tayi tunanin azabtarwa da Vera tayi jimiri bayan shaida Kristi ga wani fursuna, wani laifi ne da lallai a kama Richard da shi. Sabina ta tuna yadda da ita da Richard suka godewa Allah cewa zasu iya zama shaidu ga sojojin Russia masu mamaya...... sojojin dai da gashi sun kama mata miji sun tsare.

Jita jita ta bazu cewa an tafi da Richard zuwa Moscow, kamar dai yadda aka sha yiwa wasu. Amma Sabina taki ta yarda cewa ya tafi. Dare, bayan dare, takan shirya abinci ta zauna a bakin taga, da tunanin, zai dawo gida a daren yau. Richard bai yi wani laifi ba. Ba da jimawa ba zasu sake shi. Ai kwaminisawa ba zasu fi yan Nazi mugunta ba, wadanda sukan sake shi baya yan makonni daya ko biyu. Takan kwantar wa Mihai zuciya duk lokacinda yake kuka yana neman ubansa. Ta gayawa danta cewa Allah ne yake kula maka da ubanka, harma dasu duka. Tare kuwa sukanyi addu'a domin Allah ya tsare shi da kuma fatar zai dawo gida bada jimawa ba.

Amma bai dawo ba. Kuma hirar da suka yi da Richard yan watanni baya ya fara bata tsoro: "Idan aka tsare ni a da bana wuce sati biyu sai a sakeni. Da kwaminisawa kuwa yana iya daukar shekaru....."

Zuciyar Sabina na cikin damuwa. Da ita da Richard suna zama kauna tare, amma yanzu kam da ita da Mihai ba ta san yadda zasu yi ba idan ba tare da mijin ba. Bayan yan makonni pastor Solheim ya dauki Sabina zuwa ofishin jakadan Sweden, kasar da suke dasawa can baya domin neman taimako Jakada Reuterswärd yace zaiyi magana kai tsaye da ministan Al'amuran Kasashen Waje, Ana Pauker.

Amsar Mrs. Pauker kuwa da ma can ashirye yake: Labarin da muke da shi, shine cewa Pastor Richard Wurmbrand ya gudu daga kasar da wata jaka cike da kudi da aka bashi amana domin agaji ga ayyukan bada abinci. Kuma ance yana Denmark."

Daganan fa sai Jakada ya kai maganar a gaba wajen Prime Minister. Groza, amma ya maimai wannan labarin, sai kuma ya kara da alkawari na wasa; Ashe ji ake Wurmbrand yana daya daga cikin kurkukun mu? Idan zaka iya tabbatar da haka din, zan sake shi!"

Yan kwaminis masu ji da kansu ne. Watakila shi yasa ake fadi a cikin mutane, "Da zarar wani ya shiga hannun yan sandan sirri na Romania, to kuwa mutumin ya daina kasancewa."

## TURBA ZUWA RICHARD

Bayan famar nemanfara sakamako ta watanni da dama, Sabina tana majami'a wata yammaci, sai aka kira ta domin ta sadu da wani bako mai gashi buzu buzu kuma sai warin barasa yake yi ya nace da cewar ita kadai zai yiwa magana.

"Na sadu da mijinki." Ya fada a saukake, sai gaban Sabina ya fadi. Wannan shine labari na farko da zataji game da mijinta. "Ni mai tsarone kada ki tambayeni wane kurkuku ne-kawai ki sani nine mai tsaro da ke kai masa abinci. Ya gaya mani cewa zaki biya ni sosai in na kawo maki labari."

"Nawa ne?" Sabina ta tambaya, tana shakkar ko lallai yana da labari. Akwai masu karya da yawa.

"Ina yin kasada nefa ki sani".

Kudin da ya fadi suna da yawa-kuma yaki yin ragi. Pastor Solheim ma kamar Sabina shakka yake. Ya gaya wa mai tsaron ka kawo mani sako da rubutun hannun Wurmbrand. "Ya bashi sandan cakuleti daga cikin wurin ajiye kayan abici na agaji. Ka kaiwa Wurmbrand wannan kuma ka dawo da sako dauke da sa hannunsa".

Mai tsaro ya tafi, sai Solheim ya juya wajen Sabina" Abinda kawai muke iya yi a yanzu kenan." Bamu da sahihancin ko gaskiya yake fadi, kuma gashi yana son kudi masu yawa.

Sabina ta sani cewa pastor Solheim bayaso ta sa rai kuma azo a tarar ba haka yake ba. Amma bayan kwana biyu sai gashi ya dawo. Ya cire hularsa, ya zaro takarda dayatsunsa a cikin shafin hularsa, ya zaro takardar cakuletin nan ya mik mata. Ta bude a hankali, ta karanta ." Makaun aciyar matata, ina gode miki. Ina lafiya. Richard."

Sabina taji dadi har da fargaba yana nan da rai! Rubutunsa ne! gashi a fili, ga dagewa ga damuwa. Babu wani batun kuskuren sa zuciya a rubutun nan.

"Yananan kalau", inji mai tsaro. "Wadansu basu iya jure zaman ka daici." Shi kuwa sai warin barasa yakeyi." Yana aiko da gaisuwar sa ta kauna gareki".

Sabin ta yarda ta bashi kudi idan zai cigaba da kawo mata sako. A karshe yace, "Na yarda. Amma ina yin kasada da gaske, kin sani. Wadansu mutane sun sami daurin shekaru goma sha biyu ga yin haka.

Ya amince yayi kasada da yancinsa ta wurin raba hankalinsa. Yana kaunar kudi kuma yana kaunar barasa da kudin ke bashi kuma yana yna sha'awar Richard, saboda da haka wataran yakan saci jiki ya ba Richard karin burodi.

Sabina tayi godiya domin bada kai da mutumin yayi na cigaba da kawo mata sako. Mashayin mai tsaro ya zama sula na jin sako daga Richard. A yanzu kam, wannan din ma dai yayi.

## KUNTATA WA IYALIN FURSUNA

Dokokin kwaminisawa tsanani garesu. Matar wani fursunan siyasa ba ta da ikon samun kati na raba abinci. Katunan anyi sune domin "ma aikata" kawai.

Kuma ba bu damar a baiwa matar wannan fursuna aiki. Me yasa? Domin ba ta da katin rabo, sabo da haka babu ita kenan a kasance.

Sabina ta roki hukuma. "Ta kaka zan iya rayuwa? Ta kaka zan iya ciyar da dana?

"Wannan ruwankine, ba namu ba." Sabina tana damuwa game da Mihai. Ta lura cewa tunda aka kama Richard, sai kara ramewa yake yi domin rashin abinci maikyau. Kuma ta sani har yanzu yana bakin cikin rasa "yan'uwansa maza da mata," marayu guda shida wadanda Sabina da Richard suka diba bayan kisan gilla da Nazi suka yi a gabashi Romania.

Amma fa, da suka ji labarin cewa Russia zata sake rayar da wannan yakin ta wurin tattar yan gudun hijira zuwa wadannan yankunan gabashi guda biyu da sukci karfi da yaji, watau Bessarabia da Bucovin, Sabina da Richard sun sani cewa ko ba jima ko ba dade za a debe yaran nan daga garesu a mayar da su gabas. Marayu daruruwa zasu fuskanci wannan matsala. Sabina tayi tunanin zasu kaisu Palasdinu, inda ake shirin kafa sabuwar kasar Isra'ila, kome zai yi kyau. Sabo da haka, a wata rana mai cike da kaddara, ciki bakin cikin suka dauki yaran domin su hadu da wani dan rukuni na yan gudun hijira akan wani jirgin Ruwa na Turkiyya mai suna Bulbul. Akwai nauyin ganinsun tafi, amma aika su zuwa Palasdinu yafi su jira abinda zai same su a karkashin mulkin Russi. Anyi makonni amma babu labarin jirgin, Sabina tana kara damuwa a kowace rana. Sai aka fara nema irin na kasa da kasa, daga Bakar Teku har zuwa gabashin Baharmaliya. Amma babu duriyar jirgin, kuma a hankali aka m fitar da rai. Ana zaton cewa jirgin Bubul yaci karo da bamabamai da aka boye a ruwa a lokacin yaki kuma ya nutse da kowa da ke ciki.

Irin bacin rai da ya same su yana da yawa. Sabina da Richard sun kaunaci yaran nn kamar ya'yansu, kuma Mihai yaji dadin su a zaman yan'uwa. A lokacin da Sabina tayi na'am da gaskiyar batun cewa an rasa wadannn marayu, bata yarda taga ko tayi magana da wani idan ba iyalin ta ba. Ta kaka Allah zai bar irin haka ya auku? Ta kaka Allah zai dauke mani ya'yana? Tana ta tambyar kanta akai akai.

Babu shakka Sabina ta sani a cikin zuciyarta cewa babu dama ta baiwa Allah laifa yakina dan adam shine musabbabin hadarin nutsar da jirgin ruwan. Amma ai ta kaunaci yaran, kuma tanajin kaka ma zata iya ketare wannan jin kunci.

A cikin bakincin nata, sai kuma Sabina ta juya gun Mihai. wanda yakanyi kuka kwarai duk yayinda ya tuna da su gama sun shiga ransa. Sai ta rungume shi tana gaya mashi wani labari da taji Richard yakan gaya masa:

Ance akwai wani shahararren rabbi d ya'yansa guda biyu maza suk amutu a lokacin da baya gida, duka yayan biyu kyawawane ainun kuma masu ilmin sanin doko ki. Kidimammiyar matarsa ta kai su cikin daki ta rufe su da fararen zannuwan gado. A wannan daren kuwa shi rabbi ya dawo.

"Ina ya'ya na?" ya tambaya. "Nayi ta dubawa a kewaye da gidan, kuma ban gansu acan ba." Ta kawo masa rowan sha, mma yaci gba da tambaya," Ina ya'ya na?"

"Ba zasu yi nisa ba," inji ta, ta jiye masa abinci domin yaci.

Bayan da yaci abinci sai ta fuskance shi:" Tare da iznin ka ina so inyi tambaya."

"Ba da jimawa ba can baya wani amini yabani lu'u lu'u masu kyau guda biyu amana, kuma na adana wadannan lu'u lu'u kamar ma nawa ne. yanzu ya kamata na mayar?"

"Mene?" inji rabbi. "Har zaki yi jinkirin mayar da abinda ba naki ba?"

"A'a," inji ta" Duk da haka a tunanina naga yafi mafi dacewa shine na tambayeka kafin na mayar."

Dagnan ne ta dauke shi takai shi cikin daki ta kware zanin gado da ga gawarsu. "Ya'yana! Ya'yane!" uban yana bakinciki. "Ya'yana, hasken idanuna!"

Uwar ta kau daga nan tayi ta kuka mai zafi. Bayan wani lokaci sai ta rike hannun mijinta tace; "Shin ba kaine ka koya mani cewa kada mu zama masu kiwuya da amanar da aka bamu ajiya? Ubangiji ya bayar kuma Ubangiji ya karba; albarka ya tabbata ga sunan Ubangiji,"

Wannan labari dai bai shiga sosai ba ga Mihai, amma ya fahimci abinda uwarsa take fadi kuma ya sami karafa daga nata karfin kashin kumatu, da kwayoyin idanu masu haske. A makaranta yana koyon mawuyacin darasi ne yadda zai zama dan" bare na zaman jama'a". Mihai yana kaunar ubansa, saboda haka ba abu ne mai sauki ba tayiwa Mihai bayani cewa an tafi dashi daga garesu kuma aka kullé shi a cikin kurkuku domin kawai shi pastor ne.

Yanzu kuma, gashi mutane suna ta bata a kullum.

Akwai wani lokaci guda da aka sallami wasu fitattun fursunoni. Sun isa gida a cikin motocin asibiti suka nuna kukkujewa da tabbunan jikinsu suka kuma bada labarin azabar da suka sha.

A lokacin da labari ya bazu sosai game da irin azabtarwa da akeyi, sai aka sake kama su.

Sabina taki jinin tunawa da munanan azabu da take jin mijinta ke fuskanta. Tayi addu'ar kada ya karai ya tona asirin abokansa. Yayi alkawarin cewa zai gwammaci mutuwa da yin haka, amma wa ya san abinda mutum zai iya jurewa? Bitrus yayi alkawarin ba zaiyi musun Kristi ba, amma duk da haka yayi sau uku.

## KWANKWASA KOFA

Sabina ta sanyaya zuciyar ta da tunanin cewa idan Richard ya mutu tasani zasu sake saduwa a rayuwa na gobe kiyama sun yarda su jira juna a daya daga cikin kofofin nan gomasha biyu na samaniya, kofar Bilyaminu. Yesu yayi irin wannan shiri da almajiransa, ya sadu da su a Galili bayan mutuwarsa. Kuma ya cika haka din.

Amma abin ya dami Sabina, kwankwasa kofarta da akeyi da karfe biyar na asuba............

Sabina tayi aiki har zuwa dare a jiya, wajen ayyukan ba da kai na majami'a da kuma ziyarce ziyarce. Mihai yana kauye tare da abokai, kuma wata kawar Sabina na tare da ita cikin karamin gidanta. Wannan murya mai tsauri ya tsoratar da matan suka farka firgigi: "Sabina Wumbrand! Bude! Mun sani kina ciki."

Sabina ta nufi kofa, da tsoron mai yiwuwa mutanen su shigo da karfin tsiya.

"Sabina Wurmbrand?" wani mai kaurin wuya kamar bajimi yayi tsawa a lokacin da ta bude kofa. "Mun sani cewa kuna boye makamai anan. Nuna mane inda suke-yanzu!" Kafin ma tace uffan, sun fara zaro kaya suna watsar da abubuwan da ke ciki akan dabe. Wani kanta da aka jera litattafai ya fado kasa, sai kawar Sabina tayi hamzari domin kwashe su.

"Kada a damu da wannan," daya daga cikin mutanen ya tsawata," Sa tufafinku."

Dole matannan guda biyu suka sa tufafi a gaban mutanenan guda shida, wadanda suka tattaka kome lokacinda suke binciken gidan. Daga lokaci zuwa lokaci suna tsawa, sai kace sunayi ne domin su karfafa juna ga cin gaba da yin wannan bincike maras ma'ana.

"Watau ba zaku gaya mana inda kuka boye makaman ba? Zamu kacaccala wannan wurin!"

Sabina ta gaya musu a hankali," Makami kawai da muke dashi anan gidan yananan." Sai ta durkusa kuma a hankali ta daga Littafinta Mai Tsarki daga karkashin kafafun daya daga cikin sojojin.

Hafsa mai wuyan bajimi yayi tsawa, "Zaku taho tare damu kuyi bayani!"

Sabina ta ajiye Littafi Mai Tsarki akan tebur tace, "Ku bamu daman na dan lokai muyi addu'a. Sa'nnan zan tafi tare daku."

Kan hanyar ta ta fita, Sabina ta dauki wani pakiti da kawarta ta bata-safa da kampai zasuyi amfani kwarai a wurinda suka tasam ma tafiya.

## RANAR YANCI

Daya daga cikin masu tsaron ya wa Sabina idanu kafin su bar gidan, domin kada tasan inda zasu, sa'annan aka fice da ita daga gida. Bayan wata yar tafiyar da mota sai aka tsaya aka jawo ta zuwa ketaren wurin ajiye motoci, kuma aka kwance daurin fuska da aka yi mata, suka tura ta cikin wani daki cike da wasu mata. Kowane lokaci akan kira suna. Idan ba haka ba kuwa sa kaji tsit. Ranar 23 ga watan Agusta, ita ce ranar yanci, inji su kwaminisawa.

Akan rabar da bakin burodi da wata miy mai ruwa ruwa kafin faduwar rana. A krshe sai aka kira sunan Sabina, kuma sai ka sake rufe mata idanu aka shiga mota. A wannan karo Sabina ta sami labari daga baya cewa shalkwatar yan sandan sirri ne, aka cusa ta a cikin wani karamin daki da ke cike da wasu mata.

## TAMBAYOYI A KARSHEN WANNAN DAURIN GWARMAI

Bayan yan kwanaki sun wuce, aka fito da Sabina daga wannan daki da suke a cushe aka kai ta dakin kurkukun daga kai-sai kai.

Da ta duddubi karamin dakin sa tayi lura da abin da babu a ciki. Bokiti. Acikin gajeren lokacin nan da take a tsare, ta rigaya ta koyi cewa bokitin ma ba ta dashi.

Sabina tana iya jin takawar sawayen masu tsaro saye da takalma kan kura akai akai suna kaiw suna kawowa a kwararo, sai tayi tajin kamar duk lokacinda taji sudtake kamar gurinta aka taho. A karshe kuwa yazo kanta. Tanajin bude kofar aka sake rufe mata idanu.

"Yi gaba! Juya hannu dama. Yanzu yi hagu. Yi gaba!" Tsoro yazo mata lokacin da mai tsaron ya tur ta suka bi wani hanya mai kama da daurin gwarmai. Sai ta fara tunanin ko wannan jujjuyawa zai kare a bakin wurin harbe mutane ne kuma ta mutu ba tareda gargadar da ita ba a cikin duhu. Sai tayi kokarin jawa kanta ragamar tunanin da takeyi a lokacin da taji alamar daurin gwarman ya kare, kuma aka cire daurin.

Ta sami kanta a tsaye a gaban wani mai tsaro dogo, mai farin gashi wanda akwai alamar kusan shekarunsu daya ne. "Kina sane da laifinda kasa ke tuhumarki da shi, ko ba kece matar Wurmbrand ba?" Sabina ta dan jinkirta domin wani kamanni da ta gani na mutumin yazo daya da wani mutum daya taba fita da ita a Paris, "Yanzu zaki yi bayani a rubuce game da haka," mutumin ya umurta, yana nuna alkalami da takarda.

"To, amma me zan rubuta? "Sabina ta tambaya ban san dalilin da kuka kawo ni nan ba." Mai badaumarni yaci gaba, "rubuta laifin ki da kika yiwa kasa!"

Sabina ta dauki alkalami da aka bata ta rubuta yan kalamu tana cewa ba atasan laifin da tyi ba. Hafsan ya karanta abinda ta rubuta sai ya fusata ya maida ta a cikin dakinta. Da ya rufe dakin kuwa sai shi mai tsaro ya gaya mata. "Yanzu ne zaki zauna har sai kinyi shirin rubuta abinda leftana ya gaya maki. Idan kuma baki yi ba to zaki dandana.

Mezan dandana? Sabina tana juyayi, cin zali da yi mani ba'a? Kaskantarwa?: azabtarwa? Ansha fadin batutuwa game da wahalun da fursunoni Krista suke fuskanta a kurkukun kwaminis, tana sane sarai da irin muguntar da zasu iya aikatawa.

Wasu tsofaffin fursuna har sunyi maganar azabtarwa ta fitar hankali, wanda sukan shirya ne domin su tausasa hankalin mutum wanda agaresu zai basu saukin yi masa tambayoyi kuma ya amsa. Yan kwaminis sukan kun na rakoda da muryar mutane na ihu sai su gaya wa fursuna wai ai muryoyin da yake ji suna ihu, muryoyin ya'yansane da ake azabtarwa. Shin wane mahaifi da yake cikin hayyacinsa zai ji haka yakau da kai?

Saduwa na biye tare da wannan laftanar ya fito da al'amuranda ke kawaye da tsare Richard. "Matar Wurmbrand," injish, ana tuhumar mijinki da laifin ayyukan da suka shafi batun juyin juya hali na kasannan. Ana iya a harbeshi. Abokan aikinsa sunyi magana kuma suna goyon bayan caji da ake yi masa."

Gaban Sabina kuwa sai faduwa ya keyi. Karya mutumin yakeyi, ya zuba ido yana lura da yadda zata yi. Tayi iy kokarinta ta nuna kamar babu kome a yayin da yacigaba. Watakil kokari suke su fitar da kansu. Kila ma sune masu ayyukan juyin juya hali na kasa. Ba zamu iya tantancewa ba sai kin gaya mana komai da komai game da mutanen da ke aiki acikin mishan, injishi, komai da komai. Ki fitofili ki haramtasu, mijinki kuwa zai sami saki gobe.

Sabina ta jarabtu da wannan tunani kwarai, amma bata yarda da yan kwaminis ba. "Ban san kome ba,! Inji ta, tana hada ido dashi.

A wannan daren, tana jinyar kukkujewa da doke doke da masu tsaro sukayi mata, sai ta kwanta akán karamin gadon yara, taji kafarta na taba karshen gadon. Dan taliki Richard, tana tunani. Gashi dogo, kafafun sa zasu kai har can waje.

Kome suke yi masa a yanzu? Wani lokaci sai taji kamar zata yarda ta fadi komai ma domin su sake saduwa dashi; wani lokacin kuma sai ta dage taki. Tunanin nan guda biyu sun sha yin karo a zuciyarta. Tana so Richard ya rayu, kuma tana son sa da ya dage.

Wani guntun plasta mai kama da alli ya fado daga kan rufin dakin sai ta dauka ta zana alamar giciye akan bakin bargon ta kuma sai tayi godiya.

Kum kamar wata amsa aka rada mata daga shi wanda ya ji addu'arta, sai wani tunani ya bijiro mata a zuciya: bakwai, Sabina ta lura cewa tana cikin daki na bakwai. Wata lamba mai tsarki.

Lamba na kwanakin halittar duniya ya zama kamar wata baiwa ta karfafawa, Sabina ta kwanta akan karamin gadon nan tayi kuka. Koda shike jikinta na cikin duhu, tanajin ruhunta a tsaye yake a cikin wani haske da yasha karfin iyakokin tsaro na fursuna. Ta goge hannunta akan alamar giciye da ta zana akan bargonta kuma a yayin da barci ke kwasarta, sai ta rada, "An giciye mu tare da Kristi". "Tashi," Mielu, shugaban masu tsaro ya shigo, rufe mata idanu, aka kuma bi wannan hanyan daurin gwarman.

Wannan karon Mielu, mutum ne da ya girmi Sabina, ya ba ta wuya na tsawon awa guda. "Ke da wa kuka kwana? Me kikayi tare dasu? Inaso in san da wanene kuma sau nawa-komai."

Da gajiyar jiki da na sosuwar rai abin ya faskarawa Sabina kai game da sauyi na irin tambayoyi da ake yi mata. Sai ta amsa a hankali, tace. "Ba zan gaya maka abinda kake so kaji ba". Tarihin jama'i mafi muni bazai dakatar da mutum daga zama shararren waliyi ba idan Allah ya nufe shi da zama." ta gaya masa. "Maryamu Magdalin ta taba zama karwa amma za a cigaba da darajan tata bayan ma mun tafi an manta damu da jimawa."

Mielu yayi gurnani yana furta mugayen kalamu, ya maida Sabina zuwa dakinta.

Alokacin tambayoyi na biye, aka tilasta wa Sabina ta kalli wasu hotuna na mutane dabam dabam. Ta shaida daya daga cikinsu, wani dan Russia da suka yiwa baptisma a boye a gidansu, kokin gane wani daga cikinsu?" wani mai saiko ya tambayi Sabina. Sabina tasan abinda zai faru idan ta bada wani suna. Sai mai tambayar ya dadada batun. Gaya mana abin da mukeso mu sani, mu kuwa zamu saki mijinki." Wannan jarabtar ta zahiri ce, amma haka kuma a shirye take ta bada ranta domin dan'uwanta. "Bangane ko daya daga cikinsu ba."

Mai saikon nan yana jin cewa karya takeyi sai ya tambaye ta me takeso ayi mata. Ko wace mata tana da farashi. Menene naki? Yanci? Kyakkyawan mukamin pasto domin mijinki? Kudi? Fadi farashinki."

Sabina ta gaji da wannan nuna iko akai akai da kuma alkawurran da ba za'a cika su ba. Sha'awarsa kawai na kar zuwa a kamo mutane ne, Sabina kuwa ba zata yarda hannunta ya shiga ba. "An rigaya an saye ni!" inji ta. An azabtarda Yesu har ga mutuwa domina. Zaka iya bani farashin da ya fi wannan?"

Fuskarsa ta baci, har Sabina tayi zaton zai kai mata duka maimakon haka aka maidata zuwa dakinta.

A hankali kuma sai aka dawo da Sabina a cikin dakin mutane masu yawa. Watanni sun wuce kuma sanyin hunturu ya fara shigowa. Ta kan damu game da Mihai. Ko wa ke kula dashi? Ko a titi yake makalewa? Yana jin sanyi? Ba lafiya? Watakil shima yan kwaminis sun tsare shi. Tunani marasa iyaka da kuma damuwa suna cika wa Sabina zuciya a kullum.

A watan Nuwamba shugaban kurkuku ya zo dakin da Sabina ke tsare yace "zamu karanta wasu jerin sunaye". Kuma duk wadanda suka ji sunayensu dole ne su shirya babu sauran karin nayani. Fursuna suka zuba idanu a yayinda mai tsaro da yazo tare da shugaban ya fara kiran sunaye, harda na Sabina.

"Me kike zato?" Sabina ta radawa wata mata kusada ita wacce ita ma tana tara nata kayan domin tafiya.

"Ina jin ko sallarmu za ayi, ko kuma za a kai mune a harbemu." Ta fada da murtuke fuska.

## IDAN HAR AKA KAI KA JILAVA TO SAI DAI ALLAH YA TAIMAKEKA

Ai kuwa ba a sakesu ba, kuma ba a harbe suba a kalla dai tukuna.

An tafi da Sabina da sauran zuwa Jilava, kurkuku mafi bada tsoro a cikin dukan Romania. Sabina ta tuna jin ana maganar wannan kurkuku mai kaurin suna. Kuma akwai wani daki musamman mai ban tsoro daya wuce misali. Allah ne kadai zai cece ka idan ka shiga dakin kurkuku na Jilava mai lamba hudu," haka jita Jitar ke zagayawa. Wani mai tsaro daya gabatar da kansa wai shi Saje Aspa ya jagoranci fursuna ta hanya mai duhu da hanyoyin da suka bi ta karkashin kasa can suka tsaya a bakin wani katon kofar karfe mai cike da karafa da suka yi tsatsa daga sama har kasa. da zuwa daki mai lamba hudu", inji Aspa yana fadi da jin kai. Da tsakiyars afiya suka isa, amma dakin yana cikin duhu. Wata yar fitila ce ma ke kunne mara haske sosai da ke rataya akan silin. Akwai gadaje adakin. Can sama, wajen karshen dakin akwai karamar taga da aka tare da karafa da yasha penti.

Idanu barkatai aka zuba wa sababbin zuwannan, Sabina da take jin kamar ta shake da rashin iska it a aka baiwa gadon karshe wanda bokiti ke karkashin sa.

Bayan da gari ya waye, kiran tashin mutane daga barci na karfe biyar da asuba ne ya tada Sabina. Nan da nan kuwa mata guda hamsin suka shiga layi domin yin amfani da bokitin. Daga baya Sabina ta sami labari cewa ana rike da mata guda dari biyu a dakuna guda hudu a yayinda ake rika da guda dubu uku a cikin sauran dukan dakunan kurkuku. An tsara kurkukun Jilava ne domin tsare yawan fursuna dari shida.

Da karfe goma sha daya mata sun shiga layi aka shigoda tukunyar abincin kalaci. Sabina tana mamakin yadda abokan dakinta suka yi tsit a lokacin da ake raba abincin. Amma ana cire tukunyar kuwa, sai dakin ya kaure da fada. Mata suka fara yiwa juna tsawa da zage suna kokawa akan abinci. Masu tsaro suka dawo nan da nan suka fara dukan matan da sanduna hagu da dama sai da daben yayi kaca kaca da miya. A fusace kuwa Aspa yayi alkawarin cewa gobe ba za a raba abinci ba.

Daki fa ya sake yin shiru mata suna tunani cewa gashi gobe babu kalaci. A hankali kuwa sai suka fara hira kasa kasa. Daya daga cikin fursunonin ta tambayi Sabina dalilin da aka kawo ta kurkuku. "Babu alamar cewa ke muguwace a fuskarki," inji ta, wannan kalami ya gamshi wannan sabuwar fursuna.

Sai Sabina tayi murmushi. "Ni matar pastorce," dajin amsarta, wasu fursunoni kalilan suka yi yan zage, zage suka juya baya. Amma wasu yan jamhuru ne. "Idan hakane kuwa to lallai zaki san wasu labaru na cikin Littafi Mai Tsarki," wata fursuna mai suna Elen ta fadi, a zaune kusa da Sabina akan dabe.

"I na sani," Sabina ta amsa, ta sake yin murmushi. "Ko zaki so jin guda?"

Sabina ta sami hankulansu, suka yi ta sauraron labaru daya bayan daya na tsawon sa'oi. A a majmi'ar su ma kowa ya yarda cewa ba da labaru, har matan sun mance zuwa wani dogon lokaci cewa ba fa zasu sami abinci ba nan da wasu sa'oi talatin da shida.

Sabina ta sami karfafawa ta wurin sha'awar labarum Littafi Mai Tsarki da take basu, amma ba a jima ba ta fara ganin alamar cewa jita jitar da ta sha ji game da Jilava gaskiya ne. ma'aikatan tsaro mata sukan bi umarni da ake basu da ido-rufe. Idan aka umurce su suyi wa fursuna duka, sukanyi mata dukar-kawo-wuka da sanduna babu tausayawa. A hankali kuma da tsanani. Babu nadama babu tausayi. Tamfar ma kamar fursuna ta zama darduma.

## SAI SU KWADAITAR DA ZUCIYA....

## SA'ANNAN KUMA SU DAUKE

Kuzo ku karbi miyan karas, mutane na!" Wannan gayyata ta mai tsaro mai cike da gatse da kuma doyin da ke fitowa daga cikin tukunya mai tururi ya bugo tun kafin a shigo dashi. Amma mata da dama da suka fi dadewa basu ko motsa ba.

Basu da kwarin da zasu iya tsayawa a layi domin karbar abinci. Ko da shike Sabina bata sani ba a lokacin, wannan abinci mai kamar dafi akan shirya shine domin sansanonin gwale gwale. Kuma yana cika aikinsa, ta wurin nuna mata marasa kwari.

"Wannan aikin bauta ne sosai," wani saurayin malami ya gaya mata amma a mashigin ruwa ana rabar da burodi mai nauyin Laba guda daya da rabi a kullum hard a taliya!"

Kurkuku na cike da jita jita game da sabon sansanin gwale gwale na mashigin ruwan danuea. Kowane sabon zuwa yana da wani abu da zai kara game da wannan gagarumin shiri, wanda zaici bilyoyin kudi, ko da shike yawancin aikin kwadagon yana samuwa ne daga fursuna da suke yin aikin dole. Za a gina mashigin ruwan na tsawon mil arba'in yana ketare budaddiyar Danube da Bakar Teku.

"Acan mashigin ruwan, kana iya samun dukan abinda kake so daga gida!" daya daga cikin ma'aikatan kurkuku ya gaya wa fursuna.

"Har cakuleti?" Sabina tayi mamaki. Dayake ta sadaukar da yanci, batun su cakuleti ai mafarki ne kawai.

Akwai kuma jita jitar ana iya samun tufafin kare sanyi barkatai a mashigin ruwa har na duba lafiyar mutum a asibiti. Amma wannan alkawari na karshe ne ya fi jan hankalin Sabina. Fiye da tufafi ko cakuleti, ance ana barin fursunonin mashigin ruwa su sami dammar ziyara daga iyalin su!

Sabin a kuwa ta rungumi sa zuciy na sake ganin Mihai fiye da wani tunani dabam.

"Amma ba kowa ne zai sami damar zuwa mashigin ruwa ba domin yin aiki," Viorica wata ganduroba tayi gargadi. "Kamar yadda jami'i mai kula da ofishin siyasa ya gaya mani kwanaki, 'A cikin jama'a ta mulkin gurguzu, yin aiki wata dama ce, amma ba lada domin yan fashi ba."

Wannan yanayi ne irin na al'adar kurkuku: A bada wani sa rai kuma sai a janye.

Daga baya kuma a sake bayarwa ta wata hanya. A zagayowar ranar haifuwar Mihai ta goma sha biyu shida g watan Janairu, 1951, Sabina ta gano sabon shirin nasu.

"Zan baki wani zabi," inji Kaftin Zaharia Ion wata safiya. "Maimakon tafiya aiki a mashigin ruwa, kina iya zama anan a mukamin tsararriya ta musamman kuma hade da jin dadi daidai gwargwado. Zaki sami dukan dama da kike iya samu acan mashigin ruwa amma ba lalle ne kiyi aiki ba. Lallai wannan zabi ne mai karimci."

Sabina tana sane, sarai da cewar ba a bada dama haka a kurkuku ba tareda wani dalilиba, saboda haka sai ta jira a tsanake har sai ganduru ban ya bugi kan kusar. Abinda kawai zaki yi shine ki bani rahoton sauran fursuna daga lokaci zuwa lokaci-a cikin sirri fa amma. Abune mai sauki, kuma kada kowa ya san dan shirin namu."

Ba tare da bata lokaci ba, Sabina tabata amsa. "Na gode," ta amsa da ban girma," amma acikin Littafi Mai Tsarki kana iya karatu game da maciya amana guda biyu, daya wanda yaci amanar Sarki Dawuda da daya kuma wanda yaci amanar Yesu. Dukansu biyu sun rataye kansu. Banason irin wannan karshe, saboda haka bazan iya zama mai kawo rahoto ba."

A cikin jijjifi kuwa kamannin Ion suka sauya daga abin sha'awa zuwa na harara mai ban tsoro. "Idan hakane ba zaki kara samun yanci ba!" ya tsawatar.

Sabina tayi tunanin kila ta rasa damarta na zuwa mashigin ruwa kenan. Ta sani cewa sunanta na cikin jerin masu tafiya, kuma ta sani wadanda aka zaba zasu tashi bada jimawa ba. Taki jinin aikin gwale gwale, amma a shirye take tayi abu kome wuyarsa domin sake ganin Mihai- amma ban da zama maicin amana.

Bayan yan kwanaki, aka aika Sabina zuwa sansanin gwale gwale na Danube. Cikin sauri kuwa suka fahimci cewa an yaudare su ne.

MASHIGIN RUWA

A safiya ta farko acikin sansanin, Sabina ta farka a cikin warin kashin bera. Taji wata murya na gayawa makwabciyarta," Ki ajiye musu burodi da dare. Ya kansa sudaina cizo."

A kullum Sabina takan tafi aiki tare da sauran fursuna-maza da mata. Suna gina madatsa, kuma aikin Sabina shine daukan manyan duwatsu akai shi nisan yadi dari biyu zuwa inda baji yake kamar bayan ta zai karye don tsananin nauyi. Mikewa ma yana yi mata wuya.

A kowane gangin leburori akwai helma wanda masu taimakon sa sukan tabbatar da yawan aiki da fursuna sukeyi. Adadin yawan aiki da ake bukata a kullum yakan kai dunkulen yadi takwas a rana. Idan ma'aikata suka cika aikinsu, sai kuma a kara yawa washegari. Idan suka kasa cikawa, sai ayi musu horo.

Sabina bata iya misalta irin yanayi da suka jure wa a sansanin. Lokacin da ta tambayi batun dama da ake yi alkawari, sai aka yi mata dariya.

Karin mata fa suka zo domin aikin mashigin ruwa. Kamar Sabina, ko wacce na marmarin saduwa da iyalinsu, musamman ma yayanta. Yin la'akkari da gagarumin aikinda akeyi mata da yawa sun fara fitar da rai.

Amma Sabina ta makalewa sa zuciya wanda yafi aikin madatsan ruwa ko wani kurkuku. Can fa sai sauran fursuna suka fara lur. suma suna son irin wannan sa zuciya da take da shi.

"Idan kin yarda, Sabina, kara gaya mana labaru daga Littafi Mai Tsarki,"

Sabina tasan hadarin yin haka, ta san abinda zai faru idan aka kamasu. Amma tayi amfani da dukan da ta samu domin shaida bishara ga fursuna. Karin fursuna sun zo wurinta, suna shaida zunubansu suna kuma tambya ko zai yiwu a gafarta musu.

Sabina ta tabbatar musu cewa yana yiwuwa, kuma ta gaya musu wani abu da Richard ya fadi:

"Jahannama shine inda zaka zaune kai kadai a cikin duhu kana tunawa da mugayen abubuwa da kayi." Lallai wadannan mata suna dandana wannan jahannamar anan gurin.

A yayinda Sabina taki zama mai kawo rahoto, wasu basuki ba wani lokaci fursunan sukan san ko su wanene yan kai rahoto, amma fa basa iya tabbatarda haka, haka dai aka cigaba da wannan zaman kaka-nikayi.

Wata fursuna na iya gayawa Sabina tana so taji karin labarun Kristi domin tayi mata wayo ta yi shaidar bishara wanda aka haramta yi da horo mai tsanani. Mai yiwuwa kuma ya zamana da gaske ne matar tana so ta sani. A gaskiya babu yadda Sabina zata sani ko tambayar ta gaske ne ko kuma tarko ne, amma galibi dai takan zabi tayi magana.

Sau da dama bayan mai rahoto takai kararta. Akan kulle Sabina a cikin wani babban kabod wanda girmansa yakan dauki mutum daya ne kawai kuma a tsaye. Akan sa ta a ciki bayan an tashi daga aiki, ta kwana a ciki, kuma a fito da ita da safe domin tafiya wajen aiki. Abin har ya zamarwa Sabina jiki a lokacin da take can mashigin ruwa.

## DAN HASKE KADAN MAI ALAMAR ALHERI

A kullum takan tambayi sababbin fursuna ko sun taba jin labarin Richard. Amma ba ta samu ba har saida wata fursuna ta gayawa Sabina labarin wani mai wa'azi da ta gani a Vacaresti. A halin gaskiya ba ta sadu dashi ba, inji ta. Taji shi dai yana Magana a dakinsa na kusa da ba-haya, kuma lokacin da fursuna suka shiga layi suna jira, sai shi "mai wa'azin kurkukun" yadinga karfafasu domin subi Kristi kuma su amshi kaunarsa. Kowa na cikin kurkuku sukan tambaya shin ko wanene shi, amma babu wanda ya sani. Amma ita tana gayawa Sabina cewa tana kyanta ta zato Richard ne.

Fuskar Sabina kuwa ya haskaka da farin ciki. Richard din ta yana da rai! Lallai wannan mai wa'azin Richard ne. Mai ziyararta ta kara bata labari. Watarana sai mukaji wai mai wa'azin na muguwar rashin lafiya. Bayan wannan kuwa, bamu cika jinsa kwarai ba daga baya ma sai muka ji shiru. Akwai jita, jita wai ya mutu. Kiyi hakuri."

Hawaye suka zubo wa Sabina, amma ta ki tayi magana. Za ta mika damuwarta ga Allah ya kara dorin shekaru wa bawansa, Richard dinta, idan har yana raye.

Ta kuma yi addu'a domin Mihai, da tsoron cewa, shima, ana iya kama shi a aika shi zuwa mashigin ruwa. Akwai ranar da gabanta ya fadi da taga wani yaro mai shekarun Mihai yana aikin gwale gwale a mashigin ruwa. Ko da shike tadan huce da taga ba Mihai bane, amma tayi kuka domin yaron-da uwarsa, ko da a ina take-kuma tasa su a cikin addu'a.

A karshe dan hasken fata mai alheri yazo. Ranar lahadi zai zama ranar ziyara! Sabina taji kamar mafarki ne. wai, zan sake ganin Mihai-wane mutum! Da ranar tazo, wata fursuna ta baiwa Sabina aron tufafi, nata ya zama tsumma don daukar duwatsu. Tana cike da doki tana lissafin mintoci har sai da ta sake rungumar danta. Amma fursunan suka taru domin ziyarar, aka gaya musu cewa dole ne su tsaya a daya gefen dakin kuma minti goma sha biyar kawai za ayi.

Sai kuwa ta ganshi, kuma kauna dai irin ta uwa tayi masa, idanunta cike da hawaye nesa daga daya bangaren dakin. Ya rame! da uwa da da sunga juna amma kowa ma ba a bari sunyi magana ba, kuma ma babu sirri kowa da kowa ne adakin babu damar kadaicewa. Da lokaci yakare Sabina ta kira Mihai daga can inda aka shaitse su: "Mihai! Wayyo, Mihai! Ka bada gaskiya ga Yesu da dukan zuciyarka!"

Ita ce shawara mafi dacewa da nayi tunanin bayarwa.

Kalmomin Sabina sun tsaya daidai da wata cabke hannun ta da ganduroba yayi sa'annan suka yi waje da ita.

Kalmomin Sabina sun tsaya daidai da wata cabke hannun ta da ganduroba yayi sa'annan suka yi waje da ita.

Bayan da suka koma ciki, sai mata suka kewaye ta suna tambayar abinda Mihai ya fada, kuma yaya yake. Amma kada kai kawai ta ke tayi. Tajima bata yi magana ba, domin t shiga damuwa game da danta.

Abin damuwa wadansu fursuna sun jira amma babu wanda yazo musu. Sabina tayi musu addu'a suka kwanta akan katifunsu ta ciyawa suna kuka lokacin hutun yazo, kuma Sabina da saurana fursun suka kara zama abin tausayi. Taci gaba da aiki acikin Kogin Danube mai kankare suna lodin manyan duwatsu a cikin baji. Galibi a lokacin hunturu tsanantar yanayi ya riba, domin babu dama a jefarda duwatsun a cikin baji ba tare da ruwan kankara ya fantsama ba yana jika ma'aikatan. Dafara aiki kenan tun safiya sai Sabina ta jike. Kuma iska mai kankara kuma sai ya daskara tufarta a jikinta, sai ta yi ta aiki a cikin sanyi. Yatsunta sun farfashe kuma a kumbure daga aiki kuma a kandare daga bala'in sanyi.

Cikin dare kuma in ta dawo cikin bukka, takan kwanta da kayan haka a jike, babu wurin shanya, kuma ma duk kayan da aka shanya sace wa akeyi. Saboda haka takanyi matashi da jikakkun kayanta da safe kuwa tasasu ba tare da sun bushe ba. Idan tayi sa'a kuwa yakan dan bushe kadan akan hanyarsu ta tafiya wurin aiki, kafin su fara jikewa kuma. A yanzu dai Sabina ta rame ainun, kamar ma iska zai iya ture ta.

Sabon aikin Sabina shine lodin duwatsu acikin kura. Sauran mata kuma su tura kurar suje su juye duwatsun a cikin baji a kan kogin.

Aikin da yasa duk gababuwanta suna mata ciwo farcenta duk sun karairaye jina jina. A cikin gatse na keta da tsananin gajiya ya ma hana ta jin wasu ciwo da ke damun jikinta.

A karshe Sabina ta farka wata safiya tana jin ruwa na diga daga kan bukkar. Bazara tazo, amma sunzo tare da wata sabuwar kalubale: kasar da take share yanzu kuma tabo.

Gandurobobi maza da kan raka su kai da komowa sansani ne kadai maza da matan su ke gani, kuma wadansu daga cikin matan sukan yi kalamu na batsa game da mazan ayayin da suke kaisu.

Annie wata karamar karwa mai wayo, da kawarta Zenaida sune sukan jagoranci irin wannan dabi'a ta wurin yin zaurance.

"Hannun Bitrus kamar na goggo," Zenaida tafada wata rana, da muryarta kasa kasa domin kada mazan su jita." Dubi yawan gashin da ke bayan hannun! Na tabbata duk jikinsa gashine har kasa, da wani zai duba."

"Ai, akwai mata anan da suka gani!" Ann tayi wasa, tana nuna bakinta cike da hakoran zinari. Sai sauran mata suka yi dariya.

"A'a," Zenaida na nishi, tana yi kamar taga abin ban tsoro. "Ko da shike bansan abinda suke gani ajikunanmu suyi sha'awar mu ba. Amma na lura cewa kuwa shin akwai ma mata marasa abin da zai sa ayi sha'awa a jikin mace kamarmu?"

Ashar da Annie tayi don abinda Zenaida ta fada ya sa abokansu sukayi dariya suna shewa. Suka cigaba da amfani da kazamun kalmomi.

Sabina kuwa tasa hankalin ta a gaba, tana kokarin kyale su.

"Yar waliyyar tamu bata son munanan kalamu," inji Annie. "Tana ganin cewa mu bamu da kyau!"

Sabina tayi shiru, amsar kenan da yasa sauran suka fusata. Kuma a wannan lokaci Annie, wacce ita ma mai kazamun kalamu ne, sai dai ita ba mai yin hassada bace tayiwa Sabina keta fiye da yadda ta nufi yi.

Matan sunyi layi a karshen aiki kamar yadda suka saba a gajiye kuma ga tafiya takan hanya mai tabo da yabi ta gefen Danube.

Peter daya daga cikin masu tsaron ya tunkudi abokin aikinsa wani saurayi mai kama da bebe mai fadin hanci, sai yasa kafa ya tade Sabina da tazo wucewa, sai ta fadi a cikin tabo dumu dumu.

Sauran masu tsaro suka fashe da dariya.

Sai Peter ya kama Sabina ya daga ta, dukan jikin ta kaca kaca da tabo har ka.

"Abinda kike bukata yanzu, malama, "yana gurnani "wanka".

"Nutsa ta a cikin Danube!" muryar wata mace na fadi. Sabina tayi kokarin ficewa daga rikon da akeyi mata, amma wani mai tsaro ya gudo domin ya taimaka masa. A yayin da Peter ke rike da hannayenta, daya mutumin ya rike idanun sawayen ta don ya daga kafafunta sama. Sukayi lilo da ita sau daya sai kuwa suka jefa ta, ta fada wuri mara zurfi mai duwatsu, sai tayi kamar numfashin ta ya dauke. Sabina ta suma amma har'ilayau tana jin ruwan kankarar na bi ta jikinta, kuma igiyar ruwa najan dan karamin jikinta takan duwatsun.

Ana magana da karfi daga gaci amma bata iya ganewa ba. Duk lokacin da tayi kokarin tashi, sai igiyar ruwa ya kaita kasa. Babu amfani, Sabina ba zata iya ta ceci kanta ba.

Can kuwa sai karfafan hannaye suka cafko ta suka fito da ita gaci. Wani kuma ya tilasta mata ta zauna a zaune, sa'annan ya mammari doron bayanta, taji kamar zata haras, tana haki don jin tsananin zafi ta hakarkarinta.

Jiri yasha mata kai, kuma sai kara takeji a cikin kunnuwanta. Wannan ruwan rai ne da ke gudu a cikin Aljann? Tana tunani amma da ta bude idanuna sai taga tabon, masu tsaron da ramammu kuma kazaman mata da ruwa da tabo ya kazamtar abakin kogi, sai ta gane ba a samaniya take ba tukuna. "Ba abinda ya sameta, tashi!" wata mace na fadi da karfi, tana zurawa Sabina idanu. Sai tace a hankali "Ko ki kama hanyar tafiya idan ba hakaba kina iya daskarewa fiyeda sanyin. Tin rike kirjinta, don tsananin ciwo da yake yin gaba gaba a kowane minti.

Da suka isa bukka. Sabina ta dudduba duk wuraren da taji ciwo. Ta sami kujewa sosai a gefen ta da kuma fatar hannayen ta ma ciwo yake yi mata kwarai.

Tayi kokarin samun barci, tana ta juye juye cikin dare ko taji dadin kwanciya. Amma ina.

Washe gari taga likitan sansani, wata muguwar mata mai suna Cretzecunu. Wani wuri da ta kuje babba dashi yayi launin algashi da rawaya da siffa mai kama da taswirar Africa yana shimfide a gefen jikin Sabina, kuma a yanzu ma dai ba ta ko iya daga hannunta.

"Tana iya zuwa aiki!" inji ita likitar. Sabina ta fara nuna rashin yarda da haka, amma sai ta sake yin tunani. Yin musu kara mata horo zaiyi, watakil ma wannan kullewa a cikin kabod. Sai ta wuce wajan mutanan da ke jiran tafiya aiki, amma ta tsaya agefe yayin da layin ke tafiya gaba. "Me ya sameki?" helma ya tambaya, yana kallon yanayin tsayuwarta.

Sabina tace, bazan iya yin aiki ba yau. Ina cikin jin radadin ciwo, ina zato na karye ahakarkari."

Da helma zai dan tausaya, amma sai Peter mugun mutum ya hana. Ya rike hannun Sabina ya jata, yasa tayi kara don jin zafi. "Abinda ya faru da ita shine bata cika aikinta jiya ba, maza tafiya!" Ya juya ta kuma ya shure ta da takalmi a bayanta. Ya tuttura ta cikin layin mata. Sabina ta tafi aiki a ranan nan da kuma kullum tana faman kokartawa, harma daga baya likitoci sun tabbatar cewa hakarkarinta guda biyu sun kaye.

## DA DIANA DA FLOREA

Lokacin rani yazo musu a cikin wannan gida mara dadin zama, kuma Sabina tana ta jin akwai fata nagari a zuciyarta. Sababbin mata guda biyu sun sauka a cikin sansani kuma an tura su cikin bukkar Sabina wasu matan "agazazzun sun san su da suka iso, amma basu yi musu magana sosai ba. Da jin kunya kuwa sai suka zabi gadaje can nesa wajen kusurwar dakin.

Daga baya Sabina ta sami labarin cewa su yan'uwan juna

ne, Diana da Florea. Kowacce cikinsu akawala ce, kuma suna da kyawawan halaye da rashin ta da murya. Amma karwai ne su, inji su da suka sansu, kuma an kwaso su ne kamar sauran domin suyi "aikin hukuma" na hukumci da akayi musu a mashigin ruwa.

Damuwa da rashin fahimtar abubuwan da ke tafe ya sha ma wadannan mata guda biyu kai. Babu wanda ya iya samun sanin irin halayensu na can bay sosai, ko da shike dayawa sunyi takala da tsokana. Yan'matan nan suka yi ta butar su kuma suyi barcinsu kuma da Diana taji maitsaro ya kira sunan Sabina ranan nan b da baza a san wani abu game da su ba.

Nan da nan Diana tayi hamzari zuwa wurin Sabina. "Kin san Richard Wurmbrand?" ta tambaye ta. "Ni matarsa ce," inji Sabina.

"Ayya!" inji ta. "Wane irin tunani zakiyi a kaina?" "Mahaifina mai bishara ne," inji Diana, muryar ta n rawa. "A da yakan karanta mana daga litattafan Richard; yakan kira su "abincinsa na ruhaniya". Ankai ubanmu a kurkuku domin ban gaskiyarsa, yabar matarsa a cikin rashin lafiya da kuma yaya shida. Da florea dani mune manya. Dukanmu kuma muka rasa aikin mu a masana'anta lokacin da ubamu ya tafi kurkuku. Iyalinmu kuma suka fuskanci rasa abinci samsam."

Sabina ta dora hannu don kwantar da hankalin ta a yayin da taci gaba da bada wannan labari mai sosa rai." Watarana wani saurayi ya tambaye ni domin mu fita tare. Muka tafi kallon silima sa'annan muka je cin abincin dare. Ya gaya mani cewa zai iya samo mani takardar izni nayin aiki. Daganan............ "Di'ana ta sunkayar da kanta tana hawaye. Munsha giya da yawa kuma sai ya...... yayi lalata da ni."

Bada jimawa ba haka ya sake faruwa, inji ta, amma a wannan karo ko maganar takardar iznin yin aiki ba a yi ba. Koda shike mutumin ya ba ta kudi.

Sanin irin matsayin da uwarta take ciki na agazawa iyali, Diana ta karbi kudin. Bayan mako guda mutumin ya gabatar da ita ga abokinsa-kuma ya bar su tare. Lokacin da mutumin ya nemi yayi lalata da ita, ta fusata. Amma shi ma, ya nuna mata kudi, da yake a cikin bukata suke, yace, ya yi haka ne akan abin da abokinsa yace yayi. Diana ta karba amma da jinkiri.

Zuwa gaba kuwa sai Diana ta hada abokai da yawa masu zuwa akai akai, tayi watsi da kunya da take ji ada, ta saba da irin wannan rayuwa, harma tafi son haka maimakon aikin masana'anta mara dadi.

Duk da irin munin labarin da Diana take bayarwa, Sabina tana jin cewa akwai abinda Diana take boyewa. Ana cikin haka sai Diana ta tsaya ta dubi fuskar Sabina. "Na zaci zaki ji kyama," inji ta. "Sanin cewa na fito daga gidan iyali na Krista na zama karwa bai bata maki rai ba?" Sabina ta amsa a hankali, "Ke ba karwa ba ce, ke fursuna ce. Bayan haka ma, babu wanda take karwa ko waliyi ko ma kuku ko kafinta na din din din. Abubuwan da kakeyi sanadi n na bangaren rayuwar kowane mahaluki. Suna iya sauyawa akowane lokaci. Kuma na bada gaskiya kin rigaya kin sauya, ta wurin gaya mani wannan labari."

Diana taso ta gaskanta kalamun Sabina, amma fa ba'a sasanta mata zuciya ba. Sai ta zauna abakin dan gadon ta na cikin bukk, hannayen ta na rike da gwiwoyin ta, fuskarta cike da damuwa da tsarguwa. "Idan dani kadai ce," ta furta a karshe, da bata yi muni kamar haka ba. Amma na sa kan wata ta shigo. Saurayi na ne ya bada wannan shawarar. Yace wai bai dace ni kadai ce na dauki nauyin iyali ba, saboda haka a karshe ya fita tare da ita."

Bada jimawa ba kuwa aka shigarda Florea a cikin rayuwa na karwanci. Mawuyacin abu garesu shine boye wananan al'amari daga kaninsu, yaro dan shekaru goma sha biyar wanda yake ji da yayyensa kwarai. Kamar dai ubasa yaron mai ibda ne ainun mai karfin tunemi mai halin kara amma bbu

sanin sha'anin duniya. Baya kaunar ko kuda ne ya wahala," Diana ta fadi tan girgiza kai. Mun sani cew idan ya sani, zai cik da fusata. Mukayi iya kokarin mum u boye daga gareshi."

Amma wannan sabuwa rayuwa ta yayyensa dawasa gida cikin dare da kuma alamun samun kudi ba zato ba tsammani ga iyali-yasa makwabta suka cikin mkwabta ya tabbatar da abinda ke faruwa kuma ya gayawa yaro.

"Labarin ya girgiza kwakwalwarsa," Diana tafadi da bacin rai. Saida haka din yakai shi ga shiga asibitin mahaukata."

Bayan nan ne aka saki ubansu. Daya gano tsananin dulmiya da yayansa suke shiga, yace," Ina rokon Allah domin abu guda kawai, shine ya mayar dani acikin kurkuku domin kada na cigaba da ganin abinda ko faruwa da iyalina."

Yanzu kam hawaye na zuba daga fuskar Diana sosai. "Ya sami yadda yake so, inji ta. "Ya fara koyarda yara darussa, can kuwa aka gaya wa yan sanda. Mai rahoton ya gaya mani daga baya cewa, yayi haka domin a kawar da ubanta daga hanya domin kasuwansu na karwanci. Shine mutumin nan na farko daya fara yin lalata dani." Sabina ta girgiza ta kuma yi bakinciki da wannan mugun labari, ta mika hannu ta rungumi Diana. "Kina jin kunya domin abubuwan da kika yi, kuma haka din daidai ne, inji ta. "Acikin duniya mai wahalarwa, inda har Allah m an giciye akan itace, ba zaka bari a gurbata sunansa ba, wanda kake amsawa a zamanka na Krista. Amma jin ciwo da tsarguwa na yin laifi zai bi da kai zuwa ga adalci mai haskakawa. Ki tuna, akan kalfari sojojin nan basu soki Kristi a gefe domin su bude shi, domin kuma masu zunubi kamar ke da ni mu sami shiga cikin zuciyar sa domin samun gafartawa ba."

Diana tayi game da kalmominta kuma ta amsa a hankali. "Kunya da shan wahala, na san su. Amma har yanzu kuwa munanan tunani na zuwa mani a kullum. Ba na iya kauce musu."

A kullum Sabina nayin addu'a domin Diana da ke cikin taraddadi, kuma a hankali kuwa yar talikan nan ta furta laifinta.

Sabina tayi ta tunanin yadda Diana da kanwarta suka yi zunubi domin su kawo abinci ga iyali. Watakila zunubi mafi girma, tayi shawara, na Krista da suke kashashe masu yanci ne wadanda basu hamzarta kawo abinci da zai rayasu ba.

## INA GANIN KAINA A CIKIN KWAYAR IDANUNKI

Bayan yan makonni aka kawo Sabina a gaban mukaddashiyar kwamandan sansani, wata mata mai jar fuska da hannaye garda garda ga kuma manyan hakora. Kayan sarki da take saye dasu sunyi kusa kamar ma zasu hanata sakewa sai kace sulke.

Kikan yi wa'azi game da Allah ga fursuna, lallai ne ki daina, aka gargadeta.

"Yi hakuri, amma babu abinda zai tsayar". Inji Sabina. Da fusata kuwa mukaddashiyar kwamanda ta dauki hannu zata naushi Sabina sai ta tsaya tana harara.

"Murmushin me kike yi?" ta tambaya, Sabina tace, "Idan har ina murmushi, dalili shine domin abinda nake gain a idanunki." "Menene shi?" "Ni kaina," inji Sabina. "A lokacin da mutane suka kusanci juna, sukan ga junansu a cikin idanunsu. Acikin idnunki nake ganin kaina. Ada nima nakan yi zuciya haka. Na kan fusata na mayar da bakaken maganganu da yin tunani na son kai-har sai da na koyi sanin ma'anar yin kauna. Idan aka sami iya yin kauna, zaka iya sadaukar da kanka domin gaskiya ta dauwama. Tunda nakoyi wannan darasi, bana dunkule hannaye na domin kai bugu."

Wannan hafsa da alamar ta girgiza da irin wannan karfin zuciya na Sabina. Da yake tayi shiru sai Sabina taci gaba tace, idan kika dubi cikin kwayar idanuna, zaki ga kanki

kamar yadda Allah yayiki!"

Sai ya zama ƙamar ma mukadarsiyar, kwamanda ta zama dutse. Nuna fusatarta bai sauya ba, amma ta fadi a hankali, "Tafi daga nan." Sabina taci gaba da shaida Kristi ga fursuna.

## YANCI

Sai kuwa, ba tare da zato ko tsammani ba aka sallami Sabina, tayi kokari ta karanta takardar da ta bada iznin shikarta. "Takardar shaida ta bada yanci" Shine kan maganar, amma rana ta fadi a lokacin, duhu ya hana ta iya karanta sauran rubutun, aka sasu a cikin babbar mota aka fitar dasu daga cikin sansani. Bayan nan basuyi nisa ba aka sauke ta bayan an fita daga birnin Bucharest. Tayi tafiya mai tsawo dauke da kazamin kunshin ta mai wari ta cikin unguwannin waje na birnin.

Ganin ta na farko kenan cikin shekaru uku na mutane da suka tashi aiki akan hanyoyinsu na komawa gida bayan an tashi daga aiki, suna shiga kanti tare da iyalansu, suna ta harkarsu ta rayuwar yau da kullum wanda ita ma tayi kafin a kaita kurkuku.

Sabina tayi sauri tana dokin takai gida sai kuma ta shiga tunanin ko gidan na nan har yanzu.

Tana kuma juyayin irin sauye sauye da zata fuskanta. Bata san abubuwanda suka faru da danginta ba da kuma abokanta.

Mihai kuwa yanzu shekarunsa gomasha hudu ne. Yaya wadannan shekaru suka yi dashi? Har kusan ma tsoro takeji ta bincika, amma kuma tana dokin ganinsa.

Sabina ta bi ta titin Victory, tana juyayi game da caji ofisna na yan sanda inda aka kulle ta. Babu abinda ya sauya. Manya manyan mutum mutumi na mutanen da kwaminisawa ke kira "masu madaukakiyar iyawa" guda hudu-Marx,

Engels, Lenin, Stalin-har yanzu sunanan suna fuskantar titi inda mutane ke wucewa.

Sannu a hankali ta isa wani dogon gini mai gidajen kwana da ta sani kuma ta hau bene. Ta kwankwansa wani kofa, da fatar wannan ma bai sauye ba. Ta kusa faduwa don dacewa domin mai bude kofar kawa ce.

"Sai Sabina taji kamar zuciyar ta zatarfashe lokacinda taga fitsowo ya zama saurayi.

"Sabina! "kawar tari ihu, tana tafa hannu tana kama bakin ta hard a jada baya wai domin ta kara dubawa sosai. Haka na yiwuwa kuwa? Matan nan biyu suka mugumi juna suna hawaye. Sai kuma Mihai ya shigo cikin dakin. Sai Sabina taji kamar zuciyar ta zai fashe da taga shigo warsa ya rame kuma ya kara tsawo ya zama saurayi..

Da suka rungumi juna sai hawaye. Mihai ya share mata hawaye da yatsunsa.

Sabina taji dadin sake ganin danta, t ace idan har zata iya Diana kuka yanzu to ba zata bukaci kara yin kuka ba kuma.

## KALMA GUDA DAYA AKE BUKATA

Acikin yan kwanakin farko, Sabina ta zama kamar wata da aka dawo da ita daga mutuwa. Tana cikin dokin samun yanci! Amma fa tabbacin abinda rayuwa ke ciki ya fara kunno kai" ko da shike ba tacikin kurkuku kuma, har yanzu ita fa abar kyamace ba domin ita matar fursunace, kadai ba amma ita ma fursuna ce.

Idan ba tare da katin raba abinci ba, to ko burodi ba zata iy saye ba. Kuma samun kati ba ya yiwuwa. Wata safiya tajira a layi na dogon lokaci a ofishin gwamnati, da ta isa karamar tagar, yarinyar tace, "Ina katinki na aiki? Idan babu wannan ba za a baki katin raba abinci ba"

"Amma ai ni tsofuwar fursuna ce, bani da wata hanyar karbar katin aiki." Sabina tayi bayani.

Ba zan iya taimakawa ba. Idan babu katin aiki da lamba, to kuwa babu katin raba abinci, inji yarinya, tana kokarin ganin wanda yake kan layi a bayanta, "Na biye".

Har'ila yau Sabina da Mihai zasu dogara ne ga taimakon wasu. An kwace dukan mallakar iyalin Wurmbrand na gida da kayansu. Sa'arsu shine abokai ne keda zama a cikin gidan inda suka zauna, kuma suka gayyaci Sabina da Mihai su zo su zauna a cikin yan kananan kujerun sun lalace babu kwari gadon ma ya karye, kuma babu ruwan famfo babu dakin wanka. Amma Sabina tana godiya domin danta yana tare da ita shi yasa ta dage da ganin wannan wurin ya zama gida sosai.

Wata safiya watanni da dama bayan shikarta wani jami'i daga ma'aikatar cikin gida yazo, wani mai kiba ne gashi da babbar murya da bakin gashi da aka rabashi biyu a tsakar ka. Yana dauke da jakar hannu cike da takardu kamar jakar zata fashe.

Mutumin ya fara karagi wai Sabina ba uwar kirki bace, bata kula dad an ta yadda ya kamata. Sabina ta zauna shiru tana kallonsa. Tasan me zai biyo baya.

Menene amfani inji mutumin na ke ki zauna haka kina jiran wani wanda ke ba zaki iya kara ganinsa ba? Wannan batu ne na yin aiki da hankali cewa mase mai basira irinki ta sami rabuwa da wannan abokin gaban kasa. Idan bata yi haka yanzu ba, to tabbas zata ga cewar nan gaba dole tayi. Har zuwa yaushe takejin zata ci gaba da tsayayya da gwamnati cikin irin wannan makahon wawan rashin biyayya?

Mutumin yana hautsuna tsoratarwa da shegantaka a yayinda yake nuna mata alamun muguwar makoma da zai faru da Sabina. Kauna? Yana mata dariya, kauna? Duk shirme ne, kauna bata kasance ba. Abinda Sabina ke bukata shine sabon miji, sabon uba ga danta, inji shi. Babu kauna domin mai gaba da juyin juya hali na kasa.

Tana ta fasa a cikin cikinta, Sabina tayi tunani, kazo gidana ka gaya mni irin wannan? Ban auri mijina domin lokaci mai dadi kawai ba, hadi ne na har abada, kuma da ko menene zaizo, babu rabuwa.

Mutumin yayi ta magiya na karin rabin awa, kuma dukadai Sabina ba ta ce masa koma ba. Sai ta tuna da watakarin magana wai: Allah da kansa ma ba zai karyata wanda yayi shiru ba.

A karshe mutumin ya tafi yana kada kai. "Ko ba jima ko ba dade zaki zo wajen mu" inji shi. "Sukan zo, ki sani." Duk da rashin kyautatawar wannan mutumin akwai alamar alheri tafe. Sabina tayi tunani: Idan har kwaminis na bukatar ta nemi kashe aureta, to ashe kuma ma'anar ita ce Richard na da rai!

Sabina tajishi yana ficewa, ya tafi gun wata kuma, tana tunanin haka, inda watakila zai yi sa'a.

Hukuma sukan matsa wa matan fursuna su kashe aure domin tsayayya na wannan fursuna da yake yi, har ma na dagewa musamman wanda ya yi alkawarin tsayawa tare dashi ko da me zai faru. Kashe aure yakansa matan su shiga taimakawa kwminisanci. Da zarar an kashe aure, mata sukan yi maza su manta da mazajensu, watakila domin dalilin tsarguwa, hanya mafi saukin yin haka kuwa shine shiga cikin siyasar su. Sabina tasan mata da yawa wadanda suke shelar taken siyasa suna yiwa fursunan da suka haifar wa yaya ba a.

Na uku, yayan da iyayensu suka mutu kuwa, sai abinda hukuma ta yi dasu, wajen cusa masu ra'ayin gurguzu tunsuna kankanana. Kalma guda daya kawai ake bukata yasa haka din yiwuwa. Lokacin da matar wani ta amsawa jami'in kashe aure tace ta yarda, shi zai dauki nauyin yin kome. Bayan yan kwanaki kuma sai a shaidawa mijin, a gaban fursuna abokan dakinsa, "Matarka ta nemi a kashe aurenku."

Sai kuma mutumin yayi tunani, wa kenan nake dashi kuma yanzu mai kula ni? Na zama wawa da ban basu hadin kai ba na sa hannu a takardar ko da wane irin shirme suka rubuta domin na sami yanci na, na fice. Amma idan ma yasa hannu ba lallai ne a sake shi ba har zuwa wasu shekaru. Daga nan kuwa matarsa zata sake yin aure ta haifawa sabon mijinta ya'ya. Ta haka kuwa suke rushe gidaje-iyali-da rayuka.

Sabina takan karfafa matan da ake daure mazansu, tace musu su shirya wa ziyarar irin wadannan jami'ai, kuma su dage wa goyon bayan mazansu, da su kaunaci mazansu a yadda suke, ba wai don yadda ya kamata su zama ba, takan shawarci matan su tuna da lokacin da suke cikin jin dadin aurensu, suyi amfani da wannan domin cin nasara da jarabobi.

Amma a wasu lokuta ba a dacewa domin matsi yayi wa matan fursunan yawa.

## WATA JARABTAR KUMA

Sai kuma wata jarabta tazo ma Sabina, a lokacin tana yar shekaru arbain da uku. Sunansa Paul, kuma ta sani yana son ta. Ya shiga rayuwarta a lokacinda tayi watanni bata ji daga Richard ba, kuma ta fara jin alamar shekaru na tafiya, kuma ma tunani takeyi wai shin yana da rai kuwa.

Da yawa sun zo har kofar gida suna gaya mta cewa sun ga Richard Wurmbrand cewa ya mutu. Gaskiya ne ko kuma dai irin dabarun kwaminis ne?

Idan tayi tunanin Paul, Sabina takan sami wuyar sauraren nata kalamu na basira shi mutumne mai tausayawa, kuma Bayahuden Kristane kamar ita. Yana zaune a cikin daki guda daya tare da iyayensa, kuma watarana yakan dauki Mihai ya kaishi kallon silima ko kuma ya taimaka masa wajen karatunsa. Sabina takan yi tunani. Ga wani wanda mace zata iya zama dashi a cikin kauna da amincewa.

Wasu lokuta Paul yakan rike hannunta a yayin da suke yin magana, kuma Sabina takan sami kanta a cikin kiwuyan zare hannunta daga rikonsa. Cudanyarsu ba ta kaiwa wani matsayi da majmi'a ko doka zata kira shi fasikanci ba, duk da haka Sabina ta sani cewa ba daidai bane.

Watarana paston Sabina yazo wurinta da fuskar damuwa. "Sabina kinsan yadda nake kaunarki kuma ina jin dadin kokarinki," injishi, "Wannan kuwa ba zai sauya ba, ko da me zai faru. Nasan ku duka biyu ke da Richard shekaru da dama, kuma ina fata kin sani cewa ko kinyi zunubi ko baki yi ba, ko kin kaunaci ban gaskiya ko kin ajiye, zanci gaba da kula dake ba tare da bambamci ba domin nasan ko wacece ce ke, ba abinda kike yi ba." Yayi magana da sosa rai sosai kuma cikin gaskiya; sa'annan ya dan dakata kafin yayi tambayar, injishi, yana kallon cikin kwayar idanun Sabina. "Yaya tsakaninki da Paul yake?"

Sabina tayi shiru na dan lokaci. Yacigaba: "Kada ki fitarda tunanin nima na taba shiga irin wannan jarabta. Amma, idan kin yarda Sabina, ki amsa tambaya ta."

"Yana kauna ta", injita, tana sunkuyar da kai. "Ke kuma fa kina kaunarsa?" "Ban sani ba," ta amsa da gaskiya.

"Watakila." Pasto yacigaba. "Na tuna da wani abu da Richard yakan fada: Babu jarabta da kan daddage kafin kaiwa ga abinda hankali zai dauka. Idan kika yi jinkiri, idan kika baiwa kanki lokaci, zaki ga irin barna da zaki yiwa mijinki ko matarka, ko yayanka, kuma. Yanzu ina so ki yanke shawara mai nauyi, Sabina, shawara mafi nauyi da ke akwai. Kada ki sake ganin wannan mutumin daga yau."

Pastor yayi daidai. Ita ce shawara mafi nauyi." Sabina tanaso ta kwaci linzamin gudanar da rayuwarta, ta juyawa tunanin ta game da Paul baya, amma kuma ita mace ce kuma uwa. Ta sani Paul zai zama miji mai kyau, abokin zama mai tunani, wanda zai dauke mata kewa na zama ita kadai.

Kuma zai dace da zama uba ga Mihai. Wannan jarabta ya kusan kaiwa ga inda Sabina ba zata iya hayewa ba, musmman ma da yake abokanta na majami'ar su sun gaya mata mijinki ta mutu, kinyi rayuwa mawuyaci ai ya isa haka. Bari wannan mutumin ya kula da ke. Shi kyakkyawan Krista ne kuma yana kaunarki."

Paston ta shi kadai ne yayi karfin zuciya da yake ya amince mata domin gaya mata abin da ya kamata a gayamata. Kuma Sabina ta sani cewa yayi daidai. Ta sani shaidan yaso ya rushe shaidarta. Saboda haka dakyar ta sami karfin gayawa Paul cewa bai kamata su kara sake saduwa ba, daganan sai ta sake kara bada kanta ga jiran Richard din ta.

## LAYI GOMA NA RUBUTU A JIKIN KATIN AIKA GAISUWA

Bayan yan makonni Sabina tana majami'a, tana wanke dabe, sai ga kawarta Marietta a guje, tana daga katin gaisuwa a hannunta. Hawaye ne zubo mata. "Ina zato-Sabina, ina zato wannan katin daga...."

Ta kasa cingaba da yin magana, ta durkusa akan jikakken daben kusa da Sabina.

Sabina ta juya wannan dan kati. An sa hannu da sunan "Vasile Georgescu." Amma rubutun na Richard ne gasu kwara kwara kuma amma gwanin kyau, babu wata shakka. Idanun Sabina suka cika da kwalla sai ta rungumi katin a kirjinta.

Ta sani cewa fursunan siyasa layi goma kacal na rubutu ake yarda suyi a jikin katin gaisuwa tare da takunkumi-duk yayin da aka yardar musu da yin haka. Me Richard zai iya fadi bayan irin wannan dogon lokaci da baima sani ba ko matarsa da dansa suna da rai?

Sabina taja numfashi kuma ta karanta kalamu da kwalla cike cikin idanunta.

"I tsawon lokaci, da kuma nisa da ke tsakani yakan kashe kauna mara zurfi, amma kauna mai zurfi kam sai kara zurfafa zata cigaba da yi, "ya rubuta. Sai kuma yace tazo ta ziyarceshi a wani lokaci da aka basu a can Tirgul-Ocna, asibitin kurkuku.

Katin gaisuwa na Richard shine labari mafi kyau da Sabina ta taba samu. Ko da shike abin ya taba mata zuciya, ta sani ba zata iya ziyararsa ba. Dole ne takai kanta a jaji ofis na Bucharest a kowane mako, kuma sunki su saukaka mata hana fita daga cikin birni da akayi.

Saboda haka ba zata iya bayyana acan ba a wannan ranar domin ganin fuskar mijinta masoyi. Amma tana farin cikin cew Mihai zai dauki gurbinta.

Tirgul-Ocna na arewacin Romania, daga daya gefen jerin duwatsun Carpathian. Jirgin kasa da ke tashi daga Bucharest yakan yi tafiyar daruruwan miloli suna kewaye duwatsun kafin su kai ga wannan karamin gari.

Sabina ta shirya da wata kawarta da ake kira "Anti Alice" ta tafi tareda Mihai zuwa kurkukun. Amma Mihai kadai ne za'a bari ya gana da Richard.

Sabina tayi ta jira cikin doki a baya. Mihai da Anti Alice sun tafi yanzu kwana biyu kenan, kuma a cikin wannan lokaci tunani da damuwa iri iri sun shiga tunanin Sabina: Shin kuwa Mihai zai iya ganin ubansa? Ko za a yardam ma Richard ya karbi tufafi da abinci da ta aika masa? Tunda a asibitin kurkuku yake to watakila bashi da lafiya ne. ko zai iya mikewa tsaye? Kai ko ma zai iya yiwa Mihai magana? Kuma yaya amsar Mihai zata zama ganin ubansa bayan wannan dogon lokaci na shekaru? Ko zai sami damuwa idan yaga Richard a cikin irin halin da yake?

Sun iso gida a makare wajajen karshen watan Disamba da dare. Sabina taji su suna hawo matakalar bene, kuma kafin ma ta isa kofa, Alice tace, "Mun ganshi! Yana da rai. Kalau yake!" suka shigo ciki a jike da dusar kankara a kafadunsu. "Mihai!" Ta rungume shi.

"Iya! Baba yana lafiya, kuma yace a gaya miki cewa ya sani ya kusan dawowa gunmu. Idan har Allah zai yi wannan al'ajibi na bari ya ganni, to nasan cewa yana iya yin wani al'ajibin kuma na sake kawo mu gabadaya tare."

Suka yi kwalla "Munyi ta shan jira na tsawon lokaci a cikin dusar kankara," inji Alice. "Sun bari mun shiga ta tsaya a wani fili da aka killace shi daga gine ginen asibitin. Fursunonin kuma aka sa suka ketare wani budadden fili suka karbi bakinsu. Ganinsu ma babu dadi. Abin tsoro! Gasunan kawai taron wasu ramammu kamar fatalwa! Kuma acikin su da ke wucewa na hangi Richard! Sam ba ka kuskureshi, dogo ne shi. Nayi ta daga hannu kamar zan haukace amma bai iya dago niba. dukkanmu a tattare muke kuma kowa na daga hannu. Na ganshi-amma Mihai kadai aka bari su gana.

Acikin irin wannan yanayi, basu iya samun damar gaya wa juna wani abu takamaimai ba, inji Mihai. Amma kalamu na karshe da ubansa ya gaya masa sune, "Mihai, kyauta kawai dazan baka a zaman uba shine ingaya maka wannan: A kullum ka nemi halin Krista mafi nagarta, wanda shine na auna dukan abubuwa yadda ya kamata."

Sabina ta soka katin Richard a cikin littafinta mai tsarki. Daga lokaci zuwa lokaci kuwa takan zaro ta sake karantawa. Daga baya ya gaya mata cewa, a kurkuku ya zama gwanin tsara takai tattun sakonni da ake yarda fursuna su rubuta-ta haka kuwa wasu sukan zo wurin sa domin taimakawa ya tsara musu yan harufan da aka yardamusu su zama. Sukan kuma tuntubi juna game da abin da Richard ya tsaramusu, saboda haka tsarin Richard ya mamayi ko ina. Kuma galibin sakonnin fursuna ya kan fara da, "Tsawon lokaci da nisa da ke tsakani yakan kashe karamar kauna, amma babbar kauna kuwa sai kara karfi take yi." Sai gashi kalmomin Richard na kauna da karfafawa na samun karbuwa a kusa da ma nesa. Mai wa'azin kurkuku fa ya koma aikinsa.

## WATA SAFIYA MAI GAMSUWA

Shekarar 1956 ya fara da bangaren kwaminis kacokan suna cikin yanay ina tawaye. Tsari na aiwatarwa a cikin shekaru biyar na Soviet bai je ko ina ba. Har yanzu ana cikin karancin samun abinci, kuma albashi yayi kasa. Duk alkawurran kyautatuwa da akayi musu bayan mutuwar Stalin ya sha ruwa.

Daganan a watan Fabrairu, a lokacin babban taro na kungiyar kwaminis, sai Primiyan Soviet, Nikita Kruschev ya shirya wani bayani a boye na sukar Stalin da ayyukansa. Mutanen Russia basu taba yarda sun buga wannan bayani ba, amma kafin wani lokaci, a cikin kowace kasa da take gabashin Turai, mutane sun ji iskar siyasa mai dumamawa tana narkowa tana tsiyayowa daga Moscow.

Alamu na rage-dogaro ga ayyukan Stalin suka fara hamzartowa. Aka rage yawan masu tsaro na rukunai dabam dabam da nayyan sandan sirri ainun. Aka shiga yin yarjejeniya ta kasuwanci na milyoyn dala da kasashe yammaci domin farfado da tattalin arzikinsu. Aka saukaka batun tattare tattaren komi a hannun hukuma. Kuma mafi kyau duka aka fara sakin fursunonin siyasa masu dinbin yawa a kowace rana, a karkashin wani shirin gwamnati nayim ahuwa.

Sabina ba ta ma yi tunanin Richard zai zama daya daga cikinsu ba. Bata sami wani labari ko alama ba, cewa zai sami fitowa da wuri. Tunda yake yana da sauran shekaru da yawa a kurkuku.

Sai kuwa a wata safiya mai gamsuwa acikin watan Yuni 1956 ta fita zuwa ziyarar abokai, da ta dawo gida kamar kwarangwal ba mutum ba, Akarshe dai Richard ya dawo gida, da ya rumgumeta Sabina ta kusan suma. Wata rumguma ce da take tsoron mai yiwuwa bazai sake faruwa ba. A wannan daren abokai sunzo daga ko ina cikin Bucharest domin su gaishe shi, tare kuwa akayi dariya kuma aka zubar da hawaye-biye da karin dariya da karin zubar da hawaye.

Richard ya azabtu ainun a kurkuku. Ansha yi mas duka da kayan azabtarwa iri iri, ansha bugar dashi da kwayoyi iri iri. Manyan tabbuna guda gomasha takwas sun rufe jikin sa, daga baya likitoci suka gano huhunsa na rufe da tabbuna da suka warke na tarin fuka. Kowa yana ta'ajibin yadda yayi ya rayu a cikin wadannan shekaru takwas da rabi (kusan uku daga shekarun acikin dakin daga-kaisai kai a karkashin kasa) ba tare da samun magani ba. Yanzu dai an bashi gado mafi kyau a asibiti. Abin mamakin shine fursunoni da aka sallama suna samun kula da mutuntawa duk inda suka tafi. Sune suka zama rukuni da ake sha'awar yiwa alheri a cikin Romania wani matsayi kenan da ya baiwa yan kwaminis haushi.

Bayan da Richard yaji sauki, da shi da Sabina suka yi bukin zagayowar ranar aurensu na shekara ashirin. Babu ko dayan su da ke da kudin sayen wata kyauta, amma Richard yayi kokari ya sami wani dan karamin littafin rubutu mai kyau wanda yake rubuta ayoyi a ciki kowace yamma-kalmomin kuma da yake rubuta wa Sabina, kaunatacciyar sa.

Dukan su sun tsere wa jaraba da kuma azaba. Allah ne karfinsu. Kauna kuma itace dalili. Amma a yayinda yanzu wannan taraddadin na bayansu, wani damuwar na jiransu a kofar gida.

"Kaine Richard Wurmbrand?" Kaftin shugaban yace da tsawa, "ku shiga wan can daya dakin dukanku. Kuma ku dakata a ciki." Kuma sai gashi dan karamin gidan nasu ya cika da mutane, suna bude kabad, suna zubarda takardu a kan dabe. Akan teburin Richard aka sami shafuka da akayi rubutun, wa'azi da aka buga da kekken rubuta, da kuma tsofaffin Littafi Mai Tsarki. Aka kwace duka. Daganan suka gakyaytar ranar haifuwa wa Sabina wanda Richard ya rubuta mata kalamun kauna a ciki.

Idan ka yarda kada ka dauki wannan. Wannan batu ne na tsakanin mutum da mutum, kyauta ce. Bashi da amfani a gareka, "Inji Sabina. Amma ina sun dauka.

Kaftin dinnan yasa wa Richard ankwa a hannu ya fita dashi ta bayan daki. Sabina tayi magana da karfin zuciya. "Bakwa jin kunyar cin zarafin mutanen da basuyi komai ba?" Richard ya nufi wurinta, amma suka rike hannunsa suka jawo shi baya. Ya gargadesu, "B azan bar gidannan haka ba, har sai dole kun barni nayi wa matata adabo." Bar shi yaje," inji Kaftin. Daya daga cikin yan sandan ya kwance ankwar.

Suka durkusa tare cikin addu'a, da yansandan kewaye da su. Sai suka raira waka a hankali. "The Church's one Foundation is Jesus Christ her Lord." Wani tafin hannu mai fadi ya fada kafadun Richard, yakamata mu tafi. Kusan karfe biyar kenan lokacin." In ji kaftin din a hankali. Kaunar da Richard da Sabina ke yi wa juna ya bashi mamaki. Idanunsa na kwalla.

Aka maida ankwa a hannayen Richard suka fita dashin Sabina ta

bisu har kasan bene. A kasa Richard ya juya kai yace, "Ki aika kaunata ga Mihai, "sai ya tsaya shiru."

Daganan suka tafi. A yayin da motocin yan sanda suka kama hanya, Sabina ma na binsu da gudu a cikin dusar kankara, tana kìra tana kuka, santsin kankara na ta kwasar ta. "Richard! Richard kaunataccena!,"

Mota kuwa da takai kwana sai ta bace mata, sai ta tsaya tana haki ga bacin rai. Bayan tana kuka tana addu'a. "Ubangiji na bada mijina a bannunka," tayi kuka. "Ni ban iya yin kome ba, amma kai kana iya wucewa dashi ta cikin kofofin da ke kulle. Kana iya kewaye shi da mala'ikunka. Ka dawo da shi! "Ta zauna a cikin duhu tana addu'a, har sai da rana ta fito Anti Alice tazo da safe kuma ta tarar haryanzu tana kan dabe a kwance. Sabina ta dubi Alice da jajayen idanun tan a kuka tace. 'Sun sake sace mani Richard dina."

## JAWABI

Richard ya sake tafiya sai bayan wasu shekaru shida, kuma Sabina dama guda daya kawai ta samu na ganinsa cikin tsawon wannan lokaci.

Taci gaba da aikin tan a majami'ar karkashin kasa cikin kanun kai tana jiran dawowan mijinta, bata yarda tama yi tunanin cewa Allah ba zai kawo shi gida ba.

A watan Disamba na 1965 aka fanshi Richard akan kudi dala dubu goma. Kungiyar Mishan ta Norwegia domin hadakan Krista na Yahudawa da Ibraniyawa su suka biya kudin. Farashin biyan kudin fansa na fursunan siyasa a wancan lokacin dala dubu daya da dari biyar ne. Richard da Sabina basa son barin kasarsu ta Romania, amma masu bi da majamiar karkashin kasa suka rinjaye su da su tafi, domin su zama murya ga wadanda ake azabtarwa domin ban gaskiyar su da kuma zama shaidar kaunar Allah na al'ajibi a tsakiyar lokacin shan azaba. Shekara na biye kuwa sai Richard, Sabina, da Mihai suka sauka a Amirka.

A cikin samun tsananin barazanar kisa daga kwaminis, nan da nan iyalin Wurmbrand suka zama murya domin yan'uwansu maza da mata wadanda bangaskyarsu ke cikin tsanani.

A cikin watan Oktoba, 1967, dauke da dalar Amirka guda dari kacal da kuma wata tsohuwar kekken rubutu da aka dora akan teburin kicin, iyalin Wurinbrand suka fara rubuta mujallar da ake kira Muryar Shahidai. Tundaga wannan bugu na farko, anci gaba da dab'i akai akai, kuma an rabarda kusan miliyan goma ko ina a cikin duniya kuma a cikin harsuna da dama.

Daga lokacinda Richard da Sabina suka sauka a Amirka, sunyi aiki babu gajiyawa domin yin shaida ta karfin zuciya da kauna a cikin tsakiyar shan wahala da shahidancewa. Rayuwarsu ta karfafa neta wurin jarabobi da suka yi jimiri.

Ba da jimawa ba kafin rasuwar Sabina da ciwon daji shekarar 2000, ta roki kaunataccen mijinta (Wanda shima bashida lafiya kwarai) ya zo gefen gadon da take kwance. I bainar wasu abokai da suke wurin, Sabina ta sake gaya wa Richard irin kaunar da take yi masa, kuma ta rokeshi ya gafarta mata duk wani kasawarta a rayuwa. Sabina tana cikin tsananin ciwo a lokacin. Amma taki shan magani, domin ta zama tana cikin hankalinta a lokacin da zata yi bankwana da wannan rayuwa na duniya da ya tsawwala mata ainun amma duk da haka ya kawo mata farinciki.

Nata rayuwa ne da yasami taimako ta wurin kaunar Kristi da kuma irin kauna da take nunawa duka wadanda suka santa.

# Tara:

## Rayuwa A Cikin Guje Guje

*Pakistan*
*Yuni 1985*

Ma'aikacin gidan waya ya iso wannan babban gida kuma ya leka ta taga. Zauren shiga gidan kawai ya ka girman gidaje da yawa a cikin kauyukan Pakistan. "Ina da pakiti domin Tara," inji ma'aikacin a lokacin da wani baran gidan ya amsa. "Ina da bukatar sa hannunta. In shigo?" Yana dauke da wani dan akwati mai launin kasa kasa akarkashin hamatarsa, da alkalaminsa a shirye.

"A'a, ba zaka iya shigowa ba," inji baran. "Bani pakitin na kaiwa Tara. Baban ta ba zai barta ta zo bakin kofa ba."

"To," Ma'aikacin gidan waya ya yarda. Amma lallaine sami hannun Tara ko kuma wani babba, idan ba haka ba bazan bar pakitin ba; an gane?" "I, inji baran, hannayensa'a mike.

Tara tana kallo daga wani lungu tana mamakin ko me ke gudana, kuma ko wanene?" Baran ya motsa kafadunsa ya mika wa Tara takarda ta sa hannu, sa'annan t a dauki pakitin. Pakitin na da dan nauyi fiye da yadda ta zata. Sai ta dauka ta nufi dakinta, ta shiga ta rufe kofa. Koda shike gidan iyalin Tara na da girma duk da haka tana da nata daki gwanin kyau da ado mai tsada na kayan daki.

Baban Tara yana ji da diyarsa, kuma dakinta na cike da irin kyautattukan da uban ya keyi mata.

Yanzu kuwa Tara take zumudi irin da kowace yar shekaru gomashabiyu zata yi idan ta sami pakiti irin haka da bata tsammata ba daga gidan waya. Ta ajiye pakiti a kan dabe, ta durkusa ta daye tep da aka nane dashi ta bude. Ta duba cikin pakitin. Sai Tara ta yi haki, zumudin farin cikinta ya zama abin tsoro da damuwa. Ta mike ta nufi kofa, ta bude dan kadan ta leka waje, tana dube dube domin ta tabbatar cewa babu kowa kusa, ta sake rufe kofar, amma yanzu kam kullewa ma tayi kafin ta dawo gun pakitin a tsakar dakinta.

Wata murya na gaya mata cewa ta baiwa ubanta pakitin. Shine abu mafi lafiya, tana gaya wa kanta. A saukake sai ta gayawa uban cewa bata san yaya sukayi pakitin ya iso da sunan ta ba. Amma gaskiyar ita ce Tara ta san dalilin zuwan pakitin. Yana kunshe da wani abu da ta nemi a aiko mata. Yan makonni da suka shige ta cika wata takardar nema da aka buga a jarida ta aika. Yanzu gashi abin da ta nema ya iso, kuma tana tsoron abin da zai faruda ita idan aka same ta da su. Tunanin ta irin na yaro yayi ta kaiwa yana kawowa. Lallai ne ta yanke shawara, ko ta ajiye, amma a boye, ko ta gaya wa ubanta. Kwakwar ta ya sha kan tsoronta, sai ta dauki daya daga cikin Kananan Litattafan cikin pakitin. Littafin da dauka yana da kan magana daya tak; Farawa. A zaune kan gadonta sai ta fara karantawa.

Daga ranar farko da darusan koyar da Littafi Mai Tsarki ya iso. Tara tayi kokari ta koyi darusa biyuko fiye kusan ko wane mako. Ta nane amsoshin tambayoyi na karshen darusa a cikin ambulo da yazo da pakitin ta baiwa baran gidan aka aika gidan waya. Bayan wani dan lokaci takardar shaidar kammala karatu zai iso, tare da gaisuwa ga Tara.

Tara, diya ce da aka haifa a cikin wani sanannen iyalin Musulmi na Pakistan, ba ta yi shiri na sauya addininta ba.

Ta dai sami kanta ne a cikin yin nazarin darusan Littafi Mai Tsarki, kuma ta yi ta sha'awar samun takardun yabo na shaidar yin karatu. Gasu da sauki kuma da ban sha'awa, ko dashike wataran takan damu wajen zarowa da mayarwa inda take boyewa a kullum. Barorin gidan dake karbowa ko aikawa da sakonnin sun rantse da cewa babu wanda zai sani. Amma kuma kowa ya sani cewa Tara ce yar gaban goshin ubanta. Zai fusata ainun, amma mai yiwuwa fada kawai zai yi mata kuma ya kwace takardun.

Bayan shekaru biyu da rabi, Tara ta aika da jarrabawar ta ta karshe. Ta kammaia karatun duka. Taji dadin cewa ta iya kammala kwas mai yawa haka, kuma tana yin mamakin cewa dukan kwas din nan kyauta ne bata biya ko anini ba, kuma asirin ta bai tonu ba har ta gama. Bayan yan makonni ta kara yin mamaki domin wani pakitin ya sake isowa, kuma da nauyi. Tara ta sani daga wadancan mutanen ne da suka aiko da fari, amma ba ta san ko menene ke ciki ba. Tayi mamakin ganin shudin Littafi Mai Tsarki gwanin kyau da zane na ruwan zinari a bakin Littafin.

Wannan shine Littafi mafi kyau da ta taba gani. Tana bude shafin farko sai taga sunanta a rubuce da kuma godiyar kammala karatun ta. Tara ta bude yan shafuka tana duba wa kafin ta boye wannan kyauta ta ta a karkashin gadonta tare da sauran Litattafan. Takardun darusa ma akwai hadari, ballantana kuma gashi Littafi Mai Tsarki ne, idan aka kama ta da shi ta sani akwai tashin hankali. Da gaske ma dai bat a iya sanin abin da zai faru.

## KRISTA

A cikin shekara na biye, bayan ta gama shekararta ta goma a makaranta da sakamako mai kyau, an gayyaci Tara taje tayi nazari a Iran game da darasin nazarin kwatanci na addinai. Iyalin ta sukanyi ziyara ta addini zuwa kasar Iran akai akai, Tara kuwa tana dokin daukar wannan kalubale na zuwa can. Kuma ta bada gaskiya cewa wannan darusa da ta koya a cikin sirri zasu taimaka mata wajen fara nazari akan addinin Krista.

Iyalinta sun raka ta zuwa wannan nazari, kuma lokacin da suke Iran ne Tara ta gamu da Krista na farko a rayuwarta. Ya faru ne a lokacin da ta fita daga hotel da rana dan daukar hotuna a cikin kewayen hotel din wajen masallacin domin shirin gabatar da wani darasi na ajinsu. Akwai hadari ga karamar yariya kuma bakuwa ta yi yawo ita kadai, amma Tara ta yi wa wanta alkawari, shi kuwa yana cikin nemanta cewa ba zata yi nisa da hotel din ba, dakyar ya yarda ya barta tafita.

A yayinda take ratsa filin cikin gidan tana daukar hotuna, sai wani abu yaja hankalinta. Wani mutum yana zaune kusa da wata yarinya wacce ta gaza wa Tara da shekaru. Hannayen sa a nade, kuma ya daga kansa a sama, kamar yana magana da wani.

"Me kake yi?" Tara ta tambaya, tana jin wani irin jan hankali ga wannan mutum. 'Ina magana da Allah," ya amsa.

"Ba zaka iya yiwa Allah magana ba," Tara ta musa, tana hada kalamunta da dariya. "Ba zai sauka kasa yayi magana da kai ba, kuma ba zaka iya tafiya gurinsa ba sai dai in ka mutu. Sabo da haka yaya zaka fadi irin wannan, cewa kana yin magana da Allah?"

Mutumin ya dubi Tara da jimirin hakuri, tare da murmushi kuma sai ya kara, "Ba wai kawai nayi magana da Allah ba, har na sami amsa."

Yanzu kam ga Tara mutumin nan hauka yakeyi "ka sami amsa? Kai ba annabi bane ko kuma wani mala'ika. Ta kaka zai yiwu ka sami amsa daga gun Allah?"

"Kina so kisan yadda zaki iyayin magana da Allah?" "I, lallai ina so in sani," inji Tara, Bata gaskanta shi ba ko kadan, amma tana so taji bayaninsa, koda shike a gareta ji take ba mai yiwuwa bane. To ki same ni gobe da karfe hudu, anan, zan rubuta maki sunan wurin." Ya zaro takarda ya rubuta mata adireshin majami'arsa. "Ki zo nan, kuma ba kawai zaki koyi iya yin magana da Allah ba, amma zaki sani cewa yana kaunarki kuma."

A lokacin da Tara ta koma cikin hotel ta fadi abin da ta gani wanta ya fusata. "Tunanin me kike yi?! Ba zaki tafi wannan wurin ba. Majami'a ce ta Krista! Wannan kasar Iran ce, kuma ke Musulmace. Ana iya rataye ki idan aka kama ki a irin wannan wurin!"

"An bani aikin yin nazari game da addinai dabam dabam. Kaka zanyi na kammala karatuna idan banyi bincike ba?" Tara ta dage.

Wan Tara ya yarda amma saisun nemi izini daga caji ofis mafi kusa domin ta ziyarci majami'ar. Daga can aka tura su zuwa Kotu, inda ake ba da izni. Amma hukuma tana bukatar yan sanda guda goma sha biyu su raka ta tare da wanta, a lokacin da zata ziyarci majami'ai.

'Kada kiji tsoro," in ji wanta, "Ina waje tareda yan sanda ko da wani abu zai faru."

Tara tayi ta mamaki, wai shin me ke tafiya ne a cikin majami'a da zai bukaci irin wannan gagarumin tsaro.

Washe gari da karfe hudu, Tara ta shiga cikin Majami'a. Ta shiga a hankali, jikin ta yana ta rawa, a yayinda yan sanda da wanta suke jira a waje. Banda mutumin nan da tagani a cikin filin hotel bata taba ganin wani mahalluki ba a duniya wanda ba musulmi ba. Sai mamaki take cewa ko yaya kamannin Kristoci yake, yadda suke, su mugaye ne?

Ta sami wurin zama ta baya, ta zabi wurin zama kusa da kofa domin saukin ficewa, kuma an fara raira wakoki.

Mambobi suka yi wakoki iri iri, kuma Tara tace ta gane da wadansu kalmoni a cikin wasu ayoyi da tayi nazari akai. Bayan wakokin wani ya tsaya akan bagadi yana magana game da yin addu'a. yace duk wanda yake da bukatar addu'a ya zo gaba. A yayin da wasu suka fara zuwa gaba, Tara taga mutumin da suka gamu wanshekare. Yana dauke da wata yarinya yar shekaru takwas: Tara ta dauka ko daya daga cikin yayansa ne. Wannan kuwa da alamar kafafunta sun shanye, hannayen ta na reto a bayan ubanta da yake dauke da ita,

gatanan ne kawai kamar ma baat da rai.

Mutumin ya fito zuwa gaba ya fara addu'a da murya, yana rokon Allah ya warkadda diyarsa. Sauran jama'a suka shiga yin addu'a tare da shi suna rokon Allah ya warkadda diyarsa. Tara ta sake yin tunani ai haukane ma mutum yace zai yi magana da Allah ta haka. Me yasa Allah zai sauko domin ya warkarda wannan ya? Ga Tara, wannan baiyi ma'ana ba sam. Amma duk da shakkarta, abin da ketafe yana faskara mata kai, shi yasa take san sanin dukan abubuwan da ke faruwa domin ta sami rubuta su a nazarin ta da tazo yi.

Sai Tara ta lura da cewar gurguwar yarinya ta fara motsi. Kafafunta na mikewa a hankali, sai ubanta ya ajiye ta a kan dabe a hankali, yana taimaka mata da ta tsaya a tsaye ya Allah na! Tara tana tunani, ba zan iya gaskata wannan na faruwa ba.

Wadanda ke cikin majami'a kuma suka shiga yin wakoki ga Allah a yayinda yarinyar ta sami warkarwa, sai ta taka ta bi hanya zuwa kofa ta dubi Tara a fuska. Lokacin da ta isa benci da Tara ke zaune, sai tace "Emmanuel" daga nan sai ta juya ta koma inda babanta yake.

Abin da ya faru ya girgiza Tara ainun - da kuma dukan tunani da ke cikin kanta. Me ya sa wannan yarinya ta zo wurinta, cikin dukan mutanen da suka cika majami'ar? Yaya kafafun nata suka dawo? Kuma menene ma'anar Emmauel? Tara yar nazarin addinai tana samun tambayoyi fiye da amsoshi. Ta dage da son fahimtar abinda ke tafiya.

Ba ta kuskura ta gaya wa kowa abin da ta gani a majami'a ba. Amma fa batun ba wanda zata manta bane. Bayan da ta koma Pakistan, sai ta tafi wurinda anan ne kadai take jin zata sami amsa. Sai ta tafi ga shudin Littafin ta Mai Tsarki. A wannan karo ba karatu na cin jarrabwa Tara takeyi ba, tana kokarin bincike domin sanin gaskiya. A kullum tana duba ayoyin, tana kokarin fahimtar bambamci tsakanin Littafi Mai Tsarki da Kur'ani, kuma tana kokarin sanin ko menene dalilin da Musulmi ke gaba da Krista ainun.

Allahn Kristana zahiri ne, tana tunani. Idan ba haka ba yaya zai ji su idan sukayi addu'a?

## AN TONA ASIRI

A karshe dai Tara taga cewar ta kure iya kokarin kanta game da wannan al'amari. Dole tayi magana da wani. Maimakon kara mata sani, wannan nazari na addinai a kuma abin da ta gani a cikin majami'a kuma ta karanta a cikin Littafi Mai Tsarki - ya bijiro da karin tambayoyi, kuma ta matsu da ta sami fahimtar abubuwa.

"Baba, zan fita tare da wasu abokai," Tara ta gaya wa ubanta tana cikin shirin fita. Na farko kenan a cikin rayuwarta na shekaru goma sha shida, da tayi wa uban karya, sai kuwa tayi ta jin tsarguwa akan hanyar ta ta fita daga babban gidansu mai cike da kayan alatu. Amma lalle ne ta binciki batun addinin Krista ko menene ke ciki. Kuma komawa cikin majami'a itace hanya kadai da ta sani na yi.

Ta kama hanya zuwa wata majami'a a ketaren birnin, ta sake zama a benci na baya daidai fara sujada. Daga nan ta gabatar da kanta ga mutumin da ya jagoranci sujadar, ta gaya masa tana so tayi wasu tambayoyi. Pastor ya amince. Tara ta dauka cewa dukan Majami'a, majami'a ce kuma dukan Krista, Krista ne, kuma ko wannensu ma nai ya taimaka mata. Amma, a wannan kam, ba haka yake ba.

Pastor ya fara gajiya da tambayoyin Tara masu yawa, da yake tana zuwa daga mako zuwa mako tana yi masa tambayoyi. Ya damu domin lafiyar sa ikuma ya gaya mata fiye da sau daya cewa zai fi dacewa ta daina zuwa. To ina zani na sami amsoshin nan in ba nan ba?" in ji Tara.

Nacin da takeyi yakai har zuwa wani lokaci, amma a karshe sai Pastor ya ga cewa hadarin yana da yawa ainun. Yana tunanin cewa zai iya rubutawa uban Tara ya gaya masa cewa Tara na zuwa majami'arsa tana yin tambayoyi masu

yawa game da Littafi Mai Tsarki. A cikin karamin lokaci ya tona asirin yarinya musulma, wacce take neman sanin Allah.

"A zatonki me kikeyi?"! Uban Tara yayi mata tsawa da ta dawo gida da rana. "Ko kina same da irin abin kunya da kika kawo kaina da kuma wannan iyali? Ko me zai kawo kije wurin wancan mutumin? Shi ba musulmi bane. Shi Krista ne! Wace irin yarinya ce ke? Yanzu kin zama daya daga cikinsu ne?"

Fusatar da uban yayi ya girgiza Tara, bata taba ganin haka da shi ba. Ta yi kokari ta yi bayani cewa tambayoyi kawai take yi, babu batun sauya addini zuwa zama Krista, amma yaki ya saurare ta. Da fushi kuwa ya kore ta daga gabansa, kuma Tara ta fice a guje tana kuka. Ba ta da masaniyar abin da ta shiga ciki ko kuma yadda zata sasantawa ubanta rai daga fushinsa.

Kuma gashi har yanzu tana da tambayoyi da ke neman amsoshi. Can cikin dakinta, duk da abin da ya faru, Tara ta sami kanta ga duba Littafin ta shudi. Tana share hawaye, ta bude Littafi Mai Tsarki tayi kokarin ta karanta, a yayinda irin fusata da ubanta yayi yana ta bi a cikin zuciyar ta.

A hankali kuwa kalmomin suna jan hankalin ta, suna kwantar mata da zuciya, suna tattausa damuwar ta kuma suna karfafa ta da kaunar Allah. Taci gaba da karatu har ma bata san lokacin da ubanta ya shigo dakin ta ba, da farko fuskarsa ta nuna nadama ga yiwa diyarsa tsawa haka.

Amma lokacin da yaga abinda take karantawa sai fuskar ta koma ta fusata.

"Ke Krista ce! Yanzu na sani! "yayi tsawa. "Baba, nayi alkawari ni ba Krista bace. Ni ina dokin neman sani ne, Lallaine ka gaskanta batu na!"

'Kada kiyi mini karya! Me zaisa ki karanta Littafi Mai Tsarki?" Idan ka yarda, Baba! Ai Littafi ne kawai nake karantawa.

Kasan nasha yin nazari kwanaki." Tara tana iya kokarinta ta rinjaye shi cewa babu wani nufi, a lokacin ne kuwa ya kai mata mari a fuska.

"Yaya zakiyi wa wannan iyali haka? Mu Musulmi ne!" Ta ja da baya cikin cin zafi, idanunta a bude da mamaki cewar ya buge ta. Yanzu ma ya sake zuwa ya nareta. "An haifemu musulmi, kuma zamu mutu musulmi. Kuma daga yau ke ba diya ta bace!

Kukan da Tara takeyi ya jawo hankalin wanta ya taho a guje zuwa dakinta domin yaga me ke faruwa. "Yar'uwarka ta zama Krista! Takan ziyarci Pastor, kuma gashi yanzu na sameta tana karanta Littafi Mai Tsarki!"

Daga jin haka, nan da nan wan Tara ya fusata ya juya kan Tara, tare da uban suka hauta da duka. Da idon sa ya fada kan Littafi Mai Tsraki sai ya dauka ya

yayyaga. Uban Tara ya dauki bel ya ninka yayi ta jib gar Tara a fuska da baya a lokacin da take kwance kan dabe tana kuka.

Baba kayi maza ka samo mata miji, kafin irin wannan ya ci gaba', inji wanta, fuskarsa yayi jawur da fusata. A lokacin da suka fice daga dakin ta uban yana kada kai.

## EMMANUEL, EMMANUEL

A yayinda Tara ke kwance akan daben daki tana kuka sai ta furta addu'ar ta ta farko. "Allah, bansan abin da ubana da yayana suke magana akai ba ni Musulmace, amma a yanzu bansan wane hanya ne ya kamata na bi ba. Ina roko, ka nuna mani, kuma ni zan bi. Tara taji wata salama bayan addu'a, kuma a kwance anan barci mai nauyi ya kwashe ta. Tana iya jin wata murya; kamar ma wanio ne ke tahowa gurin da take. Muryar na cewa "Emmanuel, Emmanuel." Tara ta tashi zaune ta duba cikin dakin, amma babu kowa. sai ta lura ai mafarki ne, ko ba haka ba? tana kokarin maimaita kalamun nan da taji na mamaki a karo na biyu, 'Emmanuel".

Tara ta kwanta akan gado tana tunanin abinda ya faru a kasar Iran.

"Menene ma'anar wannan?" ta na fadi. :Kuma ko me ya sa nake ta cin gaba da jin wannan kalma?"

Ta taba fuskarta a hankali tana jin zafi. Ubanta bai taba dukan ta ba a dukan rayuwarta, kuma wannan fushi na ubanta ya ragargaza ta. Da ita da ubanta sun shaku ainun, amma yanzu ta san ba zasu kara kusan tuwa ba. Ta sani fusatar da ke zuciyar uban ba zai huce cikin sauki ba, kazalika nata zumudi na neman sanin gaskiya. Bayan yan kwanaki sai uban Tara ya zauna da diyarsa, da fuskarta a kukkuje daga duka da tasha. Anan ma ya fuskance da fuskar nadama a idanunsa. " Tara kiyi hakuri domin abin da nayi maki," inji shi. "Abin kunya ne uba yayi wa diyarsa duka. Lallai ne ki gane cewa bani da nufin inji maki ciwo. Wannan alama da kika bani ya fi gaban na daure. Idan kin yarda ki gafarta ma ni". Tara ta zauna shiru, ba ta yarda ta amince da wannan sabon ba da da hakuri ba. "Na sani yanzu ne lokacin," ya ci gaba, da ya kamata kiyi aure."

Tara ta tuna da abin da wanta ya fadi bayan da suka yi mata duka. Amma shekarun ta goma sha shida ne kawai kuma ba ta yi shirin yin aure ba. "Baba, ban isa yin aure ba, ina so in karasa karatu na. "Da kokarin yin magana a tsanake.

Ubanta ya tashi tsaye, da kakkausar murya :Nace zai fi dacewa idan kika yi aure. Ba shawara nake baki ba."

Tara ta tsorata da irin muryar da yayi lafazi da shi, amma ita ba ta yi shirin ba da kai a saukake ba. "A,-a, Baba, bana so, na yi kankanta kuma naïf so na karasa karatu na tukuna, bana son auren shiri, Baba! Wanene shi? Menene sunansa? Menene addininsa?"

Kalmomin sun sullube kenan kafin ta farga da abin da take fadi. Wawanci ne ga yar musulma ta fadi haka. Ga iyalinsu kam akwai addini daya tak: Islama. Ubanta ya sake fusata, ya yi tsawa, "Me kike nufi, da wannene addininsa?

Mu addini guda daya tak ne anan! Mu musulmi ne! Ya cabki hannunta ya jawo ta kusa gareshi yana kallon idanunta. Ke Krista ce! Kwarai, yanzu kam na tabbatar!" Kafin Tara taoyi furicin kare kanta, sai ta sake jin bugu a fuskarta. Ya rigaya ya hakkake cewa diyarsa ta shiga addinin Krista, kuma a sakamakon haka ne yayi abin da ya ke ganin ya wajaba.

Yarta tana shigowa daki kenan daidai lokacin da uban ya kaiwa Tara duka a fuska sai da yar ta yi ihu don tsoro.

Duk da rokon da iyali suka yi har da barorin gidan da uban da wanta suka sake janta zuwa dakin ta suka kulle bayan sun shiga. Ta koma gefe a cikin daki jiki na rawa don tsoro. Tara tana da kwakkwaran dalili na jin tsoron rayuwarta.

Ubanta da wanta suka yi ta dukanta da duk abin da ya shiga hannunsu, igiyar wayan fitila ne itacen rataye tufafi ne. Sa'annan suka tattara kayan dakin komai da komai suka watso su waje, bayan da suka gama sai ga Tara jina jina a kwance. Kalmomi na karshe da uban yayi mata kafin ya banke kofar ya fice sune, "Ko kiyi aure, ko ki mutu. Idan ke Krista ce kuwa to babu wuri dominki anan birnin. Amma idan kika yi aure to zaki zama ya ta.

## AREWA

Tara ta kwanta akan dabe mai sanyi tana suma tana dawowa hankalin ta. Ba a yarda kowa ya make ta ba. Iyalin ta na zaton cewa zata dawo cikin hankalin ta idan aka barta babu abinci ko magani. A rana ta uku Tara ta fara tashi zaune, amma taron jini ya sa gashin ta sun kame a kan dabe. A gigice amma tare da kokarin fahimtar abin da ya faru, sai jin alamar amai ga kuma bakinciki a lokacin da take dudduba jikinta inda aka ji mata. Ba ta taba tunanin cewa binciken ta na Allahn gaskiya zai kai ta irin wannan matsayi ba. Amma yanzu tunanin ta daya ne, ta tsira da ranta. Da yakeba ta taba yin kwana ko daya ba a waje sai tare da iyalinta, ba ta ma san me yakamata tayi ba, amma ba batun ba kenan yanzu lallai ne ta fice.

Tayi kokari taja jiki zuwa inda kabod yake ko zata ga wani abu a ciki, kuma ta sami abu guda da suka bari a baya, dan karamin jaka ta tafiya da tayi amfani dashi da yan kaya, da yan kudi har da wani dutsin wuya da passport din ta. A hankali Tara ta tu be jina jinan kayanta, tana ta fama da zafin ciwo ko ina a jikinta da kowane motsi da tayi duba na karshe. Ta sani cewa idan ta tafi ba zata kara dawowa nan ba. Bisa ga al'adarsu gudu daga gida muninsu daya ne da zama Krista, kuma ta sani iyalin ta ba zasu tab a karbar kaskanci ba. Idan suka kamata, kashe ta za'ayi nan take, tabbas.

Tare da nauyin zuciya, ta sulale ta tagar dakinta hankali kuwa ta isa tashar mota. Tara na cikin radadi kuma ga karayar zuciya, abin da ma kawai ya karfafa tafiyar ta shine tsoron abin da ubanta da wanta za suyi idan suka same ta da kuma wannan yunwar da ke cikin zuciyar ta na kara sanin Allahn Krista. Da ta isa tashar mota, sai ta sayi tikiti zuwa wani birni mai nisan tafiyar awowi da dama, wuri da ta dan sani kadan. Sun taba tafiya can fiye da sau daya tare da iyali, kuma ta yi shirin neman mafaka a wata majami'a da ta gani acan. Ta amince cewa kowane mutumin Krista zai iya taimakon ta, a tunanin ta.

Tafiyar da tsawo, kuma mutane suna harrarta suna rada game da yarinya mai jini a jiki. Da yake kyakkyawar yarinya ce daga wani shahararren iyali Tara tayi kamar ba hakan ba, sanin irin tunanin da sauran pasinjoji zasu yi. Wannan sabon abu ne a gareta, kuma fatar ta shine wannan kishirwar neman sanin Allah yafi dacewa da dukan abubawan da ta juya wa baya. A yayin da take kaucewa idanun masu kallonta, tana ta fatar kada mutanen su jawo mata yan sanda. Matan kasarsu basu da yanci sosai, kuma ba kasafai ake ganinsu a titi su kadai ba saida wani namiji tare dasu daga iyali.

Da motar ta isa, sai Tara tayi maza ta sauka ta shiga cikin jama'a, ba abu ne mai saukin yi ba a cikin irin matsayin da take, amma tayi tunani cewa da zarar ta isa majami'ar za ta wanke ta tsabtace.

Lokacin da ta isa majami'a Jami'in Sojan Ceto (Salvation Army Officer) wanda yake tsaye a wajen kofa) shine ya karbe ta. Abin mamaki shine mutumin yayi kokarin hana ta neman taimako a wurin. Idan da nine ke ba zanso kadaicewa da shugaban wannan majami'a ba. Akwai jita jita, inji mutumin.

Kamar Tara ta zubar da hawaye. "Menene haka?" ta tambaya. Na dauka duk Krista, Krista ne, kuma yanzu kana gaya mani cewa wannan majami'a, ba ta dace da ni ba? Wannanne abinda na bar gida dominsa?"

"Taho gida tare dani," mutumin ya fada da tausayi. Zan taimaka na kare ki."

Ko da shike Tara tana shakkar zuwa gidan mutumin, ta ga alamar fa bata da zabi. Da ki da so dai, ta tafi tare dashi. Ta tarar yana da mata da yaya biyu maza, kuma kowa a cikin iyalin yana kyautata mata har misalin sati niyu. Daganan sai jita jitar iyali ta fara zagayawa, matar tana shakkar wai ko mijinta yana neman yayi lalata da kyakkyawar bakuwarsu. A karshe dai' Tara bata iya jure wa wannan halin ba, ta nemi mutumin ya kai ta wani wuri dabam. Ai zakasan wani wanda zai iya taimakona a wani birnin dabam." Taroka. Kaini can kawai, kuma zan nemi aikin yi. Na ji dadin taimakonka amma bana so na kara muku damuwa a cikin iyali."

" Akwai mutumin da nasani zai iya taimaka maki ainihinsa ma daga garinku yake," jami'I ya fada. Dajin haka sai Tara ta tsorata. Banajin zai dace," inji ta. "Ina rokanka, ubana ɓai san inda nake ba - kuma bana so ya sani. Ina rokan ka kada kayi mani haka."

"Kada ki damu, mutumin ya tabbatar mata. "Na san wannan mutumin. Zai taimake ki."

## HARAMTACCEN KAWU

Da yake bata da wani zabi, Tara ta yarda ta sadu da mutumin. Amma da fara ganinsa yana jira inda suka shirya haduwa, sai da ta kusan suma don tayi tsawa.

"A, a" ba babanki bane. Ina tabbatar maki, "inji shi. "Shiga ku sadu da mutumin."

Abin mamaki ga Tara, shine ta gane cewa mutumin kawun ta ne da bata taba gani ba, mutumin da yake da kamanni irin na ubanta sak. "Me yasa babana bai taba bamu labarinka ba?" Tara ta tambaye shi.

"Na zama Krista a shekarar 1952, kafin a fara aiki da dokar Shari'a," in ji kawu, yana yin batun fara aiki da dokokin islama. "Kafin wannan lokacin shari'a bata hana wani sauya addini ba, amma fa ba karbabben abu bane ga bainar jama'a. Ubanki ya haramta danganta karmu ya kini. Tun lokacin kuwa na dawo nan ina aikin pastor. Gashi yanzu na gani Allah ne ya aikoki zuwa nan, kada ki damu, zan kula da ke, ki zama ya'ta.

Sai wani sauki ya zubo wa Tara a jiki; ta fara jin alamar nasara zuwa gaba a jikinta, watakila zata natsu a wuri guda, ta sami aikin yi kuma taci gaba da makaranta.

Ba da jimawa ba kuma ta gane cewa kawun ta mai tausayawa ne, kuma nagarin mutum, ta zama mai kauna da sha'awar kawun ta. Yakan dauki tsawon lokaci yana yiwa Tara magana game da addinin Krist a, kuma yana amsa dukan tambayoyin ta. Har ya bayyana mata ma'anar Emmanuel. Bayan wasu watanni tare da kawunta kuma suna nazari tare sai Tara taji cewar ta sami isasshen sanin ko wanene Yesu, a karshe tayi addu'a tana rokon Allah ya ga farta mata dukan zunuban ta daganan sai ta bada zuciyarta gabadaya a gareshi. Neman sanin Allah na Tara ya yiwu, amma jarabobi kuwa yanzu suke farawa.

Damuwa ta fara sake zuwa a lokacinda kawun Tara ya sami ziyarar wani dangi wanda yake cewa ya gane Tara. "A,a" in ji kawunta yana tabbatar masa. Wannan wata kawace ta iyali da tazo yar ziyara."

Amma wannan dangin bai rinjayu ba, da ya koma gida kuwa sai ya kira uban Tara ya gaya mashi cewa yana zaton yarinyar da ke tare da dan' uwansa Tara ce. Bayan yan

kwanaki kuwa,Tara na aiki a cikin kicin, sai taji takun sawaye na gaggawa tafe zuwa gidan. Tara ta nufi wannan wurin saura kadan tayi karo da kawunta a yayin da shima ya shigo kicin a guje yana daga hannu, ubanki ne ke tafe! Yana zuwa. Ki tafi yanzu yanzu! Ki tafi kitafi gonar a boki na can wajen gari, wanda na baki labarin sa. Ga wasu kudi, maza yi'gudu! Kuma kada ki damu. Ba zan gayawa babanki komai ba. Zan waiwayeki bayan yan kwana ki."

Da uban Tara da wanta sun kusan kai bakin kofa a yayinda tayi waje ta bayan gida. Babu lokacin tsayawa ayi tunani ayi gudu kawai. Tsigar jikin ta da ya tashi shi ya bata karfin gudu, kafa me naci ban baka ba. Ta tattaba aljihu domin adireshi da kawu ya bata, tana haki har takai babban titi sa'annan ta fara tafiya maimakon gudu. A wannan sashe na unguwar bata so ta jawo hankalin mutane. Bayan ta tsayarda Taxi, sai ta shiga ta zauna ta rufe idanunta. Bata yarda da tunanin cewa tana cikin gudu kuma ba, bayan yan watanni biyu kacal tare da sabuwar tsintiwar kawun na ta. Ko dashike tsigar jikinta ya tashi kuma tayi gudu ainun har yasa kirjinta na bugu don haki. Tara ta ji wata salama na mamaki a cikin birnin ranta. Sai tayi addu'a a zuci domin babanta da wanta, kuma tayi addu'ar fatar ba zasu tayarwa da kawunta hankali ba.

Tara tayi kwanaki goma a gonar domin abubuwa su lafa can cikin birni. A karshe kawunta yazo ganinta, Tara kuwa tana dokin komawa tare dashi. Amma lokacin da ta dubi fuskar hawunta zuciyar ta ya kadu. "Me ya faru kawu?" ta tambaya. "Tara, kin san yadda naji' dadin zuwanki aikin wadannan watanni biyu," ya fara, yana kallon ta." Ya zama kamar Allah ya bani diyar da nake so a cikin jini da kuma ruhu. Amma ba zai yiwu ki koma tare da ni ba, akwai hadari ainun. Abin bakinciki ne ya zamana nine mai gaya maki haka, amma ubanki yace lallai ne ki mutu.

Yace batu ne na kare mutuncin sa da na iyali."

Tara ta sani kawunta na gaya mata ba zasu taba daina nemanta ba kuma ba ta da shakkar abinda zai faru idan har ta shiga hannunsu.

Sai tayi tausayin kanta, amma bacin ran kawunta shi yafi damunta, har ya taimaka mata juya nata damuwa tana ji da damuwar kawun ta.

"Kawu, kada ka sami damuwa," tana rike da hannunsa. "Nice ya kamata na baka hakuri domin na jawo maka wannan. Ina godiya kwarai da Allah ya kawo ni gunka. Ka bani amsoshin da na nema, yan zu kuwa ina da salama da ban taba jin irinsa ba. Bazan taba iya biyan ka ba.

Wannan bankwana ce mai ban takaici Tara ta shirya sake kama hanya zuwa sabon mazauni. Kawunta ya shirya mata ta zauna da wani iyali da ya sani a wani gari mai nisa daganan. Ta yi iya kokarinta na boye damuwar ta yayinda suke rabuwa. Amma daga can ciki kam, ji take anya wannan guje gujen nata zasu dainu....

An marabci Tara a sabon gidansu da hannu bude. Wannan iyali ya kunshi pastor na wurin, matarsa, da ya'yansu maza guda uku. Nan da nan kuwa yaran suka dauki Tara tamfar sabuwar yar'uwarsu. Babban dan, Rubin, yana sha'awar karfin hali irin na Tara.

Domin kare ta daga ubanta da wanta, wadanda ke ta cin gaba da bin sawunta, wannan sabon iyali na Tara suka gaya mata ta rika zama a cikin daki abinta duk yawancin lokaci. Haka take wuni a daki duk rana, kuma da dare idan wani ya zo ziyara (tunda shi pastor ne kusan dukan lokaci).

Dakin Tara a rabe yake kashi biyu: daya na kwanciya daya kuma na zama da kuma yin nazari. Dakunnan duka biyu a hade ma ba zasu kai rabin dakin ta ba. Ga iyali da zata amince dasu, amma rashin sakewar yana ji mata, ta sani ba zata iya cin gaba da zama haka ba.

"A barni, in fito daga daki," Tara ta roka da wata safiya." Na sani kuna kokarin tabbatarda tsarona, amma ji nake kamar ni fursuna ce. Wannan ba hanya ne na rayuwa ba."

Pastor yana so ya bar Tara ta saki jiki, amma ya sani cewa da ubanta da wanta suna nemanta. Alhali ma dai sun shigo

garin suna yin tambayoyi kuma suna anniyarsu na son kasha ta. "Tara, ki dan kara saurarawa, sannan zamu barki ki saki," ya gaya mata. "Ki kara hakuri, abu ne mafi kyau a gareki."

Tara tasan cewa ba ta da wani zabi. Idan aka ganta a waje, ba ita kadai ce za ta shiga hadari ba, amma harda wannan sabon iyali ma.

Tayi kokarin yin moriyar lokacin domin yin nazari, amma akwai kwanaki da ba ta yin kome sai kuka. Dan dakin ya zama mahallin ta na tsawon shekara guda.

A karshe, watarana da yamma Tara ta ji pastor yana magana game da bukatarsu ta daukar sabuwar sakatariya aiki. Washe gari da yazo dakin Tara, ta roke shi domin a ba ta wannan aikin." Idan ka yarda, Pastor," ta roka, "ina so ka bani wannan aiki! Nasha buga maka takardun wa'azinka; na san zan iya yin aikin, shekara guda kenan tun da nazo nan. Na tabbata da babana da wana sunyi gaba."

Pastor yana jin nauyin yanke shawara, amma kuma ya sani ba zai bar Tara a cikin daki har abada ba. Sai ya amince cewa zai tambayi pastor na gaba dashi ko zai yarda ya baiwa Tara aikin.

Mako na biye kuwa, Tara ta zama sakatariyar Majami'a. Tara, ki saurara da kyau," pasto ya umurta. Ni kawunki ne kin zo ziyartata daga gari. Ki daina kirana pastor, daga yanzu ki kira ni kawu, mu kuma zamu kira ki Rebecca. Kada ki gaya wa kowa labarinki. Kin gane?"

Ba fahimta kawai Tara ta yi ba, ta zama mai farinciki.

Ta kware a sabon aikinta. Ta karanta Turanci, kuma shi babban pastor wanda yake baturen Ingila ne sai ya so kokarinta sosai.

Aka bata al'amarin kula da kudaden majami'a, har ma ta fara koyaswa a ajin Sunday School.

Shi babban pastor, da ya karanta tarihin Tara, sai ya kuma

ba ta wata dama ta tattaunawa daya bayan daya da musulmi da suka tuba a cikin sirri.

Tara fa ta fara jin lallai wannan aiki shine zai zama tushen hidimarta, kuma tayi wa Allah godiya da ya bari ta shiga irin wadannan gwaje gwaje kamar dai wadannan sababbin tuban da ke da bukatar karfafawa ta wurin nata shaida.

Bayan ta fara aiki da wata shida aka yi mata baptisma a boye a wani karamin baho a karkashin ginin majami'ar. Iyalinta da babban pastor da kawunta ne kadai aka bari su shiga.

## SHAUKIN YADA BISHARA

Bayan tayi shekaru biyu da sabon iyalin ta, Tara ta zama yar shekaru goma sha takwas, kuma tana dokin fita domin yin hidima. Tana jin dadin aikinta na sakatariyar majami'a, amma tana da dokin yin bishara.

Yawancin ma'aikatan cikin mishan din tashin iyali ne na Krista tun haifuwarsu, amma Tara zata yi wa musulmi magana a zaman ta na musulma can baya. Tara ta haye muguntar ubanta da na iyan, uwanta, kuma an cireta daga aikin lissafin iyali. Tana da shaida da zata bayar, kuma tasan wasu zasu saurare ta.

"Ku bari, Rubin! Ku barni na tafi tare da ku," ta roka ranannan, a yayinda babban dan pastor ke shirin yin tafiya zuwa wa'azi.

"A'a" Tara," in ji shi, amma ya fadi haka din ba da sonsa ba, domin ya san irin tsananin sha'award da takeyi na fita yin bishara."Akwai hadari ainun.

Wani zaiji haushin shaidarki, kuma yakai kara a gaban hukuma. Ni ana iya kama ni babu kome, amma ke idan aka kama ki kashe ki zasuyi."

Rubin ya tashi a cikin son Tara kamar ya'uwar sa. Shi yasa baya yarda ta shiga wani hadari. Amma ya san zata yi naci aka tafiyar." Rubin me yafi muhimmanci,"

Kare lafiyata ko kuma rayukan da suka bata da kuke kokarin kaiwa garesu?"

Rubin ya amsa kasawarsa, kuma Tara ta ya tafiya tare dashi yana koya mata dabarun yin bishara.

An kara yin shekaru biyu da rabi ba tare da wata damuwa ba. Tara ta zaunu sosai a sabuwar rayuwarta na cewa pastor kawunta ne kuma t a gama wasu fannoni na ilmin koleji. Kuma ta sami wani sabon fanni na yiwa Musulmi da Hindu da suka tuba baptisma. An sami yawancinsu ta wurin kokarin hidimar Rubin da Tara.

Kuma ta taimaka wajen fara darasin koyon karatu da kuma ta hidimar yara.

A kullum Tara tana lura, amma bayan wannan tsawon lokaci sai take jin yanzu ta shiga rayuwarta can nesa da barazanar ubanta da yan'uwanta. Damuwa kadai da take dashi yanzu yana zuwa ne daga wasu mambobin majami'a kalilan da suka ki yarda wai pastor kawunta ne, wadanda kuma suke kishi da habakar da bishararsu take yi. Wannan damuwa ce da zata iya magantarwa.

Damuwa da ba zata iya magantarwa ba na jiran ta a kofar majami'a wani lahadi da rana a lokacin da Tara ta taka ta fito ta kofa.

## SAKE GUDU KUMA

Tara ta gane shi nan da nan danginta ne shi, tsigar jikinta ya tashi gaba daya da ta ga shi mutumin yana kallom idanunta, amma Tara ta dage da ta wuce shi ba tare da nuna alamar ta gane shi ba.

"Tsaya, ina so inyi magana da ke," yana kiran ta, daga jin muryar sa Tara ta sani cewa bai tabbatar ita ce ba, yana shakka. Fiyeda shekaru hudu kenan da barin gida, abubawa sun sauya. Sai kawai ta kyale shi kamar ma ba ta jishi ba ta ci gaba da tafiya. Sai taji kalmomin da ke tsoratar da ita....

"Tara!"

Tara ta juya ta amsa kamar ba ita ba, "Ayya sannu, da ni kake magana? Sunana Rebecca. Bana zaton nasanka, kayi hakuri; ina cikin sauri."

Idan ma dai fuskar Tara bai basheta ba, to muryarta ta basheta. Ta sani cewa dangin nata ya sami abin da yazo nema. Yanzu kuwa cikin wani lokaci kadan ubanta da dan'uwanta na iya bayyana. Sai taji tsoro ya mamaye ta, lokacin da take sauri ta bace a cikin dan taron, gabanta kuwa sai dar dar yakeyi kamar kirjin ta zai fashe.

Da kaiwa bakin titi sai Tara ta dauki Taxi." Kaini filin Jiragen Sama," injita. Tana da kudi a cikin Jakarta amma kuma ba ta san ina zata ba. Bata san na zabi ba; so kawai take ta tsere kafin ubanta da wanta su cinmata. A filin Jiragen sama ta duba jarin jirage masu tashi da inda suka nufa tana kokarin sanin ina yakamata ta tafi. Sai ta kare da tafiya wani birni a gabashin kasar, tana jin zata kauce wa badari idan ta tafi can, a kalla na wani lokaci. Idan ta sauka ma bata san ina zata nufa ba, a karshe ma dai a filin Jiragen Sama ta kwana. Ta buga wa Rubin tarho domin kada iyalin su sami damuwa. Amma bayan haka kuwa, babu wani abin yi illa zama da tunani iri iri tana kwantarda zuciyarta da addu'a. Ta dage da kin tambayar Allah, domin me nake shan wannan wuyar? Amma fa ta gaji da rayuwa na guje guje, kuma tana tunani wai shi na rayuwarta zata sami zama wuri guda da kuma sakewa kuwa?

Washe gari cikin gajiya Tara ta dawo gun iyalin ta. Ta damu game da su. sun nuna mata kauna da taimako, kuma ta wurin yin haka sun sa kansu harda majami'a a cikin hadari. Yanzu kuwa Rubin ya gaya mata suna kokarin samo mata iznin barin kasa. Tara tayi juyayi kuma taji dadin yin tunanin barin kasar domin hagadri ga abokai zai kawu. Ba abokai kadai ba, ta sani idan aka kamata gwamnati na iya amfani da batun nan su shirya wani sharri da zai shafi kusan galibin Kristocin Pakistan gaba daya. "I, zai fi dacewa idan ta fita.

Tara ta dauka idan ta labe shiru na wani lokaci ba zai zama da hadari ba. Amma wasu mambobin majami'ar da suke jin kyashin yadda iyalin pastor ke kuza da Tara suka yi shawarar kai kara. Suka kira yan sandan ciki na Pakistan akwai wata budurwa a majami'a da take yada bishara.

## DIYAR DA TAYI RIDDA

Aka gayyaci Tara zuwa ofishin CID, inda aka gaya mata cewa hukuma zata bude fayi! a kanta, kuma zasu ci gaba da tattara bayanai domin suga ko abin da aka fadi game da ita gaskiya ne. Kuma hukuma tana so ta tun tubi iyalin ta. Tara fa ba ta iya daukar haka ba, ta sha tserewa sau dayawa domin kawai wani mamba a majami'a ya shigarda ita. Ta sani yawancin mambobi mutanen kirki ne, kuma ta gane cewa lallai ne taja bakinta game da baya. Amma kuma gashi daya ko biyu kawai suna so su rusa sha'anin. Sai taji kamar wata da aka nutsar a kogi mai igiyar ruwa da yake janta kasa kamar ba zata kai ga gaci ba.

Tara ta kai kukanta a gaban Allah domin ya sake kara ceton ta. Wannan kalma Emmanuel ya sake zuwa mata arai. Yanzu dai tasan ma'anar watau Allah yana tare da ita, wannan tunanin kadai ya gamshe ta. Ta bada gaskiya cewa idan Allah zai sa kifi ya amayar da Yunana a gaci zai iya fitar da Tara daga bakin CID!

Amma bazai zama abu mai sauki ba. CID sun kwace passport din Tara kuma suka ci gaba da yi mata tambayoyi suna cika takardun bayanai.

Galibi Rubin yakan tafi tareda ita kuma yakanyi kokarin rinjayarsu cewa yar'uwarsu ce, amma ba sa yarda. Sunayen da ke cikin passport basu zo daya ba. Kuma passport din Tara yanuna cewa ita musulmace. In hakane me takeyi a cikin iyalin Krista?

Bayan an tsare ta na rana guda a CID, sai aka bar Tara ta

tafi gida amma ɗa gargadin kada ta bar gari. Hukuma zasu na me ta nan gaba. Tara tana bukatar alamu daga Allah, tana neman wani abin da zata jingina dashi. Yanzu dai bata da passport kuma, kuma batu ne na lokaci kafin CID su hada ta da iyalinta na ainihi batun da zai zama karshen ta. Wataran takanyi tunanin wai wane irin hanya uban zaiyi amfani dashi wajen kasha ta....

A kofar fita ofishin CID, daya daga cikin jami'an yayi wa Tara rada. Yasan iyalinta amma bai ce komai ba, sanin irin hadarin da take ciki. "Tara ki saurare ni," ni abokin daya daga cikin danginki ne. Na san ki. Lallai ne ki bar kasar nan maza maza. Ba ke kadia ce ke cikin hadari ba."

Tara tayi mamaki kuma taji dadi. Abin al'ajibi ne da wannan jami'i bai ba da ita ba. Kuma ba ma wai ya rufa mata asiri kadai ba, ya kuma gaya mata abin da ya kamata tayi. Lallai ne ta bar kasar Pakistan. Amma ta yaya? Bata da passport. Kuma ko da akwai, ina zata nufa?

Nan da nan Rubin ya fara zuwa ofishin jakadun kasashe dabam dabam yana kokarin samar mata visa. Amma bai samu ba, gaya masa suke wai lallai ne ta sami wani a can kasar wanda zai tsaya mata. A karshe dai wata kasa a Gabashin Kasashen Larabawa ta ba da visa ta watanni uku a farashin dalar Amirka guda dubu. Tafiya zuwa wata kasar musulmi bai burge Tara ba, amma kuma, ba bu wani za bi. A ranar da ta biya kudin, ta ji labari CID na shirya takardun kamata. Masu ba da rahoto sun ji cewa tana shirya yin baptisma ga musulmi da suka tuba, kuma ita kanta ma sauya addini tayi, ridda kenan. Tara ta kuma sami labari cewa iyayenta sun gabatarda kisa a kan ta. Sun tabbatar da sauyin addini da tayi, kuma bisa ga dokar musulunci, sun ba da shawarar a rataye ta.

Tara tana samun damuwa ya sa ta fara kulle kanta a daki na tsawon kwanaki. Tana tsoron ko zasu cin mata, su kashe ta. Mafi muni, shine kila su kashe sabon iyalin ta kuma.

Watau zai zama a dalilin ta kenan. Addu'ointa sun fara gajarta, amma cike da tsananin kuka zuwa ga Allah zama mata Emmanuel din ta, ko da a gaban igiyar rataya ta tsaye.

## DA ALAMAR ALLAH YANA DA AYYUKA KWARAI DOMIN KI

A lokacin da take yi kamar zata fitar da rai, Rubin yana can yana faman samun sabon passport da takardun shaida da za a hada da visar da suka samu. Ya sa Tara ta yanke gashin kanta kuma ta sa tabaron kare rana domin daukar hoton, kuma yana da takardar da akayi sojan- gona cewa ba ta da lafiya kwarai kuma bata iya zuwa ofishin gwamnati da kanta ba domin karbar takardun. A lahadin Eastar na 1996, Rubin ya shiga dakin Tara da wannan labari mai kyau: "Tara, "Ina dauke da dukan takardunki na tafiya. Gaisuwar murnar Easter. Ta kaka kayi?

Abin mamaki. Inji Tara

Kuma nawa ka kashe?

"Kada ki damu da wannan," inji shi yana murmushi. Na gaya maki Allah zaiyi ikon sa. Bai kawo ki nesa haka domin ya mika ki ga CID ha. Babu shakka yana da aiki kwarai dominki. Tara. Muamman ma da dukan irin dawainiya da kika shiga." Murmushinsa yana nuna farincikinsa na taimakawa.

Irin bangaskiyarsa da dagewarsa ya baiwa Tara sha'awa. Ta nuna shi dan uwa ne kwarai, aboki na kwarai. Da wannan tunanin kuma rabuwa da sabon iyalin ta na Krista da kuma dukan shirye shiryen ayyukan majami'a da suke yi.

"Ina da rokon abu guda kafin na tafi." Ina so na tsaya wajen yin baptismar da muka shirya kafin na tafi."

"Rubin yaso yace a'a, amma gaskiyar ita ce a gajiye yake da zai iya musu da Tara, idan ma suka yi musu yasan wa zai ci nasara. Sai ya yarda, amma daga nan sai kiyi maza ki tafi.

Washe gari aka tafi wajen baptisma ta boye, ta san kowannen su, kuma Tara tana amince musu. Duk jirgi daya ya kawo su. Wasu masu tuban daga Pakistan ne, amma yawancin su daga wasu kasashe ne. daya daga China yake, daya daga Afghanistan daya daga Iran da ilraq. Ba sabon abu bane masu tuba suyi tafiya suna ratsa Pakistan daga wasu kasashe.

Tara tayi al'ajibin yadda Allah yayi amfani da ita. Zata bar kasar a dalilin bangaskiyarta, a yayin da wasu kuma sun zo kasarta domin samun bangaskiyarsu. Kuma yawancin Krista na wajensu harda wadanda suke majami'ar su basu san abin da ke faruwa ba. Yana da wuya a amincewa mutanen da suke makalewa nemar wa kansu kadai zaman lafiya.

## AN SAKE TONA MATA ASIRI

Tara tabar kalubalolin Pakistan ta tsunduma a cikin karin gwaje gwaje. Ta sami kanta na wani lokaci daga nema da iyalin ta keyi mata sau-da-kafa, amma dole tayi hankali kada ta bari a santa.

Har a wata kasar ma akwai hadarin kamu a tsare na yan sandan Islama, kuma in hakan ya faru, to za a kai ta hannun ubanta kenan. kuma anan zata kare. Tara tana kuma fuskantar wani kalubale. A duniyar Musulmi mata sukanyi aure kafin su cika shekaru 25 da haifuwa, idan bata yi ba, sai a dauka ita karwace in hakane kuwa tsaresu akeyi, a sake-ilimantar da su kuma a shirya musu miji. Tara ba ta yi shirin aure a cikin irin wannan ha'ula'i nata ba. Kuma tabbas ba ta bukatar wani irin auren da jami'an Islama zasu shirya mata. Fiye da haka kuma, yanzu gashi bata da goyon bayan iyali, kuma visarta ta watannin uku ne rak.

Nan da nan ta gane cewa yin tunani akan matsayin da take ciki in taci gaba a haka zai dakile mata karfin zuciya da take dashi. Na yi hasarar komai da komai, tana gayawa kanta,

amma na sami Allah dan karamin rashi domin irin wannan gagarumin samu. Emmanuel Allah yana tare da ni. Wa zai iya yin gaba da ni? Naci riba fiye da dukan hasarar da na taba yi. Emmanuel Allah na tare da ni. Ya zama addu'arta wanda ya kara karfa fata ga sake shiga wahala da kuma fitowa....

Rubin ya rigaya yayi shiri domin a bata aikin wucin gadi na sakatariyar majami'a a wancan kasar, amma abinda take samu bai wuce na cin abin ba ballantana ta biya haya. Kuma tana aikin wucin gadi na dafuwar abinci wa matar pastor, wadda tafi yin maganan kayan wuya da kayan adon zamani fiye da maganar Kristi. Tara na mamakin ashe bangaskiyar da take sadaukarwa rayuwar ta kenan, sai ta fara damuwa. A hankali sai ta sake samun aiki a ma'aikatar tsara tufafin zamani, sai ta sami damar neman visa ta shekaru uku na izinin zama a kasar. A warkar da wata damuwa, amma babbar na zuwa.

Da iznin zamanta a hannunta na sabuwar kasarta, sai Tara ta fara bada kai ga wasu ayyukan majami'a na fita waje. Samun sababbin abokai babu wuya ga Tara, amma sanin wadanne za a amincewa shine abu mai wuya.

Ko da shike Tara ba ta farga da haka ba a lokacin, daya daga cikin sababbin abokan wani mutum ne da yayi wa Mujallar Krista ta Pakistan aiki, yace ai Tara ba sunanta na ainihi take dashi ba. Yana so ya sami labarinta, ya tunkare ta wani lahadi bayan sujada. Tara na sani abubuwa na da wuya anan a cikin wata kasa, ga bakon harshe ga babu iyali,in ji shi. Me zai hana kizo gidanmu muyi zumunci kuma aci abinci tare? Bari mu taimaka maki."

Tara ta yarda. Zai dace ayi sababbin abokai tana gaya wa kanta.

Ziyarce ziyarce na farko dai, dan jarida ya nuna mutunci. Ya gayyaci Tara da wasu mata yan Krista kamarta zuwa gidansa domin cin abincin rana da kuma yin sujada. Amma da kowace ziyara, dan jarida ya fara tambayoyi ga Tara game da labarinta.

"Ka bari ba zanso yin magana game da labarina ba" in ji ta ba tare da son bata wa sabon aboki ba. Da wata gayyatar ta sake zuwa Tara ta ki ta halarta.

Da yake baya so ya hakura, sai ya sake kiran Tara washe gari, 'Tara nasan kina samun wahala rashin kudi hanan, kuma dani da abokaina muna so mu taimaka" Ki zo ki shaida labarinki garemu, zamu tara maki wasu kudi. Mu abokaine, kina iya amince mana.

Tara ta yarda amma da kyar, A wannan lokacin wadanda suka san labarinta cikakke sune sabon iyalinta na Krista a Pakistan su kadai. Tana maida hankali kwarai ga boye ko wacece ce ita. Boye kamannin ta batu ne na ko rai ko mutuwa.

Har wata guda ya shige kuma Tara tayi kira ga yan jaridar sau da dama, duk lokacin da akayi kirar sukan nuna tausayawa da alkawarin zasu taimaka mata.

Wani watan ma ya wuce kuma sai hira, da zubar da hawaye kawai amma babu taimakon kudi. Tara ta fara mamakin ko me ke faruwa. A karshe wata mata ta tambayi Tara ko nawa ne banki suke aiko mata a kowanae wata.

Me kike fada, ai bani da ajiya a banki, kuma ma babu bankin da suka aiko mani kudi. Me zai sa banki suyi haka?" Tara ta tambayi matar.

"To, lallai akwai wani kuskure", in ji matar mutane suna ta aiko da kudi a cikin wannan asusu, da gaskata wa cewa asusun ki ne.

"Daga abinda na fahimta kudi ya taru sosai a asusun," Anyi amfani da Tara, ta tabbatar da gaskiyar, sunshirya kasuwanci, wasu na cin ribar shaidar ta da ta bayar. Daga baya kuwa sai ta ga mujallar.

Babban labarin mujallar shine. Wata yarinya Musulma da ta karbi Kristi cikin al'ajibi, a yanzu kuwa tana cikin gujewa iyalin ta, wadanda suke so su kashe ta. Labarin na dauke da sunanta! Abin ya faskara mata kai.

"Ta yaya za ayi irin wannan?" tayi haki. Kuma mafi muhimmanci ta damu, "Kaka zan hana iyalina daga nema da sukeyi mani?"

Abin ya ishe ta. Tana tunanin irin wannan rudi da cin amana guda nawane za a gani nan gaba, a lokacin kuma wani mutum daga majami'ar ya tsaida ta daidai lokacin da ta tashi tafiya zuwa sujadar Lahadi da safe. Zancen daya ne. "Ki shaida labarinki tare da mu," in ji shi, Kuma zamu tara kudi domin taimaka miki."

"Amma wannan mutumin ya gabatar da roko mai murdiya. Yace a ganinsa Tara kyakkyawa ce ainun, kuma yana yi mata ganin tana cikin kadaici. Shikenan kuwa sai Tara ta dauki hannu takai masa mari a fuska.

Kana da mata da diya!" Ta yi masa fada. "Kai Krista ne! Kaka zaka yi irin wannan?"

Mutumin yayi mamaki kwarai da irin wannan hali na Tara. Yasa hannunsa a wurinda yasha mari yayi gurnani, "Bashi na wannan sai kin biya." Bai yarda ya jawo hankali ba, domin akwai mutane kusa. "Dakyau," inji Tara, tana ta fushi har yanzu domin irin maganarda mutumin yayi. Ka gaya mani ko nawa ne zan biya, kuma biya zanyi. Kai dai ka rabu dani.

Damuwar ita ce, shi ba kudi yake tunani ba. Bayan kwana uku, aka jefo guntun tubali ya rusa gilashin tagar dakinta. Tara tana jin mutane suna surutai akan titi amma ba ta fahimtar me suke cewa domin suna magana da broka na Larabci wanda ba ta gane ba. Ta labe a jikin labule taga mutane na diban duwatsu daga kan titi. Suna jefa su a tagarta kuma suka ragargaza dukan gilashin da ke tagar. Yanzu dai ta gane wasu kalmomin suna cewa: Musulma.... Yanzu kuwa Krista!.... Mai ridda ce! Yan sanda a kira yan sanda...."

Da ta sake lekawa sai tagan su suna shiga Taxi suna gujewa. Ta gane mutum biyu. Su abokan mutumin da ta mara ne. Tara tayi fatar razanar su ta kiran yan sanda ya

zamana burga ce kawai, na kokarin tsoratar da ita. Amma ba burga bace. Bayan yan awowi, yan sanda sun isa kofarta, suna tambayar ko minene ya faru, suka tafi da Tara zuwa caji ofis.

## MIKA DUKAN KOMI GA ALLAH

"Muna da rahoto cewa ke musulmace, kuma kin juya kin zama Krista-cewa kuma baki da aure," aka fara yin tambayoyi. Tara ta sani cewa yan sanda zasu iya yin binciken da zai kai harga sanin wanene ubanta a cikin sauki a Pakistan kuma su sami ganin fayil din ta na can. Sai ta dinga basu karkatattun amsoshi, tana maimaitawa kanta wannan kalma: Emmanuel tsakanin tambayoyi.

Bayan wasu sa'oi yan sanda suka saketa, amma sun yi alkawarin sa ido akanta. Suka yi ta tambayar dalilin da ya sa ba ta yi aure ba, kuma suka gargade ta da cewa lallai ta sami miji, har sun ba ta wani mutum wanda suka sani zai dauke ta.

Abin mamaki, Tara da aka yiwa laifi aka far ma gidanta yanzu ta zama mai yin laifi.

Wadanda sune irin "dama" na Krista a kasar Musulmi.

## MIJI DOMIN TARA

Watanni hudu na biye sun shiga ba tare da wata tsangwama ainun ba. Tara ta fara kwarewa wajen tsara tufafin zamani, kuma aikin ta na majam'a na cin gaba. Kuma ta sami damar taimakawa musulmi da suka tuba kuma suna cikin gujewa, aiki da ya dace da Tara, wadda yanzu tena da fiye da shekaru goma na sanin irin wannan wahala na guje guje domin sauya addini. Har yanzu ta sani mutumin da ta kai wa mari bai gamsu da irin sharri da ya kulla mata ba. Yana so ya kara, Tara na iya ganewa ta irin kallon da yake yi mata. So yake ko ya same ta ko kuma ya rusa ta. Ga Tara kuwa ba ko daya cikin biyu.

Tara na zaune a dakinta sa'anda tarho yayi kara. Wannan mutumin ne dai, kuma yana da labari. Yana alfaharin shaida mata cewa, ya rubuta wata yar kasida na cewa Tara karwa ce. Shi ya sa take add da tufafi masu kyau kuma har yanzu babu miji. Ya gayyace ta, ta tafi taga aikin hannunsa.

Cikin fusata, Tara ta maida kan tarho ta ajiye. Mutumin nan fa bai daddara ba. Bata damu ainun da abinda mambobin majami'a zasu yi tunani ba. Duk wadanda suka santa zasu san gaskiyar.

Ba ta iya yin aure ba domin irin al'amari' da take ciki na hadari, tufafin kuwa samfuri ne daga kayan da ta tsara da kanta. Abin damuwar zai zo daga batun yan sanda; kafin a jima rahoton zai kai garesu. Sun rigaya sun gaya mata a fili cewa tayi aure, saboda haka wannan kasidar zata zama zuga zugi ga wannan batu. Idan suka sani, za a kamata.

Bayan mako guda, abin da Tara take tsoro ya tabbata. An kai ta wurin da ake tsare mata na Islama, inda ake sake ilmantarda koyarwa ta Islama ga mata daganan sai a aurad dasu ga wani namiji Musulmi.

A tsare a cikin wani karamin daki, Tara tayi addu'a. ita dai ba ta da masaniyar yadda zatayi ta bar wannan wurin tsaro ba tare da ta yarda tayi aure ba. Yanzu fa gani take kome yazo karshe. Ubanta ya nemi da tayi aure, kuma a shirye yake ya kashe ta idan taki. Ba bu bambamci kwarai da wurin tsaron. Idan Tara ta gagara, za a mayarda ita wajen iyayenta a Pakistan. Amma ai Tara taki yin na'am da shirin ubanta dominta, kuma ba a shirye take ta ba da kai ga jami'an wannan matsara ba. Ba tare da wani karin zabi ba, ta yi addu'a, tana mika komai ga Allah.

Watanni hudu suka wuce. Tara kuwa ana ta faman bata darasi a cikin kur'ani. A lokacin da bata cikin aji kuwa, ta zama fursuna ga dakinta.

Ananan kuwa sai wani jami'i ya shaida mata cewa : "Tara, kina da bako."

"Ta kaka zanyi bako? Babu wanda ya sani cewa ina nan." Yace yana so yayi magana da ke. Muna ganin zai yi kyau idan kika tafi tare dashi." "Tafi tare dashi?" Tara ta tambaya, "Ni ban ko san mutumin ba, kuma kuke aika na fita tare dashi?" Tara ta bata rai ainun, tana ganin wannan wani wayo ne kuna aurad da ita. Amma mutumin yayi alkawarin zai dawo da ita bayan anci abincin rana. Tara ba ta ji dadin wannan shiri ba, ko dashike barin dakin na wani lokaci ma wani abu ne. Ta yarda ta tafi, amma za ta yi wa mutumin kyaliya a lokacin cin abincin.

Mutumin dan shekaru:ne irin na Tara, kyakkyawa, kuma yana magana da na tsatsiyar murya. Tara, na san ko wacece ce ke: ya gaya mata. "Na sami labarinki daga wani Musulmi abokina". Tara tana kokarin kyale shi. Amma yana kara yin magana, ita kuma tana kara kawo hankalin ta gareshi.

"Nima Krista ne". Amma babu wanda ya sani. Na guje ne daga Pakistan, kamar dai yadda kika yi. Gaskiyar ma dai garinmu daya. Kuma na san cewa matsaran nan sun shirya su aurar da ke ga musulmi wanda yake da mata uku.

Tara ta sha jikinta. Aṇ rigaya an gaya mata batun wannan shiri. Tayi kokari ta nuna rashin sha'awarta ga abinda mutumin ke fadi, kuma har ta kusa cin nasara, sai da ya gaya mata. "Idan kika ki, za a mayar dake zuwa Pakistan - can gurin ubanki."

Tara ta rasa sanin wanne zatayi na'am dashi. Ta kaka wannan matsara zata iya shirya Krista namiji wanda bashi da mata kuma daga garinsu yazo ya hadu da ita?

"To me kake so? Tara ta tambaya a karshe. "Ina so in aure ki," in ji shi.

## AL"AJIBI A CIKIN JIKI

A lokacin da Tara ta dawo cikin matsara, akwai jami'ai guda uku da ke jiranta. "mun yanke shawara, Tara". In ji daya daga cikinsu." Zahid yanzu yana da mata uku, kuma a shirye

yaken ya aure ki. Mutumin kirki ne. zamu kammala shirye shirye duka. Kada ki damu da kome, amma idan kika ki, za a mayarda ke zuwa Pakistan."

Wannan shine lokacin yanke shawara. Bata bada amsar tambayar mutumin nan da ya nemi ya aure ta ba. Abubuwan sun cakude mata ainun. Abubuwa na faruwa cikin sauri, gashi kuma tana bukatar lokaci na yin tunani lokaci na yin addu'a. Tana marmarin yin magana da iyalin ta na Krista - da kowannensu da yasan duk labarin ta, wanda dai zai bata shawara.

"Ba zan auri Zahid ba." Tara ta bada amsa ga jami'ai masu yin mamaki.

"To idan hakane sai ki tattara kayanki, zaki koma Pakistan."

"Zan kwashe kayana, amma domin wani dalili dabam. Zanyi aure amma ba ga Zahid ba. Zan auri mutumin da yakai ni cin abinci,: inji Tara.

Jami'an sunyi mamaki, amma kuma sun amince, da dukan abinda zai kawo ta karkashin iko. Tara ta kira mutumin, ta bashi labarin yardar ta-za ta aure shi. Har yanzu tana shakka ko aniyyar sa da gaske ne, saboda haka kasada ce. Amma ba babbar kasada ce kamar auren Zahid ba, duk da haka, ita tasan inda ta tsaya.

Yanke wannan shawara yasa Tara sake yin kira ga Emmanuel. Allah da ya kawo ta har zuwa wannan matsayi. Ta kusa shekaru 27, kuma tana cikin guje guje fiye da shekaru goma kenan. Idan har wanda zata aura ya rude ta ne, ta san irin damuwa da zata fuskanta. Amma idan da gaske yake. To shi al'ajibi ne a cikin jiki.

Zai sa ta fice daga matsarar Islama da kuma jita jitar batun karwanci. Har za ta sami mataimaki wajen hidimarta ga wasu da suka tuba a cikin sirri daga Islama.

Amma shin ba shirya kanta take ga wani tarkon ba ko? Tambayoyin sunyi yawa.

A karshe Tara ta tuna da addu'ar da tayi, a lokacin da ta shiga cikin matsarar Islama. Ta mika komai ga Allah. Kuma sai ta sake yin haka. Yanzu kam abin ya fice daga hannunta. "Emmanuel, Allah tare da mu." Tayi addu'a, "ka kasance tare damu duka biyu."

## JAWABI

Mutumin da Tara ta aura ya zama al'ajibi cikin jiki. Krista ne mai ba da kai, yayi aiki tare da Tara a cikin hidimar ta ga wadanda suka tuba suka zama Krista daga Islama.

Dashi da Tara yanzu suna da da namiji, James, kuma haryanzu akan guje guje suke. Hukumar matsara ta Islama na zuba idanu akansu har yanzu. Sukan kawo ta suyi mata tambayoyi akan ayyukan ta daga lokaci zuwa lokaci." Wa zai zo cin abincin rana?" jami'an na tambaya. "Me yasa wancan matar ta je gidanki jiya da dare?" Me yasa kika bar gida har na tsawon sa'oi hudu yau?"

Ga Tara kam rayuwa ya zama wasan mage da bera. Mai yiwuwa kalu balen ta mafi girma na gaba, a cikin yan shekaru masu zuwa na gaba, a lokacin da danta zai kai ga iya yin magana, babu shakka shima zai sha tambayoyi daga jami'an Islama.

Wani kalu bale ma na kusa. Yan watanni kafin yin hira da "Zukata Masu Kuna", wani dangin Tara wanda aka bashi aikin nemo ta, domin a mayar da ita gun ubanta ta fuskanci kisa, ya hange ta.

Domin tsare lafiyar Tara, babu karin abin da za a fadi game da inda take da zama, koma bayanin aiki ko hidimar Kristanci da ta keyi. Amma abu guda shine matabbaci. Tana rayuwa a wata nisan duniya daga yawancin Kristoci. Galibi na har su wadanda ke cikin nata majami'ar suna cikin duhun sanin rayuwarta a zaman Musulma da ta tuba ga Kristi, game da kasadar da take fuskanta a kullum. Wata kila yana da wuya su fahimta. Watakila shi ya sa Allah yake bukatar mutane irin Tara wadanda za su haskaka hanya domin sauran yaya maza da mata masu ridda su bi.

# Ling:
## A Cikin Makarantar Shan Wahala

*China:*
*1973*

Ling yar shekaru tara ta fice daga kauyensu tun da safiya tareda yarta, suna barar abinci, suna hutawa a karkashin wata babbar bishiya da tasha kan bukkarsu a lokacin da uwar ta kira ta "Ling, kizo maza" in ji ta. "Babanki yana son ganinki" Da ita dayyan uwanta sukan kashe yawancin lokacinsu a waje kuse da dan dakin bukkarsu da aka yi da gwangwala da kuma ciyawa da iyalin su ke kira gidansu.

A yawancin lokaci za a same su ne ko suna barar abinci ko tsintar bolar kwal daga wata masana'antar sarrafa karafa kusa dasu, sukan kawowa iyayensu gawayin kwal domin su sayar ko kuma su yi makamashin dafa abinchi dashi. A sanin Ling dai iyalinta matalauta ne kwarai, amma yanzu abubuwa sun kara tabarbarewa. Rashin lafiyar ubanta na kara tsanani, Ling kuma na damuwa game da gobensu kuma game da uwarta.

"Ling, maza, kada mubar baba yana jira", in ji uwar. Da kiwuya dai Ling ta bar gindin itace mai inuwa ta tafi tare da uwar, yanuwan da karamin kaninsu suka kewaye gadon iyalin gadon da dukansu shida ke mora. Shine ainihin kayan daki kadai a cikin wannan bukka mai ciki daya tak.

"Ling, matso kusa" in ji ubanta "bari na duba kyakkyawar fuskarki" ling ta zauna a bakin gado tana kokarin yin murmushi. Taki jinin ganin babanta a cikin irin wannan hali. Tun da ya dawo daga asibiti, wancan karon, jikinsa yana rage karfi, kusen ma babu taimakawa. Uwarta bata ce komai ba, amma tana ganin alamar cewa zai mutu. Ciwon jeji ya cinye jikinsa, kuma bai iya yin aiki ba na tsawon watanni.

Yanzu dai babanta ya daga hannunsa ya motsa a hankali a gefen gadon, yawancinsu na kuka, "yara, kuyi mani alkawari cewa zaku kula da uwarku. Kuma ku kula da juna, bazan jima tare da ku kuma ba, amma akullum kutuna cewa ina kaunar ku "Uwar Ling tana zubarda hawaye, sai babanta ya riketa yayi mata sumba, yi mani alkawari cewa bayan na tafi......"

Yaci gaba da magana da matarsa da sauran kadan zata zama gwamruwa,....zaki auri wani mafi jin karfi a jika. Wani wanda zaki fi dogarawa da shi, wanda zaifi kulawa da ke fiye da yadda nayi. Kuma ki tuna da cingaba da yin addua ga Allah".

Kaunar da ke.tsakanin su biyun nan sanannen abu ne ga kowa da ya sansu. Ling bata taba jin su suna yiwa juna tsawa ba, ballantana bakar magana ga juna. Ba ta iya yin juriyar ganin ubanta yana mutuwa, kuma taki jinin ganin uwarta cikin bakinciki. Kuma yadda suke magana game da Allah a kullum kuma suyi addu'a, bata taba ganewa ba. Ling takan ga iyayenta na durkusawa a gefen gado akai akai. Ta taba tambayar su abinda suke yi, kuma sukace suna yiwa Allah magana ne".

To ina Allah yake yanzu? Ling na mamaki da kuma shakka. Idan har lallai akwai Allah, me yasa ubana ya ke mutuwa? Ta fita daga dakin a guje don tanajin zata fashe da kuka.

Daga baya a wannan ranar, uwar Ling ta gaya wa yaran cewa surukanta da kakanninsu zasu zo ziyara. Ling tayi mamaki; ta sani cewa kakanninta basu kula da dansu kuma da iyalinsa ba. Gaskiya ma dai fadar hakama an rage batun

ne kakarta ta tsine wa iyalin wai sun kasa haifuwar karin ya'ya maza!.

Bayan yan kwanaki kakannin suka zo, amma shigarsu cikin dan bukkar ke da wuya sai dansu ya rasu. Suka ki su taimaka da jana'izarsa.

Da yake babu kudin sayen akwati, kuma ba bu taimako da ga surukanta, uwar Ling ta lullube gawar mijinta a cikin wani shudin kyalle mafi kyau da ta iya samu, za'ayi jana'iza mai tabshi, irin da mutane mafiya talauci sukeyi.

Da Ling da uwarta da ke cikin makoki da sauran ya'yan suna zaton al'amarin iyalinsu bazai wuce haka a muni ba; amma sunyi kuskure. A yayinda suke shirin tafiya sai kakannin suka shaida cewa zasu tafi da kanin Ling tare dasu. Da uwar Ling da sauran yaran suka ki kememe, amma ina an dauke yaro daga garesu.

An bar yammata guda uku da uwarsu a cikin bukka, dukansu suna ta juyayin har zuwa yaushe zasu iya zama haka.

"Idan kin yarda, Ling, durkusa muyi addu'a tare" uwarta ta gayyace ta wata safiya. Da kiwuya, Ling ta tafi wajen uwar a gefen gado. Hunturu na shigowa, kuma daben na da sanyi akan gwiwoyinta. Ling ta ki jinin wannan tambaya ta uwarta, tana tunanin sun rigaya sun sha wahala da yawa.

Agefenta kuwa, uwar Ling na kuka. Da farko, Ling ta dauka tana kukan bakinciki ne, amma sai ta gane cewa uwarta tana bada zuciyar tane tana yin magana da Allah kuma. Ling da kanta dai ba ta da abin durkusawar, amma fushi kadai ta iyayi.

Bayan ha kama, menene ma'anar yin magana a cikin iska? Kuma koma da akwai Allah din, ita ba ta son yin managa da shi bayan dukan irin wadannan wahala da suka sha. Yan watanin farko na mutuwar uban, iyalin Ling sun yi manejin rayuwa ta wurin taimako daga makwabta wadanda suka tausaya musu, amma rayuwa ya kara tsamari agaresu.

A karshe uwar Ling ta shaida musu cewa zasu kaura su zauna tare da iyayenta a Lardin Henan. Bisa ga al'adun China an koyarda mata cewa dole suyi dogaro ga namiji. Baya dacewa su zauna zaman kansu, kuma gwamnati ba ta yarda ta taimaka musu ko ta kaka.

Da Ling ta isa gidan kakanninta, tayi mamakin girman gidan. Iyayen uwarta ba masu arziki bane, amma suna da gabjejen gida idan ka kwatanta shi da bukkar da Ling ta tashi a ciki. Kakar Ling ta bi da yammatan ta cikin kicin zuwa wani daki a baya. Wani karamin dan daki ne da aka yi amfani dashi a zaman wurin ajiye kaya. "Dukanku kuna iya zama anan" kakar Ling ta fadi. Ling ta dudduba kewayen daki mai tarkace marasa tsabta sai ta yi murmushi da nuna ai munzo gida kenan.

Sabuwar rayuwarsu ya kawo gardama tsakanin uwar Ling da kakarta. Kuma rashin jituwa yazo ne domin uwar Ling tana so ta nemi aiki a ofishin kwadago na yankin domin ta sami nata gida amma kakar Ling tafi so uwar Ling ta sake yin aure maimako.

## UBAKI (MIJIN UWARTA)

Wata rana da Ling ta dawo daga makaranta, taji irin hayaniyar da ta saba ji tun ma kafin ta isa bakin kofa." Amma iya, bana so na sake yin aure!" uwarta na gayawa kakar da karyayyar murya. "Bazan iya kara kaunar wani kamar yadda na kaunaci Jun ba. Kin sani cewa shiri na ne na zauna ni kadai a lokacinda na yarda na dawo nan da zama. Zaifi idan kin yarda ki yi magana da kungiyar masu sarrafa ayyuka su barni nayi aiki, kuma su taimaka wajen samar mani dagida, na sani zan iya kula da ya'yana. Kinji, iya ina roko kada kiyi mani haka".

"Shekarunki biyu kenan anan yanzu" kakar Ling tana tsawa. "ya ishe ni haka! Ba haka ake abubuwa ba Shu Tan

mutumin kirki ne kuma zai kula da yaranki. Bayan haka ma, babanki ya rigaya ya shirya komai; za ayi maki aure mako mai zuwa"

Mako nashigowa kuwa Ling ta sami sabon ubaki.

Irin kakkarfar murya da ubaki ke dashi yana ta da tsigar jikin Ling, yana kuma kawo mata tunanin muryar ubanta mai sassauci da dadadawa.

Shu-Tan yana wulakanta Ling da yan'uwanta kamar ma su dabbobi ne, a boye kuwa Ling ta raina shi. Zaŋa cikin talauci wani abune, amma abu mafi muni ne a zamana a talauce kuma tare da ubakin da ya maida ta tamfar wata baiwa.

Ling dai tabarwa kanta wannan tunani, yanzu da yake uwarta ta sake wani aure, an yardar masu suyi aiki, kuma duk lokacinda Ling bata makaranta, takan yi aiki a gonaki tare da makiyaya a kungiyar sarrafa ayyuka. Jami'an yankin suna da wani tsari na mizanin abinda yakama a biya ladan aiki. Ma'aikacin gaske zai iya samun mizani goma a rana daya. Ling ta sami tara.

Kuma Ling ta taimaka wajen tsara wani inji mai sauki na yin tofu idan sa ya juya shi inji din yakan murtsuka waken soya a tsakanin duwatsu guda biyu. Shu-tan yaji dadin wannan, amma bai iya sayen sa ba. Maimakon haka sai yasa Ling da yarta suyi aikin. Shekaru hudu gaba kuwa wannan aikin da ba zaiyi suba suka yi ya zama aikinsu na kullum.

Sakamakon wannan aiki tukuru da take yi, a cikar tashekaru goma sha biyar, Ling ta zama kakkarfar yarinya ga kuma rashin lafiya, tana zuba ido zuwa lokacin da zata iya cin gashin kanta. Kin jinin ubakinta kuwa sai karuwa yakeyi a kullum ga yadda yake samun riba daga tofu wanda Ling da yar'uwarta suke faman yi. Duk da haka yaki ya sayi sa don me zai saya? Yana da agololinsa da zasuyi masa wannan aiki maradadi.

Uwarta, da tayi ta kuka a farkon makonnin aurenta ga Shu-Tan, ta daina yin addu'a akai akai yanzu. Masu bi na boye

basu da yawa a kauyen. Kuma Littafi Mai Tsarki guda daya ne tak, wanda ma bata iya karantawa. Addu'a guda daya ne ya rage a lebunanta. Wataran Ling najinta da tsakar dare, "inaroko, ya Allah, ka tsare mani ya'yana, musanman ma Ling da yar' uwarta. Ana tilasta musu suyi aiki mai zafi, ina roko ka tsare su rokona kenan duka."

Ling na mamakin dalilin da uwarta take yiwa Allah magana game da wannan aikin bauta da ita da yarta suke jimiri, maimakon tayi magana da shugaban bayi da kansa! A tunanin Ling cewa take wai Allah ba ya taimaka wa a wannan sha'ani domin takanji kuna kwarai duk lokacinda ubakin ta ya kara musu aiki. Watakila ya fara ganin alamar yadda Ling takeji game da shi, sai ya bata shawarar ta nemi miji. Har ya bada kai ga taimaka yin haka ya zaba mata wani "hakan zai fi dacewa ga kowa", ya gaya mata.

Ling ta sani yana so ya korate ne. watau ya rage yawan wadanda ake ciyarwa.

## ALLAHN DA BA A GANI

Ling ta sami kanta a tsakanin kwazon ta da kuma biyayyar ta ga iyalinta. Idan taki yin aure, zai zaima cin mutunci ga iyali, kuma zata kunyata uwar, wannan kuma wani abu ne mai wuyar jimrewa, idan tayi kuwa tana tsoro kada mijinta ya zama kamar Shu-Tan zabi daya kawai ya rage mata: Zata kashe kanta. Akwai alamar mutuwa ce kadai hanyar da zata tsere wa wannan bauta, damuwar da ke ranta ya fara kafuwa a cikin zuciyarta.

Uwar Ling ta gane diyarta na cikin tsananin damuwa, kuma ta fara tsorata da abin da zai faru. "Ling, kina da baiwa ta shugabanci" tana kokarin kwantar mata da zuciya. Tabbas Allah ya shirya wani abu musamman dominki".

Ling taki ta saurari uwarta tana magana game da Allahn ta a baya gani. Abin duk kamar a banza yin al'amari da wannan camfi na wofi da kuma aiki tukuru na ubakin ta ya kara tabarbare damuwar Ling.

Sanin tsananin damuwa da diyarta ta shiga, uwar ba ta bari tayi nesa da inda Ling take, domin tsoron kila ta kashe kanta. Watarana kuwa sai taci nasarar kawo diyar a taron daya daga cikin dakin addu'a da aka kafa a kauyen. Ling ta yarda cewa wannan yafi nikan waken soya nayin tofu, kuma ma taron ya bata nishadi. Mutane hudu ne kawai a taron; Ling, uwarta, da wasu mutane biyu.

Da Ling ta zauna tana sauraren sauran uku suna raira waka, sai tayi tunani game da bangaskiyar uwarta. Ta yaya take gaskatawa da ido a rufe wani Allahn da ba ta iya gani? Ling na mamaki. Duk da shakkar da takeyi. Ling ba ta iya kawarda kai daga abinda ke haskaka fuskar uwarta ba. In ka ganta kamar tana wakar ne ga malaiku da ba a gani.

## ZAMOWA WANI ABU DA ALLAH ZAIYI AMFANI DA SHI.

Bayan yan kwanaki, sai Ling taji uwarta nayin addu'a dominta kuma amma a wannan karo kalmomin sun jawo hankalin Ling. "Ya Allah" uwar na addu'a a hankali, "ina roko ka ceci ya'yana, musamman Ling. Kasan irin karfin zuciya da taurin kanta. Ina roko ka juya wannan taurin kan nata zuwa wani abu da zai yi amfani". Wannan bangaren addu'a nata a sane yake, sabo da haka jin kalmomin yasa Ling tayi nurmushi. Daya bangaren addu'ar uwar ne ya fi jan hankalin ta. Naji labarin Ibrahim, wanda ya bada dansa, Ishaku, agareka a zaman hadaya", uwar taci gaba "Yanzu nima, zanso in bada daya daga cikin ya'yana a gareka. Ina so in bada Ling." Ling tayi makyarkyata, a yi hadaya da ni? Shin uwata ta haukacene?. Wannan addu'a yazauna a ranta na tsawon kwanaki yana cakunarta. A karshe da taji uwar ta sake yin addu'ar da safe, sai ta fada cikin dakin ta takale ta" zaki sake yin hadaya dani ga Allahnki kuma, Iya?

Kina so ne ki sashi ya kasheni da aiki mai wuya ko kuma

kawai ya buge ni da tsawar aradu? Kuma ma wai ina shi wannan Ubagiji Yesu da kike ta magana game dashi? Kisa ya tsaya a gabana domin na taba shi, sa'anan zan yarda! Kuma wai wadanne irin mutane ke tafiya aljanna? Tsofaffin mata marasa bege irinku? Kuma yaya ake isa can? Kinajin zaki hau itace ko tsani kikai can? "Ling na iya ganin irin bakin raida take sa wa uwar a fuskarta. Taki jinin abin da zai bata mata rai, amma yanzu kam abin ya ishe ta.

Ling taji tsattsaurar murya da ke fitowa daga uwar, irin wanda take yiwa yan' uwanta. Ta rigaya ta kafa kanta a tsakanin yan'uwan a zaman shugabarsu da irin wayon nan nata. Galibi yan'uwan sukanyi na'am da bukatunta, sun san cewa zata yi musu rigima idan suka ki. Yanzu kuma gashi Ling taje tana yi wa uwarta bakar magana da kanta. Irin wannan addu'a uwar keyi ga wani Allahn da ba a gani ya ishe ta.

Lokaci na ja, kuma Ling ta cigaba da aiki sosai. Tayi kokari ta kaucewa shawarar ubakinta na batun aure, shima ya hakura kuma ya fara yi mata kyaliya. Ling ta ji a ranta cewa lallai wannan sauyi na ubakinta dalilin uwar ne. koda shike taji dadin haka amma takan tsargu game da yadda ta yi wa uwarta fito na fito na roshin kunya. Da fatar zata yi gyara ga furucin da tayi wa uwar sai ta fara bin uwar zuwa taron mako mako na majami'a.

Lokacinda bazara yazo Ling tayi watsi da tunanin kashe kanta. Watarana tana fama da aikin nika tofu sai uwar ta taho a guje tanacewa, "Ling gashinan!" "wanene anan?" Ling ta tambaya.

"Mai bisharannan da mukasha jin labarinsa!" in ji uwar. Baki tunaba? Zai yi wa'azi yau kuma na gayawa sauran cewa zamuje. Jeki maza ki shirya. Yi sauri!.

Kafin ma Ling tayi tunanin ki, uwar ta rigaya ta juye ta tafi. Yawwa, da kyau, Ling na tunani, na zama wani jigo game da maganar Allah. Ta tafi taron majami'a wannan daren, domin ta kyautatewa uwar. Wannan tsohon mai bishara yayi

magana a sarari yana wa'azi kamar yana bada labarin Adamu da Hawa'u yana bayanin yadda zunubi ya shigo cikin duniya,, kuma yana tabbatar musu cewa Allah yana kaunarsu kwarai shi yasa ya aiko Dansa ya mutu a kan giciye domin su sami gafarar zunubai. Ling taji zuciyarta ya sanyaya a yayin da kalmomin sa suka shigeta ainun. Bata taba sanin irin wannan kauna da ba da kai ba. Ta taba jin labarin, amma baiyi mata maana ba, sai yanzu.

Daga baya a wannan daren, kalmomi da suka shiga ranta suka kara habaka da taga wani hoton giciye a rataye a jikin bangon gidan wata babarta. Sai ta matsa kusa da hoton ta mika hannu ta taba hoton, tana tunawa da labarin da mai wa'azi ya basu. Idan Yesu ya mutu domina, ni me nayi dominsa? Ta tambayi kanta a yayin da tunanin yin tuba ya cika mata ruhu. Ling ta fadi kasa tayi kuka, sai taji hannun uwar a kafadarta.

"Wayyo, iya, kiyi hakuri", Ling na hawaye. "Kiyi hakuri da duk abubuwa marasa kyau da nasha fadi game da Allahn ki da kuma yadda nake yi maki ba'a tareda kin gaskata abinda kika gaya mani. Ni ban kyauta ba ko kadan. Ta kaka ma Allah zai gafarta mani?"

Uwar tana zubar da hawayen farinciki ta rungumi diyarta da tasami kuma sabuwar ra'yuwa cikin Ubangiji. "Ling kaunatacciyata, an gafarta" in ji ta, Alherin Allah ne yajawo ki zuwa nan yau da dare, kuma zaki zama nasa har abada. Babu abinda yafi haka farinciki. Na bada gaskiya yana da shiri na musamman domin ki, na gaskantarda haka da dadewa can baya." Ling batayi irin wannan kukan ba tun mutuwar ubanta.

## TUMAKI A TSAKIYAR KERKETAI.

Taci' gaba da zuwa addu'ar mako mako na taron nazarin Littafi Mai Tsarki tare da uwarta na tsawon shekara guda, ba a zaman yar kallo ba amma a zaman mamba na wannan kungiya mai habaka.

Damuwar ta na da ya tafi, farin ciki na ruhu ya dauki gurbinsa, kuma ta bada gaskiya damuwa da take da su, sun wuce. Daga nan sai tayi mafarki. Wani siririn hanya ne ya ketare filin gona. Agefen hagu alkamar tayi siriri amma kore shar, iska na daukarsu. Amma a hannun dama, alkamar ta nuna, kuma wadansu na faduwa don nauyin tsabar kwayar alkamar. Ling ta duba daga gefe zuwa gefe a yayin da alkamar take bacewa. Tana mamakin yadda irin wannan kasa da kuma yanayi suke da suka iya ba da irin wanan amfani.

Ling ta gayawa uwarta wannan mafarki da safe. Abinda ya baiwa Ling mamaki shine cewa uwarta ma tayi irin wanan mafarki. Taga nunannun kwayar alkama, amma kuma taga yan tsiro na wake a tsakiyar gonar, kuma taji murya na umurtar ta da tayi ban ruwa ga kananan tsiron" in ba haka ba zasu bushe".

Babu wata acikinsu da ta fahimci inafarkin, amma sun sani akwai dalilin da yasa hakan ya faru. Amsarsu ta fito a makon gaba a wajen taron addu'a lokacinda karatun wannan yammacin ya fito daga Bishara ta Hannun Luka, sura goma: "Aikin na da yawa, amma ma'aikata kadan ne, saboda haka kuyi addu'a domin Ubangijin girbi ya aiko da ma'aikata garin yin girbinsa. Ku yi tafiyarku gama, ina aiken kune kamar tumaki a tsakiyar kerketai".

Suna tunanin ko wannan shine ma'anar mafarkansu, Ling ta zama mai jin tsoro kuma mai doki game da abinda Allah yake dashi dominta.

Ta kagara da son sanin daya gefen bayanin abinda yake nufi. Amma kaka ma za ayi na zama mai wa'azi? "ta tambayi uwar a yayin da suke tattauna wa game da wurin da sukayi karatu. "Nayi kankanta, kuma gashi bansan komai ba. Ba nima da Littafi Mai Tsarki".

Uwar ta dube ta tayi murmushi. Ta gane abinda mafarkan ke nufi sarai: diyarta zata kawo bishara ga batattun rayukan China. Wannan tasani sarai. Jim kadan bayan tacika shekaru

17, da yan kudi kalilan babu ko abinci, babu Littafi Mai Tsarki kuma babu garin da ta nufa takamaimai. Ling ta kama hanyar yin wa'azin bishara ita kadai. Taso tajima har sai takara nazari, amma uwar ta matsa. "ba lallai ne sai kin kware ba kawai ki shaida labarin Yesu. Gaya wa mutane abinda kika sani idan batun na Allah ne zai albarkaci hidimarki" kuma da karfafawa daga uwar Ling ta kama hanya.

Ling dai a saukake tafiya take daga kauye zuwa kauye, tana shaida bangaskiyarta. Duk lokacin da ta isa wani kauye da suke da Littafi Mai Tsarki, sai tayi nazari ta haddoce wasu ayoyi da zatayi amfani da su a kauye na gaba. Ta kuma koyi raira wakoki, bata taba sanin zata iya waka sosai haka ba, saida taga yadda take jan hankalin mutane idan ana waka, sai kuma su tsaya domin jin wannan budurwar mai wa'azi me zata fada? Batun cewa ita karamar yarinya ce, babu miji, kuma tana tafiye tafiye ita kadai tana ratsa China ya isa ya jawo hankalin mutane su saurare ta.

Allah ya albarkaci hidimar Ling. Karin tafiyar ta karin masu sauraren ta. Tayi mamakin ganin inda ake da mambobi bakwai ya zama mambobi saba'in bayan juyawar mako. Nassi ya fada gonaki sun nuna, mutane suna yinwar bishara, kuma Allah ya kira ta tazama daya daga cikin yan aikensa. Ling kuma tacigaba da yin addu'a domin zama mai dacewa da wannan kira.

Fiye da duka sonta shine, ta zama misali. Tana so tayi wa'azin abinda ta sani da wanda ta gogu dashi.

Kuma tana kewar samun Littifi Mai Tsarki na kanta, sai ta fara rokon Allah da yayi mata hanyar guda daya. "Ta kaka mai wa'azin maganar Allah kuma ace babu Littafi Mai Tsarki? Tana tambaya.

Kwarjini Ling da karfin bangaskiyar ta ga Ubangiji yana jawo hankalin matasa musamman. Wadansunsu sukan bada kaisu tafi tare da ita, kuma takanyi farincikin haka.

A yayin da taro na kara girma kuma shaukinta domin

Bishara na kara karfafa. Ling ta ga cewa ba zata iya cigaba haka ba, ba tare da Littafi Mai Tsarki ba. Ta ziyarci' wani kauye inda masu bi na wurin suke da wasu shafuka kawai na Bishara daga hannun Matta, kuma sun karanta a sura 25 labarin misalin budurwai guda goma. Biyar masu wayo da suka dauki karin mai domin fitulunsu, da guda biyar marasa wayo da basu dauki karin mai a fitilunsu domin fitulun su haskaka ba. Domin rashin fahimtar ainihin ma'anar, kowane member na wannan majami'ar kauyen sukan dauki karin mai a fitilunsu a kullum domin kada su rasa mai a lokacin da Ubangiji zai dawo.

Ling tayi kewar samun Littafi Mai Tsarki na kanta domin tayi nazari kuma ta taimaka wa wasu masu bi fahimtar sa. Saboda haka da taji labarin wata mata mai nisan mil hudu daga inda take tana da Littafi Mai Tsarki, sai tayi maza ta garzaya. Sai ta taras matar tana da Litattafan kalilan ne da ruwan teku ya turo gaci bayan an talista wa wadansu yan kungiyar Mishan ta Krista da su jefo su a cikin teku daga cikin jirgin ruwa inda aka kama su suna fasa kwaurin shigo da Litattafai Masu Tsarki zuwa cikin China da dare. Wasu masu bi da ke zaune kusa da bakin teku suka debo litattafan, wannan matar kuwa tabi a hankali ta shanya shafukan daya bayan daya suka bushe a rana.

Lokacinda Ling ta nemi abata daya, tana bayanin yadda Allah ya kira ta ga yin bishara, matar tayi mamaki. Kin san irin wuyar da ke akwai kafin a sami Littafi Mai Tsarki? Kuma ta yaya ma zan sani cewa ke maibi ce?"

Ling tana ce ga rokon matannan, amma bata ci nasàra ba. Matar fa bata yarda ta rabu da ko daya ba. Ayya, Ling ta karaya, matar ta gaya mata tayi addu'ar Ubangijin mu ba tare da kuskure ba, in tayi matar zata duba rokon da tayi.

Ling ta hakura ta tafi, da sanin cewa gaba tafi baya yawa. Sai ta tafi wani kauye inda tasan suna da Littafi Mai Tsarki a gidan wata tsohuwa mai bi.

Dan uwanta yana rikon littafin da daraja, da Ling ta gani, ta gane dalili, Littafi Mai Tsarkin dattijon nan da hannu aka rubuta gaba daya. A yanzu ma dai, hannayen dan'uwan sun murde daga rubutu na sa'oi dubbai daya dauka yana kwasar ko wace aya daga kalma zuwa kalma.

## DASHE MAI KARKI .... FARAWAR AIKIN MISHAN

A lokacinda Ling tayi tambayarta, dattijo ya dauki littafin sa a hankali ya mika mata ta kwashe Addu'ar Ubangijin mu domin taje ta haddace. Ling tayi mamaki matuka ga yadda aka tsarar rubutun kuma cewa take ko shekaru nawa ya daukeshi yana kwasa dubban ayoyin nan. Zata ga Litattafai Masu Tsarki irin wannan a yayin da taci gaba da tafiye tafiyenta. Wannan irin aiki tukuru na nuna kauna ya kara mata yin na'am da sanin darajar maganar Allah. Kuma ta shiga haddace nassoshi da dama. Ta kuma ci alwashin raba Litattafai Masu Tsarki ko ina cikin China ga wasu masubi....... Idan Allah zai tabbata da yiwuwar haka.

Akan hanyar ta na komawa wurin matar, Ling ta fara tunanin shin ta haddace Addu'ar Ubangijin mu dai dai. Kaka kenan idan mutumin yayi kuskure wajen rubutun? Kaka kenan idan ita ce bata rubuta nata daidai ba? Amma bata da bukatar damuwa, domin taci jarrabawarta ta karanta Addu'ar Ubangiji babu kuskure. Bayan haka, sai matar tasa Ling tayi addu'a da murya domin ta kara gamsuwa. Sa'annan tayi ta yin tambayoyi game da aikin bisharar Ling da yadda ta karbi Kristi. A karshe yin tambayoyi ya kare, kuma matar ta durkusa tare da ling ta dauki Littafi Mai Tsarki ta mika mata. Tace Ling tayi hakuri don irin hanyarda tabi, tayi bayani cewa,"Bayan da yan'uwanmu suka debo litattafan daga bakin ruwa, sai suka fara rabar dasu a cikin China. Akwai hatsari, kuma wadansu ma sun biya da rayukansu. Yanzu ina darajanta litattafan nan fiye da da idan na tuna da rayuka da muka rasa."

Ling ta tafi da littafinta wani gefen a jike har yanzu domin matar bata karasa busar da dukan shafukan ba tukuna. Ling ta bude Luka sura goma, a hankali tana daga jikakkun shafuka sai ta karanta kalmomi da ta saba dasu da hawaye a idanu: girbi na dayawa, amma ma'aikata kadan ne; saboda haka yi Addu'a Ubangijin girbi ya aiko da ma'aikata a cikin girbinsa. Kuyi tafiyarku, gama, na aike ku tamfar tumaki ne a cikin kerketai".

Ling ta fahimci sashe na farko na umarnin Yesu. Ta fita ita kadai a zaman ma'aikaciyar Ubangiji kuma girbin da girma yake. Yanzu tana juyayin yadda sashe na biyu zai yiwu tayi addu'a domin samun kar fafawa.

## NEMA

Takardar da aka nane a bango akwai nahisa; "Ana nemansu domin yiwa kasa laifi," kan maganar shekar kenan. "Dukan wanda ya ga daya daga cikin mutane da aka zana sunayensu yakai rahoto maza a gaban hukuma. Za a bada kyauta." Da Ling ta karanta sai tayi makyarkyata idanunta na bin sunayen da aka rubuta, lebunanta na motsi tana karanta sunayan da ta sani. Dayawa abokanta ne da kuma abokan aiki. Sai kuwa a ciki ga nata sunan.

Bata yi mamaki ba, amma dai, ganin sunan da damuwa. Abubuwa sun yi ta tafiya lami lafiya. Tana tuna yadda tsohon mai wa'azi yazo kauyensu yayi magana game da Adamu da Hawa'u, game da zunubi, kuma game da ba da kai ga Yesu Kristi, Ling ta bi misalinsa. Da wuri ta koya cewa hanyar isa ga mutane mai sauki ita ce na karanta wasu zababbun nassoshi daga Littafi Mai Tsarki ana karantawa mutane suna bi.

Mutanen China da yawa sun san wuyar samun Litafi Mai Tsarki, saboda haka sukan saurari labarun cikin marmari, suna kuma rike abin da suka ji.

Abin mamakin shine damuwar ya faro ne daga danginta. Tafiye tafiyen Ling a cikin kauyukan kewayan, da labarin cin gaba cikin bishara ita ke yaduwa, dangin Ling suna bata laifi wai tana kawo kunya akan iyalinta. "Gashi tana tsufa" suna hargagi a tsakaninsu" cewa ya kamata tayi aure, ba wai tayi ta yawace yawace kamar wata mahaukaciya ba!"

Ling tayi shawarar komawa gida amma domin wani dalili dabam. Ubakinta ya fusata cewa mai yi masa tofu ta tafi. Da farko ya dauka zata dawo da zarar taji yinwa.

Amma da lokaci ya ja, sai ya lura cewar tafa tafi kenan. Ko da shike takanzo wani lokaci amma bata wuce wuni. Yaki ya dauki wani ma'aikaci ko ya sayi sa. Shu-Tan ya sa uwar Ling a madadinta. Da Ling taji labarin irin wannan bakar zuciya ta ubakin ta, sai ta lalubo gida ta gaya wa uwar "wannan yayi maki yawa. Zandawo gida" "A'a! sam sam," in ji uwar" dole kiyi mani alkawarin zaki rike amanar kiran da Allah yayi maki, zan iya kiyi bishara. Kin gane? Lallai ne kici gaba da aikinki cikin gonar Ubangiji."

Ling tayi biyayya, amma jim kadan kuma wasu al'amura suka taso. Yan sanda sun fara shiga kauyuka suna fasa tararruka da basu da izni.

Masu bi da yawa sun fara jin tsoron barin Ling ta sauka a gidajensu; a wasu wurarema ana hana, ta abinci. Ling ta sami kanta tana dogon tafiya da kafa, tana shiga karkara. Tana iya tafiya a mota amma ko dashike kudin motar centi 50 ne kawai amma bata da shi.

Amma tayi sa'a, a lokacinda masu taimaka mata sukaji labarin tafiye tafiyenta, sai suka yi mata kyautar takalma. Ling ta karba da murna. Duk da tsananin da take samu, bisharar Ling sai karuwa yakeyi akan sami taron mutane fiye da dari daya kuma muryarta na kara karfi a yayin da take yiwa jama'a masu yawa bishara, gidajen addu'a na ta tashi a ko ina cikin kauyuka, wannan kuwa sai ya jawo hankalin gwamnati. Dafarko kristocin sunce basu rabu da majami'ar da gwamnati

take gudanarwa ba, wacce ake kira (TSPM) kuma su Krista ma suna shirin su shiga TSPM amma babu ko daya a kewayen mil dari daga inda suke!

Yan sanda fa suka fara nuna wa Krista tsanani dalilin wannan sai masu bi suka maida wuraren taron su a cikin kurmin jeji, kuma wakoki da wa'azi da ake ji a cikin gari ya zama babu. Lallai ne Ling ta maida hankali ainun game da wa zata amince dashi kuma ta daina dadewa a guri guda. Ta rigaya ta zama sananniya ga masu aikin mishan da dama daga kasashen waje da ke yankin, kuma sukan nemi ta sadu dasu.

Ling ta sani irin wadannan taron na da hatsari da kuma jan hankali ga yan sanda, amma ta kan yi dokin gamuwa da yan'uwanta cikin Kristi daga Kasashen waje domin ta gaya musu abinda Allah yake yi a kasar China masu aikin mishan sukan kawo Litattafai Masu Tsarki, wadanda Ling takan rabar da murna ga gidajen majami'u. har yenzu suna wuyan samuwa duk inda ta tafi, galibi madai takan bada guda daya ga ko wane taro, saboda haka masu kwasar rubutawa da hannu suna cingaba dayi.

## GWIYOYI DA TABO AMMA ZUKATA A CIKE

A cikin hunturun 1983, tsanantawa da kuma kama Krista ya bazu ko ina. Yanzu dai Ling tana kan gujewa akai akai, sanin cewa sunanta da na abokan aikinta masu yawa na cikin jerin sunaye da gwamnati ta tsara na wadanda ake nema. Yanzu batun tafiya gida taga uwarta kam babu dama. Babu shakka yan sanda na zuba ido. A yayin da take ziyarar wani kauye da ake kira Towkil, saida Ling takai kauyawan a cikin zurfin gonaki domin yin bishara garesu. Ana ruwan sama, kuma babu makari. Amma kowa ya tsaya, domin sakon na shiga kuma suna rike kowace kalma.

A lokacinda Ling ta shugabanci yin addu'a na tuba masu saurare suka durkusa a cikin tabon. Gwiwoyin Ling suka

nutsa a tabo kamar na kowannensu. Fiyeda mutane dari suka karbi Kristi a wannan rana, kuma Ling ta taya su murna amma kurna abinda ke tafe a gaba yana tsorata ta. Amma fa tasan cewa gobarar tsanani zai sa iskar ruhu mai tsarki ya kara karfafa ya kuma kara ỹin gaba. Sai ta sake bada kanta ga yin aminci da wannan kira, ko da menene ke tafe a gaba.

A kauyen Datwin, mai nisan mil 20, Ling ta sadu da wasu masu yada bishara wandanda ke tafiye tifaye a cikin karkara suna wa'azi a yayinda suke kokarin kauce wa tsanani. Ana kiran daya daga cikinsu Uncle Foone, kuma dashi da wasu suna da irin hange da kuma marmarin da Ling take da shi; sunyi shekaru suna hidimar Ubangiji. Uncle Foone shine yafi yawan shekaru a cikinsu. Ya rigaya yayi fursuna na shekaru biyar a cikin sansanin gwale gwale. Da Ling da sauran a hade masu bishara guda goma: maza tara da Ling kuma suka bada kansu cewa zasu cigaba da yada sakon Kristi har sai gidajen addu'a sun kafu t are da nadaddun shugabanninsu a yankunansu. Kuma sun yarda a tsakaninsu wadanda basuyi aure ba, kamar Ling su cigaba a haka harsai wannan aiki nasu ya kafu.

Babban kalubale da suka fuskanta ba tsanani bane amma bukatar Littafi Mai Tsarki fiyeda yadda ake tsammani. Sun yarda cewa Ling ce zata yi wannan aiki na kawo Littafi Mai Tsarki tun da yake ta rigaya ta sami hanyar sadawa da ma'aikatan mishan daga waje, wadanda sukanyi fasa kwaurin Litattafai Tsarkaka wajen kafa majami'u, Ling, tare da taimakon Uncle Foone suna bin sawun duk jita jitar da sukaji na cewa akwai Litattafai Masu Tsarki.

## AIKI TUKURU, KARUWAR HADARI

Tsakanin wa'azi da rarraba Littafi Mai Tsarki, Ling tana yin tafiyar mil talatin ko fiye a rana guda amma yanzu yawanci akan basukur ne tafiye tafiyen na kara zama da hadari; Ling ta sani cewa yan sanda suna zuba mata idanu. Ta sani cewa

lokaci ne kawai take jira na shiga hannunsu. Domin ta zama da shiri, sai ta fara karatun nassoshi da suka shafi batun shan tsanani a cikin Littafi Mai Tsarki tana yiwa kauyawa wa'azi game da haka. Tana sone su zama da shiri, kuma idan hakan ya faru da ita kuma ta zama misali maikyau.

Aiki fa sai kara yin wuya yakeyi. Galibi ma watarana takan tafi babu abinci na fiye da kwana daya, kuma wasu mambobin majami'a na sukanta. Ita yar shekaru ashirin ne kawai, babu aure, kuma mace, inji su me yakai ta daukar wannan aiki? Gatsine da wasu sukeyi na faruwa ne domin masu yin sukar suna la'akkari da yaddda suka taso a cikin irin al'adunsu; saura kuwa kyashine kawai. Ko wannene ma dai batun ba ya yiwa Ling dadi. A lokacin da Ling da abokan aikinta suka cigaba da tafiye tafiyensu a cikin shekarun 1980 sun sa mi karin rahotanni game da razanarwa, kamu da azabtarwa da hukamar China ke yi wa Kristoci. Gwamnatin China ta tsakiya tana damuwa game da saurin yaduwa na gidajen addu'a a ko ina cikin kasar a yayin da majami'an TSPM na hukuma na rasa mambobi. Ga Ling da sauran masu wa'azi a fili yake cewa masu bi suna neman samun albarkar zubar Ruhu Mai Tsarki da yake samuwa a majamiun gidajen addu'a masu tasowa.

Domin wannan sai shugabanin gwamnati suka yi shela a ko ina cewa a kashe habakar wadannan majami'u. tsanani ya kara karfafa domin an baiwa yansanda izinin kuntatawa Krista, musamman shugabannin Krista, duk yadda suka zaba, wannan yana nufin azabtarwa da kuma dauri ba tare da anyi shari'a ba.

A cikin farkon shekarun 1990 dubunan masu bi sun san Ling wata shugabace mai hikima kuma mai tausayi, zuwa yanzu dai ta tsere wa kamu daga hukuma.

## RIKE ALKAWARI

A watan Afrilu 1994, Ling taji gajiya a jiki "ya kamata ki dan

huta" Uncle Foone ya gaya mata. "Kuma watakila lokaci kenan da Allah ya nufa kiyi aure".

Amma Linga ba ta yarda da shawarar sa ba. "Ka sani nayi alkawari ga saura acikin rukunin mu. Munce ba zamu huta ko yi aure ba har sai an gina majami'a tukuna. Masu bi suna da bukatar shugabanci da zaici gaba da karfafa su domin su iya tsayawa gaba da tsanani da ake ciki. Bayan haka ma, akwai kayan Littafi Mai Tsarki da aka sauke daga jirgin ruwa a Guangzhou. Zan tafi tare da Shen da Jan mu kawo wasu. Zamu dawo cikin yan kwanaki."

Dattijo Foone yaji abin bai kwanta mashi a rai sosai ba, amma ya danne wani muradi na yin magiya da ita. Ling mai taurin kai ce, amma ai dalili kenan ma da ya kawo ta cikinsu tun farko. Ya sani Allah na iya amfani da matsanancin sa kai irin nata domin taimakawa gidajen addu'a masu tasowa su girma kuma su wala. Bayan haka Uncle Foone da matarsa suna kaunarta kamar diyarsu.

Yasan irin gwagwarmayar Ling, wadda a wasu lokuta takanyi fama da kyashi daga mambobin majami'a domin matsayinta, da kuma yadda take fama da rashin fahimta ta kullum na wadanda basu iya gane dalilin tana rashi aure ba. Yin tunanin dukan kalubale da take fuskanta, Uncle Foone yayi addu'ar zuci a yayin da ta kama hanya.

## A KARSHE DAI TA SHIGA HANNU

Da yamma rana na faduwa kenan bayan Ling da abokan aikinta sun dauki kayan Litattafai Masu Tsarki kuma suka isa gidan abokansu akan hanyarsu ta komawa gida. Suka yi sujada tare suka kuma dan huta bayan doguwar tafiya, kuma dare ya rigaya yayi ainun a lokacin da Ling ta nemi fita ta buga tarho kafin ta kwanta. Fitar ta kan titi ke da wuya ga duhu kuma ko ina shiru, amma sai taji wani mutum ya kira sunanta. Ya nufo ta cikin sauri, da yazo kusa, a karkashin fitilar titi, sai taga hafsan yan sanda ne. Tunanin Ling na farko

shine na tserewa, amma da ta juya, sai ga wani hafsan kuma.

To, Ling tayi tunani, a karshe dai gashi sun kamani, tun lokacinda taga sunanta a jerin sunaye da ake nema shekarun baya, tasan wannan ranar zata zo.

Amma ita ta bada gaskiya cewa ba za a iya kamata ba har sai Allah ya yarda da haka kuma a nashi lokaci da ya dace; yanzu kuwa ta rage bakincirinta da wannan tunani.

"Lallai ne ki taho tare damu" daya daga cikin hafsoshin ya fada suna nuna bajojinsu. Da alamar suna fakon ta, kuma ko dashike tana sane da me zai zo, tadan sami sake jiki, tana tunanin ita kadai za a tafi da ita, ba tare da taba sauran masubin ba ko kuma bincika cikin gidan. Amma maimakon kaita cikin motarsu sai suka juya suka nufi masaukin.

"Ina zaku kaini?" in ji Ling "A ciki" inji hafsan. Dogone shi, kamar Ling, kuma yana magana da murya mai tabshi da yake bata haushi. A yayinda suke komaŵa cikin ginin, tunanin Ling yayi gaba; Shen da Jan dukansu masu aure ne; bata jin yan sanda zasu kaisu kurkuku, Littafi Mai Tsarki guda nawa zasu taras? Shin ko na yayyaga takardar adireshi na zuwa gidan pastor bayan na kwashe litattafan?.

Ta rigasu shiga gidan sai tayi maza ta rada wa Shen da Jan, "Kawai ku gaya musu nayi hayarku ne baku san komai ba. Kubar komai a kaina".

Yan sanda sukayi maza suka ware Ling daga sauran, suka zaunar da ita kan kujera, suka shimfida wata takarda akan tebur a gabanta. Taga sunanta a rubuce. "Sa hannu a wannan" in ji Malam Dogo kuma mamugunci. Ya maka mata alkalami a hannunta, Ling kuwa tayi maza ta duba takarda. Waranti ne na basu iznin yin bincike kuma su debi dukan shaida da suka samu su tafi dasu. Ta sa hannu a takardar daganan kuwa sai ta fara jin gajiya. Tasani cewa za a dade ana wannan abu.

Hafsoshi suka shiga aiki suna bincika dakin, tana kallon su

suna bincika tufafinta. Sai suka gano akwatin Litattafai Masu Tsarki. Aha, kai Ling a kurkuku mai lamba 91, daya daga cikin shahararrun kurkuku guda hudu a China. Hafsoshin da sukayi mata tambayoyi abubuwa guda uku kawai suka nema: sunaye, sunaye da karin sunaye. "Hake baki taimako? Su wanene sauran shugabanni? Wa ya baki wadannan Litattafai Masu Tsarki?". Sanin sakamakon da zai biyo baya ba ta yarda tace komai ba game da kungiyarta.

An yi ta maimaita tambayoyin nan har zuwa watanni biyu gaba. Baicin tambayoyi a kullum, Ling na yin aiki tare da sauran fursunoni. Ayyukan fursuna a wannan lokaci shine yin laita na kunna sigari, kuma anakula da hadashi da aminci sosai domin ana aika su kasashen waje na Turai. Ling ta yi rashin lafiya, tayi zazzabi mai tsanani ainun ta kwanta. Amma idan bata cika aikin tana kowace rana ba, sai anyi mata duka.

## MUNSAN YADDA AKE BUDE BAKUNA

A watan Yuli a ka kaurarda Ling. Yan sandan garinsu sun sami labarin kamata, kuma suka nemi a dawo da ita gida. Bayan bin sawunta har na tsawon shekaru goma, sunji dadin jin cewa ta shiga hannu. Yan sandan garinsu sun fi goguwa wajen yin tambayoyi ga fursuna. Kamar yadda daya daga cikin su ya gaya mata, "munsan yadda ake buda bakuna."

Da yake tana jin gajiya daga zazzabi da kuma aikin gwale gwale na kurkukun lamba 91, Ling ta wahala ainun da tambayoyi suka cigaba. Lebunanta sun yi sanyi, kuma tana kusa da suma. Lokutan tambayoyin sun yi tsananin kwarai, amma basu sami kome ba.

Sun mori wasu dabaru dabam da yan sandan farko, amma abu guda suke so: sunaye, su wanene saura da kuke aiki dasu? "suna tambaya akai'akai" su wanene kuke hulda dasu a kasashen waje?" gaya mana batun taron ku mara izni. Wa yake baku litattafanku da Littafi Mai Tsarki? Tambayoyin suna kawo hajijiya, amma lokaci zuwa lokaci Ling ta dage kuma

bata bada sunan kowa ba, ko da shike jan hankalin tayi haka din yana da karfi. Wani lokaci masu tambayoyin sukan nuna wa Ling hotonta tare da abokan aikin ta. Idan har sun rigaya sun san wadanda na ke aiki tare da su, me zaisa su so sanin sunayen daga gurina? Ling na juyayi. Kuma wace barna wannan zai kawo a yanzu?

Wata rana mai tsoratarwa, mutane guda goma suka shigo dakin tambayoyi, daya yana rike da wani karfe mai baki bude. Mutane biyu suka kwantarda Ling akan (ruwan cikinta) rub-da-ciki a kan dabe suka rike daya hannunta aka sa a bayanta, sai suka ja daya hannun takan kafadar ta yadda hannuwanta zasu zama yan inci kadan ne a tsakani da kashin gadon bayan ta. Sa'annan wani cikinsu ya dora duddugen kan kurar takalminsa a bayan ta domin ya sami isasshiyar dama na jawo hannayenta, suka yi maza suka sa wannan karfe mai baki bude akan manyan yatsun hannunta guda biyu suka rufe bakin suka daure tam tam da kusa noti.

Ling taji kasusawanta na motsawa a yayin da takeji kamar duk kafadunta suna cikin fita daga mazaunansu ta halitta. Sa'annan mutanen suka saki hannayenta, kuma wannan mugun matsayi da aka kai hannayenta tawajen murde su ya aika da wani irin zafi mai radadi a jikinta.

Wannan karfe mai budadden baki da aka sa mata a manyan yatsun hannu bakar mugunta ce kawai, gwamnati ta haramta yin amfani dashi akan mata. A cikin wahalarta, Ling tayi kukan zafi tana tunawa da gatsen: Dayawa a cikin kauyukan suna hana ta shiga wannan aiki domin ita mace ce, tana yin aikin da an sani na maza ne. Yanzu kuwa gashi ana yi mata azaba irin ta maza.

Ling tasan abin da ke tafe. A wannan lokacin sai taji cewa tana da zabi; fuskanci mutuwa ko kuma ki tona asirin yan' uwanki. Sai ta yanke shawarar cewa mutuwa zata fi saukin ciwo.

"Tashi!" wani hafsa ya kwala ihu ya shure ta tana kokarin tashi akan gwiwoyin ta sai aka buge ta da sanda a doron

bayan ta. Jikinta na ciwo ko ina. Ba ta iya numfashi; da kyar take motsi. Hannayenta sun kumbure domin murde su baya da aka yi.

"Yi hakuri, bazan iya ba........"muryar Ling na rawa tana kokarin zama cikin hayyacinta. Jibi na ta zubowa a fuskarta yana shiga mata a ido kamar yaji tana kai kukanta ga Allah, tayi ta juyayin ko hakane shima Yesu yaji a yayinda yake addu'a a Gethsemane, da sanin zai sha wahala kuma ya mutu, juyayi take ko mutuwa za ta yi ....

Sunci gaba da tambayoyi har na tsawon sa'oi uku da yatsunta a daure da wannan karfen a bayanta, jikinta ya zama a murde, a karshe kuwa sai ta suma.

A lokacinda ta farka sai taga kanta a rub da ciki a cikin dakin tana kurkuku. Tanajin muryoyi kusa, daga baya kuwa wani ya shigo dakin ta ya daga ta ya dora ta akan gadon ta na katako. Ba ta iya motsi; zafin ciwon yayi yawa. Bata ko iya tashi tachi abinci, ko tayi amfani da bokiti, ta kwanta ken gado har kwanaki goma sha biyar, a yayinda hafsoshin ke shawarar abin da zasuyi da ita. Sannu a hankali ta zo ta warke daga wannan azabar, kuma ta haye mugun yanayi na wannan kurkuku na karin wasu watanni biyar. Daganan, da yake hukuma basu sami wata shaida takamaimai ba game da ita, kuma ba a iya sa ta bada sunaye na wasu masu bi cikin aikinta mai fadi ba, sai suka sake ta amma ba da sonsu ba.

## SHAN WUYA MAKARANTA CE

Ana sanyi mai tsanani, a cikin Janairu 1995 lokacin da Ling ta kwankwasa kofar wani abokin aiki "Ling" kawarta Ruth ta fada da karfi lokacinda taga ramammen jiki da ke tsaye a gabanta. Tayi maza ta ja Ling zuwa cikin gida, ta rungume ta, kuma ta hauta da tambayoyi. "Ling munyi ta damuwa game da ke. Me yasa baki aiko mana ba? Kin rame! yaya kike? yan sanda sunki su gaya mana kome game da ke. Yaya kika yi kika haye? Yaya kika yi kika fito?

Bukin da babu shiri ya samu, labarin fitowar Ling ya bazu a tsakanin masu bi. Ling tana gajiye amma tana jin dadin wanzuwa cikin yan'uwa Krista maza da mata. Da suka taru domin nuna godiya ga Allah da yin addu'a. Ling tace na gode muku domin addu'oinku da kukeyi domina game da watannin nan da suka shige. Na sani da ba don taimakon Allah kuma da addu'oin ku ba da babu yadda zanyi na haye. Ku gaskanta ni akwai kwanaki da yawa da nakanji kamar bazan kaiba. Amma Allah mai amincine yakan tunashe ni game da kaunarsa a wadannan lokuta. Inajin cewa shan wahala makaranta ce, idan aka kammala da nasara to kunyi aikin ku. Amma idan aka fadi, an ruguje komai. A gareni, kurkuku ne wannan makarantar. A lokacin da nake can bana dogara ga kome, illa cikakken dogarawa ga Allah. Kuma wannan dogaro shi ya kara matso ni kusa gareshi. A kullum nakan koya maku cewa kuyi karfi domin Allah da kuma fuskantar jarabta. Yanzu ina gaya maku da babban tabbaci cewa Yesu yana tare daku, ko da wane irin hali kuke ciki"

Kafin kamata, Ling tayi nazari ta koya cewa dukan rayuwar Bulus da sauran manzannin Sabon Alkawali wadanda suka sha wahala domin Kristi. Yanzu kuwa tana wasa da abokan aikinta cewa idan ta isa aljanna, tana so ta gaida Yesu, sannan ta sha hannu da Bulus ta tambayeshi," lokacin da kake raye a duniya shin rayuwarka tayi tsanani irin tawa?.

Kusan shekaru talatin kacal da haifuwa, Ling ta shiga munanan halaye na cin mutunci, yana da wuya mutum yaci gaba da irin haka. Duk da haka domin son nuna misali nagari, ta koma kan aikinta a cikin gidajen addu'anan take, tana koyarwa tana shugabantar nazarin Littafi Mai Tsarki, yin taro da baki daga waje domin shirya taimako da bayanai ana tabbatar da cewa rabar da Littafi Mai Tsarki yaci gaba ba tare da yankewa ba zuwa cikin China. Domin tsananin azabtarwa da gwamnati tayi a shekarun 1980, masu bi sun watsu a ko ina cikin China, kuma hada hada na gidajen addu'a ya girma zuwa milyoyi da dama na yawan mutane. Tare da karin

hamzari yanzu Ling tana aiki tukuru domin ganin akalla kowace majami'a ta sami Littafi Mai Tsarki guda daya.

Watarana da yamma a watan Satumba 1996, Ling tayi sallama da wadansu masu aikin mishan daga Turai kenan ta dawo gida, sai da ita da abokanta sukaji kwankwasa a kofa wajen karfe goma na dare.

Muryar namiji na cewa, "Alo! Muna sone mu duba katin iznin zama" Ling ta dubi Foone da Shen sai ta girgiza kai. Ta sani yan sanda ne, Ling ta bude kofa kuma hafsoshi shida suka shigo ciki. "Mun kamaki wani hafsa yana shela a yayinda sauran suna sawa Ling ankwa tare da abokanta. Ling ta zuba ido tana kallon hafsoshi na birkice komai. Wannan zai dauki dogon lokaci yau...

## TSOFAFFIN ABOKAI

Da suka isa caji ofis, sai aka gabatarda Ling ga kwamishina, mutum mai sassaukar murya wanda ya ji da ita a wancan tsarewa da aka yi mata. Ranka ya dade, wannan ita ce Malama Ling.....shi na kasan ya fara bayani ga babban. "I, nasanta," inji babban yana murmushi irin na mugu. "mu tsofaffin abokai ne. To ling wannan karon kam banajin zaki tafi wani wuri daga nan zuwa wani lokaci. Fayil dinki dana kungiyarki ya yi kiba sosai. Kuma mun kamo karin shugabanin ku guda biyu a yau. Gabadaya dai, zance aikin yau yayi kyau." Ku sakata a dakin kurkuku lamba 12" yana fita waje yana bada umarni. "Zan tafi gida"

Bayan mako guda dokin Ling ya karu tana tunanin irin hali ban kula ba na hafsan. Me yasa ba a yi mata tambayoyi? Me yasa wannan hafsan ya saki jiki haka? Yaya suka sami sauran da aka kama? Ling tana yakar damuwa kan damuwa da ta farga da cewar kila sun san abu dayawa game da su. Tana tsammanin yan sanda sun riga sun fahimci abubuwa fiye da da akan yadda tayi fice sosai yanzu. Watakila sunyi ta binta tun daga lokacinda aka saketa daga tsareta na farko,

saboda haka sun sani kenan ko sau nawa take saduwa da mutanen waje. Kuma tanajin kamar sun san dukan mutanen da suka ziyarci gidan ta kuma suka nemi saduwa da ita a game da batun kungiyar gidajen addu'a.

To, in ji Ling a tunanin ta duka da ma'ana, majami'a na girma da sauri sauri, sabo da haka lallei ne yan sanda su sami wasu bayanai na ayyukan ta, ko ba dade-ko-ba jima. Ta mika kanta ga rayuwa a cikin kurkuku, tana tsoron tayi tunanin kalmomin Yesu- "Gama, na aike ku kamar tumaki a cikin kertetai suna sake zama zahiri kuma.

Watanni hudu da suka shige lokaci ne na tashin hankali ga Ling "idan kun yarda," wani lokaci takan roki masu tsare ta, "idan kuna so ku kasheni, to ku kashe kawai. Idan kuma so kuke ku daure ni to ku daure idan kuma so kuke ku sake ni to ku sake ni. Amma ku daina ajiye ni anan ba tare da dalili ba, kamar yadda kukayi acan baya.

Ta fadi abubuwa haka a fili, amma babu wanda ya kula ta saidai wani lokaci wani mai tsaro yakanje ya tsarta mata miyau ko kuma yayi mata ba'a. wani lokaci Ling takanji kamar zata haukace. A kullum takan zauna a kan benci mai tauri wanda kuma shine gado. Dan karamin dakin yana yoyon ruwa. Watarana akan cika shi da mata kamar ashirin, wadanda sukan kashe yawancin lokacinsu suna kwalfe ruwa daga kan dabe.

Ko da shike wasu fursuna sukan shiga suna fit a daga wannan matattara na wucin gadi ji ana aika su zuwa wasu kurkuku, ko kuma kafin a sake su. Hukuma ta kyale Ling a ciki kuma ba kasafai take barin wannan karami kuma matsattsen wuriba. Ba a yarda ta kwanta ko kuma ta jingina a bango, amma ana tilasta mata ko ta mike a tsaye ko kuma ta zauna a zaune amma a mike babu jingina. Yawan sauro da kudaje yasa wannan kazamin wuri ya zama wuri mai ban tausayi.

A karshe, kwamandan yan sanda ya je kofar dakinta dauke da takardar cikewa a hannunsa. "Sa hannu a nan,: ya

umurta, Ling ta mika hannu tsakanin karafan kofa ta karbi takardar. "Menene wannan?" Ta tambaya. "ki sa hannu kawai" kwamanda ya kwala, yana mika mata takardar. "za a sake maki wuri". Gaban Ling ya fadi da take maza maza ta karanta takardar, sai ta gani ashe doka ce na a aika ta zuwa sansanin gwale gwale na jaddada gyara hali na tsawon shekara uku. China takan ba fursuna dama ta kwanaki goma sha biyar suyi kara ko suyi kokarin kare kansu bayan sun karbi irin wannan sanarwa, amma na Ling kam babu irin wannan damar. "Yau zaki tafi can" kwamanda ya gaya mata.

Kafin Ling ta ce a'a, ya rigaya yayi tafiyarsa dudugen takalmansa masu walkiya suna kara akan dabe har ya bace Shekaru uku.

Ya, Allah ka lura da majamiunka. Ling tayi addu'ar zuci a yayin da motar kurkuku tazo ta tafi da ita zuwa wani wuri wai shi Eighteen Mile River, inda sansanin gwale gwale yake. Tayi godiya da irin nasara da suka ci tare da abokan aikinta, amma kuma tana damuwa da abinda ke faruwa da su a yanzu. Daga cikin shugabanninsu guda goma na kungiyoyin addu'oi, akalla tana sane guda hudu na cikin kurkuku. Banda ita. Uncle Foone yana tsare a kurkukun yanki, kuma wasu shugabanni guda biyu an kaisu wani sansanin gwale gwale dabam.

Da saukarsu sai aka baiwa Ling kwaryar shinkafa da dan karamar akwati kunshe da yan abubuwan amfani na yau da kullum, sa'annan aka kaita a dakinta.

## MUHIMMANCIN YIN ADDU'A

## A CIKIN KURKUKU DAIDAI YAKE DA NA YIN NUMFASHI.

"Ling, barka da zuwa! Mun ji cewa kina tafe!" wata murya ta gaisheta a yayinda ake kulle kofar. Ashe akwai wadansu masu bi daga kungiyar ta da zaman daki zai hada su a sansanin. Jin gaisuwarsu mai fara'a, yasa tayi murmushi.

Da alamar suna nuna farincikin shigorwata kurkuku, amma ta sani suna murna ne kawai domin an turo ta zuwa cikin dakinsu. A yayinda suke rungumar juna suna gaisuwa tare da yin addu'a, Ling tana yin juyayin ko karin masu bi guda nawa za a kawo ciki zuwa gaba.

An bata gadon sama. A wannan dare na farko, Ling ta hau kan gadonta ta fara yin addu'a da murya. "ke!" daya daga cikin yan dakin tayi magana. "ba a yin haka anan idan suka kama ki, za a baki horo."

"Amma ai babu wani abu da ya hana Krista yin addu'a, zai zama kamar ma an hana mutum yin numfashi kenan," in ji Ling. "Ta haka dai abin yake" in ji daya matar. "kuma ba ma wannan kadai ba, ba a yarda da barin gashin kai yayi tsawo."

Ling ta shafa dogon bakin gashin kanta mai silki da yatsunta ta sani cewa yadda take dinnan, haka take, amma babu zaton yin tunanin yanke gashinta. A kullum ta saba barin gashinta da tsawo kamar na uwarta, tana ta tunanin yadda zata yi muni idan ta yanke gashinta da gajarta. Sai taji hawaye ya cika mata ido a lokacinda take rokon Allah ya sa abar mata gashinta, ta sani cewa wannan babu ma'ana kafin ma ta gama rokon. Ta dudduba cikin dakin, sai ta lura cewar dukanin matan na saye da gajeren gashin kai kuma dukan su munana.

Rayuwa a cikin sansani dabam yake dana kurkuku. Bayan tsarewa na tsawon makonni, Ling tayi murnar samun fitowa waje da rana. Kyaun abincin na da dan dama dama anan, amma tsawon watanni uku na gwada hali, takanyi aiki awa gomasha shida a rana suna sakar hular gashi ta mata. Aikin yin hular gashi ta mata mawuyacin aikine, sabo da haka ba abin mamaki bane mai aikata suyi amai karkashin tsananin aikin da aka dibar wa mutum na rana guda. Ya zamar wa Ling mawuyacin abu ta sami damar yin tunani akan wadansu al'amura dabam.

Rayuwa ya zama wani abu, ana maimaici tashi daga barci, cin abinci, aiki da yin barci sai kuma tashi daga baci, cin

abinci, da sake yin aiki. Wasu lokuta yan sansanin sukanyi aiki har dare idan aikin yayi yawa ko kuma idan ba a cika yawan aikin rana daya da aka dibar wa mutum ba. Ga Ling kam, kalu bale mafi girma shine samarda lokaci domin fuskantar Allah da addu'a yadda ta saba yi. Kuma bayan shekaru da dama na tafiye tafiye babu tsangwama ko ina a cikin kasar China, tana wa'aazi, koyaswa, da kulawa da mutane, wannan rayuwa da dukan dokokin kamar ma wani naushi ne.

## ALLAH YANA DA WANI NUFI DOMINMU ANAN

A kowace safiya yan sansani sukan sauko daga kan gado da karfe biyar na asuba da ake hura usur, daga nan suna da minti goma na gyaran gado kuma suje su shiga layi a filin gida, minti goma sha biyar na cin abinci, kuma dukan sauran rana ayi aiki a cikin masana'anta. Ana bin wannan shiri babu fasawa kwana bakwai a mako. Ga yawancinsu, harda Ling, rayuwa ya zama wani matsayi ne na gajiya tikis da kuma gundura. Ling na aiki gefe da gefe tare da karuwai, yan kwaya, barayi, masu satar mutane da sauransu da ake kira "sharar juji da jama'a suka zubar."

Dogon lokacin yin aiki ya cinye mata karfi, yanci yana mata wuya kari bisa kari, ta yi addu'a da dare domin tana kewar yin barci ainun.

Bayan yan makonni kuwa, Ling taji alamar dawowar yadda take a da ta mika al'amuranta ga Allah. Ta sake jin lallai ne ta yi zumuncin bangaskiyarta tareda sauran masu bi. "Manufar Allah na karshe a cikin kowane matsayi shine na mu koyi yin biyayya, haka? Tana gaya musu. "saboda haka na sani Allah yana da wani nufi dominmu anan.

A kewaye muke da masu laifi kuma masu mugun baki wadanda suke nuna kowane irin mugun hali, kuma na sani Allah yana so mu koyi yadda zamu kaunaci wadanda suke abokanmu da abokan aikinmu. Amma Allah yana so mu koyi yadda zamu kaunaci wadannan mutanen ma"

Ling tayi godiya domin dan yawan masu bi a cikin wannan babban sansani mai mutane da yawa. Duk lokacin da mai bi guda daya ta karaya, wata tananan domin karfafa ta, kuma ko da shike Ling ba ta ji dadin rashin samun damarsu ta taruwa suyi addu'a tare ba, ta sami wasu lokuta da wurare, inda zata iya yin addu'a domin mata su sami karfafuwa a lokacin da aka basu damar shiga ba-haya, ko kuma a lokacin da suka shiga layi na cin abincin rana, misali.

Kafin a tafi da nisa kuwa, kwarewar iya shugabanci na Ling yana fitowa fili a idanun ja mi'ai, sai suka sa ta zama shugaban yankinsu. Wannan karin girma ya baiwa Ling karin dama na yin wa'azi da ta dauki shugabancin mata hamsin na dakinta kuma tayi aiki a mukamin mai duba aiki na sakar hular gashi ta mata da ma'aikata guda dari biyu. Aikin cike yake da kalubale kuma fadace fadace a tsakanin matan fursunan wani lokaci yakan sa ta fusata, duk da haka, Ling tayi aikinta da aminci, a hankali kuwa da yawa a cikin mutanen suka fara jin dadin al'amuranta.

"Kina da kirki, ga iya shugabanci. Zaki iya gudanarda kyakkyawar sana'a a waje" Ling ta dauki duk wata dama da ta samu na shaidar dalilin da yasa take tsare, kuma sakamakon shaidar ta yasa dayawa suka zama masu bi acikin sirri. Koda shike ba su da Litattafai Masu Tsarki, Ling ta koya musu ayoyi da wakoki da ta haddace, kuma ta koya musu yin addu'a. Ta tuna da Littafi Mai Tsarki na dattijon dan'uwa da aka kwasa a hankali da rubutun hannu da kuma bada kai da tayi na haddace wurare masu yawa a cikin Littafi Mai Tsarki, Yanzu kuwa tana farin cikin yin haka a baya domin gashi taga ranar sa.

## "KO MUTUM KAMAR NI NA IYA BADA GASKIYA?"

Hukumar kurkuku sunci gaba da yin uwa da kyawawan ayyukan Ling kuma gashi mata da ke karkashin ta suka zama zakaru wajen aiwatarwa kuma anan aka sami karancin aukuwar fadace fadace da huma hadura fiye da sauran dukan yankuna.

Watarana wata shugabanta mai suna, Malama Tao ta tsayarda ita akan hanya a cikin masana'anta. "Ling, na ga fayil naki" in ji ta. "ina sane da irin ayyukanki kuma gaskiyar ita ce ke shugaba ce ta Krista mai kwarjini. Kuma yanzu da yake kina nan har tsawon watanni goma sha daya, na ga irin aikinki da irin halinki game da sauran fursunoni, musamman marasa ladabi masu fusata a kullum wadanda suke jawo gardama.

Akwai alamar kina nune kauna ga irin fursunonin nan, amma kuma ke baki nuna irin halayensu. Me yasa?

Ling ta ji dadi a yayin da take gayawa shugabanta, "ba na nuna irin halayensu domin ni Krista ce, kuma na bada dukan rayuwa ta ga Yesu Kristi. Shine dalili da nake a raye. Shine dalilina na kaunar dukan mutanen nan marasa abin kauna" Ling ta ja numfashi, tana jiran taji abinda malama Tao ta fadi. Furta kalmar addini kadai zai iya kara tsawon zamanta a kurkuku ko kuma a kulle ta a cikin "akwati" wani daki ne na daga kai sai kai. Bata sani ba ko wanan mai bincike tana kokarin shigar da ita ta sa mata tarko .

Amma abin mamaki ga Ling, shugabanta tace, "ko mutum irina na iya bada gaskiya ga Yesu?" Kwarai kuwa!" Ling ta amsa. "Amma ba kya tsoron rasa mukaminki?" ba kya tsoron gwamnati zasu kore ki daga aiki?

Baki ji tsoro cewa zan iya kara maki tsawon lokaci ba domin gaya mani shirme?" Malama Tao ta amsa. Muddin ina sane cewa zuwa na nan akwai manufa muddin ina sane cewa kinzo ga bada gaskiya ga Yesu A shirye nake na zauna anan har'abada" "Kina jin dadin zama anan?"

Sam, sam, in ji Ling. "amma domin Yesu yana kaunar ki shi yasa nake nan. Da raina da naki Allah ne ya bada su" Malama Tao ta dan yi magiya kadan, amma Ling ta amsa dukan tambayoyin ta kuma ta cigaba da gaya wa shugabanta game da kaunar Allah.

Malama Tao ta nuna sha'awa, amma rinjayar ta ba abu ne

mai sauki ba, kuma suka cigaba da irin wannan hirar tasu na tsawon watanni. A karshe watarana, sai ta gaya wa Ling. Ko da na bada gaskiya, a boye zanyi. Kin sani akwai Kristoci a unguwarmu, amma ban taba yi musu magana ba. Yana da wuya domin mukami na, kece Krista da na taba sani sosai a rayuwata".

Ling ta yi murmushi tana addu'a domin Malama Tao a zuci. Taci gaba da aiki tana bauta wa Allah a sansani iya kokarinta har zuwa shekaru biyu gaba, amma lafiyar jiki ya fara tabarbarewa da aiki tukuru zuwa rashin abinci mai kyau. Wasu ranaku takanji kamar ba zata kai ba. Daganan wata rana cikin watan Disamba Malama Tao ta kira Ling zuwa cikin ofis. Tana zaune a bayan teburin ta da fuska a tsare, tana rike da wata takarda.

"Menene?" in ji Ling "An bayarda takardar karin lokaci dominki, kuma da bukatar a sa hannu, " inji Malama Tao. Ling ta girgiza. Tayi ta tunanin abinda zai kawo karin lokaci amma babu, ko da shike wani yana iya yin karya ga hukuma. Malama Tao da Ling sun zama abokai,kuma sun cigaba da magana game da Kristi. Watakila wani ya jisu suna magana ne ya kai kara.

Tunaninta ya yawaita. Tana kokarin kawo abin kusa, sai taji Malama Tao tana karanta takardar, cewa an kara shekara guda" Gaban Ling ya fadi. Daganan sai Malama Tao ta dube ta, tana mamakin bakin cikin da Ling ta shiga yi. "Ling kin saurare ni?" Malama Tao ta fada da karfi. "sun lissaftaki a cikin wadanda aka farfado dasu sosai kuma an rage maki kurkuku na tsawon shekara guda daya."

Ling ta kasa yin magana. "lallai, ni zan fadi cewa wannan shine lokaci na farko da na taba ganin kin rasa abin fadi." Malama Tao na murmushi yenzu. "barkanki Ling; za a sallameki kasa da mako uku".

## WANI NISAN DUNIYA A TSAKANI

Bayan mako uku, Ling tana jira bayan ta fice daga sansani kafafu anutse cikin dusar kankare har zuwa idanun kafa ga sanyi na sharbar ramammen jikinta, tana jiran Uncle Foone. Farfadaddiya tayi murmushi. Don dai kawai ba a kamata tana koyarwa ko yin bishara ba ga kursuna. Kuma yana nufin, fatarta kenen cewa zasu kyale ta na wani lokaci.

Ling na dakon komawa aikinta na bishara da karfafa mambobin majami'a, amma kuma ta sani karfin jikinta ba kamar na da bane. Akwai al'amura da dama na batun kurkuku da yake da wuya a kau dasu cikin gaggawa. Ya Ubangiji, ka taimake ni na sake sabawa da rayuwa ta waje da kurkuku, kuma ka cigaba da kasancewa da yan'uwa da ke cikin kurkuku. Ling taji dadin sake saduwa lokacin da Foone da Shen suka ja birki a gabanta da karamar motar su. Domin batun zai kawo su ga mawuyacin al'amari idan ko wannensu ya ganta a cikin kurkuku, shi ya sa ba ta samun ziyara ainun a cikin shekaru biyu da tayi.

Yanzu kuma zata sami labarin wasu daga cikin shugabannin sunyi aure, wasu manbobi kuma sun haifu, kuma akwai sababbin kungiyoyi.

Shigar ta motar ke da yuwa, sai Ling ta fara jin amai. Ga wani abu da na dade banyi ba, tana tunani, shiga mota. Tafiyannan na tsawon awa hudu baiyi wa Ling dadi ba, ta kudundune a kujerar baya tana jin hararwa, ga kuma jin samun yanci.

Kamar dai yadda aka zata Ling ta sami wuyar dawo da hankalinta ga rayuwar waje da kurkuku. Kurkuku wata duniya ce dabam, Lokacinda take sansani, jami'ai basa bari a kashe fitila.

Ma'aikata kullum a cike, kuma har dakunan su kullum da fitilu. Shugabancin majami'a ya kafu sarai ba tare da ita ba, wanda ma ya kara kawo wata wuyar yadda zata dawo aikinta na shugabanci, musamman da yake ita mace ce.

Tana nuna bakinciki domin ma kamar babu wuri dominta yanzu a tsakanin shugabannin majami'ar, amma kuma tasani cewa tana da bukatar hutawa, kuma ta daina daukar aiki mai nauyi a yayinda take murmurewa. Saboda haka kila shine mafi alheri.

## AN KAMA KOWANE DAYANSU

Ling ta zauna a gidan daya daga cikin shugabanninsu na Krista tare da iyalinsa. Suna zaune a wani gida babba a cikin tsakiyar kasar China, kuma aka baiwa Ling daki a hawan bene na biyu. An yi shirin yin taro na shugabanni a cikin sirri a wannan gida daga goma sha tara ga watan Agusta har zuwa ranar ashirin da uku. Ling tayi shirin halarta, amma maimako sai aka bata wani aiki na musamman zuwa yammacin China a cikin wannan mako da ake yin taron. Ita ta na tsammanin shugabannin na kawad da ita ne daga hadari, amma ba ta iya tabbatar da haka ba. Fiye da shugabanni guda talatin aka sa rai zasu halarci taron, kuma wannan zai zama wata dama na saduwa da tsofaffin idon sani kuma ta sabunta sa kai ga batun shugabanci. Amma haka bai yiwu ba.

Ta kammala aikin da tayi a yammacin China a ranar 23 ga Agusta, daga inda ta sami sakon gaggawa, "Ling! Ki dawo maza maza," aka gaya mata "An kama dukan shugabanin kowane dayansu. Ke kadai aka bari!"

Ling ta iso gida washe gari kuma ta tarasda maşubi a rude. Wasu daga cikin matan shugabannin majami'a suka nuna fusatar su ga Ling, suna tunanin ko tana da hannu a ciki. Fitowar ta daga kurkuku da kadan ya dara wata shida, kuma abokai sun gaya mata cewa ita ma yan sanda na nemanta.

Nan da nan Ling ta shiga aiki. Na farko ta kira dukan masu bi na yankin, kuma ta sa kowace kungiya aikin bin sawun daya ko biyu daga cikin shugabanni da aka kama. Aikinsu shine su debi tufafi, abinci, da kudi su kai caji afis inda aka tsare shugabannin.

Wannan kuma ya shafi majamia ainun cikin dukan kasar China domin pastocin sune ainihin shugabannin Krista a bangarorinsu. Labarin kamasu ya bazu da sauri zuwa kasashen waje ta wajen aika sako ta na'ura mai kwakwalwa, kuma abin ya bazu da sauri ko ina cikin china ta rediyon Muryar Amirka. Ling tayi kokarin sarrafa labaru a yayinda mutane daga ko ina a cikin China da kuma duniya suka fara kira suna neman karin bayani. Jim kadan kuwa matan pastocin nan suka fara isowa, Ling kuwa ta sauki kowa tana amsa masu tambayoyinsu da dukan iya kokarinta.

Bayan makonni biyar an saki shugabanni guda shida ne suka rage, amma fa sai da aka biya tara mai tsada (har yen dubu goma kowane daya), wande kuma Ling ce tayi gwagwarmayar samo kudin. Masu bi matalauta ne, samarda wannan kudi domin fito da yan'uwa masu bi yana da wuya. Amma ita Ling bata yi kasa a gwiwa ba. Darajar yan uwanta dake tsare yafi kowane irin yawan kudi tamani a gareta, kuma sai taci gaba da roko har sai da ta tara isasshen kudi.

Ling tana jin gajiya sai ji take kamar zata zube don tsananin nauyi da ke kanta, amma bata iya hutawa ba sai da ta hada komai na pastoci guda shida, mafiya kwarjini a cikin kungiyarsu wandanda kuma sune sukafi tsadar farashi agurin yansanda. Yanzu a tsorace take cewa kila a kashe su.

Abu guda daya kadai ya rage da za ta yi. Ling ta kira wannan caji ofis. "Ling so nake nayi magana da kwamishina" "wanene wannan?" akawun caji ofis ya tambaya" "Sunana Ling, kwamishin yasan kowacece ni; yana nema na"

Ling, tsofuwar kawata! Ina mamakin ji daga gareki", wannan muryar tasa dai da aka sani mai sassauci ta fito a cikin tarho. Daga ina kike kira?" "Kada ka damu, ina so in yi magana da kai game da abokaina da kake rike da su a cikin kurkuku".

"Me zai hana kizo caji ofis kawai muyi magana" "A'a zan yarda dai mu gamu dakai a Bright Moon Hotel. Kuma lallai ne

kazo kai kadai. Zan zuba ido, kuma idan wani ya biyo ka, to bazan nuna kaina ba".

Ling ta san zai yarda. Idan ma ba wani abu dokinsa zai kawo shi. Ta yaya mai wa'azi da ta gagare shi na tsawon watanni da dama za ta gayyace shi akan su hadu? "Na ji, Yaushe kike so mu hadu? "Yau da dare karfe bakwai," in ji ta, bayan ta sauke waya, Ling ta sadu da wani dan'uwa da ta amince wa. Tayi masa bayanin matsalarda ke kasa, ta tambaya idan zai iya raka ta zuwa hotel din ya jira a waje. Idan ban fito ba, to kasani cewa an kama ni".

Da karfe 6:50 na yamma da Ling da dan'uwa suka tsaya kusa da hotel, suna zuba ido suna jira amma suna boye. Suka ga kwamishina yana tafe tare da wasu hafsoshi. Gaban Ling ya fadi, tana shirin tafiyarta sai ta lura kwamishina kadai ne ya shiga cikin hotel, sa'anda hafsoshin ke jira a kofa. Ta bi ta baya ta shiga ciki ta taras da kwamishina a dakin cin abinci.

Ling nayi murna da ganinki"; in ji shi, sai kace dama abokai ne na gaske a da. Amma bakijin tsoron na kamaki?" idan da ina jin tsoro bazan zo ba. Amma gani."

Suka bada odar abinci, kuma Ling tace ita ce zata biya. Daganan sai ta shiga batun da ya kawo su. Me kakeyi da abokaina? Ka saki wasu ka yanke musu tara, idan kudi kakeso, zan baka kudi. Nawa kake so?

"Yi a hankali, Ling!" in ji kwamishina." Bamu ma ci abincin ba tukuna. Bayan haka babu abinda zan iya yi dominsu, kuma wannan laifinki ne. ke ce ke maida wannan al'amari ya fito bainar jama'a"

Ling ta sani so yake ya bata laifi, ita kuwa taki janyewa. Amma ashirye take tayi amfani da wasu dabaru dabam. Sun tattauna har na tsawon awonni biyu, kuma Ling takan shigarda kalmomi game da bangaskiyarta; tayi bayanin dalilin da ita da pastocin da ke tsare suke da sha'awar shaida labarin Yesu Kristi. Kwamishina ya saurara sosai, yana ganin damuwa a cikin idanun Ling game da abokanta, amma ba zai

yiwu ba. Yaki ya bata wani sa rai akan cewa za a sake su.

Ling ta sa hannu ta gyara gashinta, sun fara yin tsawo. Ta tuna da addu'ar uwarta na zama hadaya, saita ambaci ayan nan da ya kawo ta har nan: girbi yana da yawa..... amma ma'aikata kadan ne.... tumaki a tsakiyar kerketai." Ling tayi tunani ko lokaci yayi na komawa makarantar shan wahala.

## KOMAWA MAKARANTA

Da kwamishina ya gama cin abincinsa, Ling ta sani lokaci na kure mata, tana sane da hafsoshin nan da ke jira a waje a bakin kofar hotel, sai tayi badakai na karshe. To kasa a nemo ni, to gani. Rike ni ka bar abokaina su tafi".

Kwamishina ya kada kansa yayi murmushi. "Ling, ya fada da gaske babu shakka kina daya daga cikin mata na musamman da ban taba gani ba".

Sa'anan, ba tare da kara yin wata magana ba ya fice daga dakin cin abincin. Ling ta zauna shiru na wani lokaci, tanajin cewa ba ta ci nasara ba. Da nauyin zuciya kuwa ta dawo gida tasan abin ba zaiyi wa abokan aikinta kyau ba abokanta da ke tsare.

Can bada jimawa ba kuwa, Ling ta sami labari cewa an sake kama karin Kristoci guda biyu, kuma an kai shugabanni da ke tsare zuwa gaban hukuma ta tsakiya daga inda ake ajiye da su a hukumomin yankunansu, inda ake azabtar dasu ainun. Horon da hukumci ya yanke musu, ya kama daga watanni goma sha biyu zuwa ashirin da hudu tare da tsananin aiki.

Ling ta cigaba da aikinta, tare da jin kadaici kwarai. Har yanzu ma dai lafiya bai ishe ta ba sosai daga fama a kurkuku na baya, kuma ganin lafiya bata ishe ta sosai ba, da dama daga wasu shugabanni sun shawarce ta da ta dan saurara wa jikinta. Amma taki,, tana tuna yadda uwarta takan karfafa ta da kuma yadda uwarta ke nika waken soya domin Ling ta

iya cingaba da aikin bishara. Tana kewar ganin uwarta. Anyi shekaru ba ta ga uwarta ba. Amma a yanzu kam zuwa ganinta yana da hadari kwarai.

Ling ta ci gaba da zama mace guda daya tilo a tsakanin shugabannin, kuma watarana takan sami kanta tana kuka ita kadai a daki, tana rokon Allah ya bata karfin kammala aikin ta. Ranar 16/4/2002 wayar tarho na ling ya sake yin kararrawa. Masu tsattsaurar akida ta al'adu" China sun sace Kristoci guda talatin daga cikin kungiyarta. Ling ta kira "abokinta" a caji ofis. An komaiki aiki...

## JAWABI

Ling taci gaba da rayuwa a cikin mawuyacin hali, amma ladan ayyukanta ba a baya suke ba. Ta wurin shirin gamuwarta da kwamishinan yan sanda, Allah ya bude mata kofa domin tayi magana a madadin irin rashin adalci da ake fama, kuma tuntubar juna da tayi da hukuma shima ya kawo karin magiya, har kristoci da yawa sun nuna kin abinda take yi. Wajen basu amsa, Ling tace, "Muna iya zama Ktista, amma ai har yanzu mu mutanen China ne, kuma ai har yanzu wannan kasarmu ce".

Ling bata taba yarda ta sauya ra'ayinta ba, ko kuma ta ja da baya game da aikin ta na bishara. Haka kuma bata taba bari tsoro ko kasadar zuwa kurku ku ya hana ta daukar duk wata dama na tsayawa a fili domin yan'uwanta maza da mata ba.

Har yanzu tana cikin jerin sunaye da gwamnati ta tsara na wandanda ake zuba wa idanu, amma kuma sunanta na cikin jerin sunaye da Allah ke zubawa idanu, kuma ya kara sa ta ahanya mai ban al'ajibi kuma ya kebe ta daga komawa cikin kurkuku.

Amma Ling a shirye take ta koma idan har hakan ya zama dole. "A shirye nake na koma makaranta", in ji ta. "Na sani idan Allah ya kirga gashin kaina, zai yi amfani da ni a yadda

yakeso, kuma zan cigaba da dogara ga nufinsa.

Wani kalubale da yazo wa Ling shine sa kai da tayi na cingaba da zama babu aure har saida shugabancin majami'a ya kafu sosai.

Kungiyar ta yi harsashe zai dauki shekara goma, kuma Ling tana jin akwai lokaci da yawa na yin aure bayan nan. (ita yar kasa da shekaru 19 ne a lokacin) amma fa a kasar China mawuyacin abu ne a sami mata mara miji da ta wuce shekaru talatin wanda shine shekarun Ling a yanzu.

An sha gaya mata akai akai (harda pastocin gidajen majami'u da ta taimaka ga kafawa) cewa mukamin mace a gidanta na aure yake tare da kula da yara. Ling bata musun wannan batu, amma kuma ta sani wani lokaci Allah yana da shirinsa dabam dabam daga irin shirin da ake tsammani, tana tunatar da masu sukar ta cewa, a lokacin farkon tasowar kungiyoyin gidajen majami'a, mata ne suka dauki ayyuka da suka fi hadari na yin bishara. Kuma ta nuna cewa, kamar yadda shugabannin China suke sane, biyu bisa uku na rukunin masu yin bishara da ke aiki a cikin karkarorin China mata ne.

Yanzu Ling tana da hange domin guje guje da tsalle tsalle na kasa da kasa, wanda yake tafe zuwa Beijing a 2008. ta gaskanta wannan zai zama wata dama mara misaltuwa domin habakar gidajen majami'u

An koma aiki.........

# Gladys:

## Madogaro Domin Gafartawa

*India:*
*Nuwamba 1981*

An tashi a cikin dumi dumin yanayi mai laima a ranar da Gladys Weatherhead ta sauka a yankin Mayurbhanj, misalign nisan mil 110 kudu maso yamma da Calcutta a cikin yankin kasar Orissa, wanda keda iyaka da Bay of Bengal. Yanzu ji nake da gaske na iso nan, tana tunani, a yayinda hankalinta ke la'akkari da dukan abin da take gani da abinda take ji. Kamshi mai karfi na kimba da yake fitowa ta tagogin gidaje da shaguna hade da wari da ke tashi daga juji, budaddun kwatami, da shanuda ba a tabawa dasuke yawo barkatai akan tituna. Zafin ya sha kan warin, amma Gladys tana murnar dawowa cikin yanayi mai dumi dumi bayan shan iska mai sanyi a arewaci.

Tahowa daga iyaka da Pakistan ya zama wani darasi na bangaskiya ga Gladys da yadda direbanta yake kurde kurde tsakanin motoci, yana kaucewa manyan motoci, amalanke, taxi, shanu, basukur, da shirgin yawan jama'a ko ina a kan titi a hargitse kuma cike da hargagi. Da yake ta girma a kasar Australia a cikin karkara inda babu hayaniya, Gladys tana mamaki cewa irin wannan hargagi karbabben batu ne na rayuwar yau da kullum a India.

Takan gani ta tagar dakinta na hotel idan ta duba kasa yadda ake kaiwa ana kawowa yana bata damuwa da juyayi duk lokacin da taga wata uwa ta hau kan titi da kananan yara sai ta shiga yin addu'a, idan taga mata suna hawan babur, suna rike da kayansu maimakon rike mai tuka babur. Wataran sukan zo kusa kamar zasu gogi jikin motocin safa ko na kaya a kan cusasshen titi.

Yawan mutanen India yana wajen biliyan daya, kuma Gladys na mamakin tsananin yawan mutane ko ina kaje, ko ina ka duba duk mutanene kawai. Tana al'ajibin irin mutanen da ke kewaye da ita akan titi gasu iri iri: yara babu ko takalma a sawayensu da fuskoki masu dauda, iyaye mata da adonsu na sari launi dabam dabam a cikin tsarin al'adarsu ta Hindu na digon lamba a goshinsu, tsofaffi da fatar jikinsu yayi kama da wata jemammiyar fata da aka yi wa paci, ko wane dayansu kuwa halittar Allah ne.

Gladys tana kaunar wannan darasi da take dauka. Bayan shekaru goma sha biyu na bata shawarar ta hakura, gashi a karshe mafarkinta ya zama zahiri kuma tana saurarawa kiran Allah ga rayuwarta na yin hidima ga talakawa a kasashen waje. Takanyi juyayi akan ko wannan rana zata taba zuwa.

## KIRA ZUWA GA RAYUWA NA YIN HIDIMA

Gladys tana yar shekara 18 kacal a lokacinda ta halarci wani taron mishan na Krista a kasarsu ta Australia kuma ta amsa kiran Allah zuwa aikin mishan. Ta girma ne a gidan gona a Queens land.

Gladys tasha sauraren wa'azi da yawa a cikin majami'a, kuma tasha saduwa da masu aikin mishan da dama da iyayenta sukan gayyata zuwa gidansu. A kowane asabar da rana uwar Gladys takan tara yara a kewaye da ita ta karanta musu labarun masu aikin misha a Afirka, India, China....labarun suna baiwa Gladys sha'awa na rayuwa a wurare masu nisa, kuma sha'awar irin sakai da suke dashi.

Babu shakka a cikin zuciyarta cewa Allah yana jawo ta zuwa rayuwa ta yin hidima a bakuwar kasa; tana sane da haka a yayinda wani abu a zuciyarta ya ji dabam. Ta fara fahimtar dalilin da masu aikin mishan suke da tsananin son sakai ga aikinsu.

Dukan lokacin da take cikin shekarunta na ashirin, Gladys tana tsiyayar dukan tunaninta ta wajen sa kai ga zama mai aikin zama mishan watarana. Ta kammala karatun ta na koyon aikin malamar asibiti, zabi na zahiri ga maison yin aikin mishan a kasashen waje, kuma tayi iya kokarinta na kaucewa yin saurayi idan bashi da irin niyyarda ita take dashi. Wannan kam akwai wuya, amma Gladys ta sani Allah bazai so ita ta zama da wani ba idan har zai sa ta kaucewa manufarta. Ta kware a sana'arta har tayi shugabanci a wani karamin asibiti. Kuma ta koyar a Sunday school tana kuma ba da taimako duk lokacinda ya samu.

Gladys takan yi farinciki musamman duk lokacinda Krista masu aikin sakai suka ziyarci karamin taronsu; takan rike dukan kalamu na mai ziyara kuma tana fata watarana ita ma zata sami yin haka. Takanyi tunanin wai shin zai yiwu anemi ita tayi wa jama'a magana; wannan sashe na aikin mishan babu doki cikinsa abin da tsoro. Ba domin Gladys mai jin kunya ce kwarai ba, amma domin bata jin Allah yayi mata baiwa a wannan sashe. Zan gansu da nuna kaunar Allah a aikace, da kwarewa ta ta aikin asibiti, tana gayawa kanta.

A shekarar 1980, Gladys ta kai shekara 29 kuma sai ta fara jin anya zan taba tabbatar da wannan mafarki nawa. Acikin birnin zuciyarta, tana da karfin zuciya cewa Allah yana jagoranci kuma komai kan faru bisa ga nasa lokaci.

Amma lamirin ta cike yake da tambayoyi kuma ta yaki tunanin zuci na ta kauce taje ta yi aure. Ba wani kara zama yarinya takeyi ba, kuma acikin shaidarsu, yawancin mutanen sukan nuna yadda Allah ya kaisu filin aiki a cikin kurunciyarsu, wadansu ma kafin sukai 20.

A yanzu kuwa sa'annin Gladys da dama sunyi aure kuma suna da ya ya; sha'awar ganin yaransu na girma a cikin iyali ya sa abin yayi wa Gladys wuya ta makalewa mafarkinta na yin hidima ga matalauta a wata kasa.

Daga baya a wannan shekarar Gladys ta gamu da Mike Hey, ma'aikaci na kungiyar da ake kira: Operation Mobilisation. Yayi aiki a India na wasu shekaru, nan da nan kuwa tayi sha'awar kokarinsa. Domin irin dokinta tayi ta yi masa tambayoyi game da aikin OM a India. Yaya mutanen suke? Ana iya isa garesu a fili? Yaya suke karbar mutane? Yaya OM ke gudanar da ayyukanta? Ina kuke samun taimako?"

Mike yayi murmushi; yana ganin irin doki da take dashi kuma ya bata amsoshin tambayoyin ta duka.

Watakila wannan shine, Glays na tunani watakila wannan shine amsar da nake ta jira dukan wadannan shekaru!

Cikin yan makonni na gaba kuwa Gladys ta binciki dukan takardar da ke bayani game da Operation Mobilsation. Ta sami sanin cewa bada kai na shekaru biyu ake bukata, kuma kowane mutum ya nemi nufin Allah game da kasar da yake so yayi aikin.

Da taci gaba da fahimtar yadda Operation Mobilization take da kuma zurfin matsayin ba da kai na ma'aikatanta da shugabancin ta, sai ta ga lallai wannan ita ce kungiyar da ta dace da ita. Taji salama a birnin ranta kuma tashiga aiwatarda wani shiri tsakanin ta da Operation Mobilisation.

Wajen Mayu 1981, Gladys tayi shirin barin Australia sau na farko a rayuwarta. Bata san inda zata yi aikinta na shekaru biyu ba tukuna, amma ta tashi ne domin yin nazari a Turai domin samun horon fara aiki. Zuciyarta na cike da doki a yayin da take sallama da iyali da abokai. Shawarar yin aiki a India shine ya shiga zuciyarta a yayinda ta tuna da hirar su da Mike Hey, amma kuma ashirye take zabin yazo daga Allah. A daren tashinta, iyali suka kewaye ta suka yi wakar daya daga

cikin wakoki da take sha'awa, "Domin yana sona zan iya fuskantar gobe" Gladys ta kara bayan an gama wakar, "Domin asani shi ke rike da gobe na."

Wannan ziyara ta Turai ya zama wani darasi na koyarwa a zahiri ga Gladys, kuma ta rike komai da amintaccen sa kai da yakai ta can. Kwanciye akan dabe mai sanyi, yi wanka sau daya a mako, wanke ba - haya a dakunan kwana, yin bishara ga mutanen Asia a cikin Ingila, da kuma neman alkibla daga Allah game da wurin zuwa bayan karbar horo domin tafiya aiki a kasashen waje. Gladys ta fuskanci dukan al'amuran da hali na niyyar gaske a yayin da taci gaba da mafarkinta na tafiya India.

Bata san abubuwa kwarai ba game da kasar ko mutanen ta, amma doki da son yi da yake karuwa a cikinta baya barinta. Kusa da karshen taron, Gladys na cin abinci da wani iyali wanda ke gudanar da aikin wannan mishan a Ingila, sun tambaye ta inda take so taje tayi shekarunta biyu na aiki.

Gladys ta yi bayani cewa ta rubutawa Operation Mobilization da kuma kungiyarsu ta India. "A yanzu haka bazan iya tabbatarda ina na nufa ba." "so dai kawai nake na tafi inda Allah zai fi morata".

"Gladys, ke mai shekaru ce", matar ta fada a hankali. Gladys ta fusata da wannan kira cewa ita mai shekaru ce" mai yiwuwa tafara aikin a makare, amma ai shekarunta 30 ne kawai. Ganin damuwa a fuskarta, sai matar tayi murmushi ta kara yin bayani. "A'a, ke ba tsohuwa bace. Ina nufin kinfi saura shekaru, kuma kinfi kwarewa a cikin mambobin ma'aikatan Operation Mobilisation. Kinfi samun koyarwar Littafi Mai Tsarki da koyarwar shugabanci da kuma abubuwan rayuwa. India na bukatar mutane irinki.

Gladys tayi murmushi kuma tayi wa Allah godiya domin kalamun wannan mata mai cike da hikima da karfafawa. Mike Hey ma irin wannan shawara ya bata, yanzu kuma tanajin tabbacin abinda takeyin addu'a domin sa. Kalmomin

wakannan da ya shiga mata a rai ya zo mata. "Na sani shike rike da gobe na, kuma rayuwata ta dace ne kawai domin yana da rai".

## GIDAN KUTARE

Tana kan hanyarta na zuwa tasharta ta farko ta aikin Operation Mobilisation a Cuttack, India, sai direban ta ya tambaya ko zai iya tsayawa na karamin lokaci a hanya. Dayake tsananin yawan mutane, maza da mata ko ina ya dauke mata hankali, ashe ma ba ta saurari direban ba sai da taji yace, ......a Gidan kutare na Mayurbhanj. Ina fata baki damu ba, Gladys? Ba zamu jima ba".

A can gidan kutare, direbanta ya sadu da wani dogo, kyakkyawa dan Australia mai aikin taimako sunansa Graham Staines. Gladys ta sami labarin akwai yan Australia suna aiki a wannan yankin, amma ba ta gane da sunayen ba. Graham ya raka Gladys zuwa cikin gidan mishan din, inda ta jira ita kadai, a yayinda mutanen biyu ke tattauna batunsu.

Tana duddubawa kewaye da ita a cikin wani dan littafi game da ma'aikaciyar farko, Kate Allenby. Gladys tayi sha'awar tarihin wannan gida. Wannan daki mai shekaru saba'in yana da alamar salama Gladys ta fada. Kowane bangare na wannan gini baya nuna shekarunsa, daga daben zuwa bango mai kaurin inci 18 da aka shafeda pentin farar kasa har zuwa dakali mai rumfa da ke tare zafi.

A yayin da take jira, Gladys ta yi mamaki da matar Graham bata fito tayi mata tayin shayi ba, kamar yadda taji cewa al'adar India kenan. Amma babu matarda ta fito, jim kadan kuwa direba da Gladys suka ci gaba da tafiya zuwa Cuttacks.

Rayuwa tare da kungiyar Operation Mobilisation yana cike da aiki tukuru, kuma da ban mamaki a yayin da Gladys ke kokarin koyon al'adunsu na cudanya tare. Tayi makonnin ta shida na farko a Cuttack tare da yan kasa masu aikin agaji.

Matannan guda shida suna zaune ne a cikin dakune biyu cike da akwatunan takardu a ko ina, abincin da yake kullum launin rawaya, ruwanda kullum a bokiti yake zuwa, da kuma ba- haya da yake ramine mai daben siminti a baki. Gladys ta gode Allah cewa a gona ta girma, kuma tasan darajan yin aiki tukuru, amma wasu lokuta takan ji kasala a yayinda take yakin dagewa domin rike abinda Allah ya nufe ta dayi.

A kullum sukan fita biyu biyu domin sayar da litattafan Krista suna bi kofa kofa suna yiwa mutane maganar Ubangiji. Gladys mai sha'awar ziyartar mutanen cikin birni ne, amma zuciyarta na son fita zuwa kauyukan Santhal da suka kewaye duwatsun arewa da kuma yamma da Baripada. Sun wuce ta wadansu daga cikin kauyukan nan a tafiyar ta ta farko na ratsa karkarar. Mikakkun bangon gine gine da aka yi da yumbu da kuma jinka ta ciyawa da suke kusa da gefen hanya kuma suna kewaye da itatuwa. Akwai tabki da aka haka da hannu daura da bukkokin.

An gaya mata game da al'adun Santhal da bautarsu ta rohanai, yadda har mutane ma ana yin hadaya da su wasu lokuta domin dadadawa rohanansu. Irin halin rayuwarsu na duhun kaine,kuma kananan yara suna mutuwa ainun daga rashin lafiyar da ana iya warkar wa da kuma kare yara da alluran zamani, iyalin mutanen Santhal sukan kashe kudin su wajen sayen itacen turaren wuta a kona da kuma dabbobi nayin hadaya a kokarinsu na banza wai suna kwantar wa da rohanai rai domin a ceci ya'yansu.

A zamanta na malamar asibiti, Gladys ta sani ana iya taimakawa wadannan mutane da wani dan ilimin sanin abubuwa, kuma a zaman Krista, ta sani Yesu zai basu warkaswa mafi daraja, da yantar da su daga bautarsu ga allolinsu na rohanai. Wani abu mai karfi ya cabke ta a rai a lokacinda take tunanin abin da suke ciki, sai tayi fatar fita ta shiga cikin kauyawan ta kai musu labari mai kyau dake cinta a zuci.

Janairu 1982 Gladys ta sami nata damar. Aikinta na biye ya shafi ziyartar kauyuka da dama inda masu aikin mishan suke gudanarda "sansani cikin jeji" tare da Kristocin yankin wurin. Daya daga cikin kauyuka da suka ziyarta na tazarar mil bakwai a tafiyar kafa takan duwatsu, amma zuciyar Gladys na farincikin kaiwa can. Tayi dukan al'amura da murna ta hanyar yadda suke abubuwansu, tana jan ruwa daga ckin rijiya, yin wanka a cikin kogi, da kwana cikin kudin cizo. Matan yankin suna jin dadin kasancewa tare da wannan doguwa, mai farar fata yar Australia kuma malamar asibiti, kuma da doki suka koya wa Gladys hanyoyin rayuwarsu mai sauki.

## KAUNA DOMIN KASKANTATTU NA KASA DUKA

Wannan kauye bashi da nisa daga gidan kutare na Mayurbhanj, kuma Gladys ta sami dama ta rinka ganin Graham, wanda ta sami labari cewa bai taba yin aure ba. Yawancin gamuwarsu yana shafar batun aikin mishan ne, amma Gladys tana jin karuwar sha'awar da take yi wa Graham, ko da shike takanyi kokari ta kawar da abinda takeji din domin ta fuskanci aikin da ke gabanta.

Daga nan aka aike ta zuwa aikinta na gaba. Gladys tayi godiya domin wannan dama na ganin kasar India a yayin da take tafiya daga wuri zuwa wuri tare da kungiyar Operation Mobilisation, amma ganin gidan kutare da kuma zama tare da mutanan Santhal ya bar gurbi a zuciyarta. ganin yadda Graham da sauran suke kula da marasa lafiyansu masu fama da cutar kuturta, kuma wadanda aka ware daga jama'a abin da tabin rai. Addinin Hinduyanci yana sanar da talikai masu ciwon kuturta su gaskanta cewa zunubi daga rayuwa da ya wuce shi yasa suke dauke da ciwon kuturta. An gaya musu cewa su basu dace ma a basu ko ruwansha moda guda daya ba. Sakamakon haka su da suka kamu da ciwon kuturta sukan yi rayuwarsu a cikin mummunan matsayi, suna

bara a titi kuma gashi an haramtasu ha rabada daga gidajensu da iyalansu.

Babu kaskantattu kasa da wadanda ciwon kurturta ta kama su, kuma babu wanda ya taba nuna musu kauna kamar yadda Graham yake yi.

Masu fama da ciwon kuturta da suka shigo gidan, ana basu magani na tsaida cutar daga kara yin barna, kuma ma'aikata na nuna musu kauna da tausayawa, wadanda kuma ke koya musu su sani ciwo ne mai warkewa kuma su kara sani ba la'anta ne daga Allah ba.

Gladys tayi mamakin ganin irin rikida da ta gani a fuskar marasa lafiya da yawa na nuna tausayi da ga dan'adam da kuma basu damar jin kalmominda suka jibinci kauna. Magunguna sun yi aikinsu na warkar da mikinsu, amma tausayi da ma'aikata suke nuna musu shi ya warkar da ruhunsu.

Aikin da ake yi a wannan gida ya daburce Gladys, amma wasu lokuta takan tambayi kanta menene muradinta. Graham ne ke jan hankalinta, ko kuwa aikin mishan na gidan? Kodashike tana kara cingaba da jin sonsa; ta sani cewa ba shine dalilin zuwanta India ba. Bayan haka, ba ta da wata hanyar iya sanin ko shima yana da jin sonta. Idan kuwa hakane yaya kenan? Ta yi murmushi. Idan hakane ma aisai yayi magana da shugabannin Operation Mobilisation game da haka kafin ma wata dangantaka ta fara. Haka dokar take.

Da farkon bazara kuwa, Gladys ba ta da sauran wata bukatar yin mamaki gameda anniyar Graham. Ta sami labari Graham ya nemi iznin shugabannin Operation Mobilisation domin su fara tuntubar juna, kuma taji dadi! A tsakanin bazarar zuwa lokacin hunturu kuwa suka sami karin sanin juna da yake wasiku na shiga tsakani. Sunyi mamakin sanin cewa wasu abubuwansu makamanta ne. sun yi girma a wuraren da tsakaninsu da juna mil 40 ne kawai kuma sun tashi a wurare makamanta, kuma duka biyu sun sami kira

zuwa aikin mishan tun suna kanana. A kowane karin wasiku, suna kara fahimta cewa ko shakka babu Allah ne ya hada su. An daura musu aure a Australia a Agusta 1983 a gaban iyali da abokai masu farin ciki.

A can gidan kutare kuwa, kowa na yiwa Graham da amaryarsa farinciki. Mutanen kewayen suna kiransa "Dada" domin sonsa da sukeyi. Dada" yayi aiki da aminci babu gajiyawa a Mayurbhanj na kusan shekaru ashirin, yanzu kuma Allah ya albarkake shi da matar kirki mai kaunar Allah da kuma irin nashi hazakar na tausayawa mutanen India. Ga mazauna kauyen da marasa lafiya da ke cikin gidan, auren Graham da Gladys shaidace ta ban mamakin kaunar Allah, kuma sukayi ta jira da doki na isowar maigida da uwargida Stains daga Australia.

Amma ba abu ne mai sauki ba. Da Gladys da Graham zasu fuskanci jarrabawar su ta farko na zaman aure a lokacinda gwamnatin India suka ki su baiwa Gladys sabuwar visa. Da alamar ma ba a iya gane dalili, amma jami'an kawai ki sukayi a barta ta koma. A karshe suka yanke shawara Graham zai koma shi kadai yayi kokarin neman visa daga can India.

Wannan ya dauki watanni da dama da addu'a kafin gwamnati ta yarda akan Gladys ta sami visa, amma duk da haka sun bata visa ne kawai akan ita matar Graham ce, amma ba ma'aikaciya daga waje ba. Dole tayi alkawarin cewa bazata ja hankali ko tayi kokarin juya masu bin addinin Hindu zuwa Kristaba. Ta yarda bayan haka ma, Gladys da Graham sun sani ba zasu iya tilasta kowa zuwa Kristi ba. Makasudin aikinsu shine su nuna kaunar Allah ta wurin yin aiki a tsakanin kutare, idan kuma wadannan mutane suka zabi yin na'am da kaunar da aka nuna musu, to ai zabinsu ne.

## ABUBUWAN DA ZUCIYA KE BUKATA

Gladys ta dawo Baripada wajajen karshen 1984 gun mijinta Graham. Tayi murnar dawowa tare da mijinta, kuma tayi maza ta shirya zaman rayuwa na aure.

Tana jin rashin dadin samun damar shiga kauyuka kamar yadda ta saba, amma tayi na'am da sabon matsayinta.

Ta dauki wata aya da aka rataya a bango a zaman takenta. Ka nuna farincikika....a cikin UBANGIJI, shi kuma zai biya muradin zuciyarka. Tana jin dadin yin aikace aikace kewaye da sabon gidanta tare da taimakawa marasa lafiya. Musaman ma takanji dadin yin tafiye tafiye da sukan yi tare da Graham wasu lokuta suna ziyartar majami'un Santhal inda takan mori yin sijadar lahadi ta kuma karfafa mata.

A 1985 Gladys da Graham suka sami diyarsu ta farko, Esther Joy, wanda kanne maza guda biyu suka biyo baya. Philip a 1988 da Timothy a 1992. Gladys na jin dadin kula da iyalinta, sai kuma ta gane, wannan ya bude wani sabon bangare na hidima yayinda yayanta suke girma suna wasa tare da yaran unguwar.

## SADAUKAR DA KOMI GA ALLAH

Gladys da Graham sunci gaba da aiki cikin dukan shekarun 1990 da aminci cikin masu fama da ciwon kuturta da kuma mutanen Santhal. Gladys takanji dadin kai yaranta a kauyuka domin suyi wasa da yaran Santhal, kuma yaranta sukanji dadin tafiya tare da ubansu zuwa sansanin cikin jeji, na taron kwanaki biyar da akeyi a kowace shekara, wanda pastocin unguwar ke shiryawa. Graham ya kan halarta domin bada taimako ta koyaswa da yin wa'azi.

Graham da Gladys sun sani cewa kauyawan Santhal da dama sukan fuskanci tsanani domin bangaskiyar su ga Kristi. A kullum sukan maida hankali ainun ga bukatunsu, kuma sukan yi addu'a domin samun hikima tayin hulda dasu.

Graham bai taba zuwa cikin kauye domin ya rinjayi wani ya sauya addini ba. Mai makon haka yakan goyi bayan pastocin yankin da majami'un da Allah yasa aka kafa. Duk da haka Kristocin Santhal sun fuskanci hamayya, kuma akan basu

laifin juya addinin mutane ta wajen tilastawa da kuma ta wajen karban kudi daga turawa, an taba kaiwa wani yaro dan shekaru goma sha biyu hari kawai wai don shi Krista ne. A lokacinda ya hau itace domin ya hangi inda dabbobin da yake kiwo suke, wasu yara daga kauyukan kewaye, da fusata wai ya shiga addinin Krista, suka kewaye itacen suka hana shi saukowa. Bayan ci masa zarafi ḍa yi masa ba'a akan bangasiyarsa, suka soke shi da itace ta baya har sai da ya mutu. Uwarsa gwamruwa ce kuma wannan al'amari ya ji mata.

Wani rukuni na yan Hindu sun jejjefi kuma sun nutsar da wani saurayi domin bangaskiyarsa. Kuma bayan kai hari gadan gadan, kristoci na fama da barazana daga yan unguwa.

Watarana akan sace masu mallakarsu ko kuma a lalata a barnata, ko kuma a hana su yin aiki a gonakinsu ko diban ruwa daga rijiya a kauyen. Shekara bayan shekara rahotanni na tsanani na ta zuwa amma Gladys da Graham basu sami wata barazana garesu ba, kuma basu taba nuna damuwar ko zasu zama haka ba ga masu tsattsaurin ra'ayin addini. Gladys tayi batu, “Mu muna yin hidima ne ga wadanda suka kamu da kuturta. Yaya wannan zai zama da hadari?”

A ranar wata Alhamis da safe a Janai'ru 1999, Gladys tana more hutawarta kuma tana karanta abincin yininta. Labarin wannan rana akan wata yarinya ce yar shekaru goma sha biyu wacce take fama da ciwon idon da ake tsoron zata ma rasa idanun, lokacinda paston yarinyar ya ziyarce ta a asibiti ta gaya masa.

“Pastor Allah ya dauke mani idanuna” pastor yayi shiru zuwa wani lokaci daganan sai yace, “Jessie, kada ki bari ya dauke.” Yarinya tana mamakin abin da ya fada ta yi shiru sai yace “Jessie ki bashi idanun” ya gaya mata.

Wannan labari kuwa sai ya buga kararrawa a zuciyar Gladys a yayin da take ji azuci Ubangiji na tambaya, ko a

shirye take ta hakura da duk abinda take kauna mijinta, yayanta, dukan mallakarta domin sa. A yayin da zuciyarta ke ta saka, hawaye suka zubo mata.

Ta bada zuciyarta ga Kristi a lokacin da take yar shekaru goma sha uku kawai, kuma daga wannan ranar tayi kokarin yin rayuwa dominsa kadai. Bata ja da baya ba har lokacin da tazo India kuma da ita da Graham sun bada rayuwarsu kacokan ga hidimar sa. Tana zaton ta baiwa Allah komai da komai, amma a cikinta ta sani abin da ke ja mata hankali shine ta rungumi abubuwan da tafi kauna.

A karshe tayi addu'a tana baiwa Allah amsar da ta sani ya dace dashi. "I Ubangiji Yesu, a shirye nake dauki dukan abinda nake dashi domin amfaninka mijina, ya yana, dukan abinda nake dashi,. Na mika komai a gareka. "Tana cewa amin, sai taji salamar Ruhu Mai Tsarki yana kewaye da ita kuma tana tunawa da labarin Ibrahim lokacinda yake bada dansa, Ishaku, ga Allah.

Bata da masaniyar me ke shinfide domin iyalinta, amma tana cikeda bangaskiya Allah yana tare da su.

Mako na biye, Graham zai tafi kauyen Manoharpur domin halartar wani taron sansanin cikin jeji. Yakanji dadin tafiya tare da Philip dan shekaru goma da Timothy dan shekaru shida tare dashi, kuma su yaran ma sukanso sosai sukanji dadin tafiya sansani. Sun dauke shi kamar wani kuru ne, yin sa sani a cikin mota jip ga rashin lantarki ga babu ruwan famfo.

Amma galibi sukanji dadin tafiyar tare da babansu. Hutun Kirsimeti ya gajiyar, domin yawan baki da sukayi ta ziyara, kuma Gladys ta sani zaiyi wa yaran kyau su kadaice da babansu. Tafiyannan ta awa hudu zai basu wannan lokaci na tattaunawa.

Ita Esther yar shekaru 13 ta sami ziyara daga kawayenta na makaranta sa boda haka ta gamsuda ta zauna a gida tare dasu da kuma uwarta.

Ranar laraba 20 ga Janairu, Gladys tana shirye shiryen abubuwa domin tafiyar. "Phil, ka gama tara kayanka?" tana tambayar babban danta shi kuwa mai zafin jini ne, kamar ubansa, kuma mai fuskar jama'a ne kwarai, a kullum mai tausayawa ne shi. Gladys tana alfahari da irin kauna da yake nuna wa kowa. Mamaki' take ma wai saura kadan ya cika shekaru goma sha daya, da yake harkoki sunyi yawa gani take lokacin na wucewa da sauri sauri ainun.

"Yara, lokacin tafiya yayi," Graham ya kira Gladys ta raka yara zuwa wajen motar jip inda ubansu yake jira, tayi wa yaran sumba ta juya wajen Graham tayi masa sumba. A kowane lokaci sukanyi kyakkyawar ban kwana domin basu san me zai faru ba musamman ma a wannan mahaukatan hanyoyin motar India. Gladys ta sani cewa Tim na nuna damuwa game da wannan tafiyar domin wani hadarin mota da ya same su a watan Nuwamba. An jefa shi zuwa gaba amma baiji ciwo sosai ba.

Amma ya tsorata ainun kuma yan makonni da suka shige, an kuskuri yin wani hadari inda wata babbar mota ta yanko hanya kusa da motar da suke ciki akan tudun wani dutse. Gladys ta fahimci damuwar Tim game da tafiya a mota, kuma tayi lokarin karfafa shi kafin su tashi.

"Ku more tafiyarku da kyau! Zan ganku ranar Litinin", ta fada kafin suje mota. Tana juyawa, sai ta tuna bata duba jakar Phili ba. Ina fatar bai manta da taguwarsa ba in ji ta.

Daganan kuma tunaninta ya juya kan Tim, yana fama da mura, kuma Gladys ta shirya masa wasu yan tufafi sanin cewa akwai sanyi a karkakara kan duwatsu. Tayi murmushi, da fatar Tim ba zai sa muryarsa ta dishe ba wajen raira wakoki. Shine mawaki kuma mai wa'azin gidan. Yakanyi sha'awar yin wa'azi kamar babansa, kuma wasu lokuta Gladys kan same shi yana jera kujeru a cikin falo wai shi zai yi wa'azi. Ko da shike ya kwana biyu baiyi wannan wasan nasa ba. Sai gashi ranar litinin, Gladys ta shige ta kusa da falo sai ga Tim yana wa'azi yana waka da aniya ga kujeru da ya jera a

zaman mambobi a cikin majami'a. taso ta zauna ta saurare shi da zarar ta gama abinda take yi, amma da ta dawo sai ta tarar ya rigaya ya shiga wata harka dabam.

Bata da masaniyar cewa, wannan shine lokaci na karshe da Tim zai yi wasansa nayin wa'azi. Wayan tarho yayi kara da karfe hudu da rabi na asuba ranar asabar, 23 ga Janairu. Ta tashi firgigi daga kan gado cikin duhu, ta dauki kan waya cikin gigin barci tasa a kunne. Ta saurara kadan, tana kokarin kwantar da tsoratarwarta da faduwar gaba kuma. Karar tarho din ya tada Esther da kawayenta daga barci suka iso kofa a lokacinda take ajiye wayar "iya, me ke faruwa?' in ji Esther.

"Wani ya kona motocin jip na mishan" inji Gladys" Bansan wani abu kuma ba, sabodahaka mu natsu tukuna. zamuyi addu'a kuma ku yammata sai ku koma kowa ga kara samun barci. Ina fatar kowa lafiya.

Kuma kun sani muna da aiki da yawa. Zan gaya maku dukan abin da ya samu, idan naji su." Wadannan bayanai, a lokacin da suka zo, zasu zama da takaici fiye da yadda Gladys ke zato.

## HARZUKA MARA MISALTUWA

Wannan karamin kauyen Maoharpur a rabe yake a al'adance zuwa wani lokaci. A cikin shekara, 22 daga cikin iyali akalla 150 da suke kauyen sun zama Krista wadannan bangarori guda biyu sun dade suna zaman lafiya da juna amma ba da jimawa ba su kabilun suka fara nuna damuwa game da Kristocin.

Da ranin 1998 hankali ya fara tashi a lokacinda wadansu manoma Krista suka fusatar da mutanen kabilar ta wurin cingaba da yin aiki a gona a ranar buki tsafin su na Raja, lokaci ne da mutanen Santhal suka gaskanta cewa kasa tana haila. Chachar baki mai zafi da akayi a tsakanin Krista da mutanen al'ada na Santhal ya sami lafawa, amma abin yana

ransu, kuma yan makonni kafin ranar taron sansanin jeji wanda Graham da yayansa suka halarta, wata matsala ta sake tasowa a lokacin da mutanen kabilar suka soki batun wani shiri na shirya wakokin Krista a harshen mutanen Santhal a wani bukin auren Krista a kauyen. An san wannan kabilar da tsare al'adunsu kwarai da aniya; saboda haka wannan bambanci na rarrabuwar al'adu shi ya tunzura ţarin mambobin yan al'adu iza irin wannan harzuka mara misaltuwa.

Saukar Graham a wannan kauye shi ya baiwa yan Santhal masu fusata wata dama da suke nema. Yanzu kam zasu rama su ji ma wadanda suke yin karfin halin karya dokokin al'adunsu. Suka nemi taimakon Dara Singh, wani mai buge-bugen hulda ta jama'a kuma mai himmaga batun addinin su wanda ya kware wajen cakuda alamari duk lokacin da damar yin haka ta samu. Galibi himmarsa ta tsageranci ne da masifar haddasa tashin hakali a yayinda yake farwa Krista da ma Musulmi kuma.

A cikin asubancin Janairu 23, wannan muguwar himmarsa takai wani matsayi na harzuka. Daren da ya wuce, Graham da yaran sun gama cin abinci kuma suna ban-kwana da abokan aiki. Wajajen karfe 9.30 ne su uku suka shiga bayan motarsu, sukayi shirin kwanciya. Iskar dare na da sanyi, sai Graham ya shimfida wata tabarma akan motar domin kawar da raba kuma mota ta dumama kadan. A kullum yakanyi kokarin cewa yaran sun gamsu, kuma kullum sai sunyi addu'a tare kafin barci.

Motar jip din tana ajiye a gefen wata jip kuma kusa da dakin addu'a kuma daya daga cikin abokan Graham, Dr, Ghosh yana kwance a wani gida nan kusa na iyalin Krista. Wajajen tsakar dare kuwa sai ihu da tsawa da hargagi ya tashe shi, yayi tsalle daga kan gado ya leka waje ta taga. Ya girgiza ainun da ganin taron mutane suna gudu suna ketare fili-mutane masu damara da gatari, sanduna, da wukake kuma suna dauke da fililar ruwa agoshinsu kuma suka jeru kamar

kudan zuma akan motocin nan guda biyu. Suna ihu a fusace, mahaukatan nan suka farma motar Graham, suna sarar tayoyi suna farfasa gilasai. Suka yi wa na ciki duka suka sassara su da makamai a yayin da Graham yake kokarin kare yaransa amma ina.

Dr. Ghosh ya gudu yaje kofa, amma kofar na dode daga waje. Dayake a kulle yake sai kallon abin tashin hankali yakeyi ta taga.

Wannan gungun fusatattu basu ragewa Graham da yaran sa ba. Babu batun tserewa daga wannan kazamin hari. Masu harin sun sa mutane a gaban kowane bukka a cikin gidan domin kada wani ya fito ya bada taimako, kuma yanzu suna yi wa kauyawan tsawa cewa kada wani ya kuskuta ya fito waje, in ko ya fito zasu kashe shi!"

Hasda, abokin aikin Graham na fiye da shekaru ashirin yayi kira cikin bacin rai da bukatar a tsayar da wannan mugun hari. Yana kallo cikin razana lokacin da suka debo yayi suka zuba a karkashin motar; Dara Singh ne ya fara sa wuta. Lokancin da Hasda ya sukwano domin ya kashe wutar da ruwa, sun yi masa duka sosai. Mugayen maharan nan suka tsaya suna kallon motar na cin wuta a yayinda Graham, Phillip da Timothy suna ta ihu don azaba har sai da wutar taci karfin kukansu kuma ta mai da jikunansu suka zama toka. A lokacin da wannan bala'i ke faruwa kamar nisan yadi dari daga wurin akwai gungun matasan Santhal suna kada gangunansu na al'adu suna wani rawar su da ake kira Dangri, suna yi kamar ma basu san wannan mugun abu na faruwa ba.

Bayan awa guda, sai duk suka watse suka bace, Hasda da suka kora da dare, ya garzaya zuwa wurin sarkin yankin neman taimako. Aka tura masinja ya shaida wa yan sanda wuri mai nisan mil 15 a wani kauye dabam. Amma an rigaya an makara. Lokacin da Hasda ya dawo wurin, bakinciki yasha masa kai da ya hango fankon konanniyar jip din

Graham. A ciki kuma yana iya ganin konannun gawawwakin su uku a hade da juna a runguma ta karshe. Ya sani abinda yake gani abune da zai zauna tare dashi muddin rayuwarsa.

A yayinda razanannun Kristocin nan suka fito daga bukkokinsu, suka kewaye wannan wuri da akayi ta'asa, sun tsaya shiru zuwa wani lokaci. Ta ciki kuwa suna ta tunanin shin yaya ma za ayi a gaya wa Gladys da Esther?

## IGIYAR RUWA NA BAKIN CIKI

Da karfe bakwai na safe Gladys na shirin aiki lokacinda tarho yayi kara kira na biyu kenan a wannan safiyar. Ashe wani dan jarida ne yake tambayar shekarun Graham da na yaran.

"Maganar me kake yi? "Gladys ta tambaya. Da ya gane cewa bata san abinda ya faru ba, kuma ba tare da son taji daga bakinsa ba sai ya yi sallama ya ajiye wayar. Amma waya ya ci gaba da yin kara ana ta kira ana tambayoyi daga makwabtan kauyuka." Gladys ance wai Graham da yaran sun bace" wata kawa ta gaya mata. "Bace? Wayyo, Allah na!" Gladys tayi tsawa. Me ke faruwa da ya'yana masoya? Sun fice su kadai ne?"

A karshe dai kawarta Gayathri ta iso kuma ta shiga dawainiyar amsa tarho. Amma fa abubuwa sai kara daburcewa sukeyi, kuma har yanzu Gladys bata san gaskiyar abinda ya faru ba. Zuciyarta na cikin bala'in damuwa, amma kuma tana sa rai Graham da yara zasu shigo gida ba da jimawaba. Zuciyarta a dode take bata tunanin wani mugun abu ya faru dasu sam, sai kuwa taci gaba da fatar zuwa anjima zasu shigo gida.

Cikin sa'oi masu zuwa kuwa abokai suka fara shigowa, da karin yan jaridu suna neman karin bayanai kuma su dauki hotuna. Mutane sun taru a ciki, a waje, akan dakali, ko ina.

Wuri ya hargitse kuma Gladys ta ci gaba da gaida mutane kuma tana kula da Esther. Har yanzu bata gane zurfin abinda ya faru ba, kuma babu wanda yasan yadda ya kamata a gaya mata wannan mugun labari.

A karshe dai wajen 9:30 na safe Gayathri ta rike hannunta tace" Gladys, ina so nayi magana da ke" ta share daya daga cikin dakunan kuma ta ja Gladys ciki, Gayathri tace" Gladys, bana so ki zama kamar dutse, amma dole kiyi karfin hali domin Esther."

Gladys taji labarin nan kamar taki yarda. Zuciyar ta nason kin yarda da abinda kawarta ta gaya mata, amma a zahiri batun haka yake. An rigaya an furta kalmomin kuma babu yadda za ayi a mayar da su. Kai zuciyarta tayi kuka. Ba zai yiwu ba! Babu yadda za ayi ace suna cikin motar. Akwai kuskure. Ba a kone su da ransu ba. Ta kaka irin wannan zai faru? Wadanne irin mutane ne zasu sa kansu yin irin wannan ta'asa?

Igiyar ruwa na bakinciki yana barazanar hadiye ta, amma Gladys ta kara tambayar kawarta sau daya. Watakila kuskure tayi, kila kuma labarin yazo da kuskure....

Gayathri .....shin kina nufin sun.... mutu? Da Graham da Philip da Timothy da gaske babu su sun tafi?".

Idanun Gayathri masu cike da bakinciki ya nuna mata batun babu kuskure a ciki, sai Gladys ta zauna a kasa. "Kaka zanyi na gayawa Esther? Tayi kuka. Komai ya tsaya tsit, amma rayuwa na tafiya. Gladys kuwa tana shirin hanyar da zata bi ta gaya wa Esther. Tarho na kara, mutane na kira daga Australia domin susan abinda ya faru.

Karin abokai da makwabta sun shigo dominyin jaje, hasken fitilun abin daukan hoto na yan jarida suna ta tashi, amma Gladys tunanin diyarta takeyi "Iya, menene labarin? Esther ta tambaya. Gladys ta rike hannun diyarta ta dubi idanunta na yarinta da basusan kome ba. Akwai alamar an barmu mu kadai," ta gaya wa diyar a hankali. Daganan, ba tareda wani shiri ba, sai ta kara "amma zamu gafarta musu"

"I, Iya' zamuyi haka". Idanun Esther suka fara hawaye a yayinda ainihin wannan rashi yake ratsa tunaninta, Gladys ta rike ta da karfi tana kokarin fahimtar wannan mugun aikin ta'asa da ya sauya rayuwarsu nan take harabada. Wannan abu ya kashe mata jiki amma kaiwa da kawowa na mutane da ke zuwa shi ya taimaka mata. A karshe da likitan unguwar ya ziyarci Gladys kuma yayi sauri yace, "suna so asan yadda za ayi da gawawwakin"

Wannan furuci da taji daga bakin sa ya share dukan wata shakka da take wai kila labarin kuskure ne. "A dawo dasu zuwa Baripada. Graham ya ba da ransa domin wannan kasar. Zai so a bizne shi anan" injita.

Mako na biye kuwa gabadayansa ya zamar wa Gladys kwanaki ne na karbar baki, yan jarida, da jami'an hukumar birni. Daga baya abokan aikin Graham suka iso daga Manoharpur suka kuma yi bayanin yadda aka kai musu hari. Gladys taji cewa da dama daga cikin kauyawan sun bada shaida sunga tsirkiyar haske mai fadi daga sama akan motar da ke konewa ta kuma ji labarin razana ta Kristoci a wannan wuri domin arhana su su fito su taimaka, da kuma karfin halin abonkisu Hasda, wanda yayi kokarin kashe wutar.

A hankali kuwa sai ta lura cewa al'amarin shiri ne na wani hadin baki domin a farma jamaar Krista aji musu, kuma sai masu wannan muguwar aniya suka zabi Graham ya zamar masu wanda zasu kaiwa hari.

Dan talikin nan Hasda yana cike da bakinciki. Iyayen sa mazauna gidan kutare ne, a wurin aka haifi Hasda. Gladys tasani yana kaunar Graham da yaran kwarai, kuma tana tausaya masa sosai.

## UBA KA GAFARTA MUSU

Anyi jana'iza ranar litinin da karfe goma na safe, dai dai lokacinda yakamata Graham da yara su iso gida daga sansanin jeji. Akwatunan gawawwakin guda uku sun iso a

rufe da furanni, jim kadan kuwa sai ya zama kamar dukan Baripada ta tsaya tsit. An rufe kantuna da makarantu, kuma jami'an hukumar birni dayawa sunzo janaizar Graham da yaran. Gladys da Esther sun baiwa taron wajen mutum dubu mamaki ta wurin zaben zama a kasa akan ciyewa tareda mazauna cikin gidan kutare, wadanda ke cikeda bakin cikin rashin "Dada" na su wannan hidima ta jana'iza alamarta ma sai kace shiri ne daga samaniya domin masu makoki dayawa suna ta nuna bakincikinsu kuma suna furta ayoyi daga Littafi Mai Tsarki.

An bukaci Gladys da tayi magana, amma ba a shirye take ba ta tsaya a gaban wannan babban taron jama'a maimako, ta tambayi Esther, "zaki iya tashi kiyi waka tare dani?".

Esther ta yarda, sai taro yayi tsit a yayin da Gladys da diyarta suka nufi dandamali acan suka yi wakar da take ta karfafa ta na tsawon shekaru.

"Domin yana da rai nake iya fuskantar gobe....duk da karfin zuciyarta a yayin da take wakar da Esther, a zahiri Gladys aka take wakar. Domin yana da rai nake iya fuskantar yau . Gaskiyar ita ce, tana iya fuskantar gaba amma sai daya bayan daya. Amma wannan ya isa ya gusar da ita gaba, domin sannu a hankali, rayuwarta ya zama shaida na tsayayyar bangaskiya a cikin tsakiyar bala'i. ko da shike tana cikin bakinciki ga kuma gajiya da tunani a cikin lamirinta amma Gladys na da salama, kuma tana so ta nuna wa duniya cewa an martaba ta da yake an shahadantarda mijinta da yayenta domin Kristi.

A wata magana ga yan jarida, Esther mai karfin zuciya tace, " Ina godiya da Allah ya basu damar shan wahala domin sa," kuma Gladys ta kara karfafe batun Esther da nata maganar. "Ina addu'a (Esther ta gafarta musu, gama basu san abinda suke yi ba.) Kuma na gaskanta cewa dukan abubuwa na aiki tare domin kyautatuwa ga dukan wadanda ke kaunar Allah, garesu da aka kira bisa ga nufinsa. Na tabbata ta wurin wannan sanadi, Allah zai kammala nufinsa madawwami.

Abokai da yawa da kuma iyali suka fara damun Gladys cewa ta tattara kayanta tare da Esther su koma gida inda ke da tsaron lafiya sosai. Suna ganin kamar aiki a gidan kutare zai tsaya sai dai in Gladys zata nemo wani wanda zai dauki gurbin Graham. Kuma suna fama da yin tambayoyi barkatai: "Zaku kai gawawwakin zuwa Australia ne? dake da Esther yaya zakuyi kenan yanzu? Yaya batun gidan kutare?".

Abubuwan da mutane suke fada yana bata mamaki ita ta maida India gida kuma bata shawarar tashi. Da yan jarida suka tambaye ta gameda goben ta, ta amsa, dukan al'amura na suna hannun Allah. Kyawawan abubuwa kadai zaiyi. Shine karfina da tsayawata, yayi alkawarin bazai taba yashe ni ba zan yiwa India hidima da wannan a raina.

## GAFARTAWA YANA KAWO WARKARWA

Bayan wata biyu, Gladys tayi shirin karbar wata kyauta ta bangirma domin girmama Graham da ake kira Indo Australian Award. An kuma nemi tayi magana a wajen wannan buki, kuma fiye da mutane dari uku suka taru a karamin dakin jawabi bayan an sami labari cewa Gladys zata halarci taron.

Wannan shine na farko da ta yarda tayi magana a bainar jama'a tun mutuwar Graham da yaran da aka shahadantar. Akwai kuma yan sanda da dama domin tsaron lafiyar Gladys.

Da tayi shirin yin magana, Gladys ta zauna shiru tana karanta tsohuwar waka da Annie Johnson Flint ta rubuta, wanda ya kara karfafata kwanakin baya.

*Yana ba da Karin alheri a yayinda kayan nauyi ke karuwa.*

*Yana aiko mane karin karfi a yayinda ayyuka ke karuwa.*

*Ga kowane karin tsanani yana kara mana jinkansa.*

*Ga yawan jarabobi yana yawaita salama.*

*Kaunarsa babu iyaka, Alherinsa baya kwatantuwa.*

*Ikon sa babu iyaka ga sanin dan adam.*

*Gama daga cikin daularsa mara iyaka cikin Yesu.*

*Yake bayarwa, ya kuma bayar, kuma ya sake bayarwa.*

Ga yawan jarabobi yana yawaita salama, kaunar sababu iyaka, Alherinsa baya kwatantuwa, ikon sa babu iyaka ga sanin dan'adon. Gama daga cikin daular sa mara iyaka a cikin Yesu yake bayarwa, ya kuma bayar, kuma ya sake bayarwa.

Ta karanta layi na karshe kenan shi mai gabatar da ita yakai ga aya. Gladys ta nufi dandamali, kuma ta fara lura da yadda rahama tazo ma Graham. "dukan wurinda wani yake kwance babu lafiya, Graham yana wurin" injita. "yana iya zama da dare ko da asuba. Babu komai. Graham baya bata lokaci game da batun taimako ga wanda yake cikin bukata. Sai cika aiki kawai."

Ta gama maganar ta kuma ta karbi kyautar, sa'annan aka gayyaceta ta zo wajen cin abincin dare. Babu wanda ya tafi; kowa da kowa naso su gaida wannan gwamruwa mai karfin hali wanda ba ta da wata muguwar magana na fadi game da wadanda suka kashe mijinta da yayanta guda biyu. Da suka jeru wajen cin abincin dare, wata mata tace wa Gladys", Ni bansan yadda zakiyi ki gafarta ba."

Ba tare da wani tunani ba Gladys ta amsa, "dole ne a gafarta. Gafartawa yana kawo warkaswa" Gladys ba ta ma farga da gaskiyar abin ba sai da kalmomin suka fito. Ta gafarta wa masu kisan mijinta da ya'yanta tun lokacin da wannan mugun labari ya isa gareta. Amma fa lallai gafartawa shine ya zama mafarin warkaswa, kuma ta yanke shawara nan take game da irin sakon da zata bayar nan gaba.

Takardun gayyata na taje jawabi suka fara zuwa, kuma tayi na'am, kuma a kullum jawabinta yana game da gafartawa. A kowane taro takan ce, lallai ne kauna ta zama ta gaske. Lallai ne mu darajanta juna kamar yadda Romawa 12 ke gaya mana. "ku albarkaci masu tsananta maku, ku albarkace su kada kuyi musu la'ana. Kuyi farinciki tare da wadanda suke farinciki, kuma kuyi makoki tare da wadanda suke makoki. Ku kadaita zukatan ku ga juna. Kada kusa tunani ga abubuwa masu tamani, amma kuyi hulda da masu kaskanci. Kada ku nuna hikimar kanku. Kada ku rama mugunta da mugunta. Ku mutunta kyawawan abubuwa a idanun dukan mutane. Idan ya yiwu, ga dukan iya kokarinku, ayi zaman lafiya da dukan mutane".

Tun jawabinta na farko a bainar jama'a na wajen bukin bada kyauta, an sha gayyatar Gladys fiye da a kirga a makarantu, majami'u da kuma al'amura na cikin jama'a, wasu lokuta ma takan halarci taro guda shida acikin awa talatin da shida. Yau sakon nan nata yana taimakawa a zaman tuni ga kasa waddata farma Krista da tashin hankali yake ta karuwa kuma kamar ma babu wanda zaifi Gladys Stains dacewa ga isarda wannan sako.

## JAWABI

Har yanzu Gladys na zaune a gidan kutare na Mayurbhanj. Amma tayi tafiye tafiye a cikin duniya tana yin jawabi game da tsanani a India kuma tana shaida sakonta na gafartawa. Kasar India tayi mamaki game da shaida da kuma sakon kaunar Kristi da ke fitowa daga bakin wata mai isar da sako da ba za a taba zato ba, bakuwa daga wata kasa........ gwamruwa........mata mai saukin kai wadda abinda take da burin yi kawai shine tayi wa matalauta hidima.

Abin bakin ciki shine sai da al'amarin ya dauki ran mutumin Turai ta mummunar hanya tare da yayansa biyu sa'anan ya jawo hankalin kasar. Amma Gladys ta yi hidimarta da aminci

a zaman mai fadin abinda Allah yake so, na tabbatar da cewa yana sa dukan abubuwa suyi aiki tare da kyautatuwa ga wadanda ke kaunar Allah".

Domin amsa jawabanta Gladys ta sami dubban wasiku daga mutane ko ina a cikin India, harma masu addinin Hindu suna bada hakuri game da ta'asar da aka yiwa iyalinta.

Ta koyi ko menene karfin da gafartawa yake dashi, kuma ta sani wannan zaici gaba da zama sako na musamman, harma ga wadanda suke cikin majami'a. A wani taro na mata inda Gladys ke yin jawabi, an bata labarin wani mai shekaru 90 wanda yake jira a waje, ya nace wa ganin wannan mata, wadda ta iya gafarta wa wadanda suka kashe iyalinta. Da ya isa ga yiwa Gladys magana, ya gaya mata diyarsa ta mutu da dadewa dalilin rashin kulawa na masu aikin asibiti, kuma ya kasa gafartawa wannan likitan. Gladys tayi masa bishara na wani lokaci, kuma suka yi addu'ar gafartawa tare.

Shekara guda bayan harin. Dara Singh da wasu mutane goma sha biyar suka shiga hannun hukuma aka kuma yi masu cajin kisan Graham, Philip da Timothy Staines. A watan Yuni 2002, aka nemi Gladys taje tayi shaida a wajen shara'ar kuma ta jimrewa kalubale mawuyaci da ta taba sani tun ranar kisan mijinta da yayanta; fuskanta mutumin da ya zama sanadi. Nata gwaji kenan na cin gaba da gafartawa lauyan Singh yana nuna cewa Singh bashi da laifi, yayi kokarin ya karyata Graham cewa shine yayi sakaci ya sa wutar da kansa da rasho na dafa abinci. Da lauya yaci gaba da magana sai Gladys ta dubi Dara Singh sai kuma ta dubi nata zuciyar taroki Allah ya taimaketa ta nuna kauna da tausayi kuma kada ta taba dubansa da kiyayya.

A lokacin da ake dab'in wannan Littafi shara'ar tana nan tana cin gaba. Mun sadu da Gladys da Esther a Calcutta, kuma kafin mu rabu Gladys tayi mana wani baiti da ya zama abu mai karfafata tun mutuwar mijinta da yayanta. Marubucin wakar marigayi Edgar Guest, ana kiranta "An isa gida lafiya."

*Ina gidan zamaniya, masoyana;*
*Kai, da farinciki kuma da haske!*
*Akwai farinciki sosai kuma ga kyau*
*A cikin wannan madawwamin haske.*

*Dukan radadi da bakinciki ya kare.*
*Dukan turereniya ta kare.*
*A yanzu ina cikin salama harbada.*
*A karshe na isa gida a zama niya*

*Kayi mamaki ne cewa a natse*
*Nayi tattaki a kwarin inuwar?*
*Kash! Amma kaunar Yesu ta haskaka*
*Kowane duhu da kowane kurmi.*

*Kuma yazo da kansa ya sadu dani*
*Akan wannan hanya mai wuyar bi;*
*Kuma da damtsen Yesu domin jingina shin*
*Zan iya yin shakkka ko tsoro?*

*Idan hakane kada bakincikin yayi tsanani,*
*Gama ina kaunarka ainun har yanzu;*
*Yi kokari ka hangi gaba da inuwar duniya,*
*Yi addu'a domin amincewa da Nufin Ubanmu.*

*Akwai aiki na jiranka har yanzu*
*Don haka babu tsayawa ga yin aiki*
*Yi aiki yanzu tun da sauran rai*
*Zaka huta a kasar Yesu*

*Lokacin da dukan wannan aiki ya kammala,*
*Zai kira ka zuwa gida a hankali*
*Kai fewcewa na wannan saduwa,*
*Kai, farincikin ganin zuwanka!*

# Mai:

# Komawa Vietnam Domin Yin Wa'azin Bishara

*Vietnam:*
*Nuwamba 1989*

Suna sunsunar alamar ruwan teku kafin ma su hange ta. Mai ta bi wanta Hong, kusan ma inda ya daga kafa nan take takawa akan jerinsu na tafiya daya bayan daya.

Saura tudu guda daya da zamu haura, iska mai cike da damshin ruwan teku mai gishiri gishiri na busawa kuma jin kusatowa da teku na sa suna jin dadi. Mai taji dokin ta na karuwa, kowane takun kafa yana kawo su kusa da samun yanci!

A karshe suka haye tudun, kuma Mai tage jirgin ruwa da zasu shiga, anyishi da wani gungume da aka saro ba ko gyara sai aka dabe shi da kwalta akai kuma aka sa wani siririn itacen gwangwala a zaman mahada. Ganin jirgin sai a dauka ko zai tarwatse tamfar karan ashana idan wani ya shure ta. Sai ta tsaya ta cabki hannun Hong don ta hana shi cin gaba da tafiya.

“Bazan iya hawan wancan abin ba! “ta gaya masa tana jan damtsensa sai da ya juya ya fuskance ta. “ba zamu ma iya fita daga bakin tashar rowan ba, ballantana tafiya Hong Kong!”

Dole ki taho, Mai, Hong ya gaya mata ya juya ya nufi ruwan yana janta ta bishi Mai ta sake duba jirgin, tana jin tsoro na kama ta. Bayan bukkar gwangwalar, kan jirgin shimfidadde ne babu tudu babu kwari.

Wasu yan Vietnam masu gudun hijira suna ta hawa cikin jirgin, wasu suna yi da maida hakali suna duba bayansu, suna tsoron ko yan sanda China zasu kawo musu kame a mayar dasu zuwa Vietnam.

"Ba....ba zan iya ba, Hong, "tana i'ina "ban... ban shirya wa irin wannan abu ba" "Ai dama sam baki shirya ki yi sanda ki keto iyaka zuwa China ba, kuma gashi munyi. Yanzu taho, lallai ne mu tafi. Ba ki san irin wahalar da baba yayi akan wannan ba?".

Hong yasa hannu a cikin aljifunsa ya zaro wani tsohon hankici. Ya warware a hankali ya nuna mata sulen zinari guda biyu. Kowanne nauyisa yafi rabin oza, kuma ko wanne zai biya kudin sufurin jirgi zuwa Hong Kong, tikitinsu na samun yanci.

Wai shin kin san tsawon lokacin da ya dauki baba na tara wannan kudin? "yaci gaba" ya dade yana jira kuma yana shiri domin wannan rana na tsawon shekaru. Shi kansa bazai taba dandana yanci ba, amma ya sayo maki hanya. Yanzu maza shiga jirgi!".

Bani ya sayawa ba. Tikitin Trung ne, "mai ta amsa da nuna bacin rai. Daya daga yayyen Mai shine aka shirya zai tafi tare da Hong. Baban Mai ya shirya ya aika yaya maza guda biyu zuwa yanci, da rai zasu amfana kuma su iya taimakon sauran yan'uwansu maza da mata su fice daga Vietnam.

"Tikitin na Trung ne amma matarsa ta haifu. Ba zai iya barinsu a yanzu ba, saboda haka kece kika yi sa'a. zaki sami yanci a Amirka ko a Australia. Zaki iya samun ilmi maikyau. Kuma watarana ki zama mai arziki!"

Har a lokacin yana rike da hannun Mai, kamar yana bi da ita kamar yana janta zuwa jirgin. "Ina wurin gidan wanka? Ta

tambaya "babu wurin bahaya akan wannan abin.

"Wurin wankan na kewaya mu" in ji Hong yana gatse. A karshe ya tsaya ya juya gunta "wannan shine abinda baba ya so mana, mu fice daga Vietnam. Mu sami yanci. Mu sami ilmi. Mu sami ribar ayyuka da zamuyi. Tunanin cewa dukan yaransa zasuyi rayuwarsu a cikin talauci ya na bashi damuwa. Kuma zai kara samun damuwa idan yaganki kina nuna ja da baya. Yanzu muyi gaba!"

Sun isa tashar ruwa, kuma wani mai fuskar mafusata ya dubesu duka biyu, yana miko hannu. Hong ya san abinda yake nema sulen zinari. Ya dora hankicin a tafin hannun mutumin sai suka zuba. Shi kaftin din ya dubi kudin yasa daya a baki ya ciza don ya tabbatar ko maikyau ne.

"Ku shiga" ya fada da nishin yunkura sukayi kamar yadda ya gaya musu. Ina ma da ta kara rungumar uwarta kari daya kafin su taso! Ko kuma kara tadi da babanta fiye da yadda tayi, in ji Mai. Tana juyayi ainun ko wannan jirgin a karshe dai har ta yarda takira abin da sunan jirgi, sai tayi maza tayi addu'a ga ruhun kakanta da tattaba kunnenta domin sauka lafiya.

Sun zabi wuri kusa da gaba domin kauce wa karar inji. Mai ta rigaya ta cika da damuwa ga kuma igiyan ruwa kafin ma jirgin ya bar tasha. Tayi kuka lokacin da taga gaci na bacewa a hankali sai sararin sama. Kwanakin da sukeyi a cikin jirgin ya zama abin gajiya a zaune kawai ba abinyi kuma ma bebu sha'awa, kuma Mai da Hong suka gane cewa fa basu kawo isasshen abinci tare da su ba, sai da suka fara yin barar abinci daga sauran fasinjoji 43. kwanaki suka yi ta ja na tafiya sai kace lokaci ba ya tafiya.

## HADARI

Mai ta sake tasowa, ta keto tana tofar da ruwan gishiri mai daci tana haki.

"Taimaka mani!" tanakira, tana famada lalube a duhu domin ta kama wani abu ko jirgin ko ma menene sai wani igiyar ruwa ya sake zuwa ya angace ta kuma tayi ta famar cabke yin numfashi kafin ruwa mai kumfa ya sake rufe kanta.

Tasowarta kenan don neman numfasawa, sai taji ana rike da ita, "kiyi linkaya zuwa gaci" taji muryar wani mutum yana fadi da karfi a kunnenta. Mai ta gane shi yana daya daga cikin yan gudun hijira da suke gujewa daga kasarsu akan wannan akwalar jirgi. Sukayi iwo tare. Ta duba baya wajen igiyar ruwa mai zuwa, tana gargadadda mutane duk lokacin da igiyar ruwa ya nufo su. Shidai yasa idanunsa gabaga hango gaci.

A karshe suka ji cewa suna iya tsayawa a tsaye; suka taka suka kai bakin gaci sai suka fadi a gajiye akan yashi, sauran mutane daga jirgin suna taruwa a bakin gaci, suna rawar dari a cikin iska Mai karfi da sharo ruwa. Tufafinsu ma cike da yashi. Mai tayi ihun farinciki da ya taga Hong, suka rungumi juna. A cikin hadari haka babu yadda za ayi a hura wuta, sabo da haka sai suka tattaru ko zasu iya dumama juna amma ina, saidai kawai fatarsu shine rana ta fito.

Mai tana juyayin yadda rayuwarta yake sauyawa haka. Kwanaki kadan baya ita yar makarantace a babbar sakandare kuma yar shekaru 17 a arewacin Vietnam, tana zaune lafiya da iyayenta a cikin gida mai jan rufi na tayil kusa da iyaka da China, tana tunanin koma zasu iya kaiwa Hong Hong da kuma ga yanci.

Shi uban Mai, abu mafi so a gareshi a kullun shine cewa ya'yansa guda 7 su sami irin rayuwar da tafi tasa. Mai tasha jin maganganunsa na batun ilmi sau da yawa har tana iya fadinsu aka. Amma maganganun basu ambaci batun nutsewar jirgin ruwa ba.

Mai tayi tunanin uwarta takan yi wa mijinta dariya domin irin burin da yake dashi domin ya'yansa; a gareta makaranta bata lokaci ne da bata kudi. Ita ke gudanarda kudaden iyali kuma takanki baiwa yara kudin litattafai ko kayan makaranta.

Wasu lokuta, baban Mai yakan sayarda kaji ko wata dabba sai ya baiwa ya'yansa kudin a boye domin su iya cin gaba da zuwa makaranta na wani karin mako.

Duk lokacin da matarsa ta gane kuwa, sai su biyu su shiga yin canjin miyau, suna yiwa juna kalamu masu zafi. Yayan basa yarda su shiga cikin maganarsu. Mafi muhimmanci shine suci gaba da zuwa makaranta.

Daya daga cikin yayyen Mai ya bar Vietnam kuma yayi aikin lebura na wani lokaci a Bulgaria. Ya fita ya ga kasashen waje, kuma labaru da yake basu ya kara karfafa himmar uban na yayansa su tsere.

Yanzu Mai tafice daga Vietnam amma ba a wurinda ubanta yake hange ba. Ta kudundune a bakin gaci, bargon ta ya bace a cikin teku. Hadarin rakumin ruwa ya tilastawa dukan fasinjoji suyi linkaya su fito gaci. Shi kaftin ya tsaya a cikin jirgin, ya juya fuskar jirgin ya kalli rakumin ruwa da iska da ke tafe garin kokarin haurewa.

Bayan wani lokaci aka ji iska ya lafa, rana kuma ta fito akan ruwa. Mai bata tabe yin godiyar da takai na ganin wannan wayewar gari ba.

Yan gudun hijiran suka kudundune a bakin gaci har saida kaftin ya daga musu hannu yana yafatar su su dawo cikin jirgi. Suka yi nutso suka haye rakumin ruwa na bakin gaba sukayi linkaya suka koma cikin jirgin neman yanci mai bambaro. Iskar wannan hadarin ya wanke cikin jirgin. Tufafinsu, barguna, abinci, da tukwane da kwanuka- an share komai da komai babu saura. Mai da Hong suka yi saduda da matsalar da suke ciki suka kuma fuskance shi a haka babu abinci babu kudi, da fatar cewa, ba za a kara cin karo da wani hadari ba daga inda suke har zuwa Hong Kong. Suna juyayin anya jirgin bazai nutse ba bayan dukan fasinjoji sun dawo sun shiga.

Kwanaki arba'in da biyu bayan sun shiga jirgin, suka isa Hong Kong. Amma fa ba a marabcesu a can ba; yan sanda

basu yarda yan gudun hijira su sauka ba. Maimako, aka aikasu zuwa Tsibirin Shanu wani yanki ne da ba a sha'awarsa inda manoma suke kiwon shanu.

A karshe dai Mai, Hong da saura zasu sauka daga jirgi, amma abinda ke jiransu kusan ma rashin dadinsa yakai na wanda suka gudo. Kusan jirage guda dari ake saukewa a kullum a wnnan Tsibirin Shanu. Jami'an kungiyoyin Agaji sukan rarraba abincin gwangwani, amma Mai bata saba da irin wannan abinci ba, takan yi amai bayan kowane cin abinci.

## RAYUWA A CIKIN SANSANI

Sati guda bayan saukarsu a Tsibirn shanu sai aka sake wa Mai da Hong wuri, zuwa sansanin yan gudun hijiransu na farko. Bayan wata guda, aka sake musu wuri kuma, wannan karon zuwa sansani na tara. Bayan shekara guda aka kaisu sansani na uku.

Da saukarsu a wani sabon sansani, dole su nemi wurin kwana da na zama. Yawancin mazauna sansani suna da mugun son kebe wuri, sabo da haka Mai da Hong suka maida hankali sosai domin kebe kansu daga waņdanda zasu iya kai masu hari.

Sansani na uku yafi sauran sansanoni rikici da rashin imani na aika aika, tamfar wani filin daga.

Yan gudun hijira daga wuri guda na Vietnam suka hada kansu domin yinfada da wadande suka fito daga wasu yankuna. Komai da komai na cikin sansanitubali, kwan fitila, wayar wuta, kayan gado da karafan rodi masu tsini-duk sun zama makami. Watarana a kanyi kwanaki ana gwabzawa, da rukunai dabam dabam suna kokarin su sami galaba a sansani, saboda haka ana gudanarda rayuwa a cikin sansani ta irin mulkin rudu na Darwin.

A lokacin gwabzawa, mata da yara sukan buya, suna kokarin kada ma a gansu a lokacinda maza ke fafatawa da

juna. Kamar dai Mai takan kudundune akan gadon ta a majingini wata yarshinfida ce akan yan duwatsu da fatar fadace fadacen zasu lafa da wuri. Haka kuma kamar sauran takan yi fatar ficewa daga sansani ta sami yanci na zahiri.

## GAMA ALLAH YAYI KAUNAR DUNIYA

Bayan wani gagarumin fada, aka kaurar da Mai da Hong zuwa wani sansani, Lang Gin sansani ne na horo, da aka tsara domin kadaita masu "neman tashin hankali" kuma Mai bata san dalilin da aka kaisu wurin ba.

Akwai alamar alheri ga wannan "horo" domin sansanin yana da wani gini da ake amfani dashi a zaman majami'aba fa wai Mai tasan wani abu da ake kira majami'a ba. Amma watarana tana wucewa kusa da ginin, sai ta duba daya daga cikin dakunan. Akwai farin kyalle da aka rataya a bango, kuma a tsakiyar kyallen akwai alamar jan giciye a zane akarkashin giciyen sai taga wasu rubutu da harshen Vietnam. Sai ta leka ta kofa domin ta iya karantawa: "Allah yana kaunar duniya"

Abin ya ja hankalin ta ta shiga ciki. Mutanen da ke ciki suna wakar da bata taba ji ba, sai wani mutum ya tashi yayi magana da harshen Vietnam, kuma Mai ta saurara a hankali. Taji dadin abinda ya fada da yake bayani gameda Allah Mai kulawa, wanda yake kaunar mutane maimakon tsoratardasu ko yi musu danniya. Tana so ta kara samun bayani game da wannan kungiya da irin wannan bakon koyarwa tasu, amma bata da niyyar barin addinin da ta koya daga iyayenta.

Ta ga Allah da yake kaunar duniya a zaman wani karin abu da ya kamata tayi wa sujada, akan karin na kakanninta da kuma gumakansu.

Bayan fiye da shekaru biyu a cikin sansanonin gudun hijira na Hong Kong, daya daga cikin abokan Mai ta kaita ganin wata boka. Ta zauna a gaban matar da fatar zata iya gaye

mata ko yaushe ita da danuwanta zasu sami ficewa daga sansani zuwa yanci.

Tsofunar ta duba cikin idanun Mai sai ta dauki hannayenta duka biyu. "yawwa, Na gani yenzu. Kina da saurayi. Mai ta rude. "A,a, bani da saurayi" boka ta nuna damuwa "Yawwa" tace tana kada kai da sauri "to wannan saurayi ne daga rayuwarki mai wucewa, wanda ya biyo ki zuwa wannan rayuwar".

"Yana biyoni" Inji Mai, tana nuna shakka daga bokar zuwa kawarta tana zanton cewa matar na gaya mata wai aljanu na binta. "me yakeso?" Yaya zanyi insa ya rabu dani?" "Lallai ne ki tafi gida kiyi masa sujada. Kiyi addu'a ki roke shi ya rabu da ke" wannan ba shine na farko ba da ake gaya wa Mai cewa tana da aljanu. A lokacinda take yar shekaru bakwai. Mai tayi rashin lafiya kwarai. Zazzabi mai zafi ya ji mata a jiki, kuma har cikinta baya iya rike abinci ko ruwan sha. Uwarta ta kirawo kawun ta, wani boka, domin yayi tsafin fitarda aljanu da ke kawo mata rashin lafiya. Kawun ta ya buge ta da sandan rodi, cewar wai zai tsoratar da aljanin da rashin lafiyar su fice daga gareta. Mai tayi ta kira azo a taimaketa amma iyali suka danne ta a yayinda yake ta yimata duka. Daganan sai kawunta ya kama gashin kanta ya ja ya buga kanta da karfi a jikin karfen gadonta wai yana kokarin tifarda aljani daga cikinta" kuma yana rike da wani karamin karfe a hannu wanda yake sukarta dashi a fatar jiki domin jan hankalin aljani ya fice daga cikinta.

Babu wani kokarinsa da ya zama da nasara; Mai taci gaba da fama da rashin lafiya. A karshe uban ya kaita asibiti. Bayan yan kwanaki na shan maganin da likita ya ba ta, rashin lafiyar Mai ya tafi. Daga baya Mai tayi mamaki ko me yasa maganin da tasha yafi boka karfi. Yanzu kuwa tana tunani ko ita wannan boka mai duba ko gaskiya take fadi shin wai amincewa da wannan "saurayi" zai rinjayi aljanin ya rabu da ita?.

Mai ta tafi babbar haikali na addinin Bhudda a cikin sansani

tayi sujada yadda takan ga iyayenta na yi. Ba ta da wani karfin zuciya game da bayanin ita boka maiduba, amma kuma ba ta so tayi sake, musamman idan wannan "saurayi" zai hana ta samun visa da zai kai ta ga yanci. Ta kunna turaren wuta kuma ta roki aljanin ya rabu da ita.

Amma karin addu'arta akan bagadin karin jin rashin salama ne agareta. Acan cikin birnin ranta, ta sani damuwa da take ji ba shi da nasaba da batun duniyar aljanu. Mai tanajin zaman cikin sansanin yan gudun hijira tamfar wani tarko ne, ta kosa ta fice. Fadace fadace a kullum domin kawai a zauna kuma a ci abinci ya dameta, kuma fara'ar ta da aka santa dashi ya shude ya zama damuwa da takaici. Ta kasa gane irin wannan bakinciki da ya kafa tushe a cikin zuciyarta. Tana begen wani abu dabam kuma tana tunanin ko tafiya zuwa kasa mai yanci zai cika mata wannan begen da take ji a ranta.

Washe gari sai ta sake samun kanta tana wucewa kusa da majami'a. sake ganin wannan alamar giciye game da kaunar Allah, sai ta sake tunani wai shin wanene ne shi wannan Allah kuma me yasa yake "kaunar duniya" ita ma yana "kaunarta?".

Tana shiga ciki, ta dubi litattafai ajere sai ta zaro mafi girman a cikinsu, da fatar littafin zai gaya mata wani abu game da wannan Allah mai kauna. Da budewa sai ta karanta, "A cikin farko Allah ya halicci sama da kasa......"

Wannan ai littafin tarihi ne, in jita bayan ta karanta karin layuka. Taki jinin darasin tarihi a aji a makeranta domin irin shekaru da watanni da wurare da mutane da ake haddacewa. Sai tayi maza ta rufe littafin ta mayar a gurbinsa. Taci gaba da dubawa sai ta zaro littafi mafi kankanta ajerin, wani littafi mai rufin fata gwanin kyau. Ta bude ta duba farkonsa ga jerin sunaye masu yawa kuma sai ta fara karantawa. Labarin wani namiji da matarsa mai juna biyu. Amma fa wannan jaririn a fili yake cewa na musamman ne, domin akwai tauroro na nuna wannan al'amari, kuma manyan shehunnai sunzo sun marabce shi zuwa duniya.

Wanene wannan jariri? Tana mamaki. Wanene Yesu?

## YIN GUDU ZUWA GA ALLAH DA KE KAUNARTA.

A wannan lahadi Mai ta koma cikin dakin taro, inda wani mai wa'azi ke magana game da ikon Allah "Shaidan, in ji pastor baya tsoron kome kuma baya tsoron kowa sai guda daya kawai. Yana tsoron Allah. Duk inda yake baza a sami Shaidan ba".

Idanun Mai suka fadada. Tana tunani ko shin mai maganan yana da masaniya game da batun wannan saurayi nata na rayuwar da aka ce yana biyo ta. Mai tana so ta bada gashiya ga Allah daga jin wannan wa'azi. Batason batun aljanu abinda ya kawo mata razana da azaba tun tana karama ita dai salama take nema.

Lokacinda pastor yayi kira ga masu son tuba a karshen wa'azinsa, Mai ta garzaya gaba. Bata san sharudan ba, amma ta sani cewar tana so tayi wa Allah sujada, Allahn da Shaidan ke tsoro, Allahn da ke kaunar ta wanda kuma zai yantar da ita.

Daga wannan lokacin zuwa gaba duk lokacinda Mai taji tsoro a ranta galibi, a yayinda take kwance akan gado, tana jin masu yin fada a waje sai tayi addu'a ga Allah. Pastor ya gaya mata cewa Shaidan yana tsoron karatun maganar Allah da take yi. Saboda haka taci gaba da yin karatu a kullum.

Yawancin mutane da ke cikin sansani sukanje haikalin addinin Bhudda, kuma Mai takan tafi tare dasu har bayan ta tashi a gaban majami'a, Tayi tunani, amma kuma ai akwai hamzari a ba da hadaya ga gumaka, kila ya kara taimakawa. Har yanzu tana da wasu gumakai a cikin bukkarta, kuma kowace rana takanyi addu'a ga Allahn Krista da kuma allolin nan nata. Idan addini daya yana da kyau, a tunaninta, to ashe guda biyu zai kara fin yin kyau. Sauran yan sansani ma suna yin haka, sukan zabi bangaren da suka fi so na addinai

dabam dabam da ke cikin sansani.

A wani lahadi kuwa sai pastor na Krista yayi magana akan batun bin wani Allah ko bin wasu addinai dabam. yace dole ne Krista yabi addini guda daya tak kuma ya manne wa Allah mai gaskiya shi kadai bayan sujada Mai ta dawo cikin bukka ta zubar da dukan gumakanta.

Wasu daga cikin bhudawa suka yi kokarin su hana ta, amma Mai ta ki, idan Allah yana so ta bishi shi kadai, zata kawar da dukan alamu na addinin ta na baya.

## KA YI AMFANI DA NI KAWAI

A wani lahadi, jim kadan bayan ta watsarda gumakanta, anyi wa'azi game da mutuwar Yesu akan giciye. Ya bi fansar zunuban mu. Mai ta sake fita zuwa gaba. tana fahimtar ta ta farko na tsananin zurfin zunubanta kuma tana tuba domin wannan. "Ka gafarta mani, ya Allah' tayi addu'a. ka yi amfani da ni ta dukan hanyarda kake so, kuma ako ina da kake so. Kayi mafani dani."

Ko da shike kalilan ta sani game da Littafi Mai Tsarki ko kuma game da koyarwa ta Krista, amma sai ta fara yin magana game da haka da kowa a cikin sansani.

Ta cigaba da karanta Littafi Mai Tsarki da anniya kuma Rubu Mai Tsarki yabi da ita tana kara samun sani. Karin koyonta karin yin shaidarta domin Kristi.

Neman son sanin abinda kanwarsa ke ciki, Hong ma ya halarci wasu tararruka na majami'ar cikin sansani. A hankali shima ya zo ya karbi Kristi, amma bayar da kansa baiyi zurfin na Mai ba. Shi yafi sa gabansa akan samun yanci, na fita daga sansani zuwa cikin wata kasa inda zai sami yanci. Ya zana shirye shirye da dama a zuciyarsa na yin aiki da fara kasuwanci ya zama maidukiya. Yana tunanin ko zama Krista zai taimaka masa ga samun visa zuwa Turai da sauri sauri.

A cikin majami'a Mai ta gamu da wani mutum da ya girmeta da shekaru goma kuma suka kulla abota. Shi ma yana jiran

samun wucewa zuwa Turai, da fatar kafa kasuwanci kuma ya kudance da sauri. Da yake suna kara shakuwa da juna sai Mai ta fara kwaikwayon wasu daga cikin abubuwan da yake jin sunfi dacewa. Kwadayinta ne karanta maganar Allah yayi sanyi, kuma niyyar ta na yin addu'a ya bushe kayau. Tunanin ta yafi karkata ga yadda zata kashe kudinta idan ta sami yanci, kuma tana yin addu'a ne kawai najin cewa wannan yakai ga Yesu ya karbeta zuwa samaniya a lokacin da ya dawo.

Addu'oi masu karfi daga zuciyarta da suke fitowa daga birnin ranta duk sun bace. Yanzu galibi ma takanyi addu'a ga Allah domin samun fita daga sansani kuma ya kaita ga yanci. Da ita da saurayinta sun yi maganar aure, kuma Mai tana so ta auri wannan mutumin, amma tayi tunanin cewa shekarunta ashirin bai isa tayi aure ba.

Watarana da dare, tana kwance akan gado, Mai taji wata murya. Bazan barki a baya ba, muryar ta gaya mata, idan na sake dawowa zan dauke ki tare dani. Mai ta farka amma da alamar abinda take ji dabam ne; muryar kukan zafin ciwo.

Kinji wannan kuka da akeyi? Abin da kamar Ruhu Mai Tsarki na yi mata magana a cikin zuciyarta. "I" Mai ta amsa "menene abin? Wannan shine kukan wadanda ake bari a baya. Wannan shine kukan zafin ciwo da azaba.

## "BARI MUTAFI ....WAJE DAGA SANSANI"

Washe gari, Mai ta kawarda amajarta ta Ruhaniya a gefe. Yin adduointa da anniya suka dawo mata kuma a yanzu bukatunta sunfi gaban yin addu'a domin arziki da tikitin tafiya Turai. Ta fara yin addu'a domin iyalinta a can gida Vietnam da kuma Kristocin da ke cikin kasarta wadanda suke shan wahala domin Kristi.

Watarana a yayinda take karanta Littafi Mai Tsarki ta bude Ibraniyawa 13:12-15, domin wannan Yesu kuma domin shi

tsarkake jama'a ta wurin jininsa, yasha radadi a bayan kofar birni. Mufa bari mu fita zuwa gareshi a bayan sansani, muna dauke da zarginsa gama daga na bamu da madawwamin birni amma muna bidan wanda ke zuwa. Ta wurinsa fa bari mu mika hadaya ta yabo ga Allah kullayaumin, watau, yayan lebunan da suke shaida sunansa.

"Bari mu tafi gareshi, a waje da sansani" Kamar ma kalmomin na yiwo tsalle ne daga cikin shafin da aka rubuta su, su shiga lamirin Mai. Tana mamakin gaske game da wannan kira da Allah ya sa a cikin zuciyarta; ki koma Vietnam. Kiyi bishara ta acan. Gaya wa wadanda aka bari a baya a yanzu suyi kira cikin sunana. Mai ta sani cewa bautawa Kristi a Vietnam zai zo ne da tsada. Ta sani idan ta amsa kiran Allah za ta sha wahala.

Amma tana so ta tafi. Ta gaya wa Allah zata yi dukan abinda ya umurce ta, idan yana cewa ta koma Vietnam, to ashirye take ta koma. Kuma ita tasan irin zurfin duhun kai da yake Vietnam; ta ganshi a cikin nata iyali. Lokacin da take girma, iyalin ta sun ajiye wani jan bagadi da tuluna guda uku da ake kona turaren wuta a ciki domin yin sujada ga mutane uku da suka rigaya suka mutu watau kakanta, da da kakan ubanta da kakan kakan kakanta.

Idan ubanta ya mutu, iyali zasu cire tulun turaren wuta mafi dadewa a sa wani sabo a madadinsa. An koya wa mutanen Vietnam cewa rohanai suna ko ina, kuma kamar yawancin bhudawa a can, iyalin Mai sunyi iya kokarinsu su kwantar musu da zuciya.

Sukan yanka kaza ko alade suyi hadaya sai kuma susa abincin akan bagadi. Suna yin surkulle suna gayyatar matattun kakanninsu wai su zo suci abinci, da fatar samun taimakonsu. Mai tana begen shaida gaskiya ta maganar Allah ga iyalinta da saura da suke zaune a cikin mugun duhun kai a Vietnam.

Zama na gaba nayin taron Krista, Mai tace tana da bayani

da take so tayi. Ta tashi tsaye tana murmushi "na ji sako daga Ubangiji" in ji ta "ya kanyi mani managa".

Ta dubi dakin da kuma mutanen da yanzu sun zama abokanta, kamar iyali. "Allah ya kirani da na koma Vietnam yana so na shaida kaunarsa ga mutanen can, a gaya musu gaskiya.

An sami amsa daga bakin masu bi akan kari amma ba irinn amsar da Mai ta zata ba. Inji wani mutum. "wannan muryar shaidan ne!"

"Wannan ba daga Allah yake ba" inji wata tsohuwa, tana rufe Littafi Mai Tsarki nata da sauri. "Allah ne ya kawo ki Hong Kong, kuma Allah zai isar dake ga yanci lafiya zai sa kiyi albarka domin ki iya taimakawa iyayenki. Allah bazai so ki koma Vietnam ba"

"Idan kika koma can, zaki sha wahala" in ji wani "Na sani na rigaya na gani. Shan wahala zai iya sa ki juya wa Allah baya. Ba zai taba ce maki ki koma can ba".

Mai ta dubi saurayinta, tana fatar taga murmushi da goyon baya. Ya juya mata baya ya fice daga dakin. Sa'adda dayawa a cikin majami'ar suna kokarin rinjayar Mai ta yi watsi da wannan ra'ayi, wanta bai gamsu da yi mata maganar baki kawai ba, da ta dauka ma Hong wannan maganar marinta yayi a fuska.

"Me ya sa kike tsarta miyau akan mafarkin ubanmu?" ya tambaya. "Yayi tattali na tsawon shekaru domin ya kawo ki a wannan matsayi na zuwa bakin gacin samun yanci. Yanzu zaki zubar gabadaya? Ke zaki sa kafa ki tattaka zukatan iyayenki? Kada ki kara yin batun komawa kuma! ko kalma guda!"

Mai tayi mamakin yadda dan'uwanta zai yi mata haka, da kuma yadda wani Krista zai ki batun bukatarta na shaida bishara. Tayi addu'a domin samun hikima da karfin halin yin jimiri domin ta kaunaci dan'uwanta duk da kiyayyarda yake yi. Tana da karfin zuciya game da kira da Allah yayi mata,

amma tana addu'a domin saura su fahimci wannan kirar kuma.

Duka da Hong yayi mata ba shine yafi zama cikas a gareta ba. Abinda tafi jin zafinsa shine yadda saurayinta ya juya mata baya domin wannan. "Allah ya fito da ke daga Vietnam" ya gaya wa Mai, "me zai sa yaso komawarki can? Ba zaki tafi ba!"

Da ya ga ba zai iya rinjayar ta ba, sai ya rabu da ita. "bazan iya auren matarda take sadaukar da burin ta na zaman duniya ba," ya gaya mata "Allah ya kawo ki har nan, kuma wannan zai zama rashin daraja Allah da kuma iyalinki idan kika juya kika koma".

"Ina da buri" Mai ta gaya masa da murya mai cike da roko da hawaye a idanunta. "Yanzu Allah ya bani sabon buri. Ina mafarkin gayawa mutanen kasata game da kaunar Kristi. Ina so in gaya musu basu da bukatar yanka dabbobi kuma ba, an rigaya an yi musu hadaya ko!"

"Mafarkan mu sun bambamta, sa'annan, yace batun tsakaninmu babu shi kuma. Mai ta zuba masa ido yana tafiyarsa hawaye na zubo mata. Da irin abincin nan da baya isa, da kuma yanayi mara kyau na sansani, lafiya bata ishi Mai ba. Amma matsayin ta na Ruhaniya na kara karfi. Ko da shike saurayin ta yayi watsi da ita kuma majami'arta na shakkarta, bata da shakkar sanin abinda ya kamata tayi Allah yana kiranta ta koma Vietnam.

## SUNA DAYA TAK DAGA CIKIN JERIN SUNAYE

Mai ta shirya taro a ofishin sansani, inda zata gabatarda neman iznin tafiya na komawa Vietnam. A cikin dare kafin washegarin taron, ta yi awanni barci bai dauke ta ba, tana tunani game da wannan shawara da ta yanke. Tana ta mamakin yadda mutane kalilan ne a cikin sansanin suke goyon bayanta. Ta yi addu'a ta sake jaddada bada kanta ga

Allah cewa a shirye take ta tafi duk inda yake so, kuma zatayi dukan abinda yake so. Taji cikakkiyar salama har ma da zumudi da tayi tunanin zata je ta gaya wa mutanen Vietnam game da kaunar Yesu.

A karshe barci ya kwashe ta, kuma a cikin mafarkinta taga kanta tana komąwa Vietnam, amma ba ita kadai bace. Akwai wata mata da ke tare da ita da kuma wani namiji a cikinsu. Mai taji a jikinta sosai cewa wannan tabbaci ne daga Allah cewa ba zata koma ita kadai ba.

Washe gari da ta kama hanyar zuwa ofishin sansani, ta nuna bata da wata shakka game da wannan shawara da ta yanke. Ta bude kofar ta nufi teburin jami'in.

Jami'in dake wannan teburin ya kalli wannan budurwa mai ziyara, hadin ban tausayi da kuma rudewa a fuskarsa. "kina so ki koma?" "I"

"Tun yaushe kika zo nan Hong Kong?"

"Kusan shekaru biyar".

"Kinzo kusa da karshen lokacinki anan.

Mai yiwuwa ki sami visarki ki fice daga nan a cikin yan watanni. Daganan zaki iya tafiya Amirka ko Australia. "Kada ki karai a yanzu."

"Ban karaya ba". Mai ta amsa. "Bani da sauran sha'awar tafiya kasashen yamma. Ina so na koma kasata". "Bamu cika samun dayawa da ke son yin irin haka ba. Alhali ma dai sun rage yawan kudin da ake biya na takardar neman yin hakan, domin babu wanda yake nema.

"Kin san abinda wannan yake nufi sarai ko?". "Na sani sarai," Mai ta amsa da karfin zuciya "amma Allah ya kirani da in koma" "Allah ya kiraki?" ya tambayeta da alamar mamaki "To naji" tunda hakane, za a janye takardar ki na neman visa, kuma a rufe fayil naki. Zai zama kamar ma ba ki taba zuwa nan ba...kamar ma shekaru biyar da suka wuce ba su taba faruwa ba."

"Kin san abinda wannan yake nufi sarai ko?". "Na sani sarai," Mai ta amsa da karfin zuciya "amma Allah ya kirani da in koma" "Allah ya kiraki?" ya tambayeta da alamar mamaki "To naji" tunda hakane, za a janye takardar ki na neman visa, kuma a rufe fayil naki. Zai zama kamar ma ba ki taba zuwa nan ba...kamar ma shekaru biyar da suka wuce ba su taba faruwa ba."

"Nasan da haka bazan tafi kasashen yamma ba" "kuma kin sani cewa gwamnatin Vietnam basu cika son karbar mutane masu komawa ba," in ji shi. "Musamman wadanda suka fita ba tare da izni ba".

Ina sane da wannan" Mutumin ya kalleta sosai na wani lokaci, yana harararta. Daganan sai ya zaro takardar cikawa. "Zan bukaci katin shaidarki ta sansani" Mai ta mika masa katin, kuma ta karbi alkalami daga hannunsa ta cika takardar. Sai taji wani irin gamsuwa na mamaki da kuma farinciki a cikin zuciyarta, kuma ba tare da bata lokaci ba tasa hannu a takardar, ta hakura da wannan damar tata ta samun yanci zuwa kasashen yamma.

Mutumin ya zaro wasu takardu. A bisa takardar an rubuta wadannan kalmomi KOMAWA VIETNAM. A hankali kuwa ya rubuta sunan Mai akan layi na farko babu sauran wasu sunaye akan takardar.

Lokacin da Hong ya sami labari Mai tasa hannu a takardum mayar da ita gida, ya sake yi mata duka. Wata kawa Krista, Malama Xuyen ta gaya wa Mai cewa tana hauka. Amma da Xuyen ta sake ganin Mai washe gari, labarin ta ya sauya. "Ba kya hauka" ta tabbatarwa Mai "Kiyi hakuri don na gaya miki haka".

"Me ya faru?" Mai ta tambayi kawarta. "Jiya kince ina hauka zan koma Vietnam, kuma yau sai yazama shawara ce mai ma'ana?" Ubangiji yayi magana dani jiya da dare," Malama Xuyen ta gaya mata. "Kuma ya gaya mani cewa nima da bukatar na koma Vietnam domin shaida maganarsa ga mutanen Vietnam.

Mai na farinciki, jin cewa ba ita kadai zata yi tafiyar ba. Ta tuna da mafarkinta inda wata tayi tafiya tare da ita. Akwai kuma namiji a cikin tafiyar bisa ga mafarkin kuma sai take ta tunanin ko wane mutum ne Allah yake shiryawa ya tafi tare dasu.

Malama Xuyen ta tafi ofishin sansani ta cika irin takardun da Mai ta cika. Sunanta ya zama na biyu a jerin sunaye. Bayan yan kwanaki, wani mamba na karamar majami'ar su, Mallam Truong, yazo wurin Mai yace shima yaji kiran Allah na ya tafi Vietnam. Amma zama a Vietnam yana da wuya" In ji shi.

"Yaya zanyi in rayu acan kuma inyi wa Allah hidima?" "Kada ka damu" in ji Mai "Allah zai dubi al'amarin duka" Ayayinda Mai ke shirye shiryen tafiya na komawa, tana lura Allah na buda wasu hanyoyi kuma yana sarrafa batun tafiyar. A shekarar 1994 ne, kuma ta kusan cika shekaru biyar kenan a Hong Kong. Lokacin da mambobin majami'a suka taru domin yiwa masu bin nan guda uku ban kwana, dayawa daga cikinsu dake tsoro sunyi kokarin su rinjaye su kokari na karshe da su yi zamansu.

Hong ya raka Mai da sauran zuwa babbar kofar karfe ta shiga sansanin yan gudun hijira, "Yaya zaki yi irin wannan?" ya sake tambayar Mai "Na rubutawa baba nagaya mashi game da wannan batar hankali da yasameki. Bayaso ki koma. Yana so ki sami yanci. Kinsan irin tashin hankali da zaki samu a Vietnam? Ba a karbar Krista a can. Ana tsanantawa Krista, ana kama su, ayi musu duka, Mai, ba a makara ba har yenzu kina iya sauya shawararki."

"Shawarata a yanke take" ta gaya masa. Kawo ki nan da nayi kamar mafarki nakeyi" in ji shi a fusace. "wa ya kula dake shekarun nan biyar da suka shige? Wa yake kare ki lokacin fadace fadace a cikin sansani? Wa yake tabbatar da sai kin sami rabonki na shinkafa lokacin da wasu suke so su kwace? Ina ma da Trung ne yazo tare dani a maimakonki. Bazai wulakanta ni ba ko babanmu yadda kika yi Trung yana da ban

girma, yaya zaki yi irin wannan?

Mai ta dubi dan'uwanta da bakinciki. "Ina iya yin haka domin Allah yana kirana" in ji ta "kai kana so ka sami yanci, ka tafi kasa mai yanci. Amma baka ganin cewa akwai abubuwa mafiya muhimmanci da suka fi yancin siyasa ko kuma tara dukiya? Wa zai gaya wa iyayenmu game da Yesu? Wa zai gaya musu yadda zasu yi su sami yanci, yadda zasu sami tafiya aljanna?

Allah ya umurce ni da nayi wannan, kuma zanyi, maiyiwuwa bazan taba yin arziki kamar ka ba, amma ni inayin abin da Allah ya umurceni da nayi. Watarana, Hong, ina fatar zaka zo ka fahimta". Wanta yana kallo da jiki a mace suka hau wata karamar farar mota da zata kaisu filin jirgin sama. Bai daga masu hannu ba.

Wasu Krista kuma suka yi ta dubansu ta babar kofar karfe ta shiga, hawaye na zuba ta sadu da wasu Kritoci a Van Dong suka fara yin taro, suna shiga cikin itatuwa a jeji a boye domin kada yan sanda su san da taronsu. Mai taji kiran Allah domin neman batattun tumaki, kuma sai tafara fadada yin bishara. Har yanzu tana zaune a gidan iyayenta amma takan yi tafiya akai akai domin yin tararruka. Ba da jimawa ba kuwa aka kafa majami'a a Van Dong, amma a yayin da majami'ar ke girma, haka kuma tsanantawa manbobi na karuwa.

Da yake babanta ya gane da takawar da Mai takeyi ta shiga jeji da mambobi sai ya bata aiki agida domin hana ta samun damar fita zuwa yin ayyukan majami'a na wannan sabon addinin nata, amma a karshe dai ya ba da kai. Yakan barta ta tafi majami'a amma baya bari ta tafi wajen yin taro ko wata hidima ta musamman; ko kuma yin hulda da sauran masu bi. A lokacinda Mai taci gaba da zuwa tararruka da ake hanata da kuma cin gaba da yin ayyukanta, babanta ya kore ta daga gida bayan yan kwanaki kuma ya barta ta dawo, amma jim kadan kuma aka koma gidan jiya.

Yan sanda suka fara zuba wa Mai idanu a kowane motsi da tayi. Batun aikinta na Krista yana zagayawa, sai yan sanda

suka fara matsa wa uban mai cewa a taimakesu kafa wasu shaidu da zaisa hukuma ta tsareta "ina takan tafi?" Suna ta tambaya akai akai. "da wanene take saduwa wajen taro? Me suke fadi? Kuma me yasa kake barin diyarka tayi wadannan?" A yayin da watanni na wucewa, matsi kuma na karuwa. A kwana a tashi sai hukuma suka ga dai babu gamsuwa ta wajen ziyartar uban Mai a gida.

An umurceshi yazo caji ofis kuma aka gaya masa idan bakasan yadda zaka tafiyarda diyarka ba", "to mu zamu yi" Jin tsoron kada a taba lafiyarsa, da ta diyarsa, sai ya dokace ta sau da yawa da ta zauna a gida babu fita.

"Ba zaki tafi ba", baban ke gaya mata. "Kinsan abinda zasu yi mani? Da abin da zasu yi maki?" da farko, Mai ta nuna cewa zata tafi ganin abokai ko kuma tayi wani aiki dabam.Amma da yake tana kara yin karfin zuciya game da shaidarta, sai ta kara fitowa babanta a fili "Zan tafi yin aikin Allah" ta gaya masa a cikin sauki.

Ganin ubanta yana gaba da ita wani abune kusan ma da ba zata iya jurewa ba. Addu'ointa suka fara zama da anniya kwarai. Allah, in ji ta, a wani dare, ni zan iya yin kome dominka. A shirye nake na tafi kurkuku dominka. Ni ina iya mutuwa ma dominka, idan haka shine nufinka. Amma idan ka yarda, Yah, Allah, kada ka bari ubana ya tsananta mani. Abu ne da bazan iya jurewa ba.

Amma tsananin bai daina ba. Bayan wasu shekaru, Mai ta fahimta cewa Allah ya yi amfani da wannan lokaci a zaman filin koyo idan zata iya juriya a karkashin ubanta masoyi, to babu wani tsanani kuma da zai hana ta yin aikin da Allah yakira ta tayi.

## SAKE KIN KARBAR YANCI

Ananan ananan sai Mai ta gamu da wasu ma'aikatan mishan daga Amirka a Vietnam. Da suka ga irin kwazonta da

ba da kanta, sai suka dauki nauyin yin shiri na t a tafi makarantar koyar da Littafi Mai Tsarki a can Amirkar. Wannan wata dama ce na ban mamaki, mai tayi shekaru biyar a cikin sansanin gudun hijira na Hong Kong tana jiran samun tafiya kasashen yamma. Yanzu, bayan ta dawo Vietnam, ana gayyatarta ta tafi Amirka tare da daukar nauyin komai!.

Lokacin da Mai ta shaida wa iyayenta game da wannan dama da ta samu, baban ta yayi na'am sosai. "Wannan wata damace muhimmiya" inji shi. "Iyayenki yan Amirka suna so su shirya maki tafiya Amirka inda zaki sami yanci kuma ki sami ilmi. Wannan labarine maikyau! lallai ne ki tafi"

Amma al'kiblar Mai ba ta sauya ba sai ta sake karanta Ibraniyawa 13:12-15 ayoyin nan da Allah yayi amfani dasu domin kiranta zuwa Vietnam. "Matsayinta game dasu da ke waje da kofa a kasarta bai yi sanyi ba. "ina so nayi aiki a cikin Vietnam," ta gaya wa iyayen. "Allah yakirani ne domin nazo mai nayi aiki da mutane na anan".

"Bakijin wannan shine hanyar da Allahnki yake so ya taimake ki? Ubanta ya tambaya" kin tafiyar ma ai haukane!".

Amma Mai ta zabi ta zauna a Vietnam maimakon tafiya Amirka ta halarci wani koyaswa mai zurfi a Saigon. Ba ta damu da a ina ne ta sami koyarwa ta tauhidi da yin bishara ba; bukar ta kawai shine na ta yiwa Allah hidima kuma taga cewar yan kasarta sun sami zuwa gareshi. Ma'aikatan mishan din sun bada yarda ga taimaka mata da kudin makaranta a saigon, amma Mai tayi godiya tace a bari. Ta sani Allah zai biya mata bukata idan har wannan kwas din shirin sa ne.

Tayi wata shida tana zaune a wani gida a kudancin Vietnam bata zuwa ko ina saidai in zasu tafi aikin mishan a kauyukan kasar.

Da yake ita yar Arewacin Vietnam ce idan tashiga gari atitunan Saigon, za a iya gane ta kuma a tambaye ta takardun ta na iznin shigo wa kudu da yaketa shiga ba tareda

izni ba, kuma ko magana tayi za a gane ta daga lafazinta na arewa da ya sha bambam da na kudu. Sabo da haka ta zauna acikin gida har na tsawon watanni shida a mike.

Wasu lokuta takanyi ta duba titi ta taga tare da bege idan taga mutane suna kaiwa suna kawowa, tana sha'awar ta dan fita ta taka kamar kowa da ke kewayeda ita. Amma tayi zaman ta.

Kwanaki na kara tsawo, darusa da suke koyo kuma da tsamari, kuma dukan abin da akeyi a cikin sirri ne. sukan yi sa'oi da yawa kullum na yin addu'a da sujada, suna nazarin maganar Allah, kuma suna daukan darusan koyon aikin pastor.

## SO NA KWARAI GA KABILU

A cikin wannan kwas da suka yi akwai bayani game da mutanen kabilu na Vietnam. Mai ta girma da tunanin cewa dukan tsirarun kabiluna cikin Vietnam jahilaine, mugayen mutane, wadanda suke bin al'adun kabilanci na camfe camfen karya, da kidahumanci. Da ta sadu da Krista wandanda suke aiki a cikin yan tsirarun kabilun, Allah ya shirya mata a zuciyarta so na kwarai domin jawo su ga Kristi.

Vietnam tana da fiye da rukunonin tsirarun kabilu guda hamsin, kuma ana nuna masu tsanani ainun. Domin a samu a hade al'adun, gwammati ta haramta buga ka da wace irin takarda ce da ko wane irin harshe na tsirarun kabilu: sai kawai da harshen Vietnam ake da iznin buga takardu. Ana yiwa tsirarun kabilun ba'a ana raina su, kuma sukan fuskanci tsanani tun kafin masu zabi bin Kristi.

Domin isa ga wadannan mutane, akan shirya rukunan masu koyon aikin pastor su fitasu goma sha shida suna hawan babura guda takwas zuwa cikin karkara na tuddan tsakiyar ksar. Tafiye ta fiyen na da wahalarwa. A lokacin rani, kura na da yawa, yana da wuya a hangi fiye da kafa biyar a

gaban kan babur. Da damina kuwa, hanyar takan zama kamar gilashi da aka zubawa ruwa domin tsananin santsi. Don kau cewa yan sanda, rukunanin kanyi yawancin tafiye tafiyen da dare, kuma ana samun hatsari, a wani sa'i babur din Mai ya bugi kare, kuma a lokacinda ta farga da abinda ya faru, jini na zuba a fuskarta, kafadanta, giyoyin ta da kuma kai, ramammen kare Mai kaunrin rawaya kuwa ya mutu.

Tabbuna a jikunansu suka zama alamu na gwagwar maya ga wadannan shugabannin matasa, kuma sukanyi wasa game da tabbunansu a zaman wani "kambi" sukan zuba gishiri acikin rauni domin ya kashe kwayoyin cuta, sai su daure sosai, kuma sai suci gaba da tafiya. "Zaki zami sauki" daya daga cikin matan ta gayawa Mai a yayin da take taimakawa wajen tsabtacewa da daura wa mikin bandeji bayan hatsarin.

Kuntuna da abinda pastor ya fada? Idan har baka sami wani tabo ba, to baka yi shirin yin aikin Kristi a Vietnam ba. To, Mai yanzu kama shirye kike.

## SABUWAR HALITTA A CIKIN KRISTI

Bayan kwai na wata shida. Mai ta koma arewa. Tayi aikin kafa majami'u tana koyar da shugabannin wurin, kuma iyayenta sunci gaba da matsa mata cewa ta daina cikin. A karshe ubanta ya kosa, yakira taro na dangin iyali baki daya, harda dangi na nesa, "kaka zamu yi da Mai?" ya tambaya, idanun sa masu neman shawara na zagayawa daga fuska zuwa fuska a cikin dakin. "tana fama da wannan amfi daga kasasen waje. Mun yi kokari mu kawar da ita daga ciki, mu rinjaye ta ta dawo ga hanyar iyalinmu. Amma taki. Zamu cigaba kenan da yin fama da rigingimunta, ko kuwa mu fitar da ita daga cikin danginmu?"

Da taji ubanta yana magana gaban Mai ya fadi kuma sai ta dubi fuskokin dangi da suka taru, mutane ne da ta sani kuma

tana kauna a ranta, sai tayi addu'a dominsu da suke cikin tattaunawa, kuma tayi addu'a Allah ya bata hikimar bada amsar tambayoyin su.

Kuma akwai su da yawa

Ta amsa ko wanne da nuna kauna da kuma hakuri har sai da tambayoyin suka kare. Wuri yayi tsit, kuma kowa ya sani lokacin yanke shawara yayi. Mai ta sake tashi ta tsaya a tsakiyar danginta domin tayi wani roko na karshe, tana zuba ido a fuskar ubanta. Tayi maza ta sake yin addu'a domin samun yin amfani da kalamun da suka dace.

"Baba" ta fara", ni ba zanyi musun Yesu ba, amma kuma ba zanyi musunka ba. Kana iya musum Allah na, amma ko kayi, zai cigaba da zama Allah, kana iya korata idan ka so, amma zancigaba da zama diyarka. Idan baka so ka kara ganina, yayi. Amma a cikin zuciyar ka, har yanzu ni dayar kace. Ko da ka koreni kuma kaki ka amsa ni diyar kace, ni zan amsa kai ubana ne. har abada kai ubana ne. kuma zan cigaba da kaunarka"

Bayan da aka jefa kuri'a, har yanzu Mai karbabbiya ce a cikin iyali kuma har yanzu tana yi wa Allah hidima. Daga baya a wannan ranar ubanta ya kira ta gefe. "Idan kina bukatar wurin kwana" ya gaya mata, yana kokarin boye damuwar da ke ransa, "muna maraba da ke a kullum".

Mai tayi wa Allah godiya domin danginta sun karbe ta, kuma taci gaba da yin addu'a da himma domin suzo ga bin Kristi kuma.

Kungiyar mishan da Mai ke aiki tare dasu suka cigaba da bata hoto. Ta sha tafiya zuwa saigon sau da yawa, domin samun Karin koyarwa a makarantar koyon Littafi Mai Tsarki, ko wace tafiya na nufin dogon tafiya a cikin jirgin kasa babur da takawa a kafa. Mai takan yi addu'a kafin kowace tafiya, kuma duk lokacinda suka kusato wurin da ake yiwa mutane bincike ko kuma tashar yan sanda. Bata da iznin tafiya na gwamnati kuma babu kwakkwaran dalili da take dashi

nagaya musu game da ziyarar ta zuwa saigon. Doguwar tafiya a cikin jirgin kasa yakan ba ta lokaci na yin tunari da kuma addu'oi, kuma yawancin tananinta sukan je ga ubanta ne. baza ta iya yin kome ba illa tayi addu'a domin cetonsa, kuma tana yin haka da anniya.

A wata tafiyar sai Mai ta sami sako cewa maza ta je gida "babanki bashi da lafiya kwarai" ka gaya mata "yana asibiti". Rashin lafiyar da aka gano yana dauke da damuwa da tsoro da razana a kowane harshe. Ciwon jeji, Mai ta tafi nan da nan zuwa gefen gadon ubanta ta zama mai kula dashi na cikakken lokaci. Dukan abinda yake so tana yi masa. Kuma a dukan lokaci tana yi masa addu'a kuma ta fara yi masa magana a hankali game da bangaskiya. Tana kashe lokacinta wajen karatun Littafi Mai Tsarki da murya ga babanta dake kwance akan gado. Wandansu abokan aikin ta suka zo ziyarar uban, kuma ya lura da irin damuwar da suke da ita. Sai ya sami kansa yana daina nuna damuwa gameda bakon addinin diyarsa amma yana damuwa game da batun ransa. Lokacin da wani pastor da ya taimaka wajen koyarda Mai ya zo ziyara, ya dade a cikin daki yana magana da uban Mai, a yayinda sauran masu bi suka taru a waje, suna addu'a domin bisharar da suke yi. Lokacin da pastor ya bar dakin, baban Mai ya zama sabuwar halitta a cikin Kristi.

Suka rungumi juna da hawaye da ya gaya mata yanke shawara da yayi na bin Kristi na ko da wani dan lokaci ne ya rage masa a duniya. "Yanzu ne nake ganin cewa gwamnati na majami'a tsanani" in ji shi yana gaya mata.

"A da, bana iya gani. Har na bari sunyi amfani ni da ni domin tsanantawa diya ta." Muryarsa ta kasa daukan nadamar da yake yi. Mai ta rungumi babanta ta gaya masa cewa tsananin da ya nuna mata shiri ne na Allah, wata hanyace ta jarra ba da kuma karfafa bangaskiyarta.

## DAUKAR KASADAR GASKE DOMIN KULAWA DA TUMAKI DA SUKE WARWATSE

Bayan da baban ta ya mutu, Mai tayi kukan mutuwarsa amma tana farin cikin cewa za su sadu watarana a samaniya. Kuma sai ta kuma ci gaba da aikinta na Krista da sabuntar hazaka. A 1996 kungiyar mishan da take aiki tare dasu sun shirya wata koyarwa ta Krista ta tsawon kwanaki uku domin shugabanni. Sa'adda mai keyin addu'a domin yin shirin wannan taro. Ubangiji yayi mata magana ta mafarki, kamar dai yadda yayi na komawarta Vietnam.

A cikin mafarkin, Mai tana tsaye a tsakiyar kurmin jeji "A ina nake?" ta tambaya. Wannan shine yankin tsirarun kabilu. Ina da Karin aiki anan dominki."

Yaushe zan tafi? Ta tambaya. :kuma babu wanda zai tafi tare dani domin yin wannan aiki?" Allah ya amsa tambayarta da alkawari, zan aika wani mutum, mayaki, ya tafi tare da ke."

Sai fuskoki da yawa suka zo cikin tunanin ta, mutane a cikin layi suna saye da kyawawan tufafi. Kowanne yana wakiltar kabila dabam da Mai zata yiwa hidima.

Bayan mafarkin da kuma kwas na musamman da suka je yi, Mai ta fara aiki da rukunonin kabilu akai akai. Tana hawan babur dinta, tana tafiye tafiye a cikin Vietnam, tana wa'azi babu iznin hukuma kuma tana dauke da sakon ceto. Awurare da yawa yan sanda sukan kafa wurin yin bincike. Sai su kafa itacen gwangwala suyi kofa akan hanya inda yan sanda ke tsayar da matafiya su tambayi takardu. Idan basu cika ba, sai a kama mutumin ko kuma a kalla su matsawa mutumin ya basu hanci kafin yaci gaba da tafiya.

Da yake ba ta da takardun iznin tafiya, kuma tana dauke da Littafi Mai Tsarki dake hananne, Mai takan kaucewa kofofin

bincike, takan kauce kan hanya ta bi ta cikin kurmin jeji duk lokacin da ta dauro tayi haka domin kaucewa wuraren bincike.

Tasan cewa gwamnati na sane da ayyukanta na Krista kuma sunanta yana cikin wadanda gwamnati ke nema. Akwai kasada sosai.

Wadanda suke kaucewa wuraren bincike na kan hanya ana iya harbinsu idan aka gansu. Wataran akan kama Mai kuma a saketa washe gari. Wateran sukan kwace mata Litattafi Masu Tsarki da take dauke da su. Wani lokaci Ubangiji yakan hana su ganin Litattafan da ke tare da ita. Mai takanyi murna duk lokacinda suka mayar mata da Jakarta da kayanta a ciki.

Wannan matashiyar Mai Bishara tagasaurin tashin majami'a a cikin tsirarun kabilu, kuma karfin halinsu ya zama mata da albarka a fuskarshan stanani. Su kabilun kamar tumaki ne da ke a warwatse, tayi tunani. Babu mai kare su sai Ubangiji da kansa.

Mai ta saurari yan kabilu suna gaya mata irin tsanani da suke sha kuma tayi kokarin karfafa su. An rataye wani tsoho aka yi ta dukansa saida igiyar ta tsinke, yafado kasa jinajina. Yan sanda sun tilasta wa Kristocin Hmong su kaura daga wani yanki na kasar zuwa wani yanki dabam, domin neman kadaita su daga yan uwansu. Kristocin da ke kokarin kaucewa yan sanda wani lokaci sukan bar dukan mallakarsu a baya sugudu su shiga jeji. Mai da wasu A wani kauye, Krista sun sami gayyata daga gidan wani mamba dan kabila wanda bashi da lafiya, kuma lokacin da Mai ta shiga bukkar saida tayi juriya ainun domin kada tayi amai, doyin ya baci. Iyalin suka tambaya ko ita likita ce, ko kuma ta kawo magani ne." Mu ba likitoci bane," Mai ta gaya musu, kuma bamu dauke da magani. "Amma munsan likita ma fi iyawa a duk duniya, wani wanda zai iya warkar da kai."

Suka yi addu'ar warkarwa domin mara lafiya. Bayan wata

daya, da ta dawo kauyen, mutumin ya kusa gama warkewa.

Wata na biye kuwa ya sami lafiya sosai." Mutumin yana dokin yayi magana da Mai, "inaso, ki taho tara dani", inji shi zan kaiki wajen mutane na. Amma akwai nisa daga nan, a can cikin kurmin jeji. Ba zai yi sauki ba, kuma ba zaiyi sauri ba. Lallaine kizo tare dani na tsawon kwanaki talatin."

Mai tayi addu'a game da wannan gayyata kuma taji amincewa daga Allah.

Ta yarda ta tafi tare da shi zuwa kauyensu, a wani lungun arewacin Vietnam. Kauyawan wuin suna cikin mugun talauci kuma ko wannen su yana da tufa guda kacal, wanda suke sawa duk shekara. Wadansu ma'aikatan Krista sun jijjigu da irin zaman jahilli da doyin da ke fitowa daga kauyukan. Akan ki karban wasu domin al'adun kabilunsu, wanda ya kawo rashin yarda da baki. Duk da haka mutumin da ya girma tare da su a cikin kauyen yayi gabatarwa, Aka yi wa Mai maraba. Jim kadan kuwa aka kafa Majami'a har tafara tashi. Mutumin ya gode wa Mai domin kawo Yesu a kauyensu. "Idan suka ga Kristi a cikinmu" tayi bayani daga baya, "sukan karbi' Kristi a saukake". Kabilar Hmong kuma sai ta sake shirya wata tafiya ta wata guda na hidimar bishara zuwa garesu. Tafiyar da wuya tare da tafiyar jirgin kasa na kwana guda da kuma tafiyar wani kwana daya a cikin motar fasinja mai cike da doyi, daganan kuma tafiyar rabin rana a wata mota, sauran tafiya kuma saida kafa. Turbar kan duwatsun akwai hawa da gangara ainun, lokacin damina kuwa santsi. Takun kafa guda cikin kuskure Mai zata sami kanta tana faduwa cikin kogi can kasan dutsen. Wani lokaci ma dole sai da rarrafe akan duwatsun da hannayenta da gwiwoyinta tana yakar kama abu da yatsun ta na hannu da na kafa tana dafewa sosai.

Yan sanda sun gaji sun hakura da hana taron Kristoci a wadannan kauyuka, hanyoyin da hatsari ainun. A wani kauye da suka iya kaiwa, sunyi wa iyalan Kristoci guda goma duka, kuma suka tilasta musu su kaura zuwa wani kauye a wani bangaren kasar.

Da Mai take shaida bishara ga Hmong, sai take ganin kari bisa karin ikon sauyi na maganar Allah. Da yawansu mashaya ne kafin su karbi Kristi, a yayin da wasu suke yin wata al'ada ta maita da ya kunshi shan jinin dabbobi.

Bayan karbar Kristi, ko dashike sun daina al'adan tsafi, kuma a shirye suke su fuskanci t sanani domin bangaskiyarsu. Sun bada gaskiya Yesu zai dawo ba da jimawa ba, kuma suna so su shirya.

Mai ta gane abin da suke so, kuma sai ta fara koyar da mutanen Hmong domin suyi shugabanci. Da yawa zasuyi tafiyar kwana biyu a kafa domin su isa wurin koyarwa. Babu Littafi Mai Tsarki a wasu kauyuka; a wasu kuwa. Kristoci su kanji samun albarka domin akwai Littafi Mai Tsarki guda daya tak da ake mora tsakanin iyali guda arba'in zuwa arba'in dabiyar. Wasu iyalai sun sayarda mallaka su gabadaya domin su tafi Hanoi neman Littafi Mai Tsarki guda daya. Amma har a can ma, basu samun Littafi Mai Tsarki da aka fassara a cikin harshen Hmong ba. A kowace ziyara Mai takan kai musu karin Litattafai Masu Tsarki a cikin harshen Hmong wanda masu aikin mishan da suke hulda sukan yi daba'i. Ta kanji dadi ainun duk lokacin da tagansu suna zubarda hawaye na nuna farinciki da yin godiya watau su Kristocin Hmong a yayin da suke rike da maganar Allah sau na farko a hannayensu.

Tafiye tafiyen nan masu nisa da wahalarwa sun tsotse karfin Mai. Har yanzu takan yi fama da jin kumallo garin tafiya, kamar dai yadda taji a cikin jirgin ruwa zuwa Hong Kong. Wataran takanyi mamaki, a yayin da take yakar kumallo dalilin da Allah zai kira ta zuwa yin bishara ta tafiye tafiye amma kuma bazai warkar da ita daga wannan kumallo ba. Takanyi yi kokanrin zama kusa da ba-haya a cikin jirgin kasa domin ta sani kumallo zai taso mata.

Takan kashe dogon lokaci tanagyara zaman kayan Litattafai Masu Tsarki da akan daure kuma aka dora aka babur lokacin da take haye wurare masu tabo. Kuma takanyi

tafiya na tsawon miloli a kafa, kuma kullum dauke da kayan Litattafai Masu Tsarki. Ta dinke sunayen Kristoci abokan huldarta na kasashen waje a bakin gefen tufarta domin kada yan sanda su gane idan aka kamata.

## WANI IRIN YANCI NA DABAM

Yawanci takanyi tafiye tafiye ba tare da samun wani tashin hankali ba, amma fa Mai ba bakuwar yan sanda bace. An kamata har sau goma kuma galibi akan ajiye ta daga yan sa'oi zuwa kwanaki goma sha biyar a tsare gun yan sanda. Kowane lokaci, sukan kwace Litattafai Masu Tsarki da take dauke dasu, wannan kuwa yana hana Kristoci yawan samun Littafin maganar Allah.Takan tuna abinda wanta ya fada a baya lokacin da take barin sansani a Hong Kong.

Shi kansa ma baisan cewa kalmominsa zasu tabbata haka ba, da kuma irin wahalar da zata fuskanta idan ta dawo.

"Kina wa'azi ba tareda izni ba! "yan sanda suka gaya mata. "Kundin Tsari na Vietnam ya alkawarta yancin addini, amma sai a wuraren da gwamnati ta bada izni a kafa wurin yin sujada kuma a lokacinda gwamnati ta bayar na yin sujada."

Akwai lokacin da yan sanda suka bata wata takardar amsa laifi wai asa hannu, cewa a gaskiya tasha yin wa'azi ba tare da ini ba.

"Wannan rahoto nakasasshe ne", Mai ta rubuta a karkashin shafin, ba tareda uffanba.

Kwamandan yan sanda ya matso gaba, da tunanin cewa a karshe dai ya karya lagon wannan Krista, kuma ta sa hannu.

Lokacin da ya karanta, sai ya yayyaga takardar guntu guntu. "Kina zaton mu wawaye ne?" yayi wa Mai tsawa.

Bayan wani kamu kuma, sai yan sanda suka yi kokarin tilasta mata ta sa hannu.

Munada yanci yin addini a Vietnan, sabo da haka ina iya gaskanta abin da na bada gaskiya a gareshi, ko da wane irin addini ne. A yayin da nake tafiya da Littafina Mai Tsarki, ban gaskiyata kenan. Lokacin da nayi managa da wadannan mutane (shugabanin Krista da suke daukar ra hoto) su masu bada gaskiya ne ko' saboda haka wannan ba wa'azi bane. Muna tattauna batun ban gaskiyar mune tare "amma a Vietnan". "Akwai yanci" in ji yan sanda mun killace a cikin akwati. Mu muke yanke shawarar wanene keda yanci wanene kuma bashi da yanci".

Yan sanda suka gayawa Mai ta rubuta rahoto game da ayyukan ta kuma ta sa hannu akan ba zata kara yin wa'azi kuma ba. Mai ta yarda ta rubuta rahoto, kuma sai tafara rubutun shaidarta. Ta rubuta yadda ta girma tana sujado ga kakanninta, yadda ta sadu da Allah a sansanin gudun hijira a Hong Kong kuma ta dawo Vietnan da kuma yadda ya sauya rayuwarta, ta rubuta shaidar rayuwarta gaba daya.

Lokacin da ta iso inda zata yi alkawarin daina yin wa'azi, sai ta rubuta wani sako dabam maimako: "Littafi Mai Tsarki Littafi ne da gwamnati ta bada izni ayi dabinsa (ba da yawa kwarai ba) kuma a rabar. A cikin Littafi Mai Tsarki ance mu bauta wa Allah, mu karan ta, mu shaida bishara. Nakanyi dukan abinda Littafi Mai Tsarki yafadi". Yan sanda suka karanta "shaidarta" sai kuma abin mamaki shine sun yanke shawar a saketa ta tafi.

A kowane yin hidima, takan dauki lokaci mai tsawo nayin addu'a domin yin shirin tafiya. Wataran da asuba, tanayin addu'a game da wata tafiya mai zuwa, sai taji da alamar za a sami damuwa. Sai ta gaya wa abokan aikinta game da abin da takeji, amma ta tabbatar masu cewa ita dai ko da a kurkuku ta ke ko kuma a waje a hannun nufin Allah take-wata abokiyar da ke cikin masu tafiya da Mai tayi kuka da taji irin bayenin da Mai tayi "Ubangiji shi yasan komai game da wannan" Mai ta karfafa ta. Ya yarda da haka shi yasa kike taredani a wannan karo na tafiya kuma zamu karfafa juna.

Kada ki damu.

Nice na shirya taron. Ba lallai ne ki amsa komai ba ni zan dau nauyin laifin".

Suka kama hanya a mota, matan guda biyu da mai aikin mishan da kuma direba. Kamar dai yadda Ubangiji ya nuna wa Mai, wannan rukuni sun sami matsala. Yan sanda sun kama su, a caji ofis sunkai mazan guda biyu a daki guda matan guda biyu ma a wani dakin. A bayan dakin matan akwai kazamin ramin yin ba-haya. Kudaje da tsutsotsi sun cika dakin. Aka kwace dukkan Litattafai Masu Tsarki da sauran takardu.

Bayan karshen mako, aka kai Mai zuwa Zone Fourteen, wani gidan kurkuku, lokacin da tashiga dakin kurkukun, ta tarasda wasu matan China a ciki sun tsere daga kasar China suna kokarin tafiya Malaya a lokacin dayyan sadan Vietnan suna so suyi kokarin yin magana da turanci, saboda haka Mai ke tadi dasu da dan turancin da ta iya. Rukunin sukan raba abinci a ciki tukunyar shinkafa guda a lokacin cin abinci, kowace mace ta dauki lomar cokali guda daga cikin tukunyar. Mai da kawarta Krista sukan kashe yawancin lokacinsu a cikin dakin kurkuku suna addu'a domin su wadanda ke tare dasu a ciki.

A kowace safiya da karfe takwas mai tsaro yakan zo ya tafi da Mai wajen yi mata tambayoyi. Har tsawon sa'oi uku, ana mata tambayoyi. An rigaya an maida ita a zaman fursunar siyasa" kuma tambayoyin na tsananta.

"Me yasa kike nuna wa gwamnati kiyayya? Wani hafsa ya tambaya.

Bana nuna wa gwamnatin mu kiyayya" ta amsa, da kokarin zama a natse kullum. "Ni mai bin Yesu ce, kuma ya gaya mana mu girmama shugabannin gwamnatin mu, na kanyi addu'a domin su". "kikanyi addu'a domin su?" hafsan ya fada da gatse. "Daga ina wadannan Litattaf ai Masu Tsarki suka fito? Kikan yi taro dayyan leken asiri daga kasashen waje, ko ba haka ba? Fadi gaskiya!"

“Na sami Litattaf ai Masu Tsarki a Hanoi da Birnin Ho Chi Mihn (Saigon)” ta amsa. “Kuma ni bansan yan leken asirin kasa daga kasashen waje ko daya ba”.

“Bama sanin su kawai kika yi ba; in ji hafsan, muryarsa na tashi, “harma kina yi musu aiki! Kina yiwa baki daga kasashen waje aiki gaba da tamu kasar” “Ina kaunar kasata” Mai ta nace. “Shi yasa na dawo, domin ina kaunar mutanena!.

Krista da kike aiki tare dasu, menene sunayen shugabannin? Mai taki ambatar sunayen sauran masu bi “Idan kanaso kasansu, Mai ta amsa, sai kaje ka tambayesu”. Tayiwa Allah godiya a zuci da yake basu gane sunayen da ta dinka a gefen hannun tufarta ba haka aka yi tayin tambayoyi har zuwa lokacin cin abinci aka maida ta a daki. Da rana kuwa aka dawo da ita a cikin dakin tambayoyi na tsawon sa'oi uku. An yi tayin haka har kwanaki goma, kullum kuwa ana kawo wani sabon dan sanda maiyin tambayoyi a kullum.Wasu sukan yi amfani da dabaru masu zafi suna yi mata tsawa suna dukan tebor. Wasu sukanyi magana da sanyi, suna gaya mata cewa suna san kome game da tararrukan da Kristoci ke yi, sabo da haka ta gaya musu gaskiya kawai.

A rana ta goma sai suka gaya mata ta shirya kayanta domin za a kai ta sabon wuri. Maimakon haka sai suka kaita wani daki inda zata sa hannu a takardun sallama. Ta tuna lokaci na karshe da tasa hannu kafin ta tafi.

Lokacin da suka dauki hoton ta domin a sa a takardun sallama, Mai tana murmushi. Bata yi mani laifi ba, kuma lokaci da tayi a kurkuku yana kara tabbatar da aminicin Allah a gareta da kuma bishara an isa ga wadanda ke waje da kofa."

Na sami kaina, tana tunani a yayin da tabar kurkuku, da gaske a yance nake.

Ta tuna da babanta da maganganu da yawa na batun tafiya kasashen yamma da na samun yanci. Ba irin yancin da baba yake zaton zan samuba, amma wani yanci ma fi girma.

## JAWABI

Duk da yalwatar hidimar bishara. Mai tayi begen samun abakin tafiya. Tayiwa Allah tuni cewa yayimata alkawain mayaki wanda zaiyi tafiya a gefenta a cikin gwagwarmayar rayuwa. Sauran masu bi sunyi addu'a tare da ita domin Allah ya nuna wannan mayakin a gareta kuma yayi.

Nam abokin aiki ne na Kristi, kuma tsohon dan sandan kwaminis ne, Allah ya zuga zuciyarsa da kauna ga Mai, amma bai gaya mata ba harna tsawon watanni, maimakon haka sai yaci gaba da yin addu'a domin Allah ya fahimtar da Mai idan lokacin da ya dace ya zo.

Kuma jim kadan Allah ya budawa Mai da kuma shugabannin a cikin majami'ar cewar su biyun nan sun dace da juna-suka yi aure kuma suka ci gaba da aikin bishara suna tafiye tafiyen su tare zuwa karkakara suyi wa'azi kuma su koyar da shugabannin Krista.

Baban Nam mai rike da babban mukami ne a gwamnatin kwaminis kuma, ba sai an fada ba, yana bakin cikin zabin matar aure da dansa yayi. Dafarko yaki ya yi magana da Mai ko ma su zauna a daki guda tare da ita. Lokacin da Mai da mijinta suka gayyaci Krista domin su hadu a gidan su, sai surukinta ya tsaya a bakin kofar gida yakori wadan da aka gayyata yayin da suka iso. Da Mai da Nam dai a karshe suka gina katanga kewaye da nasu gidan ta yadda babansa ba zai ga lokacin dasuke taro ba.

Mai tayi barin ciki nafarko a lokacin da suka yi wata tafiya yin bishara a cikin jeji. Likitoci suka ce bazata iya kara yin juna-biyu ba har ya isa haifuwa kuma ta haifa daga wannan, amma tsayayyun iyalin nan suka dage da rokon Allah ya basu iyali Mai ta sake daukar ciki, amma wannan juna-biyu yana bata wuya Likitoci suka bada shawarar ta zubarda cikin, amma Mai ta ki. Da lokacin haifuwa yayi, Mai ta shiga nakuda amma babu alamar ci gaba. Likitoci suka gaya wa Nam yayi zabi ko matarsa ko jaririn ya rayu, basajin duka biyu zasu iya

rayuwa. Sai suka yi addu'a suna rokan Allah ya rayarda jaririn su.

Allah ya rayar da su duka biyu. Mai ta haifi ya mace, kuma bada jimawa ba ta sami sauki. Domin haifuwa da tayi, hidimar Mai ya dauki sabon salo da yake yanzu bata iya yin tafiya zuwa karkara da nisa a cikin Vietnan. Maimakon haka aiki take tare da majami'u na kewaye kusa da gidan ta, kuma tana koyarda shugabannin Krista na karkara da suka sami shigowa cikin birni domin almajiranci.

Nam yaci gaba da aikin iyalin na tafiya karkara, yana shiga kauyuka sau daya a wata. Allah ya shirya wa Mai a zuciya bukatar sa ga marayu da yaran da basu da towa. Tana kafa tushen wannan aiki kuma tana hangen ranar da diyarta zata yi aiki tare da ita na gaya wa wadannan yara na waje da kofa game da Allah wanda yake kaunar duniya, wanda yake korar mugu, wanda kuma shi kadai ne Allah....wanda zai iya yantar damu

# Yan Bayanai

**Adel:**
**A TSAKIYAR RAZANA..........BEGE**

1. Filibbiyawa 4:13
2. Jihad alarabci "Yaki Mai Tsarki
3. Allah da Girma yake! Allah da Girma yake!

**PURNIMA:**
**DIYA DA AKASA A KASO,**
**AMMA RUHUNTA YANTACCE NE**

1. Matta 10:28
2. Duba Matta 5:10

**AIDA:**
**MURYA DOMIN MARASA IYA FADA AJI**

1. Wadannan mujallun Krista da aka haramta majami'ar Baptist ta karkashin kasa ce ke dabi'in su a kasar Soviet kwaminisawa sun bada izni ga wata mujallar Krista batutuwan da basa sukar gwamnatin Soviet Krista na majami'un karkashin kasa wadan da suke so su buga batutuwan gaskiya game da majami'a kuma su rarraba suna jawo ma kansu kasadar dauri a kurkuku.
2. Dubi Filibbiyawa 3:10.
3. Domin karin bayani game da Aida da shara'arta, dubi Michael Bourdeaux shaidar da ya daure Aida Skeripnikorya.
(England: Cibiyar Nazarin Addinai da Kwaminisanci, 1972); Dabin Amirka:
Elgin, Ill.: Madaba'ar
David Cook, 1973)

**SABINA:**
**SHAIDA TAKAUNAR KRISTI**

1. Paston! Paston !
2. Farawa 19:17 KJV.
3. Matta 16:25 KJV.

**LING:**
**A CIKIN MAKARANTAR SHAN WAHALA**

1. Luka 10:2-3
2. Duba Matta 25:1-13

**GLADYS:**
**JERIN LAYI NA GAFARTAWA**

1. Zabura 37:34
2. Duba Luka 23:34 da Romawa 8:28
3. Duba Ibraniyawa 13:5
4. Romowa 12:14-18
5. Romawa 8:28

## Akwai Litattafannan Daya Daga Muryar Shahidai

**Dukufa Ka'inda na; in Gayin Sujada**

Mawallafin wannan Littafi shine daga cikin mawallafan ran guda biyu na shahararren Littafinnan da ake kira. *"Yan Gani Kashenin Kristi"* wannan Littafin sujadar kullum yana dauke da daruruwan labarai na masu bi na da dana yanzu- kowane labari yakan kamala da darari na rayuwa da kuma aya daga cikin Littafi mai Tsarki daga zai kalu balance ka gada kayi irin naka rayuwa ta dukufa ka'in da na'in gayin sujada.



# Jarumtacciyar ban Gakiya



Jarumtacciyar ban Gaskiya ta dauki akidar rayuwa ta shaidai kuma aka kalu balancei masu karantawa da suyi irin wannan rayuwa a cikin tasu jarumtacciyar ban gaskiya. Wannan Littafi mai bada karfafawa yana dauke da sura akan kowane akida kamar ba da kai da karfin zuciya, hade da wasu misalai daga wasu Krista da suka nuna irin wadannan halaye a rayuwarsu.

"KO KIYI AURE KO KI MUTU, IDAN KE KRISTACE TO BABU WURI DOMIN KI A CIKIN WANNAN BIRNI. ZAKI MUTU ANAN KE KADAI"

Kalmomin ban-kwana na mahaifin Tara, wani tuani daya kawai ya kawo ma wannan yar shekara goma sha shida watau ta tsere da ranta. Ta kusan mutuwa da shan duka Tara diyar sanannen musulmi a Pakistan da aka kulle ta a daki kamar fursuna ba tare da kaita asibiti ba, domin an same ta da Littafi Mai Tsarki.

Labarin Tara bai zama na dabam ba a cikin wadannan mata masu karfin zuciya guda takwas na wannan littafi: Zukata Masu Kuna. Daga karamar yarinya yar Vietnam wacce tayi wasti da yanci domin mutanen kasarta na kwaminisanci zuwa ga mai aikin mishan ta Australia wacce take watsa sakon garfartawa da warkaswa ko ina a India bayan an kona mata miji da yaya da ransu. Wadannan mata sun haye tsananin wuya sun zama shugabanni kuma gwanaye a majami'un karkashin kasa a wurare da dama a duniya.

Muryar Shahidai abokan wallafar littafin: Gani kashenin-Kristi da ya shahara da kuma littafin nan:: Dukufa ka'in da na'in ga yin Sujada, yana kawo muku labarun gaskiya na mata guda takwas, Jaruman ban gskiya, su wakilai ne na mata masu yawa da suke fuskantar irin wadannan al'amura ko ina a cikin duniya. Wadannan alamu na ban gaskiya da bada kai zasu zama abin koyi a gareka domin ka nemi Krsiti da zuciya mai kuna, ko da menene tsadar yin haka din.

MURYAR SHAHIDAI wani tsari ne na taimakawa ba tare da batun cin riba ba, kuma gudanarwarta baya la'akkari da wani batu na bambanci dariku, kowa ma nata ne idan dai ya shafi batun agaji na taimakon majami'u da ake tsanantawa a ko ina a cikin duniya. Pastor Richard Wurmbrand wanda aka daure har tsawon shekaru goma sha hudu a kurkukun kwaminisanci na Romania domin bangaskiyarsa ga Yesu Krsiti ne ya kafa Muryar Shahidai watau VOM. A yanzu kuwa Tom Write, babban shugaban VOM yana fadada watsar da bishara ta majami'u da ake tsanantawa, kuma yana aikawa da taimoko na agaji ta hanyoyin gabayyar ofisoshi da aka bubbude a kasa da kasa. Ana samun shalkwartar VOM a garin Bartleville ta Oklahoma a kasar Amurka. Yanar Gizo www.persecution.com

"A kullum ana samun muhimmancin mata game da al'amuran bin Kristi. Wannan Littafi; Zukata Masu kuna yayi bayanin ayyuka na tukuru da wadannan mata guda takwas suka yi, wadanda kuma har zuma yanzu ke shaida wa duniya cewa Ya tashi yana da Rai, kuma wannan tashi daga mutuwa yazo ne cike da kauna, alheri da gafartawa"

"Kada ka kuskure wannan kauna."

MARY GRAHAM, SHUGABAN KUNGIYAR MATAN BANGASKIYA

Stephen Publishing House
Stephen House
Sewage, Gowon Estate, Ipaja,
Lagos Nigeria
Ita tayi dab'in a Nigeria
Tare da izni
ISBN 978-36432-31